Wallafar Hakikat Kitabevi Na:2

MIFTAH-UL-JANNA

(Mabudîn Shiga Aljanna)

Hüseyn Hilmi Işık

www.goFREEbooks.com Hakîkat Publishing READ NOW

Wallafar Hakîkat Kitâbevi Na: 2

MIFTAH-UL-JANNA

(Mabuɗin Shiga Aljanna)

Mawallafi

Muhammad bin Kutb-ud-dîn Iznikî

Maimaitawa daga

Hüseyn Hilmi Işık

Bugun Hausa daga

Hakikat Kitabevi

BUGU NA FARKO

Shagon Littattafai na Hakikat Kitabei
Darussefeka Cad. 53/A PK: 35
34083 Fatih, ISTANBUL/TURKEY
Tel: 90.212.523 4556 Faɗ: 90.212.523 3693
www.hakikatkitabevi.com
e-mail: info@hakikatkitabevi.com
- MARIS 2024 –

Gabatarwa akan
Mabuɗin Shiga Aljanna

Allâhu ta'âlâ ya turo Annabawa 'alaihim-us-salâm' ga bayinSa domin su samu farin ciki da nutsuwa da kwanciyar hankali a duniya da lahira, tare da zamantakewa ta 'yan uwantaka ta hanyar nuna ƙauna ga juna, haka nan da koyar da su yadda za su bauta masa a matsayinsu na bayinSa. Ta hannun waɗannanwaɗannan zaɓaɓɓun mutanen, da suka fi kowa daraja, ya sanar da bayinsa hanyar rayuwa mai inganci. Ya sanar da cewa Annabi Muhammad 'alaihis-salâm' shine mafi ɗaukaka kuma cikamakin Annabawa 'alaihim-us-salawât-u-wa-t-taslîmât' shi ne Annabin da aka turo zuwa ga dukkan mutanen duniya da za su rayu har zuwa ƙarshen duniya. Ya bayyana umarni da haninSa, a cikin littafinSa mai girma mai suna **Kur'an al-karim** wanda Ya saukar wa Annabin da Ya fi so ta hannun mala'ikanSa a tsawon shekaru ashirin da uku. An saukar da Kur'an al-karim da harshen Larabci ɗauke da darussa masu tsauri da ilimi mai zurfi da ya wuce fahimtar ɗan Adam, don haka Annabi Muhammad 'alaihim-us-salâm' ya yi bayanin saƙosaƙon da littafin yake ɗauke da shi gaba ɗayaɗaya, tun daga farkonsa har ƙarsheƙarshe ga Sahabbansa 'alaihim-ur-ridwan'. Ya ce: **"Duk wanda ya yi bayanin Al-ƙur'ani mai girma daban da yadda na yi bayaninsa, to ya kafirta."** Malaman Musulunci, waɗandawaɗanda suka ji daga Sahabbai masu girma yadda Annabi 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya yi bayani, sun yi cikakken bayani mai faɗi ta yadda kowa zai fahimta, suka rubuta a cikin litattafan tafsiri. Ana kiran waɗannanwaɗannan Malaman Ahl as-Sunnat (Ahl as-sunnat). Litattafan da waɗannan malamai na Ahlis Sunnah suka wallafa da suke ɗauke da bayanan Al-ƙur'ani mai girma da maganganu da ayyuka na Annabi 'alaihis-salâm' waɗanda ake kira **hadith-i-sherifs** (Hadisi) su ne ake kira Littafan **'Ilm-i-hal.** Mutanen da suke buƙatar samun ilimin **addinin Musulunci** wanda Allâhu ta'âlâ ya koyar a cikin Alƙƙur'ani mai girma wajibi ne su karanta waɗannanlitattafai na 'ilm-i-hal.

Asalin sunan littafin, **Mabuɗin Aljanna** wanda muke gabatarwa shine **Miftah-ul-Janna,** wanda ma'anar shi itace **Makullin Buɗe Kofar Aljanna.** Marubucin littafin shine Muhammad bin Kutb-ud-din Izniki 'rahima-hullâhu ta'âlâ', wanda ya rasu a Edirne a shekara ta 885 Hijiriyya [1480 milladiyya].

Sanannen Malamin Musulunci Sayyid Abd-ul-Hakim Efendi 'rahima-hullâhu ta'âlâ' (1281 [1865 milladiyya], Bashkal'a, Ɓan – 1362 [1943 milladiyya], Ankara, ƙasar Turkiyya) ya ce: "Marubucinlittafin mai suna **Miftah-ul-Janna** ance mutum ne mai tsoron Allah. Yana da amfani ƙwarai a karanta shi." Don haka mun buga littafin. Bayanai da aka ɗan ƙara nan da

can anyi musu alama a cikin littafin a cikin baka ( ) an tsakuro su ne daga wasu litattafai na daban. Ko kaɗan hakan baya na nuna ra'ayin mu ba ne. Muna roƙon Allâhu ta'âlâ ya tsare mu daga son zuciya da rabuwar kawuna, waɗanda dukkansu tarko ne na maƙiya Musulunci da suke zagon ƙasaƙasa ga addini tare da munafukai da maƙiya marasa Mazhaba, da son zamanantar da addinimasu fakewa ƙarƙashinƙarƙashin Musulunci, har ake kallon wasu daga ciki a matsayin muhimman mutane a cikin addini! Muna roƙon Allah ya haɗa kanmu bisa tafarkin **Ahlis Sunnah,** wadda itace hanya ɗayaɗaya tilo da take sada mu da Annabin tsira'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam'! Muna roƙonSa Ya yi mana albarka baki ɗayaɗaya ta yadda za mu ƙaunaci juna kuma mu taimaki juna! Amin.

[Idan mutum ya ƙudiri yin wani aiki, abu na farko Khatara (tunani) zai fara ɗarsasuwa a zuciyarsa, sannan ya yi niyyar aikata wannan abin. Wannan ƙudirin nashi ana kiransa **niyya(t)**. Mutum zai uamarci gaɓɓansa su aikata wannan abin. Umarnin da ya bayar ana kiransa **ƙasd** ko **teshebbus** (yunƙuri). Aikin da gaɓɓan suke yi ana kiransa **kesb**. Aikin da zuciyar ke yi ana kiransa **akhlaƙ** (ɗabi'a, hali). Akwai yanayi guda shida da khatara ke zuwa zuciyar mutum: Khatara da ke zuwa daga Allâhu ta'âlâ ana kiranta **Wahy (Wahayi).** Ana saukar da Wahy ne ga zukatan Annabawa kaɗai. Khatara da Mala'iku ke kawowa ana kiranta **ilham** (ilhama). Ita ilhama ana saukar da ita ga zukatan Annabawa ''alaihim-us-salat-u-wa-s-salam" da salihan bayi. Khatara da aka bai wa salihan bayi ana kiranta **nasihat** (shawara). Wahayi da ilhama da nasiha dukkansu suna da kyau kuma suna da amfani. Amma Khatara da ta zo daga shaiɗan ana kiranta **ɓasɓasa** (wasuwasi); khatara da ta zo daga cikin rai[1] na mutum ana kiranta **hawa** (son ƙawa zuci); haka nan khatara da ake samu daga shedanun abokai ana kiranta **ighfal** (yaudara). Ana yin nasihat (shawara) ga kowa da kowa. Waswasi da bin son zuciya suna zuwa ne ga zukatan kafirai da fasiƙan[2] musulmai. Dukkan biyun munanan abubuwa ne masu haɗari. Abubuwan da Allâhu ta'âlâ yake so ya amince da su, ana kiransu kyawawan ayyuka, waɗanda kuma yayi hani akansu, ana kiransu **fena** (munanan ayyuka). Saboda Allâhu ta'âlâ mai jin ƙai ne, ya bayyana abubuwa masu kyau da marasa kyau a cikin **Kur'an al-karim.** Ya umurci a aikata kyakkyawa, a kuma guji munanan aiyuka. Ana kiran wadannan dokoki da hani **Ahkam-i-islamiyya** (wata hukunce-hukuncen musulunci). Idan zuciya ta bi kyawawan shawarwari da abokan kirki suke ba ta, sannan ta ɗabi'antu da Ahkam-i-iskamiyya, za ta zamo mai tsarki da haske. Za ta samu farin ciki da kwanciyar hankali a duniya da lahira. Zuciyar

[1] Wata halitta dake alaƙantuwa da ɗan Adam.
[2] Musulmai masu saɓo da rashin ɗa'a.

da ta bijire wa Ahkma-i-islamiyya, ta bi rudin shaidan da son zuciya, wanda sakamakon hakan yakan ingiza mutum zuwa biye wa maganganu da rubuce-rubucen shaidanu da zindiƙai, za ta zamo ruɓaɓɓiya cike da ɓata. Tsarkakakkar zuciya mai cike da haske za ta dage wajen ɗa'a ga Ahkam-i-islamiyya. Zuciyar da ke cikin ɓata za ta cigaba da bin rudun munanan abokai da son zuciya da kuma shedanu. Sadoda jinƙai na Allâhu ta'âlâ ya halicci zuciyar kowane jarirai tsarkaka da aka Haifa a duniya. Daga baya iyaye da miyagun abokai suke gurɓata zukatan yaran zuwa duhu kamar yadda nasu zukatan suke.

ABINDA YA KUNSA

MUSULUNCI 7
ALLAH WANZAJJE NE KUMA SHI KAƊAI NE 7
SHIKA-SHIKAN IMANI 15
SIFAT-I-DHATIYYA 16
SIFATIL-THUBUTIYYA 17
MATAN ANNABI MASU ALBARAKA DA KUMA YAKE-YAKEN SA .. 38
BAYANAI DA SUKA SHAFI IMANI 41
DALILAN DA KE HADDASA KAFIRCI (KUFR) 44
AHKAM-I-ISLAMIYYA 52
SHIKA-SHIKAN MUSULUNCI 57
BABI A KAN SALLAH 59
BABI A KAN GHUSL (WANKA) 62
BABI KAN HAIDH DA NIFAS 71
BAYANI AKAN ALWALA 86
BAYANI AKAN RUWA 87
YIN ASUWAKI 89
MUSTAHABBAN ALWALA 90
MAKARUHAN ALWALA 91
ABUBUWAN DA KE WARWARE ALWALA 91
ADDU'O'IN DA AKE YI LOKACIN ALWALA 93
BAYANI AKAN TAIMAMA 94
ISTINJÂ, ISTIBRÂ DA ISTINKÂ 100
YADDA AKE YIN SALLAH 102
AZAN-I-MUHAMMADI (KIRAN SALLAH) 106
ADAB (LADUBBAN) SALLAH 115
ADDU'O'IN DA AKE YI (ko zikiri da ake yi), BAYAN SALLAH 116
MAKARUHAN SALLAH 117
FALALAR SALLAR JAM'I 124
LIMANCI A CIKIN SALLAH (ta jam'i) 125
NUTSUWA (TA'DIL-I-ARKAN) A CIKIN RUKUNAN SALLAH 126
SALLAH YAYIN DOGUWAR TAFIYA 127
FALALAR KABBARAR HARAMA 130
GAME DA JANNAT-I-ALIYYAT 132
SALLOLIN DA BA A YI A KANLOKACIN SU BA 134
BIYAN BASHIN SALLAH GA MAMACI 141

BAYANI AKAN JUMA'A 145
GABATAR DA SALLAH 152
SHIGA CIKIN UZURI ('UDHR) 153
SALLAH YAYIN RASHIN LAFIYA 155
MUHIMMANCIN SALLAH 159
FITAR DA ZAKKA 168
BABI A KAN AZUMI 180
AKWAI SHARUƊƊA GUDA UKU (DA ZA A CIKA) GAME DA (AIKIN) ƘURBAN (LAYYA) 188
HAJJI TANA DA RUKUNNAI UKU: 189
FARILLAI GUDA HAMSIN DA HUƊU 191
BAYANI A KAN GHUNAH-I-KABA'IR 195
SASSAN AL-AURA (TSIRAICI) DA SITURTA JIKI GA MATA 199
CIKAKKEN MUSULMI 207
ABIN DA YA SHAFI AKHL Â Ƙ-I-HAMIDA 209
BAYANI A KAN DARAJOJIN SAHABBAI 212
BAYANI A KAN ABINCI DA YADDA AKE CINSA 215
HUKUNCE-HUKUNCEN AURE 218
BAYANI a kan TEJHIZ da TEKFIN da TEDFIN na JANAZA 225
BAYANI a kan HALIN MUTUWA 228
BAYANI a kan MUTUWAR ƘANANAN YARA 233
BAYANI A KAN MUTUWAR MACE MUSULMA 234
BAYANI A KAN MUTUWAR WANDA aka ZALUNTA, da MAI HAKURI da SHAHIDAI-GHARIB 237
BAYANI a kan MUTUWAR KAFIRI 239
ZIYARAR KABARI da KARANTA, KUR'AN AL-KARIM 243
MUJALLADI NA UKU, WASIKANA TARA 246
MUJALLADI NA UKU, WASIKA TAMANIN DA HUƊU 247
WASIKA ta ƊARI da GOMA SHA HUƊU 249
JAWABI NA ƘARSHE NA LITTAFIN MABUƊIN SHIGA ALJANNA ... 252
WASIKA ta ƊARI da ISHIRIN DA UKU 256
WASIKA ta ƊARI da ISHIRIN da HUƊU 256

LITTAFI AKAN MABUƊIN SHIGA ALJANNA

Al-hamd-u-lillâh-illathi Ja'alana min-at-talibina wa lil'ilmi min-ar-raghibina wa-s-salatu-was-s-salamu-'ala Muhammadin-ladhi arsalahu rahmatan lil'alamina wa 'ala Alihi wa As-habihi ajma'in.

MUSULUNCI

ALLAH WANZAJJE NE KUMA SHI KAƊAI NE

[Allâhu ta'âlâ shi ya halicci dukkan halittu. Tun babu kowa da komi Allâhu ta'âlâ shi kaɗai ne yake wanzuwa. A kodayashe Allah na nan tun fil azal. Shi ba abin halitta ba ne da wanzu daga baya. Idan da akwai wani lokaci da babu samuwarSa, to da wajibi ne a samu wani abu daya halicce Shi. Rashin wanzuwar wani iko da zai halicci wani abu da babu shi, wannan abin ba zai taɓataɓa samuwa ba sai dai abin da yake wanzajje tun asali. Idan akwai wani iko da zai halicci wani abin halitta, to Allâhu ta'âlâ shi ne mamallakin wannan ikon. Alal misali, idan aka ce wannan ikon na hallita ya wanzu ne a wani zamani, to da an halicci wani ikon na daban, wanda hakan na iya bayuwa ga halittar wasu irinsa da dama. Wannan ke nuna babu farkon wanzuwa ga mahalicci. Rashin wanzuwar wani iko na farko ya nuna cewa Shi ba halittarsa aka yi ba. Idan babu mahalicci ba za iya ji ko ganin halittunsa na sarari da na ɓoye ba. Tun da akwai halittun sarari da na ɓoye, to tabbas suna da wanda ya halicce su shi kaɗaikaɗai, rayayye wanda ba ya mutuwa.

Da farko Allâhu ta'âlâ ya halicci wasu sinadarai, daga cikinsu ne ya halicci dukkan halittu na sarari da rayuka da Mala'iku. Ana kiran waɗannan sinadaran da ƙwayoyin halitta a yanzu. Waɗannan sinadaran su guda ɗari da biyar ne aka sani a yau. Allâhu ta'âlâ ya halicci, kuma yana cigaba da halittar dukkan halitu daga waɗannan sinadaran halittar guda ɗari da biyar. Misalinsu akwai Karfe da Toka da carbon da iska da iskar gishirin chlorine kowannen su sinadari ne mai zaman kansa. Allâhu ta'âlâ bai bayyana tun shekaru miliyan nawa ya halicci waɗannan sinadaran ba, kuma bai sanar da mu yaushe ya fara halittar ƙasa da sama da sauran halittu masu rai ba waɗanda ya halitta daga sinadaran can ba. Dukkan wata halitta mai rai da marar rai tana da wa'adin lokacin yin rayuwa, wanda za ta wanzu a cikinsa. Allâhu ta'âlâ zai halicce ta idan lokaci ya yi, Ya kuma ɓatar da ita idan wa'adinta ya cika. Baya ga halittar abubuwa daga babu, yakan halicci wasu abubuwan daga wasu abubuwa, sannu a hankali ko nan take, haka nan idan aka samar da wani sai kuma a kawar da wani.

Allâhu ta'âlâ ya halicci mutum daga wani sinadari sannan kuma yayi masa rai. Mutum bai taɓa rayuwa kafin nan ba. An halicci dabbobi da tsirrai

da aljannu da Mala'iku kafin a halicci mutum. Mutumin na farko da aka fara halitta shi ne 'Adam (Adamu) 'alaihis-salat-wa-s-salam'. Sannan daga jikinsa ne Allâhu ta'âlâ ya halicci mace. Daga waɗannan mutanen biyu ne dukkan jinsin mutum suka hayayyafa. Muna gani yadda halittu suke sauyawa masu rai da marasa rai suke sauya yanayi. Duk abin da yake rayayye har abada baya sauyawa. Halittu na sarari suna sauya kama da yanayinsu. Haka nan sinadarai suna sauya wasu abubuwan ta fuskar yanayi da halittarsu. Yayin da wasu ke gushewa, wasu kuma suna samuwa. A wani yanayi na kimiyyar makamashin nukiliya, sannan kuma sinadarai suna canzawa zuwa karsashi Wannan tsarin na samar da halittu daga wasu halittun ba zai ɗore ba ba tare da mafari ba. Wannan lamari na dukkan komai ya samo asali daga wanzuwar wani abu ba haka yake tun fil azal ba, yana da mafari Wajibi ne su samu alaƙa da sinadaran da aka fara halitta daga babu tun asali. Saboda, dauwamamen abu, shine abin da ba shi da mafari.

Maƙiyan Musulunci da suke fakewa da cewa masana ilimin kimiyya ne su, sun cemutum ya samo asali ne daga birai. Sun ce wani ƙwararren likita ɗan ƙasar Ingila mai suna Darwin ya faɗi haka. Maƙaryata ne. Darwin (Charles [1809-82 Milladiyya) bai faɗi haka ba. Ya yi tsokaci game da faɗi tashin rayuwa na halittu. A cikin littafinsa mai suna '**The Origin of Species**' (wato, Asalin Halittu) ya rubuta cewa halittu sun samu halayyarsu ce daidai da muhallin da suke rayuwa, don haka suka samu wasu 'yan ƙananan sauye-sauye. Shi baice wata halitta ta sauya zuwa wata. A wajen wani taro da ƙungiyar bunƙasa kimiyya ta ƙasar Ingila ta gudanar a Salford a shekarar 1980, Farfesa John Durant na Jami'ar Swansea ya ce an mayar da bayanin da Darwin ya yi game da samuwar Mutum a matsayin wata almara a wannan zamani, domin wulaƙanta darajar kimiyya da cigaban zamantakewa, ana ganin cewa lamarinsamuwar mutumdaga biri "ya kawo koma baya ga sha'anin binciken ilimin kimiyya," wanda hakan ya haddasa "gurɓacewa, tare da cece-kuce da kuma amfani da ilimin kimiyya ta hanyar da bata dace ba." Ya kammala da cewa wannan daftari na Darwin ya zo da wani sabon batu da ya haddasa shakku a cikin nazarin sa.[1] Wannan jawabin na Farfesa Durant yana cikin amsoshi na bajinta da ake bai wa masana kimiyya masu ra'ayin Darwin. Babban dalilin da ya sa ake wannan kokarin cusa ma mutane wannan tunanin na gargajiya game da samuwar ɗan Adam shi ne kawai don yaɗa wani ra'ayi. Amma ba su da manufa ta kimiyya. Ana amfani da daftarin

[1] Dr. John Durant (Daga Jami'ar Swansea, a garin Wales), kamar yadda aka hakaito magan-ganunsa acikin littafai kamar haka "How ɛbolution became a scientific myth" da kuma "New Scientist," 11 Satumba 1980, shafi na. 765.

ne a matsayin wani makami na ɗabbaƙa ra'ayin falsafancin samuwar halittu. Saɓanin fahimatar cewa asalin ɗan Adam ya samu ne daga birai ba shi da wata hujja a ilimance. Kuma ya saɓa wa kimiyya. Wannan batun ba ra'ayin Darwin ba ne, ra'ayin jahilai maƙiya musulunci ne waɗanda ba su da ilimi da sanin kimiyya. Mutum mai ilimi ba zai yi wannan zancen marar kan gado ba. Idan wanda ya kammala karatun jami'a ya riƙa rayuwa ta rashin ɗa'a ya yi watsi da abin da ya koya a makaranta, maimakon ya cigaba da karatu da binciken kimiyya da aka koyar dashi, ba zai taɓa zama mai ilimi ko masanin kimiyya ba. Abu mafi muni kuma shi ne nuna tsana ga Musulunci, ya zaɓi ya ɓata lokacinsa da kalamansa wajen yin rubutu da sunan ilimi da kimiyya, ya zama mayaudari mai cutarwa a cikin al'umma. Don haka, shaidar karatun sa na diflomarsa ta zama babbar barazana ce ta jan hankalin gurɓata matasa. Gurɓatattun masana kimiyya waɗanda suka yaɗa ƙarairayinsu da sunan ilimi da kimiyya, waɗannansu ake kira **masana kimiyya na bogi.** Abin da Allâhu ta'âlâ yake so ga mutane shine su zauna cikin nishaɗi da zaman lafiya a duniya, sannan su samu jin daɗi na har abada a lahira. Don haka, ya bayar da umarnin yin ayyuka masu amfani da za su kawo jin daɗi mai ɗorewa, ya kuma yi hani ga aikata miyagun ayyuka da za su kawo azabar wuta. Idan mutum, Musulmi ko kafiri mai imani ko marar imani, ya yi riƙo da Ahkam-i-islamiyya, wato umarni da hanin Allâhu ta'âlâ da saninsa ko ba da sani ba, zai samu nutsuwa da wadata gwargwadon ɗa'arsa ga tsarin dokokin. Akwai wani azancin magana da ake yi cewa, duk wanda ya sha maganin da ya dace, zai warke daga cutar da take damunshi. Mafi yawan cigaban da waɗandaba su damu da addini ba da waɗanda ma ba su da addinin suke samu, yana da alaƙa ne da ɗabi'a yadda suke aiki bisa tsarin da Kur'an al-karimya shimfiɗa. Amma duk da hakan Kur'an al-karim yin biyayya kaɗai na amuwa ne ga Musulmi da ya yi aiki bisa ilimi.

Umarni na farko da Allâhu ta'âlâ ya bayar shi ne mutum ya kasan ce mai **imani**. Kazalika **kufr** (kafirci) shi saɓo mafi girma daga cikin zunubbai da ya yi hani a kai. Haka nan Imani yana nufin ka shaida cewa Muhammadu 'alaihi-s-salâm' shi cikamakin Annabawan Allâhu ta'âlâ. Ta hannunsa ne Allâhu ta'âlâ ya saukar da dokokinsa ta hanyar **'Wahy'**. A wani ƙƙaulin kuma, ya saukar masa da Ahkam-i-islamiyya wato hukun-hukun musulinci ta hannun Mala'ika, shi kuma ya sanar da sauran al'umma. Kalmomin da Allâhu ta'âlâ ya saukar ta hannun Mala'ikansa su ake kira **Kur'an al-karim**. Littafin da ya ƙunshi dukkan cikakkun surorin Kur'an al-karim ana kiransa **Mushaf** (wato kwafen littafin Kur'an al-karim). Shi Kur'an al-karim ba maganar Annabi Muhammad 'alaihi-s-salâm' ba ce maganar Allâhu ta'âlâ ce. Babu wani ɗan adam da yake iya magana mai hikima kwatankwacin aya ɗaya ta Kur'an al-karim. Dukkan hukunce-hukncen da suke cikin Kur'an al-

karimsu ake kira **Musulunci.** Duk mutumin da ya yi Imani da su ana kiransa **Mu'min** (Mumini) kuma **Musulmi.** Kin ko da aya ɗaya a cikinsu shi ake kira **kufr** (butulce wa Allâhu ta'âlâ). Imani da tashi bayan mutuwa. Tabbatuwar mala'iku da aljanu, tabbata cewa Annabi Adamu 'alaihis-salâm' shine baban dukkan mutane kuma shine Annabi na farko, dukkan waɗannan yaƙini ne na zuciya. Waɗannan su ake kira ginshiƙan **iman** ko **i'tiƙad** ko **'aƙaid** (Aƙida). Kazalika, abubuwan da ake aiwatarwa da kuma abubuwan saɓo da yakamata a guje musu ta hanyar amfani da gaɓoɓi ko ƙyamatar a zuci, ya wajaba kayi imani dasu ko kuma ka gujesu. Waɗannan dukkan su ana kiransu da koyarwar **Ahkam-i-islamiyya.** haka nan yarda da su sashe ne na imani. Aiki da su da kuma guje wa saɓo **'ibadat** (ibada) ne. aikata ahkam-i-islamiyya ibada ne, ana ƙudirce niyya daga farko kafin fara aikin. Kamar yadda bayani ya gabata, bin umarnin Allâhu ta'âlâ da nisantar aikata saɓo su ake kira **Ahkam-i-islamiyya** ko **Ahkam-i-ilahiyya.** Umarnin ana kiransa **fard** (farilla), ayyukan da aka hana ana kiransu **haram.** Kamar yadda aka gani a baya, duk wanda ya musanta ko ya kore ɗaya daga cikin umarnin ya zama **kafir** (maƙiyin Allah). Mutumin da ya ƙi aikata su da gangan amma ya yadda da su bai zama kafiri ba, sai dai ya zama Musulmi **fasiƙ** (ƙfasiƙi). Muminin da ya yi imani da koyarwar Musulunci, yake kuma aiki da ita gwargwadon iko shi ake kira **Salihin Musulmi** [Musulmi na ƙwarai]. Musulmin da yake ɗa'a ga koyarwar Musulunci kuma yake ƙaunar Murshid saboda matsayin da ya samu da soyayyar Allâhu ta'âlâ ana kiransa **Salih** (mutumin kirki). Musulmin da ya kai matsayin samun daraja da soyayyar Allâhu ta'âlâ ana kiransa '**Arif** ko **Wali** (waliyyi). Waliyyi da yake shiryar da al'umma ya samu wannan soyayyar shi ma ana kiransa **Murshid.** Dukkan waɗannan zaɓaɓɓun mutanen baki ɗayansu, ana kiransu **Sadiƙ.** Dukkansu sahihan bayi ne. Salihin bawa ba zai taɓa shiga wuta ba. Kafiri (maƙiyin Allah) tabbas zai shiga wuta. Zai dawwama a cikinta kuma zai ɗanɗani azaba ta har abada. Idan kafiri ya yi imani (ya zama musulmi), za a gafarta masa zunubansa baki ɗaya. Haka nan idan fasiƙi ya tuba, ya riƙa ayyukan ibada, ba zai shiga wuta ba, zai shiga Aljanna kai tsaye, kamar salihan bayi. Idan bai tuba ba, za a iya gafarta masa ya shiga Aljanna ko kuma ya samu shafa'ar (ceto) ko ba tare da wani dalili ba, ko kuma ƙona shi a wutar jahannama gwargwadon laifin da ya aikata sannan a shigar da shi Aljanna daga bisani.

Lokacin da aka saukar da Kur'an al-karim, nahawunsa ya dace da na harshen Larabcin da mutane ke magana da shi a wancan zamanin, sannan yana da tsari na amsa amo. Wato yana da zaƙi kamar waƙe. Yana cike da kalmomin Larabci masu zurfin ma'ana. Yana kuma shahara wajen zaɓin kalmomin hikima na Larabci da suka ƙunshi Badi' da Bayan da ma'ani da kuma Balaghat. Don haka yake da wahalar fahimta. Duk wanda ba shi da

ilimin sanin kalmomi masu sarƙaƙiya na Larabci ba zai iya fahimtar Kur'an al-karim ba, duk zurfin iliminsa a harshen Larabcin. Wani zubin ko wadanda suke da ilimin kalmomi masu sarƙaƙiyar abin yana gagararsu, saboda haka shugabanmu Annabi tsira 'sallallâhu' alaihi wa sallam ya yi mana bayanin mafi yawansa. Bayanin da Manzon Allah 'sallallâhu' alaihi wa sallam' ya yi na Kur'an al-karim ana kiransa **hadith-i-sharifs.** Sahabbai 'ridwânullâhi ta'âlâ' alaihim ajma'în[1] sun sanar da koyarwar Annabi 'sallallâhu 'alaihi wa sallam' zuwa ga mabiyannsu. Bayan wani zamani al'amurra suka taɓarɓare zukata suka gurɓata, daga nan wasu sababbin shiga Musulunci suka riƙa fassara Kur'an al-karim bisa tunani da gurguwar fahimtarsu, suka riƙa guɓata ma'anoni da suka saɓa wa yadda Annabi 'sallallâhu 'alaihi wa sallam' ya koyar.

Maƙiyan Musulunci sun yi nasarar rarraba kawuna da kawo bambance-bambance cikin addini, inda aka samu rarrabuwar kai har gida saba'in da biyu (72) na addinin Musulunci da suke kan ɓata. Musulman da suka yi riƙo da irin wadannan aƙidoji ana kiran su **'yan bid'a(t)** ko **wadanda ke kan dalala(t)** (ɓata). Dukkan rabe-raben aƙidun bid'at za su shiga wuta, amma saboda kasancewarsu Musulmai, ba za su dawwama a cikinta ba; za a fitar da su, a shigar da su Aljanna.

Idan mutum bai yadda dawani hukunci daga cikin Kur'an al-karim ko kuma hadisi, wannan mutumin zai rasa imaninsa. Ana kiransa **Mulhid.** Wato mulhid shine wanda yake ganin cewa shi Musulmi ne.

Malaman Musulunci wadanda suke da ilimin i'tiƙad, wato ingantacce ilimi daga Ashab-i-kiram 'ridwânullâhi ta'âlâ' alaihim ajma'în' suka rubuta wannan tarin ilimin a litattafai ana kiransu **Ahl as-Sunnat** (ahlis sunnah) 'rahmatullâhi ta'âlâ' alaihim ajma'în'. Su ne malaman da suka kai matsayin ijtihadi a ɗaya daga cikin Mazhabobi huɗu (4) da ake da su. Wadannan malaman suna aiki ne da kaɗai da abin da suka koyo daga Sahabbai, kaɗai maimakon su riƙa ƙoƙarin fassara Kur'an al-karim da tunani ko fahimtar su. Sun yaɗa ingantaccen ilimin da yazo daga koyarwar Annabi 'sallallâhu' alaihi wa sallam', maimakon su yi amfani da fahimtarsu. Kusani cewa, daular Ottoman, daula ce ta Musulunci, kuma sun yiriƙo da aƙidar Ahl as-sunnat.

---

[1] Ayi ƙokari a duba littafin nan da ake kira SAHABA 'The Blessed' ɗaya daga cikin wallafar Hakîkat Kitâbeɓi, da ke garin Fâtih, Istanbul, ƙasar Turkiyya.

Idan an fahimci maganganun da aka rubuta a baya, kamar yadda yake a sauran manyan litattafai, idan mutum yana son guje wa shiga musiba a duniya da lahira, ya kuma yi rayuwa mai kyau cikin wadata, wajibi ne ya yi imani kamar yadda manyan malaman Ahl as-sunnat suka koyar; wato ya san ilimin aƙidarsu ya kuma yadda da su baki ɗaya. Duk wanda bai yi riƙo da koyarwar aƙidar Sunnah ba, to zai zama ko dai **Ahl bid'at** (ɗan bidi'a) ko **Mulhid,** wato kafiri. Aikin Mumini na biyu mai imani da i'tiƙad shi ne ya zamo salihin bawa, wanda ke nufin ya samu albarka da soyayyar Allâhu ta'âlâ. Don haka, wajibine mutum ya san abubuwan da ya kamata ya aikata da waɗanda ya kamata ya guji aikatawa, a aikace ko kuma cikin zuciya, sannan ya rayu cikin ɗa'a. Wato mutum ya riƙa aikata dukkan ibada. Malaman Ahlis Sunnah sun bayyana ayyukan ibada ta fuskoki guda huɗu. Wato mazhabobi[1] huɗu na Musulunci (sahihai). Abin nufi a nan shi ne, sun yi saɓani ne a wurare ƙalilan. Sannan tun da aƙida ɗaya ta haɗa su wuri guda, suna girmamawa da mutunta juna matuƙa. Dukkan Musulmi wajibi ne ya yi ibada bisa koyarwar ɗaya daga cikin Mazhabobin nan guda huɗu. Duk wanda bai yi koyi da ɗaya daga cikinsu ba, to ya yi watsi da (hanya ɗaya tilo da ake kira) Ahl as-sunnat, kamar yadda aka ambato a wani sashi na littafinsa mai suna 'Dhabayih' na Ahmad bin Muhammad bin Isma'il **Tahtawi** 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' (1231 hijiriyya [1815 milladiyya] sharhin sa na littafin **Durr-ul-Mukhtar,** na Ala'uddin Haskafi'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' (1021, Haskaf – 1088 hijiriyya [1677] milladiyya).

Idan kafiri ya ce "Na musulunta" ko da wanda aka kamo a fagen yaƙi ne ko wanda ya musulunta a lokacin zaman lafiya, wajibi ya gaggauta sanin **shikashikan imani guda shida** kuma ya yadda da su. Bayan haka zai koyi aikata hukuce-hukuncen musulunci wanda suke farillai (Fard) da kuma guje wa abubuwan da aka hana (haram) a lokuttan da ake yin su da kuma duk lokacin da ya samu dama. Idan bai koya ba, ko ya ƙi aikata ɗaya daga ciki bayan ya sansu, to ya yi watsi da addinin Allâhu ta'âlâ.

Zai iyarasa imaninsa. Mutanen da suka rasa imaninsu irin haka ana kiransu **murtadds** (waɗanda suka yi ridda). Daga cikin waɗanda suka yi ridda, suka kuma yaudare mutane a matsayin masana addini, suna ɓatar da al'ummar Musulmi ana kiransu **zindiƙs** (zindiƙai). Kada mu yadda da zindiƙai ko ƙarairayinsu. Kamar yadda aka rubuto a sharhin littafin **Siyar-i-**

[1] Mazhabobi guda huɗu da suka shafi harkokin musulunci waɗanda musulunci ya yadda dasu sune: Hanafî, Shâfi'î, Mâlikî, and Hanbalî, ƙarin bayanai akan waɗannan mazhabobi guda huɗu, za'a iya samunsu a maɗaba'ar Hakîkat Kitâbeɓi dake garin Istanbul.

kabir[1] da aka fassara da harshen Turkiyya da kuma kashi na ƙarshe na babi a kan auren kafirai (hukunce-hukuncen aure da Musulunci ya shimfiɗa) a cikin littafin **Durr-ul-mukhtar**, idan mutum ya balaga ba tare da ya ɗabbaƙa Musuluncinsa ba, kuma bai saka a ransa cewa shi musulmi ne ba, idan hakan ya faru saboda dalili na rashin ilimi ne, ba don biye wa ruɗin rayuwar duniya ba, to za a yi masa hukunci da Murtadd (wanda ya yi ridda). Haka nan a ƙarshen babin, idan aka yi wa mace auren Musulunci (nikah) ta kai munzalin balaga, sannan ba ta san addinin Musulunci ba, auren ya ɓaci wato ya mutu (ana nufin ta yi ridda). Wajibi ne a koyar da ita Kalmar shahada. Haka nan ta riƙa maimata duk abin da aka faɗa mata, ta kuma ce ta yadda da su. Ibni ‘Abidin‘rahima-hullâhu ta’âlâ’ya bayyana mas’alar kamar haka: Idan yarinya tana ƙarama (ba ta balaga ba) Musulma ce, domin za a alaƙanta addininta da na iyayenta. Idan ta balaga, ba za ta cigaba da dogara da addinin iyayenta ba, idan ta kai wannan munzalin ba tare da ta san Musulunci ba, to ta yi ridda. Idan mutum bai yadda da shika-shikan musulunci ba, sai ya ji ana ɗaɗaɗaɗar kalmar shahada, sai fada shi ma, ya ce “**La ilaha il-l-Allah Muhammadun Rasulullah”** ba zai zamo Musulmi ba. Mutumin da ya yadda da shika-shikan imani guda shida, ɗwaɗanda suka zo a Hadisin da ke cewa “Amantu billah…” kuma ya ce “Na yadda da hukunce-hukunce hani da dokokin Allâhu ta’âlâ,” shi ne cikakken Musulmi. Don haka wajibi ne kowane Musulmi ya sanya ‘ya’yansa su hardace wannan kalma mai koyar damu shika-shikan imani: “Amantu billahi wa Malaikatihi wa Kutubihi wa Rusulihi wa-l-Yawm-akhiri wa bi-l-Ƙadri khayrihi wa sherrihi min-Allahi ta’ala wa-l-ba’s-u-ba’d-al-mawt haƙƙun Ash-hadu-an-La ilaha il-l-Allah wa Ash-hadu-anna Muhammadan ‘abduhu wa rasuluhu,” tare da koyar da su ma’anarsu. Idan yaro bai yadda da waɗannan shika-shikan ba ko ɗaya daga cikin abubuwan da aka yi hani ko wani hukunci, kuma bai furta cewa ya yadda da su ba, to ya yi ridda, ya fita daga Musulunci bayan ya balaga. Cikakken bayanin waɗannnan shika-shikai shida na imani yana nan a cikin littafin **Imani da Musulunci,** (ɗaya daga cikin litattafan da Hakikat Kitabeɓi suka wallafa a Istanbul a cikin harshen Hausa). Ya kamata kowane Musulmi ya karanta wannan littafin, su kuma sanya ‘ya’yansu su karanta, domin su

---

[1] Wanda ya rubuta wannan littafin shine Muhammad bin Hasan bin ’Abdullah bin Tâwus bin Hurmuz Sheybânî (Imâm Muhammad) ‘rahmatullâhi ta’âlâ ’alaih’ (135 [752 A.D.], Wâsit – 189 [805 A.D.], Rey), ɗaya daga cikin manyan malamai Imâm Abû Hanîfa ‘rahmatullâhi ’alaih’. Shems-ul-aimma Abû Bakr Muhammad bin Ahmed ‘rahmatullâhi ’alaih’ (d. 483 [1090 A.D.]) ya karantar ya rubuta sharhi na wannan littafin wanda Khwâja Muhammad Munîb Efendi of ’Ayntab (d. 1238 A.H.). ya fassara shi zuwa yaren Turkanci.

inganta imaninsu, da kuma yi ƙoƙarin ganin dukkan ‘yan uwansu sun karanta littafin. Mu jajirce wajen ganin cewa ‘ya’yanmu ba su tashi a matsayin waɗanda suka yi ridda ba. Tun suna ƙanana ya wajaba mu koyar da su imani da Musulunci da alwala da wankan tsarki da sallah[1]. Babban haƙƙin da ke kan iyaye shi ne su tabbatar ‘ya’yansu sun rayu a matsayin Musulmai.

An ruwaito a cikin littafin **Durer wa Ghurer**[2] cewa: “Duk mutumin da ya yi ridda ya zamo wajibi a sashi ya dawo Musulunci. Sannan a warware masa dukkan kokontonsa. Idan bai tuba ba, za a ajiye shi a gidan yari tsawon kwanaki uku. Idan ya tuba (wato ya yi nadamar laifin da ya aikata, ya roƙi Allâhu ta’âlâ gafara, tare da alƙawarin ba zai sake aikata laifin ba) za a karɓi tubarsa. Idan bai tuba ba, alƙalin Musulunci zai yanke masa hukuncin kisa. Macen da ta yi ridda ba za a kashe ta ba, za a kai ta gidan yari a ajiye ta a can har sai ta tuba ta zama Musulma. Idan ta gudu ta tafi dar-ul-harb (garin da ba na Musulunci ba), ba za ta zama baiwa ba, duk tsawon lokacin da ta yi a can. Amma idan aka kama ta a lokacin yaƙi za ta zama baiwa. Lokacin da ta yi ridda, aurenta ya mutu. Sannan za a ƙwace dukiyarta. Amma za a mayar mata idan ta sake komawa Musulunci. Idan ta mutu ko ta gudu zuwa dar-ul-harb lokacin da ta yi ridda, za a bayar da dukiyarta ga magadanta. [Idan ba ta da magada, za a saka dukiyar cikin Baitul mali [3] wanda ake taimaka wa talakawa]. Wanda ya yi ridda ba ya gadon wanda ya yi ridda. Duk dukiyar da ya mallaka lokacin da ya yi ridda ba mallakinsa ba ce, zata zama ‘fey’ wato shubha ga al’ummar Musulmi. (Kalmar Fey [shubha] anyi bayaninta a cikin wani ƙaramin babi mai taken **THE DISBELIEBER’S MARRIAGE** wanda aka saka shi cikin babi na goma sha biyu a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss.**) Dukkan harkokinta da suka ƙunshi saye da sayarwa da haya da jingina da kyaututtuka za su zama bâtil. (Ana iya duba babi na talatin da ɗaya na littafin **Endless Bliss** domin bayani akan ‘bâtil’ cewa, idan ta koma Musulma za ta iya sake dawowa ƙasarta ta zauna cikin aminci. Ba za ta rama ayyukan ibada na lokacin da ta yi ridda ba ban da aikin Hajji, wanda dole ne sai ta sake wani idan ta samu hali.” Ayyukan ibada uku na farko da ya kamata wanda ya musulunta ya koya su ne alwala da wanka da sallah.

Shika-shikan imani guda shida su ne yaddaakwai Allah kuma shi kaɗai yake babu abokin tarayya da yadda da siffofinsa; yin imani da Mala’iku da

---

[1] Babi na huɗu a littafin Endless Bliss, ɗaya daga cikin wallafar maɗaba’ar Hakîkat Kitâbeɓi, anyi ƙarin bayani akai.

[2] Muhammad Molla Husraw ‘rahmatullâhi ta’âlâ ’alaih’, babban shehin malamin musulunci na daular Ottoman ya rubutashi.

[3] A duba babi na farko a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss**.

Manzanni da Litattafan da aka saukar, sannan imani da Tashin ƙiyama da ƙaddara ta alheri da sharri. Za mu yi bayaninsu ɗaya bayan ɗaya a nan gaba.

A taƙaice, wajibi ne mu yi riƙo da dokoki da hanin Musulunci a zuci da kuma a bayyane, kuma zukata su zamo masu taka tsantsan daga faɗawa shagala. Idan zuciyar mutum ba ta zamo mai taka tsantsan ba [wato ta zamo mai tuna girma da ɗaukakar Allâhu ta'âlâ da jin dadî da farin ciki da ke cikin Aljanna da azabar wutar jahannama] zai yi matuƙar wahala gaɓɓan mutum su bayu zuwa ga Musulunci. Malaman Fiƙihu (wanda ke koyar da hukunce-hukunce na hani) sun bayar da fatawa [fatwa] (wato amsoshin da manyan malaman musulunci suka bada akan tambayoyin da suka shafi hukunce-hukuncen ibada) [1] cewa ana buƙatar mutum ya kusanci Allâhu ta'âlâ domin ya samu sauƙin aikin ibada. Akwai buƙatar tsarkin zuciya domin jiki ya saba da ibada cikin sauƙi da annashuwa da kuma sa kai. Amma fa idan mutum ya bayar da muhimmanci ga tsarkake zuciya da kyakkyawar ɗabi'a, amma jiki baya aikin ibada yadda ya dace, ya zamo **mulhid.** Wato samun nasarori [da suka shafi sanin ɓoyayyun al'amurra da warkar da marasa lafiya ta hanyar yin busa a jikin su,] ana kiransu **istidraj** (istidraji) shi ne zai ja su da mabiyansu zuwa wautar jahannama. Alamar zuciya mai tsarki da kuma rai wanda ya samu rabauta shine mutum ya karkata zuwa aikin ibada ba tare da an tilasta shiba.. Faɗar da wasu mutanen da ba su ta'allaƙa rayuwarsu ga ibada ba ke yi cewa: "Zuciyata tsarkakakka ce. Ku duba zuciyata" wannan zancen fanko ne. Suna yaudarar kansu ne da mutanen da ke tare da su.

SHIKA-SHIKAN IMANI

Malaman Ahlus Sunnah sun ce, imani yana da shika-shikai guda shida:

AMANTU BILLAHI: Na yadda cewa Allah 'adhim-us-shan yana nan kuma shi kaɗai ne; na yi imani da haka.

Allahu 'adhim-ush-shan dauwamamme ne kuma shi kaɗai yake.

Ba shi da abokin tarayya ko wani tamkar Sa.

Ba shi da iyaka ta keɓaɓɓen wuri.

Shi ne muttasif (wanda ya cancancanta) siffifinsa na kamala (Kamal). Yana da cikar siffofi na kamala.

[1] Duk fatawar da aka samo dole a rubuta wanda ko inda aka samo wannan fatawar.

Siffofi na gazawa sun koru daga gare shi. Babu su kwata-kwata a tattare da shi.

Siffofi na kamala sun tabbata a gare shi, yayin da siffofi na gazawa suka tabbata a gare mu.

Siffofin gazawa da suka tabbata a gare mu su ne ajizanci da suka ƙunshi rashin hannu ko ƙafa ko idanu, akwai ciwo da lafiya, sai cin abinci da shan abin sha, da makamantansu.

Siffofin da suka tabbata ga Allah ‘adhinm-ush-shan su ne siffofin kamala da suka ƙunshi halittar ƙasa da sama da dukkan halittu da suke rayuwa a sarari da cikin ruwa da bisa doron ƙasa da kuma ƙarƙashinta, Ya yi halittu da dama da muka sani da kuma wasu linkin-ba-linkin da raunin tunani da hankalin ɗan adam ba za su iya saninsu ba. Yana bayar da rizƙ (abinci da sauran buƙatun rayuwa) ga dukkan halittunsa, da sauran siffofinSa na kamala. Shi ne ƙadir-i-mutlaƙ (mabuwayi). Dukkan halittu wani yanki ne na siffofin kamala na Allahu ‘adhim-ush-shan.

Akwai siffofi ishirin da biyu da suka tabbata ga Allahu ‘adhim-ush-shan waɗanda suka wajaba mu sani. Haka nan akwai siffofi ishirin da biyu na muhal (da suka koru daga gare Shi).

Wajib na nufin dole. waɗannan siffofin sun tabbata ga Allahu ‘adhim-ush-shan. Siffofin da suke muhal sun koru a gare Shi. Muhal shi ne kishiyar wajib. Yana nufin “abin da babu shi”.

Akwai wata siffa guda ɗaya da ake kira sifat-i-nafsiyya ga Allahu ‘adhim-ush-shan, wadda ita ma ta wajaba musanta: **Wujud**, wadda ke nufin “samuwa”.

Hujjar cewa akwai Allah a nassi ita ce faɗar Allâhu ta’âlâ ƙawl-i-sherif (alƙur’ani) cewa: **“Innani Anallahu.”** Hujja ta hankali kuma ita ce, dole ne akwai wanda ya halicci dukkan waɗannan halittu da ke rayuwa. Muhal ne gare Shi a ce babu shi.

Sifat-i-nafsiyya na nufin Dhat (zati) ba zai yiwu a ce babu zatinsa ba.

SIFAT-I-DHATIYYA

Akwai siffofi guda biyar da suka tabbata ga Allahu ‘adhim-ush-shan da ake kira da sifat-i-dhatiyya, waɗanda suka wajaba mu san su: ana kuma kiransu **Siffofin Uluhiyyat.**

1- **Kidam** wadda ke nufin babu farko komafari game da wanzuwar Allah ‘adhim-ush-shan.

2- **Baƙa** na nufin Allahu ‘adhim-ush-shan ba shida ƙarshe ko iyaka, wadda kuma ake kira wajib-ul-wujud. Tana da hujja a cikin nassi, a aya ta uku da Allâhu ta’âlâ ya saukar a cikin suratul Hadid (ta Kur’an al-karim). Hujja ta hankali itace, idan Yana da farko ko yana da ƙarshe, ba zai taɓa zama mabuwayi ba. Duk wanda yake da gazawa da kasawa ba zai iya ƙirƙirar halitta ba. Don haka ya zama muhal (korarren abu ne gare shi ya zamo yana da farko ko ƙarshe).

3- **Kiyam bi-nafsihi,** wanda ke nufin Allahu ‘adhim-ush-shan ba ya buƙatar kowa tare da zatinSa, da siffofinSa ko al-amuranSa. Akwai hujja a nassi, cikin ayar ƙarshe ta Suratul Muhammad ‘alaihis-salâm’. Hujja ta hankali itace, idan ba shi da cikar siffofin, zai zamo gajiyayye da kasawa. Gazawa da kasawa korarru ne ga Allahu ‘adhim-ush-shan

4- **Mukhalafat-un-lil-hawadith**, ana nufin Allahu ‘adhim-ush-shan ba shi da makamanci (kama) da kowa a zatinSa da siffofinsa. Kamar yadda ya zo a cikin nassi, Allâhu ta’âlâ ya faɗa a cikin aya ta goma sha ɗaya ta Suratus Shura. Hujja ta hankali itace, idan ba Shi da waɗannan siffofin, zai zamo mai gazawa da kasawa. Gazawa da kasawa korarru ne ga Allâhu ta’âlâ.

5- **Wahdaniyyat** ana nufin Allahu ‘adhim-ush-shan ba Shi da abokin tarayya ko makamanci a zatinSa da siffofinSa ko a alamuranSa. Kamar yadda ya zo a cikin nassin ƙur’ani a Suratul Ikhlas aya ta farko. Hujja ta hankali itace, idan da yana da abokin tarayya da ba a samu halitta ko ɗaya ba. Domin yayin da ɗaya daga cikinsu ya yi niyyar halittar wani abu ɗayan kuma ba zai amince ba.

[Mafi yawan manyan malaman Musulunci sun ce, **Wujud** wadda ke nufin samuwa, siffa ce mai daraja. Sun ce akwai siffofi guda shida a ƙarƙashinƙarƙashin **Sifat-i-Dhatiyya.**]

SIFATIL-THUBUTIYYA

Akwai siffofi guda takwas da suke wajibi mu san su, waɗanda suka tabbata ga Allahu ‘adhim-ush-shan waɗanda suke ƙarƙashin Sifat-i-thubutiyya. Su ne: Hayat (rayuwa), ‘Ilm (mai ilimi), Sem’ (mai ji), Basar (mai gani), Irada, Kudrat (mabuwayi), Kalam (mai magana), Tekwin.

Ga bayanin waɗannan siffofin ɗaya bayan ɗaya:

1- **Hayat** ana nufin Allahu ‘adhim-ush-shan rayayye ne. Kamar yadda ya zo a hujja a cikin nassin ƙur’ani ayoyin farko na ayoyin Allâhu ta’âlâ ɗari biyu da hamsin da biyar na suratul Baƙara. Hujja ta hankali itace, idan Allâhu ta’âlâ ba rayayye ba ne, ba za a samu waɗannan halittun ba.

2- **‘Ilm** na nufin Allâhu ta’âlâ masani ne. Akwai hujja a cikin nassin ƙur’ani aya ta ishirin da biyu a Suratul Hashr. A hankalce idan Allahu ‘adhim-ush-shan ba shi da wadataccen ilimi gama gari, da ya zamo mai gazawa da kasawa. Gazawa da kasawa korarru ne ga Allahu ‘adhim-ush-shan.

3- **Sam’** ita kuma ana nufin Allâhu ta’âlâ mai ji ne. Hakan ya zo a cikin nassin ƙur’ani aya ta farko ta suratul Isra. Hujja ta hankali kuma, idan Ya zamo ba mai ji ba, zai zamo mai naƙasu da kasawa. Naƙasa da kasawa korarru ne ga Allahu ‘adhim-ush-shan.

4- **Basar** wanda ke nufin Allahu ‘adhim-ush-shan mai gani ne. Ya tabbata a cikin nassin ƙur’ani aya ta farko ta Suratul Isra. Sannan hujja ta hankali kuma, Allahu ‘adhim-ush-shan zai zamo mai gazawa da kasawa idan ya zamo ba mai gani ba. Gazawa da kasawa korarru ne ga Allahu ‘adhim-ush-shan.

5- **Irada** tana nufin Allâhu ta’âlâ yana yin yadda ya so. Shi ya so samar da dukkan halittu, sai ya halicce su. Hujjar haka ta zo a cikin nassin ƙur’ani, aya ta ashirin da bakwai ta Suratu Ibrahim. A hankalce kuma, idan zai zamo mai naƙasa da kasawa idan ba ya yin yadda ya so. Naƙasa da kasawa korarru ne ga Allahu ‘adhim-ush-shan.

6- **Kudrat** shi ne kasancewar Allahu ‘adhim-ush-shan mabuwayi. Hujjar hakan ta bayyana a cikin nassin ƙur’ani aya ta ɗari da sittin da biyar ta Suratul Al-i-Imran. A hankalce kuma idan bai zamo mai ƙarfi da buwaya ba, zai zamo mai gazawa da kasawa. Gazawa da kasawa korarru ne ga Allahu ‘adhim-ush-shan.

7- **Kalam** abin nufi, Allahu ‘adhim-ush-shan yana magana. Kamar yadda Allâhu ta’âlâ ya tabbatar wa kansa haka a cikin nassin ƙur’ani aya ta ɗari da sittin da huɗu ta Suratun Nisa. Hujja ta hankali kuma, da bai zamo mai magana ba, da ya zamo mai gazawa da kasawa. Gazawa da kasawa korarru ne ga Allahu ‘adhim-ush-shan.

8- **Takwin** na nufin Allahu ‘adhim-ush-shan Shi ya ƙagi halittu. Wato (shi kaɗai yake da ikon ƙaga halitta) doh haka ya yi halittu. Shi kaɗai ya halicci komai daga babu. Babu wani mahalicci bayan Shi. Akwai hujja a cikin nassin ƙur’ani aya ta sittin da biyu ta Suratul Zumar. Ga mai hankali kuma, Akwai halittun Allâhu ta’âlâ daban-daban a bisa doron ƙasa da sararin sama, kuma shi kaɗai ya halicci dukkansu. Kafirci ne (wato mutum zai iya rasa imaninsa) idan ya kira wani da “mahalicci” bayan Allâhu ta’âlâ. Mutum ba ya iya halittar komai.

Allahu ‘adhim-ush-shan yana da Sifat-i-ma’nawiyya (siffofi na ɓoye) guda takwas, waɗanda suka wajaba mu sansu, su ne: Hayyun, ‘Alimun, Semi’un, Basirun, Muridun, Ƙadirun, Mutakallimun, Muƙawwinum.

Ma’ananonin waɗannan siffofin su ne:

1- **Hayyun:** Allahu ‘adhim-ush-shan rayayye ne.

2- **‘Alimun:** Allahu ‘adhim-ush-shan yana da ilimin da ake kira ‘ilm-i-ƙadimi (wadataccen ilimi da ba shi da iyaka).

3- **Sami’un:** Allahu ‘adhim-ush-shan yana ji da irin jin nan da ake kira wadataccen ji da ba shi da iyaka (sam’i ƙadim).

4- **Basirun:** Allahu ‘adhim-ush-shan mai gani ne.

5- **Muridun:** Allahu ‘adhim-ush-shan mai yin yadda ya so ne da irada-i-ƙadim.

6- **Kadirun:** Allahu ‘adhim-ush-shan mabuwayi ne da ƙudirarsa ta ƙudrat-i-ƙadima (ƙudira marar iyaka).

7- **Mutakallimun:** Allahu ‘adhim-ush-shan mai magana ne, da kalam-i-ƙadim (magana marar iyaka).

8- **Muƙawwinum:** Allahu ‘adhim-ush-shan mahalicci ne, shi ya halicci kowa da komai.

Siffofin da suke korarru ga Allâhu ta’âlâ kishiyoyin siffofin da suka tabbata a gare shi ne, kamar yadda aka zayyano su a sama.

WA MALA’IKATIHI: Na yadda da Mala’ikun Allahu ‘adhim-ush-shan; na yi imani da su. Allahu ‘adhim-ush-shan yana da mala’iku. Shi ya halicce su daga nur (haske). Suna da jism (jiki). [A nan ba ana nufin jiki irin wanda aka ambata a littattafan kimiyya ba]. Ba su ci, ba su sha, sannan ba su jima’i. Suna saukowa daga samaniya zuwa ƙasa, sannan su sake koma samaniya. Suna bayyana ta siffa daban-daban. Ba su saɓa wa umarni Allahu ‘adhim-ush-shan ko da daidai da ƙwayar zarra, balle ma su aikata zunubi kamar mu. Daga cikinsu akwai muƙarrab[1] da masu kai saƙo.

WA KUTUBIHI: Na yadda da litattafan da Allahu ‘adhim-ush-shan ya saukar.

Allahu ‘adhim-ush-shan yana da litattafai. Ƙur’an al-karim ya ambaci litattafai ɗari da huɗu. Ɗari daga cikinsu ƙananan litattafai ne. Ana kiransu

[1] A duba matsayi na biyar a Wara’ a rarrabewa ta farko sashen na shida Littafin **Endless Bliss,** akan ‘muƙarrabs’.

‘Suhuf’. Manya kuma guda hudù ne, su ne: **Tawrat** (Attaura) wadda aka saukar wa Annabi Musa ‘alaihis-salâm’, sai **Zabura** da aka saukar wa Annabi Dawud ‘alaihis-salâm’, da **Injil** (Injila) da aka saukar wa Annabi Isa ‘alaihis-salâm, sai kuma **Kur’an al-karim** da aka saukar wa Annabinmu Muhammad ’alaihis-salâm’.

Daga cikin suhuf ɗarin nan (asalin kalmar jam’i ne na sahifa, wadda ke nufin shafi ko takarda, ko allo) an saukar da guda goma ga Annabi Adamu ‘alaihis-salâm’, sai suhuf guda hamsin da aka saukar wa Annabi Shis (Seth) ‘alaihis-salâm’, akwai suhuf talatin da aka saukar wa Annabi Idris ‘alaihis-salâm’, sai suhuf goma da aka saukar wa Annabi Ibrahim ‘alaihis-salâm’. Dukkansu Mala’ika Jibrilu ‘alaihis-salâm’ne ya kawo wa Annabwan saƙonsu. Al-Kur’ani shi ne littafi na ƙarshe da Allâhu ta’âlâ ya saukar. An ɗauki shekaru ishirin da uku ana saukar da Kur’an al-karim sannu a hankali, kuma za a cigaba da bin dokokinsa har zuwa tashin duniya. An kare shi daga shuɗewar zamani [wato ba zai daina amfani ba tsawon zamani], haka nan daga cushen mutane [wato mutane ba za su iya sauya wani abu ƙari ko ragin wani abu a cikinsa ba].

WA RASULIHI: Na kuma yi imani da Annabawa ‘alaihim-us-salawat-u-wa-t-teslimat’ na Allahu ‘adhim-ush-shan.

Allâhu ta’âlâ yana da Annabawa ‘alaihim-us-salawat-u-wa-t-teslimat’. Dukkan Annabawan mutane ne ‘yan adam. Annabi Adam ‘alaihis-salâm’shi ne Annabin farko, Annabinmu Muhammad Mustafa ‘sallallâhu ta’âlâ’alaihi wa sallam shi ne cikamakin Annabawa. Duk sauran Annabawan da aka aiko sun zo ne tsakanin waɗannan Annabawa guda biyu. Allahu ‘adhim-ush-shan kaɗai ya san yawansu.

Akwai siffofi guda biyar na Annabawa ‘alaihim-us-salawat-u-wa-t-teslimat’ da suka wajaba mu san su, su ne: Sidƙ, Amanat, Tebligh, Ismat, Fetanet.

1- **Sidƙ:** Dukkan Annabawa masu gaskiya ne wajen zance. Duk abin da suka faɗi gaskiya ne.

2- **Amanat:** ba su taɓa cin amana ba.

3- **Tabligh:** Sun san dukkan horo da hani na Allahu ‘adhim-ush-shan sun kuma isar da saƙonsu ga al’ummarsu.

4- **Ismat:** shi ne nisantar aikata saɓo, manya da ƙanana. Ba su taɓa aikata saɓo ba. Annabawa ‘alaihim-ussalâm’ su ne kaɗai mutanen da ba su aikata saɓo. [Sai dai‘yan Shi’a sun ce akwai wasu mutanen da wai ba su aikata saɓo.]

5- **Fetanat:** Dukkan Annabawa ‘alaihim-us-salawât-uwa-t-taslîmât’sun fi sauran mutane hikima da basira.

Akwai wasu siffofi biyar da suke ja’iz (suka halatta) ga Annabawa ‘alaihim-us-salawât-u-wa-t-teslîmât’, su ne: cin abinci da shan abin sha, da rashin lafiya, da mutuwa, hijira daga wata duniya zuwa wata (kamar daga duniya zuwa lahira), kuma ba su damu da duniya ba.

Akwai Annabawa 28 wadanda aka ambaci sunayen su a cikin Kur’an al-karim. Akwai maganganun wasu Malamai da suke ce wajibi ne kowa ya san sunayen Annabawan.

Sunyen **Annabawa** ‘’alaihim-us-salawat-u-wa-s-salam’:

Adam, Idris, Nuh, Shis (Seth), Hud, Salih, Lut, Ibrahim, Isma’il, Ishaƙƙ, Yaƙub, Yusuf, Suayb, Musa, Harun, Dawud, Suleyman, Yunus, Ilyas, Elyasa’, Zulkifl, Ayyub, Zakariyya, Yahya, ‘Isa da Muhammad ‘salawatullahi ‘ala nabiyyina wa ‘alaihim’. Akwai saɓanin game da Annabtar Uzayru da Luƙman da Zulƙarnayn. Wasu (daga cikin Malaman Musulunci) sun ce wadannan ukun da ma Hidir ‘alaihis-salâm’ duk Annabawa ne, wasu kuma (wato Malaman) sun ce Awliya (Waliyyay) ne. An rubuta a shafi na talatin da shida na littafin Maktubat-i-Ma’thumiyya[1] mujalladi na biyu cewa akwai maganganun manyan Malamai masu ƙarfi da suka nuna cewa Hidir ‘alaihis-salâm’ Annabi ne. Haka nan a shafina ɗari da tamanin an bayyana cewa, bayyanar da aka ce Hidir ‘alaihis-salâm’ yana yi yana wasu ayyuka da siffar mutane ba ya nuna cewa yana nan da ransa. Alla ta’ala yana bai wa wasu bayinsa dama kamar Annabawa da Awliya a riƙa ganinsu a siffar mutane. Ganinsu baya nuna suna raye.

Har ila yau, abin da ake so mutum ya faɗa shi ne “Alhamdullah ina cikin zuriyyar Annabi Adam ‘alaihis-salâm, kuma ina cikin al’ummar (masu imani) Annabin ƙarshe Muhammad ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’”. Wahabiyyawa sun musanta cewa Annabi Adam ‘alaihis-salâm’ Annabi ne. Haka nan suna kiran wasu Musulmai ‘mushirikai’ suna cewa kafirai ne.

WA-L-YAWM-IL-AKHIRI: Haka nan na yi imani da ranar tashin ƙiyama: Na yadda da ita. Saboda Allâhu ta’âlâ ya sanar da mu game da ita. Ranar Kiyama(t) za ta fara ne da tashin dukkan wadanda ke kwance a ƙabari. Za ta cigaba har zuwa lokacin da mutane za su tafi gidajen da aka yi masu

[1] Marubucin shine, Muhammad Ma’thûm Fârûƙî ‘rahmatullâhi ta’âlâ ’alaih’ (1007, Serhend – 1079 [1668 A.D.], wuri ɗaya da), ɗa na uku ga Hadrat Imâm Rabbânî ‘ƙuddisa sirruhumâ’ .

tanadi, wato Aljanna ko wuta. Dukkanmu za mu mutu, kuma za a dawo mana da ranmu a ranar tashin ƙiyama. Aljanna da wuta da mizan [mizani] da siraɗi da hashr [tsayuwa] nashr [barin filin tsayuwa zuwa wuta ko Aljanna] da azaba da tambayoyin ƙabari daga mala'iku biyu Munkar da Nakir dukkansu gaskiyane (haƙ). Tabbas za su auku baki ɗayansu.

WA BI-L-KADAR-I-KHAYRIHI WA SHARRIHI MIN-ALLAHI TA'ALA: Na yadda cewa dukkan al'amurra da suka faru da waɗanda za su faru nan gaba masu kyau da marasa kyau, sun faru ne ko za su faru ne da izinin Allahu 'adhim-ush-shan, ko kuma da saninsa da izininsa tun fil azal, da kuma halittarsu bisa dadaiton lokaci, haka nan da rubutasu a cikin Lawh-il-Mahfuz, na yi imani da haka. Babu kokwanto a cikin zuciyata.

Ash-hadu an la ilaha il-l-Allah wa Ash hadu anna Muhammadan 'abduhu wa rasuluh.

Haka nan, Mazhabina na i'tiƙad, [wato ginshiƙan imani da aka yadda da su] shi ne Mazhab na **Ahl as-Sunnaht wa-l-jama'at**. Ina nan kan wannan Mazhabar. Sauran rabe-raben addini guda saba'in da biyu suna kan ɓata. Kuma za su shiga wuta. [Musulmai da suke son As-hab-i-kiram (sahabbai) 'alaihim-ur-ridwan' ana kiran su **Ahl as-Sunnat**. Dukkan Sahabbai masu ilimi ne kuma Musulmai ne masu adalci. Sun kuma samu suhuba, (wato zamantakewa mai albarka da tarayya) da shugaban 'yan adam (wato Manzon Allah) 'sallallâhu' alaihi wa sallam' sun kuma taimaka mashi. Ko sahabin da ya samu mafi ƙanƙantar (suhuba) ya fi Waliyyi daraja, wanda shi ne mafi darajar dukkan Awliya amma ba sahabi ba ne. Matsayin da sahabi ɗaya ya samu na ƙauna da kusanci da Allâhu ta'âlâ da cika ta kamala da ya samu, ba za a samu wani da zai kai darajar ko da numfashinsa ba, in ba wanda ya samu wannan suhubar da kusancin ba. Dukkan Sahabbai 'ridwanullahi ta'ala 'alaihim ajma'in sun samu kariya daga bin san zuciyarsu, daga lokacin da suka samu suhuba (da Manzon Allah 'sallallâhu' alaihi wa sallam'). An umarce mu da ƙaunarsu baki ɗayansu. An ruwaito a farkon sharhin littafin **Shir'at-ul-islam**:[1] "Ka yi ƙoƙarin yin magana a kan Sahabbai 'alaihim-ur-ridwan' cikin girmamawa da mutuntawa. Kada ka munana zance a kansu". Amma a cikin rabe-raben addini saba'in da biyun nan: akwai waɗanda suka ɗauki abin da zafi, wasu kuma ba su damu ba; wasu kuma sun yadda da su, yayin da wasu kuma suka yadda da falsafar malaman Girka. Sai suka riƙa

[1] Marubucin littafin shine Muhammad bin Abû Bakr 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' (d. 573 [1178 A.D.]). Wanda ya rubuta sharhin littafin shine Ya'ƙûb bin Sayyid 'Alî 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' (d. 931 [1525 A.D.])

yin abubuwan da babu su a Musulunci da waɗanda suka saɓa wa Musuluncin gaba ɗaya. Sun yi riƙo da bidi'o'i (yadda da kuma ayyukan da babu su a Musulunci, waɗanda aka ƙago da sunan Musulunci). Suka yi watsi da Sunnah, wato Musulunci. Akwai mutanen da suke sukar jagororin Musulunci irin su Abu Bakr as-Siddiƙ da Hadrat 'Umar 'Allah ya yarda da su' waɗanda su ne manyan Sahabbai kamar yadda ijma' (ijma'in malaman Musulunci) ya tabbatar. Maganar gaskiya ma, mafi yawancinsu suna fuskantar suka ne saboda kusancinsu ga shugabanmu Annabi Muhammad 'sallallâhu'alaihi wa sallam'. Akwai waɗansu mutanen da suke ganin cewa shugabanmu Annabi 'sallallâhu 'alaihi wa sallam', ya je sama da jiki da ruhinsa a daren da aka yi Mi'raj (wanda aka yi cikakken bayani a kai a cikin babi na sha shida na mujalladi na uku na littafin **Endless Bliss**.)

Abin damuwa ne matuƙa yadda aka samu wasu daga cikin malaman Musulunci suka ƙasƙantar da kansu wajen zama masu magana da yawun ɓangaren 'yan ƙungiyar **Isma'iliyya** wadda ke cikin ɓangarori saba'in da biyun nan (na bid'at) kuma mafi illa a ciki. Suna ta yunƙurin ɓatar da matasa ta hanyar rubutawa da yaɗa ƙarairayi, da suka ƙunshi cewa iyayen Annabi 'sallallâhu'alaihi wa sallam', kafirai ne, da cewa Annabi 'sallallâhu'alaihi wa sallam', yana yanka dabba a gaban gumaka kafin a saukar masa da Annabta, sannan suka riƙa kafa hujja da wasu litattafan Shi'a domin kare ƙarairayinsu. Idan an lura sosai, manufar waɗannan mayaudaran ita ce domin su ƙasƙantar da addinin Musulunci, da raba matasa da imaninsu, su maye gurbinsa da kafirci. A cikin wata aya ta Kur'an al-karim tana cewa: "**Duk mutumin da ya fassara Kur'an al-karim da fahimta da tunaninsa ya zama kafiri**." Malaman Musulunci suna da wata ɗabi'a (kyawawan halaye bisa koyarwar Musulunci). Suna zance da rubutusu cikin taka tsantsan. Suna yin zurfin tunani domin guje wa yin kuskure. Yin zance ba tare da kulawa ba, misali, ƙoƙarin bayyana kuskure ko sukar ra'ayin wani na ƙashin kansa da sunan Musulunci, maimakon binciko gaskiyar bayani daga **Adilla-i-shar'iyya,** wato daga manyan Mazhabobin Musulunci guda huɗu, ba abu ba ne wanda Musulmi zai yi, balle ma Malami. Wajibi ne mu guji zantuka da rubuce-rubucen waɗannan jahilan mutanen, waɗanda ba su san darajar shugabanmu Annabi 'sallallâhu 'alaihi wa sallam', ba ko Sahabbansa 'ridwanullahi ta'ala 'alaihim ajma'in saboda ƙiyayya.

A wani zancen azanci na Farisanci suka ce:

Ina girgiza kamar ganyen bishiya idan aka taɓa addini na.

Allâhu ta'âlâ ya ƙara soyayyar waɗanda yake ƙauna a cikin zukatanmu. Ya kuma kare mu daga sharrin ƙaunar maƙiyansa! Alamun imani a cikin zuciya su ne son waɗanda Allâhu ta'âlâ yake so da kuma ƙin maƙiyansa.

Akwai mazhabobi hudu na ‘amal (ayyukan ibada da ma’amala da halaye na Musulunci): Su ne Mazhabin Imam a’zam (Abu Hanifa), da ta Imam Shafi’i, da ta Imam Malik da ta Ahmad bin Hambal ‘rahmatullahi’alaihim’.

Wajibi ne ga kowane musulmi ya yi riko da daya daga cikin wadannan Mazhabobin. Dukkan Mazhabobi suna kan daidai. Suna bisa akidar Ahlus Sunnah. Mu muna kan Mazhabin Imam ‘azam. Musulmin da suke kan wannan Mazhabin ana kiransu **Hanafis**. “Mazhabin Imam ‘azam shi ne thawâb[1] (lada) da yin daidai. Akwai yiwuwar cewa ba kan daidai take ba. Sauran Mazhabobin uku ma ba daidai suke ba. Akwai kuma yiwuwar dukkansu a kan daidai suke,”

Haka nan Imani ya zauna tare da mutum har abada ba tare da ya fita ba, ya dogara ne a kan sharuddа da dalilai shida:

1- Muna yi Imani da gaibu. Imaninmu a gaib yake (wanda ba a sani ba, ba a ganin shi), ba a bayyane yake ba (wanda aka sani, ake gani da ido). Domin ba mu iya ganin Allahu ‘adhim-ush-shan da idanunmu. Sai dai mun yi imani da Shi kamar muna ganinSa. Ba mu da kokonto a kanSa.

2- A duniya da lahira, a cikin mutane da aljannu da mala’iku da Annabawa ‘’alaihim-us-salawat-u-wa-t-teslimat’, babu wata halitta da ta san gaibu. Allahu ‘adhim-ush-shan kadai ya san gaibu, Yana sanar wa da duk wanda Ya so daga halittunSa wani abu na gaibu. [Ghaib na nufin (wani abu) wanda tunanin dan adam ba ya iya hango shi ko fahimta ta hanyar lissafi ko gwaji. Ana iya sanin gaibu ne ga wadanda Ya so su sani kadai daga cikin zaɓaɓɓun bayinsa.]

3- Ka san cewa haramun, haramu ne kuma ka yadda da haka.

4- Ka san cewa halal, halal ne kuma ka yadda da haka.

5- Kar ka rika jin ka tsira daga azabar Allahu ‘adhim-ush-shan kuma ka rika jin tsoronSa a koda yaushe.

6- Kar ka yanke kauna ga rahamar Allahu ‘adhim-ush-shan, duk yawan saɓon da kake aikatawa.

Idan mutum bai cika daya daga cikin wadannan sharuddan guda shida ba, amma ya cika biyar daga ciki, ko ya cika guda daya, ya yi watsi da biyar

[1] Kalmar ‘thawâb’ ana amfani da ita ne a matsayin manuniya da suna. Idan aka kira wata dabi’a da ‘thawâb’ to ana nufin Allâhu ta’âlâ na kaunar wannan abun, kumar ranar alkiyama zai bada ladar wannan aikin.

a ciki, imani da Musuluncin wannan mutumin ba sahih (wato ingantacce) ba ne.

Akwai wasu abubuwa arba'in (40) da suke haddasa wa mai imani yanzu, ya rabu da imaninsa anjima:

1- Yin riƙo da bidi'a, wadda ke nufin mutum ya gurɓata imaninsa. [Kaucewa daga aƙidar Malaman ahlalus Sunnah ko kaɗan ne, za su haddasa wa mutum ya zamo munafiki ko kafiri. Idan mutum ya musanta ɗaya daga cikin abubuwan da suka wajaba, wannan mutum ya zama kafiri kai tsaye. **Bidi'a** ne ko **ɓata** mutun ya musanta abin da ba wajibi ba. Bidi'a da ɓata suna sanya mai su ya mutu babu imani.]

2- Raunin imani, wato imani babu 'amal (ayyukan ibada).

3- Gaɓoɓin jikin mutum su yi watsi da hanya madaidaiciya.

4- Cigaba da aikata manyan zunubai. [Don haka mutum kada ya sha giya, kuma mata Musulmi kada su riƙa nuna kansu da gashinsu da ƙwabrinsu da kuma hannuwansu daga kafaɗa zuwa wuyan hannu ga mazan da ba muharramansu [1] ba.]

5- Daina nuna godiya ga samun ni'imar kasancewar mutum Musulmi.

6- Nuna halin ko-in-kula ga yiwuwar tafiya lahira babu imani.

7- Yin ƙeta da zalunci.

8- Ƙin sauraren (Adhan-i-Muhammadi) kiran sallah wanda ake yi bisa koyarwar Sunnah. [Mutumin da ya toshe kunnensa ga kira zuwa ga ibada ya zama kafiri kai tsaye.] (An yi cikakken bayanin adhan (kiran sallah) da yadda ake yin sa kamar yadda Sunnah ta koyar, a cikin babi na goma sha ɗaya na mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss.**)

9- Mutum ya bijire wa iyayensa. Da yi masu rashin kunya wajen ƙin bin umarninsu da bai saɓa wa Musulunci ba.

10- Yawan yin rantsuwa ko da a kan gaskiya ne.

11- Rashin nutsuwa a cikin sallolin farilla, musamman a cikin ruku'u da tasowa tsaye daga ruku'u da sujada, da zama a tsakanin sujudu biyu. Nutsuwa na nufin mutum ya tsaya ba tare da motsi ba (ɗumaninat) aƙalla tsawon lokaci da za a iya cewa "Subhanallah."

12- Yin tunanin cewa sallah ba ta da muhimmanci, da rashin mai da hankali wajen koyon yadda ake yin ta, da koyar da ita ga iyalai da zuri'a, da kuma hana wasu yin sallah.

---

[1] A duba babi na goma sha biyu a mujalladi na biyar a cikin littafin **Endless Bliss** domin cikakken bayanin waɗannan kalmomin kamar su 'mahram' da na-mahram'.

13- Shan giya (khamr) da duk wani abu da ke sa maye idan aka sha shi; wannan ya shafi ko da an kurɓi kaɗan daga giyar ne.

14- Jefa al'ummar Musulmi cikin fitina.

15- Yin ƙaryar walittaka ko malami a Musulunci. Mutum ya nuna kansa a matsayin mai zurfin addini, ko mai wa'azi ba tare da sanin koyarwar Ahl as-sunnat ba. [Litattafan ƙarya da waɗannan maƙaryatan suka rubuta bai kamata a karanta su ba. Ba za a halarci wajen da suke wa'azi ko huɗuba ba.]

16- Mutum ya manta da zunuban da yake aikatawa; yaɗauke su ba a bakin komai ba.

17- Faɗin rai, wato mutum ya riƙa ganin ya fi kowa.

18- Ujb (girman kai) wato mutum ya riƙa taƙama da ilimi da taƙawarsa.

19- Mutum ya zamo munafiki, wato munafunci da nuna fuska biyu.

20- Hassada; mutum ya riƙa jin ƙyashin ɗan uwansa Musulmi.

21- Ƙin bin dokokin gwamnati ko bijirewa mai gidansa idan umarnisu bai saɓa wa Musulunci ba. Da ƙin bore ga umarninsu da ya saɓa wa Musulunci.

22- Faɗar cewa wane da wane mutanen kirki ne ba tare da ka tabbatar ba.

23- Mutum ya ɗabi'antu da ƙarya koda yaushe.

24- Guje wa manyan Malaman Addini [ƙin karanta litattafan da Malaman Ahl as-sunnat suka rubuta.]

25- Barin gashin baki ya yi tsawon da ya wuce shari'a bisa koyarwar Sunnah.

26- Sanya suturar siliki ga maza. Ya halatta su sanya silikin da aka sarrafa da sinadarai, ko gamin wani falle na silikin da na auduga.

27- Mutum ya zama magulmaci.

28- Muzguna wa maƙwabci ko da kafiri ne.

29- Yawan fushi a kan game da lamurran duniya.

30- Karɓa da bayar da riba.

31- Taƙama da sutura mai dogayen hannuwa ƙarshensu ya ja ƙasa.

32- Yin sihiri.

33- Yanke zumunci da muharrami wanda yake da tsoron Allah (salih).

34- Kiyayya ga mutumin da Allâhu ta'âlâ yake ƙauna da nuna ƙauna ga waɗanda (ka san) ba su son Musulunci.

35- Yin gaba da ɗan uwanka Musulmi har ta wuce kwanaki uku.

36- Mayar da saɓo ya zama ɗabi'ar mutum.

37- Yin luwaɗi da ƙin tauba [1] daga aikata shi. Luwaɗi na nufin mutum namiji ya saka azzakarinsa a cikin duburar ɗan uwansa (namiji ko mace). Azzakari na nufin gaɓar jikin ɗan adam namiji da yake fitsari da ita. Gaɓar mace da take fitsari da ita ana kiranta farj (farji).

38- Yin kiran sallah (adhan ko azan) ba yadda aka koyar a fiƙihun malaman Sunnah ba, da ƙin girmama kiran sallar kamar yadda Sunnah ta koyar.

39- Kin yin (nahy) nasiha cikin taushin harshe ga mutumin da ke aikata saɓo (hana shi aikata saɓon) bayan kana da iko yin hakan.

40- Nuna halin ko-in-kula ga macen da take aikata saɓo wadda take ƙarƙashin ikon ka, kamar matarka da ɗiyar ka, misali, barin su suna fita ba tare da sun rufe jikinsu ba, ko sanya turare da kayan ado idan za su fita.

Iman (imani) shi ne furuci da baki da amincewa a zuciya da saƙon da Annabawa suka kawo daga Allahu 'adhim-ush-shan. Haka nan Musulunci na nufin yin imani da Annabi Muhammad 'sallallahu 'alaihi wa sallam' da yin aiki bisa koyarwarsa.

Din da **Millat** ma'anarsu ɗaya. **Din** ko **Millat** na nufin imani, wato amincewa da saƙon da Annabi 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya karɓo daga wurin Allahu 'adhim-ush-shan.

Islam ko **Ahkam-i-islamiyya** na nufin 'amal, wato aikin ibada wanda Annabi 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya karɓo daga Allâhu ta'âlâ.

Haka nan kuma iman-i-ijmali (imani taƙaitacce) yana nufin imani nan take, ya ishi mutum ya zamo Musulmi. Ba wajibi ba ne sai mutum ya yi zurfi ko ya san komai game da imani ba. Shi kuma imani da ake kira Muƙallid, yana nufin mutum ya yi imanin ba tare da fahimta ba, ya ishe shi ya zama salihi. Sai dai ana buƙatar isasshen bayani game da wasu mas'aloli.

Akwai matakai uku na imani: iman-i-taƙlidi da iman-i-stidlali da iman-i-haƙiƙi.

Iman-i-taƙlidi (imani na nagani anayi) mutumin da yake da irin wannan imanin bai san farillai (fard), ko wajibai, ko sunnoni ko kuma mustahabbai ba. Suna kwaikwayon imani da ayyukan ibada suka ga iyayensu nayi. waɗannan sune masu raunin imani.

---

[1] Tauba shine tuba ga zunubban da wani ya aikata ta hanyar roƙon Allâhu ta'âlâ gafara da kuma alƙawarin cewa mutum ba zai sake aikata waɗannan zunubai ba.

Iman-i-stidlali (imani bisa dalilai) mutanen da suke da wannan nau'in na imani sun san farillai da wajibai da mustahabbai da haramun, kuma suna yin ɗa'a ga Musulunci. Suna da ilimi da fahimtar hukunce-hukuncen Musulunci da imani. Sun yi karatu a wajen malamai da karanta litattafai. Imanin waɗannan mutanen yana da ƙarfi.

Iman-i-haƙiƙi (imani na gaskiya, mai zurfi). Idan dukkan halittu za su taru su musanta wanzuwar Ubangijinsu (Allâhu ta'âlâ), mutanen da suke da irin wannan imanin ba za su yadda da haka ba. Babu wani ɗigo na kokwanto a cikin zukatansu. Imaninsu yana kusa da na Annabawa. Wannan nau'in na imani shi ne ƙololuwar imani sama da sauran biyun.

Hukunce-hukuncen Musulunci suna shafi ayyukan ibada ne, ban da imani. Imani kaɗai zai iya shigar da mutum Aljanna. Kuma ibada ita kaɗai ba za ta iya shigar da kai Aljanna ba. Ana karɓar imani ko babu aikin ibada, yayin da ba a karɓar aikin ibada ba tare da imani ba. Wato ibada babu imani ba ta da wani amfani. Dukkan ayyukan ibada da waɗanda aka yi bisa gaskiya da sadaka ga mabuƙata ba za su amfani wanda ba shi da imani ba a gobe ƙiyama. Ba a iya bayar da kyautar imani, amma ana iya bayar da kyautar ladar da mutum ya samu a ayyukan ibada. Mutum ba zai iya barin wasiyya game da abin da ya shafi imani ba. Amma mutum zai iya barin wasiyya ga magadansa su yi masa wani aiki na ibada bayan ya rasu. Mutumin da ya bar ibada bai zama kafiri ba, amma duk wanda ya yi watsi da imaninsa ko bai ɗauki ibada da muhimmanci ba zai zama kafiri. Duk mutumin da yake da uzuri ('udhr) na haƙiƙa ko wanda yake da wata nakasa za a ɗauke masa ibada, amma babu wani dalili da zai sa a ɗauke wa mutum imani.

Imani guda ɗaya ne tak da dukkan Annabawa suka kira al'ummarsu a kai. Amma sun bambanta ta fuskar shari'o'in da suka zo da su, da zamani, da ayyukansu na ibada.

Haka nan akwai wasu nau'in imani biyu. Iman-i-khilƙi da iman-i-kesbi.

Iman-i-khilƙi shi ne bawa yace "**mun amince**" a lokacin 'ahd-i-misak (yin mubayi'a).[1]

Iman-i-kesbi shi ne imanin da mutum ya samu bayan ya balaga. Imanin dukkan Musulmi ɗaya ne. Sai dai sun bambanta wajen ayyukan ibada.

---

[1] A duba sakin layi na uku na babin farko a littafin, mai suna **The Rising and the Hereafter.**

Imani fard-i-daim (wajibi ne a koda yaushe), shi kuma aiki yana zama wajibi ne idan lokacinsa ya yi.

Imani wajibi ne ga Musulmi da kafirai, amma aiki ya wajaba ne ga Musulmi kaɗai.

Akwai ire-iren imani guda takwas:

Iman-i-metbu' shi ne imanin mala'iku.

Iman-i-ma'sum shi ne imanin Annabawa.

Iman-i-maƙbul shi ne imanin Muminai

Iman-i-mawƙuf shi ne imanin 'yan bidi'a.

Iman-i-mardud shi ne imanin yaudara wanda munafukai suke da shi.

Iman-i-taƙlidi shi ne imanin da mutane suka samu daga iyayensu ba wajen malamai ba. Wannan imanin yana da rauni.

Iman-i-stidlali shi ne imanin mutumin da ya san Mawla-i-mute'ali ta hanyar hujjoji. Wannan imanin yana da ƙarfi.

Iman-i-haƙiƙi. Duk mutanen da suke da irin wannan imanin ba za su taɓa musanta Ubngijinsu [Rabb (Allâhu ta'âlâ)] ba, ko da kuwa dukkan halittu sun yadda cewa babu Shi, kuma babu ɗigon kokwanto ko kaɗan a zukatansu. Wannan shi ne ƙololuwar imani kamar yadda aka bayyana a baya.

Muhimmancin yin imani uku ne:

Da farko yana kare mutum daga hukuncin sare wuya da takobi.

Na biyu yana kare dukiyar mutum daga (harajin) jizya da kharja[1].

Na uku kuma yana kare mutum daga dawwama a wutar jhannama.

"**Amantu billahi…,**" shi ma ana kiransa Sifat-i-iman ko mu'minun bih ko dhat-i-iman ko 'asl-i-iman, bisa sifar girma da ɗaukaka. (Yana daga cikin shika-shikan imani na Musulunci cewa: "**… wa Malaikatihi, wa Kutubihi, wa Rusulihi, wa-l-Yawm-i-akhiri, wa bi-l-Kadari, Khayrihi wa sharrihi min-Allahi ta'ala, wa-l-ba's-u-ba'd-al-mawt, Haƙƙun ash-hadu anla ilaha il-l-Allah wa ash-hadu anna Muhammadan 'abduhu wa Rasuluhu.**")

---

[1] A duba babi na goma sha ɗaya da na ashirin a mujalladi na farko, babi na talatin da uku a mujalladi na biyu, babi na ashirin da ɗaya a mujalladi na huɗu, babi na farko da na goma sha biyu a mujalladi na biyar da kuma babi na farko a mujalladi na shida, na littafin Endless Bliss akan Jizya da kharâj.

Haka nan akwai medars na imani guda biyu, wato lokacin da ya wajaba ga mutum ya zamo mai imani: Shekarun hankali da shekarun balaga.

Kazalika akwai dalillai biyu na imani: Halittar dukkan halittu da saukar alƙur'ani mai girma.

Akwai hujjoji da suka kasu gida biyu: Dalil-l-'aƙli (hujja ta hankali) da dalil-i-naƙli (hujja ta nassi).

Imani yana kuma da rukns (rukunnai), **'asls** (asali): Ikrar-un bi-l-lisan (Ambato da harshe) da tasdiƙ-un-bi-l-jenan (tabbatarwa a zuciya). Akwai sharuɗɗa biyu da aka ɗshimfiɗa game da haka:

Sharaɗi na farko ya wajabta wa zuciya kada ta yi kokwanto ko tirjewa, abin da ya shafi harshe kuwa, wajibi ne a lura da zancen da yake furtawa.

Shin imani halitta ne? Ba halitta ba ne domin shi shiriya ne daga Allahu 'adhim-ush-shan. A ɗaya ɓangaren kuma halitta ne duba da tabbatarwa da furuci daga bayin Allah.

Shin imani a tattare yake ko tilo ne kuma jam'i?

Tattarawa ne a cikin zuciya, sannan jam'i ne a akan gaɓɓai.

Yaƙin na nufin sanin zatin Allahu 'adhim-ush-shan da KamalarSa (Kamal).

Khawf na nufin tsoron Allahu 'adhim-ush-shan.

Raja rashin yanke ƙauna ga Rahmat (Rahamar) Allahu 'adhim-ush-shan.

Muhabbatullah shi ne ƙaunar Allâhu ta'âlâ da Annabinsa 'sallallahu 'alaihi wa sallam' da Musulunci da Musulmi.

Haya shi ne jin kunyar Allah da Manzonsa 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam'.

Tawakkul yana nufin fauwala dukkan al'amurra ga Allâhu ta'âlâ. Mutum ya dogara ga Allah a duk lokacin da zai gudanar da wani abu.[1]

Shin me ake nufi da iman da Islam da Ihsan?

Iman na nufin yadda da dukkan abin da Manzon Allah 'alaihis-salâm' ya zo da shi.

Islam shi ne bin umarnin Allahu 'adhim-ush-shan da kuma nisantar haninsa.

---

[1] Babi na talatin da uku a mujalladi na uku na littafin **Endless Bliss** yayi cikakken bayani akan Tawakkul.

Ihsan na nufin mutum ya yi ibada kamar yana ganin Allâhu ta'âlâ a gabansa.

Iman; ma'anar kalmar ta asali ita ce 'tabbatarwa ta gaskiya'. A Musulunci kuma tana nufin yadda da tabbatar da shikashikan imani guda shida.

Ma'arifat na nufin sanin Allâhu ta'âlâ bisa siffofinsa na cikar kamala kuma nisanta daga siffofi na rashin kamala.

Tawhid shi ne kaɗaita Allahu 'adhim-ush-shan, kuma ba shi da abokin tarayya.

Islam (Ahkam-i-islamiyya) na nufin horo da hanin Allahu 'adhim-ush-shan.

Din wa millat na nufin tsayuwa bisa shika-shikan imani har ƙarshen rayuwa.

Akwai katangu guda biyar da suke yi wa imani garkuwa:

1- Yaƙƙini

2- Ikhlasi

3- Yin ibada ta farilla da guje wa aikata haram.

4- Yin riƙo da Sunnah.

5- Tsayin daka a kan kyawawan ɗabi'u, da kulawa da su. [1]

Duk mutumin da ya yi riƙo da waɗannan garkuwar, zai riƙe imaninsa da kyau. Rashin riƙo da su kuma zai gamu da maƙiyansa. Mutum yana da maƙiya guda huɗu: huldà da Sheɗanun mutane a hannun damansa; biye wa son zuciya a hannun hagunsa; son duniya a gabansa; da sheɗan kuma a bayansa. Waɗannan maƙiya huɗu kullum suna ƙoƙarin raba mutum da imaninsa. Huldà da sheɗanun mutane ba wai sai a mutane da ke cutarsa a cikin dukiyarsa da kuɗinsa da sauran al'amurran duniya ba, mafi muni a cikin abota da su shi ne ƙoƙarin raba mutum da imani da kyawawan ɗabi'u da kunya da halaye nagari, waɗanda ke gadar da baƙin ciki a duniya da lahira. Allâhu ta'âlâ ya tsare mana imaninu daga sharrin maƙiya Musulunci.

Ma'anar **Kalima-i-Tawhid**, wato cewa "**La ilaha il-l-Allah,"** shi ne cewa: Babu abin bautawa da gaskiya sai Allahu 'adhim-ush-shan. Allahu

---

[1] Babi na talatin da uku a mujalladi na uku na littafin **Endless Bliss** yayi cikakken bayani akan Tawakkul.

‘adhim-ush-shan shi kaɗai ne. rayayye ne. Ba shi da abokin tarayya ko makamanci. Ba shi da farko ba shi da ƙarshe, kuma ba shi da makani.

“Muhammadun Rasulullah” na nufin Annabi Muhammad, Mustafa ‘sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’ bawan Allahu ‘adhim-ush-shan ne kuma Manzonsa ne. Mu kuma al’ummarsa ne, Alhamdulillah.

Kalima-i-Tawhid tana da wasu sunaye guda takwas:

1- Kalima-i-Shahadat.
2- Kalima-i-Tawhid.
3- Kalima-i-Ikhlas.
4- Kalima-i-Taƙwa.
5- Kalima-i-Tayyiba.
6- Da’wat-ul-Haƙƙ.
7- ‘Urwa-t-ul-wuthƙa.
8- Kalima-i-thamarat-ul-Jannat.

Abubuwan da ake son mutum ya cika domin samun ikhlas[1] su ne: Yin niyyat (niyya), sanin ma’anar kalmar, da karantata cikin girmmamawa.

Haka nan mutumin da yake yin dhikr (zikiri) yana buƙatar abubuwa huɗu: Tasdiƙ da ta’dhim da halawat, da kuma hurmat.

Duk mutumin da ya yi watsi da tasdiƙ ya zama munafiki; duk wanda ya yi watsi da ta’dhim ya zama ɗan bidi’a; duk wanda ya yi watsi da halawat ya zama munafiki; maƙaryaci; haka nan wanda ya yi watsi da hurmat ya zama fasiƙi. Ƙaryata su kuma yana kai mutum ga kafirci.

Akwai na’u’in dhikr guda uku:

1- Dhikr-i-awam.
2- Dhikr-i-khawas.
3- Dhikr-i-akhas.

Dhikr-i-awam shi ne zikirin da waɗanda ba su da ilimi suke yi. Dhikr-i-khawas shi ne zikirin da malamai suke yi, sai Dhikr-i-akhas wanda Annabawa suke yi.

Sannan akwai gaɓoɓi uku na jikin ɗan adam da ake zikiri da su.

1- Zikirin da ake yi da harshe, wato ambaton Kalima-i-shahadat.
2- Yin zikirin tawhid da tasbihi da karatun Al-ƙur’ani mai girma.

---

[1] Yin abu dan Allâhu ta’âlâ yayi umarni da shi da kuma nisantar abu saboda Allah yayi hani da shi.

3- Zikirin da ake yi da zuciya.

Akwai kuma ire-iren dhikr da ake yi da zuciya:

1- Yin nazari a kan dalilai da suke shiryarwa ga fiffofin Allahu ‘adhim-ush-shan.
2- Yin nazari a kan dalilan Ahkam-i-islamiyya.
3- Yin nazari game da hikimar samar da halittu.

Malaman tafsir sun yi fassara aya ta ɗari da hamsin da biyu ta suratul Baƙara kamar haka: “**Ya ku bayina! idan kuka ambace Ni ta hanyar ɗa’a** (biyayya ga Allâhu ta’âlâ), **Zan ambace ku da rahamata. Idan kuka ambace Ni ta hanyar yabo da addu’o’i, Zan ambace ku ta hanyar karɓa maku. Idan kuka ambace Ni ta hanyar ɗa’a, Zan ambace ku ta hanyar ba ku ni’imata** [Aljanna]. **Idan kuka ambace Ni a sirrance, Ni kuma zan ambace ku a Jam’iyyat-i-kubra** [wato wurin da ake kira Mahsher]. **Idan kuka ambace Ni a lokacin ƙunci, Zan ambace ku da taimakona. Idan kuka ambace Ni ta hanyar ijabat** (wato kiyaye dokoki) **Zan ambace ku ta hanyar hidayat** (shiriya). **Idan kuka ambace ni ta hanyar gaskiya da tsoron Allah, Zan ambace ku ta hanyar khalas da najat** [tsira] **Idan kuka ambace ni da Fatiha-i-sherifa da rububiyar da ke cikin Fatiha-i-sherifa, Ni kuma zan ambace ku da Rahamata.**

Har ila yau malaman Musulunci sun bayyana amfanin zikiri kimanin guda ɗari. Za a zayyano wasu daga cikinsu:

Idan Musulmi suka yi zikiri, Allâhu ta’âlâ zai yi farin ciki da shi. Shedân zai yi baƙin ciki. Zukatan waɗannan bayi za ta yi haske da sauƙi. Za su riƙayin ibada cikin son rai da farin ciki. Zikirin zai yaye baƙin ciki daga zukatansu, su zamo masu annushuwa ya sa masu hasken fuska. Za su zamo jarumai su kuma samu Muhabbatullah (ƙaunar Allah). Za a buɗe masu ƙofar ma’rifatullah, sai su samu fayz (faydh) daga Waliyyai. Za a ƙawata su da akhlaƙ-i-hamida (kyawawan ɗabi’u).

“**Ash-hadu anna Muhammadan ‘abduhu wa Rasuluh.**” Ma’anar wanan zancen ita ce: Annabi Muhammad Mustafa ‘sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’ shi ne Annabin wannan zamanin, shi bawa ne kuma Manzon Allahu ‘adhim-ush-shan ne.

Yana cin abinci yana shan abin sha kuma ya auri mata. Ya haifi ‘ya’ya maza da mata, dukkansu Nana Khadija ‘radiyallâhu’anhâ’ ita ta haifesu , ban da Ibrahim wanda Mariya ta Haifa. Kuma ya rasu yana ƙarami. Dukkan ‘ya’yansa ban da Nana Fadîma ‘Allah ya yarda da ita’ sun rasu kafin rasuwarsa ‘sallallâhu ta’âlâ’ alaihi wa sallam’. Ya aurar da ita ga sayyidina Aliyu ‘Allah ya yarda da shi’. Sayyadina Hassan da Husain ‘ya’yan

Sayyadina Aliyu da Nana Fadîma ne‘radiyallâhu ‘anhum’ . A cikin dukkan ‘ya’yansa mata Nana Fadîma ta fi girman daraja. Ita Annabi ‘sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’ ya fi so.

Rasulullah ‘sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’ ya auri mata goma sha dàya, su ne: Nana Khadija da Sawda da Aisha da Hafsa da Ummi-Salama, da Umm-i-Habiba sai Zaynab bint-i-Jahsh da Zaynab bint-i-Huzayma da Maimuna da Juwayriyya da kuma Safiyya ‘Allah ya‘radiyallâhu’anhunna’.

Adillatul shar’iyya ta hadà da Kitab (Alƙkur’ani) da Sunnah da Ijma’-i-Ummat da kuma Kiyas-i-mujtahid. Daga wadànnan hanyoyi guda hudù manyan Malaman Musulunci suka tattaro iliminsu. Zancen Allahu ‘adhim-ush-shan shi ake kira ‘Kitab (littafi)’. ‘Sunnat ita ce Kawl-i-Rasul (zancen Manzon Allah ‘sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’), da Fi’l-i-Rasul (ayyuka da halayen Mazon Allah ‘sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’), da Taƙrir-i-Rasul (Tabbatarwar da Amincewar Manzon Allah ‘sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’). Ijma’-i-Ummati shi ne ittifaƙi (hadùwar kai) na manyan Malamai Mujatahidai wadànda suka rayu ƙarni na dàya da Sahabbai ‘Allah ya yarda da su, ko Mazhabobi hudù da ake da su. Kiyas shi ne fahimtar Mujtahidai wajen kwatanta abubuwa biyu mabambanta domin fitar da hukunci.

Ma’anar kalmar Madhab ta asali ita ce hanya. Hanyoyin nan sun kasu kashi biyu: Ta farko ita ce hanyar i’tiƙad (imani), ta biyu kuma ita ce hanyar ‘amal (aikin ibada).

Imaminmu wato jagoranmu a hanyar i’tiƙad shi ne Abu Mansur Maturidi ‘Allah ya yi masa Rahama’. Ana kiran hanyar tasa **Ahl as-sunnat**. Jagoranmu a hanyar ‘amal (aikin ibada) shi ne Imam a’zam Abu Hanifa ‘Allah ya yi masa Rahama’. Hanyarsa ana kiranta **Mazhabar Hanafiyya**).

Sunan Abu Mansur Maturdi Muhammad sunan Mahaifinsa Muhammad sunan kakansa Muhammad, sunan malaminsa kuma Abu Nasr-i-Iyad ‘Allah ya yi masu Rahama’.

Sunan malamin Abu Nasr-i-Iyad, Abu Bakr-i-Jurjani wanda ya yi karatu a hannun Abu Sulaiman Jurjani shi kuma almajirin Abu Yusuf da Imam-i-Muhammad Shaybani su kuma almajiran Imam a’zam Abu Hanifa ne ‘Allah ya yi masa Rahama’. Shi Imam a’azam shi ne babban jagoranmu a Mazhab ta i’tiƙad da Mazhab ta ‘amal.

Dukkan Musulmi suna da imamai (jagorori) guda uku; wajibi ne a sansu. Jagoranmu wanda ya yi bayani game da hani da horo shi ne Alƙur’ani mai girma. Jagoranmu wanda ya sanar da mu game da su, shi ne Annabi Muhammad ‘sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’. Jagoranmu wadànda ke

bada himma domin ganin an ɗabbaƙa waɗannan dokoki sune shugabannin Musulunci da ake dasu a garuruwan musulmai waɗanda suke shugabanci bayan Manzon Allah ‘sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam

Malamin Imam a’zam shi ne Hammad, wanda shi kuma almajirin Ibrahim Nahai ne, shi kuma ya yi karatu a hannun ‘Alƙama bin Ƙais ne kuma kawunsa ne. shi kuma ‘Alƙama almajirin Abdullahi bin Mas’ud ne ‘Allah ya yarda da shi’ wanda samo iliminsa daga Manzon Allah ’sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’.

Shi Manzon Allah ’sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’, ya samo iliminsa ne daga Mala’ika Jibril ‘alaihis-salâm’ ne. Shi Mala’ika Jibril Allâhu ta’âlâ ne yake aiko shi.

Allahu ‘adhim-ush-shan ya yi wa ɗan adam wata baiwa guda huɗu, su ne: ‘Aƙl (hankali, tunani, kaifin basira) da Iman da Haya da Fi’l, wato ‘amal-i-salih (kyawawan ayyuka).

Za a karɓi Salloli da sauran ayyuka na ƙwarai bisa sharuɗɗa biyar, su ne: Iman da ‘Ilm da Niyyat da Khulus, wato ikhlas, guje wa take haƙƙin wani (waɗanda ake kira haƙƙin ƙuls.) Abu na farko shi ne mutum ya yi riƙo da aƙidar Ahl as-sunnat, ya san abubuwan da ya kamata ya cika domin gudanar da ingantacciyar ibada.

[Aikin ibada wanda yake ingantacce ya sha bamban da kuma dakarɓar ibadar. Ibada tana da sharuɗɗa da farillai (wato jam’in Fard/Farilla) da suka wajaba a cika su domin ibadar ta zamo sahih (inagantacciya, sahihiya). Idan aka bar ɗaya daga ciki, aikin ibadar bai inganta ba. Ya zamo daidai da ba a yi aikin ba gaba ɗaya, don haka mutum ba zai tsira daga azabar da za a yi wa waɗanda ba su yi aikin ibadar ba. Ba za a yi azaba ga wanda ibadarsa ta inganta ko da ba a karɓa ba. Sai dai mutum ba zai samu thawab (ladar) ibadar da ba a karɓa masa ba. Da farko sai ibada ta inganta sannan a karɓa; wato sai a cika waɗannan sharuɗɗan biyar da aka zayyana a baya, da suka ƙunshi har da haƙƙin ƙuls (wanda shi ma bayaninsa ya gabata).] Imam Rabbani ‘Allah ya yi masa rahama’ ya faɗa a cikin shafi na tamani da bakwai na mujalladi na biyu na littafinsa (mai suna **Maktubat**) [1]“Idan mutum ya yi ibada kamar yadda Annabi ’sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’ ya koyar, amma ya yi riƙo da haƙƙin ƙuls [komai ƙanƙantarsa] ba zai shiga Aljanna ba har sai ya mayar da shi.” [Ba za a karɓi addu’o’insa ba.]

[1] Wannan ƙasida tana cikin babi na goma sha biyar a mujalladi na uku na littafin **Endless Bliss.**

Ibn Hajar-i-Mekki ‘Allah ya yi masa rahama’ ya faɗa a cikin littafinsa **Zawajir**, sa’ilin da yake bayani game da saɓo na ɗari da tamanin da bakwai cewa: Aya ta ɗari da tamanin da takwas ta Suratul Baƙara tana cewa: “**Ya ku Muninai! Kada ku ci dukiyar ‘yan uwanku ta hanyar batil!**” Abin da ake nufi da hanyar (batil) ita ce yaudara ta hanyar riba da caca da ƙwace ko sata ko zalunci da cin amana da shedar zur (ƙarya) ko ha’inci. Wasu Hadissai sun bayyana cewa: “**Musulmin da ya ci halal ya aikata farillai ya guji haram kuma bai zalunci kowa ba, zai shiga Aljanna**” haka nan “**Duk wanda ya ci haram za a ƙona shi a wutar jahannama**” kuma “**Idan mutane ba su tsira daga sharri da zaluncin mutum ba, ba zai amfana da ladar tsoron Allah ko salloli ko zakkarsa ba**” kazalika “**Idan mutum ya sanya jilbab da ya samu ta hanyar haram, ba za a karɓi sallolinsa ba**.” [Jilbab na nufin ƙyallen da mata suke rufe kansu. Wani tufafin da ake kira Jilbab kuma shi ne babban ƙyallen da maza suke rufe jikinsu. Wasu kuma suna ganin cewa ‘jilbab’ shi ne fallen kyallaye biyu da mata suke rufe kai da su, Hadisin da ya zo a baya, yana nuna cewa maza ma suna amfani da irin wannan tufafin. Ta yiwu rashin ilimi ne ya sa suka yi tunanin hakan.] A Hadisin da ya kawo a littafinsa sa’ilin da yake bayanin saɓo na ɗari biyu ya ce: “**Duk mutumin da ya yi algushu ba ya cikinmu. Makomarsa wutar Jahannama**.” An kawo Hadisi a cikin bayani a kan saɓo na ɗari biyu da goma cewa: “**Wutar Jahannama ita ce makomar mutumin da ya zalunci maƙwabtansa da harshensa, ko da yana yawaita Sallah da Azumi da bayar da sadaka**.” Ko da maƙwabtansa kafirai ne haramun ne a cutar da su, ya taimake su, ya kuma yi masu kirki. An faɗa a cikin wani Hadisi a bayanin kan saɓo na ɗari uku da sha uku cewa: “**Mutumin da ya kashe kafiri bisa zalunci a lokacin da ake zaman lafiya, ba zai shiga Aljanna ba**.” Wani Hadisin kuma ya ce: “**Idan Musulmi biyu suka yi faɗa da juna saboda duniya, da wanda ya yi kisa da wanda aka kashe a tsakainsu duk za su shiga wuta**.” An ruwaito a cikin Hadisi, a bayanin saɓo na ɗari uku da sha bakwai cewa: “**Mutumin da ya zalunci al’umma da ƙeta, za a yi masa azaba a kai a ranar tashin Kiyama.**” Haka abin yake ko da kafiri ne aka zalunta. A cikin Hadisin da ya zo a bayanin saɓo na ɗari uku da hamsin ya ce: “**Akwai mutane uku da wajibi ne a karɓi addu’o’insu: mutumin da aka zalunta da baƙo da kuma iyaye.**” Wani hadisin kuma ya ce: “**Ana karɓar addu’ar wanda aka zalunta ko da ya zamo kafiri ne.**” A cikin Hadisin da ya zo a bayanin saɓo na ɗari huɗu da biyu ya ce: “**Mutumin da ya kashe abokinsa ba ya cikinmu, ko da abokin nasa kafiri ne.**” Haka nan ya zo a cikin Hadisin da ke bayanin saɓo na ɗari huɗu da tara cewa: “**Daga cikin zanubai, yin tawaye ga gwamnati yana daga cikin abin da za a gaggauta yi wa mutum azaba a kai**.” Nan ne muka kawo ƙarshen fassarar littafin **Zawajir**. Ya ku al’ummar Musulmi! Idan kuna son samun albarkar Allâhu ta’âlâ, kuma a

karɓi ibadunku, ku yi riƙo da Hadissan da aka kawo a sama a zukatanku! Kada ku kai hari ga dukiya ko rayuwa mutuncin wani. Na Musulmi da na kafiri baki ɗaya! Kar ku cuci kowa! Ku bai wa kowa haƙƙinsa! Yana daga cikin haƙƙin ƙuls ga namiji ya biya 'mahr'[1] (kyauta) ga macen da ya saki. Idan bai bayar ba zai fuskanci azaba a duniya da lahira. Wani haƙƙi mai muhimmanci a cikin haƙƙin ƙuls (haƙƙin wata halitta a kan wata) wanda za a iya yi wa bawa azaba saboda shi, shi ne ƙin bai wa mutanen da ke kusa da kai ilimi, musamman ma waɗanda suke ƙarƙashin iko da kulawarsa. Idan mutum ya hana su tare da wasu mutane samun ilimin addinin Musulunci da hana su aikata ibada ta hanyar zalunci ko yaudara, wannan mutumin ya tabbata kafiri, maƙiyin Musulunci. Misalin irin wannan shi ne ƙoƙarin gurɓata koyarwar Ahl as-sunnat, wanda zai haddasa gurɓata Musulunci, wata hanya da 'yan bidi'a da mutanen da ba su da Mazhaba, suna maganganun ɓatanci da rubuta ƙasidu na tawaye. Kada mutum ya yi fito na fito da gwamnati ko dokoki. Mutane su biya haraji. Saboda laifi ne yi wa gwamnati tawaye, ko da azzaluma ce ko fasiƙar gwamnati. An kawo a cikin littafin '**Bariƙa**' (wanda Muhammad bin Mustafa Hadimi 'Allah ya yi masa rahama' ya rubuta: 1176 hijiriyya [1762 miladiyya], daga garin Hadim, Konya, Turkey.) Ko da ana cikin dar-ul-harb, wato garin kafirci, kada ka karya dokoki da sharuɗɗansu! Kada ka tada fitina! Kar ka yi abota da mutanen da suke sukar musulunci, da 'yan bidi'a ko mutanen da ba sa cikin Mazhabobin nan guda huɗu! Kar ka karanta litattafai ko labaransu! Kar ka bari shirye-shiryensu na rediyo da talabijin su shiga gidajenku! Ku yi **Amr-i-ma'ruf**, (wato ka yi koyi da koyarwar Musulunci) ga mutane da za su saurare ka! A wani ƙaulin, ka ba su shawara, ka yi masu murmushi da kalamai masu daɗi! Da nuna masu kyakkyawar ɗabi'a, ku nuna kyawawan halaye da mutuntaka na Musulunci ga dukkan mutanen da suke tare da ku!

Ibn 'Abidin[2] 'Allahu te`ala ya yi masa rahama' ya faɗa a cikin mujalladi na farko na littafin seɓ'eteyn (ko Saw'atayn), wato gaɓoɓin

[1] A duba babi na goma sha biyu a mujalladi na biyar sannan da kuma babi na goma sha biyar a mujalladi na shida na littafin **Endless Bliss.**

[2] Masanin Ilimin Fiƙhu, wanda cikakken sunan sa shine Sayyid Muhammad Emîn bin 'Umar bin 'Abd-ul-'Azîz (1198 [1784 A.D.], Damascus – 1252 [1836],nawuri ɗaya Shi ya rubata littafi mai mujalladi biyar mai suna Radd-ulmuhtâr wanda yake shi ɗin sharhin littafin Durr-ul-mukhtâr,wanda 'Alâ-ud-dîn Haskafî 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' (1021, Haskaf – 1088 [1677]). Ya rubuta shi mafi yawancin maganganun fiƙhu wanda ya shafe babi ɗari da talatin a mujalladi na shida na littafin Endless Bliss,an cirato sune daga littafin Radd-ul-muhtâr.

al'aura, kumadukkan Mazhabobi[1] hudu suka kira ghalidh (ƙaba) awrat. Farilla ne a dukkan Mazhabobi hudu mutum ya rufe al'aurarsa.

Duk mutumin da bai damu da rufe ta ba, to hakan kwaikwayo ne da kafirai. Mutumin da ya bayyana guiwarsa, a bashi shawar, a yi masa Amr-i-ma'ruf ya rufe guiwarsa. Ana yin Amr-i-ma'aruf ne da kalmomi masu taushi. Idan ya bijire sai a ƙyale shi. Wanda ya bayyana cinyoyisa kuma ya bijire wa nasiha sai a hadà shi da hukuma. Idan mutum ya bayyana al'aurarsa, kuma ya bijire wa nasiha, sai a gurfanar da shi a gaban kotu domin ta wajabta mashi ya rufe su [ta hanyar horo ko kulle shi gidan yari]. Wannan ya shafi har ga wadànda suke kallon al'aurar wasu." Wajibi ne a dukkan Mazhabobi hudu ga mata su siturta dukkan jikinsu ban da tafukan hannuwa da fuskokinsu ga wadànda ba muharramanta ba, da mata wadànda ba musulmi ba, haka na nufin za su rufe ƙafafunsu da hannuwansu (zuwa wuyan hannu) da gashinsu a gaban wadànnan mutanen (wato mazan da ba muharramasu ba, da mata wadànda ba musulmi ba.) (An yi bayanin mutanen da ba muharramai ba na kowane jinsi a cikin babi na goma sha biyu na mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss**.) A cikin Mazhabin Imam Shafi'i an ce wajibi ne kar su bayyana fuskokinsu (ga wadàncan mutanen). Idan iyaye da maza da mazajen aure ba su bayar da muhimmanci a kan haka ba, za su iya zamowa kafirai. Babban zunubi ne yara maza su yi rawa ko wasanni da ƙwabrinsu ko ƙafafunsu a budè, haka nan yara mata su bar kansu da hannuwansu a budè, da kuma kallonsu suna yin hakan. Kar Musulmi ya ɓata lokacinsa wajen wasanni ko abubuwa marasa amfani, su yi amfani da lokacin wajen koyon ilimi da yin salloli. An ruwaito a cikin **Kimiya-i-sa'adat**: "Haramun ne ga mace da yara mata su fita waje alhali kansu da hannuwa da ƙafafunsu a budè, haka nan haramun ne su saka matsattsen wando da adon sarƙa da awarwaro da matsattsun riguna da sanya turare mai ƙamshi. Iyaye da mazan aure da 'yan uwansu maza suka ɗaure masu gindi a kan abin da suke yi sun zamo abokan tarayyarsu a aikata saɓo za a yi masu azaba." A wani ƙaulin, za a ƙona su a wutar Jahannama a gobe ƙiyama. Idan suka tuba, za a gafarta masu, kuma ba za a ƙona su ba. Allâhu ta'âlâ yana son mutane masu tuba.

MATAN ANNABI MASU ALBARAKA DA KUMA YAKE-YAKEN SA

Manzon Allah 'sallalahu 'alaihi wa sallam' yana ɗan shekaru arba'in Mala'ika Jibrilu ya zo mashi ya shaida mashi cewa shi Annabi ne. bayan

[1] A duba babi na takwas a mujalladi na hudu nalittafin **Endless Bliss.**

shekaru uku, ya bayyana Annabtarsa a Makka. A wannan shekarar ana kiranta shekarar **Bi'that**. Ya yi jihadi (yaƙin na Musuluci) sau ishirin da bakwai. Ya yi guda tara daga cikin yaƙe-yaƙen a matsayin mayaƙi. Yayin da ya yi yaƙe-yaƙe goma sha takwas a matsayin shugaba. Ya haifi 'ya'ya maza huɗu da mata huɗu, ya auri mata goma sha ɗaya, yana da 'yan uwan mahaifinsa maza su goma sha biyu ne mata kuma su shida. Yana ɗan shekara ishirin da biyar ya yi **nikah** (aure) da Nana Khadijat-ul-kubra. Shekara ɗaya bayan rasuwar Nana Khadija, yana ɗan shekaru hamsin ya auri Nana Aisha 'yar sayyidina Abubakar 'Allah ya yarda da shi' kamar yadda Allâhu ta'âlâ ya umarce shi. Yana ɗan shekaru sittin da uku kuma Allah ya karɓi ransa a cikin ɗɗakinta wanda ke gab da Masallaci (Masjid ko a taƙaice, daga Masjid-i-Nabi ko Masjid-i-Nabi). An yi masa ƙabari a nan cikin ɗakin, kuma a nan aka binne Sayyidina Abubakar da Umar 'radiyallâhu 'anhum'. Bayan ƙara faɗaɗa masallacin, sai ɗakin ya shiga cikin masallacin. A shekarar hijira (Hegira) ta bakwai ya auri Umm-i-Habiba, wadda ɗiya ce ga Abu Sufyan bin Harb, wanda ya shugabanci Kuraishawan Makka kafin ya Musulunta. Abu Sufyan shi ne mahaifin Mu'awuyya 'Allah ya yarda da shi'. Ya musulunta ne bayan an buɗe Makka. Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' ya auri Hafsa wadda ɗiyar Sayyidina Umar ce 'radiyallâhu 'anh''. A shekara ta biyar bayan hijira (Hijrat), ya sayi Juwayriyya, wadda tana ɗaya daga cikin bayi da aka kamo daga ƙabilar Bani Mustalaƙ (a yaƙin **Mureysi**), kuma ɗiyar sarkinsu ce. Ya 'yanta ta sannan ya aure ta (wato ya aure ta bisa tsarin aure na Musulunci wanda ake kira nikah wanda aka yi cikakken bayani a kai a cikin babi na sha biyu, mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss.**) Bisa dalilai na addini ya auri Umm-Salama da Sauda da Zainab bint Huzaima, da Maimuna da Safiyya 'Allah ya yarda da su'. Ita Zainab ɗiyar baffansa ce; Allâhu ta'âlâ ne ya ɗaura masu aure.

Mala'ika Jibril 'alaihis-salâm' ya zo wajen Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' sau dubu ishirin da huɗu. Yana ɗan shekaru hamsin da biyu aka ɗauke shi zuwa sama (a wani al'amari da ake kira) Mi'raj[1]. Yana shekaru hamsin da uku ya yi hijira daga Makka zuwa Madina, (a wani al'amari da ake kira Hijrat ko Hegira.) Shi 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' da sayyidina Abubakar suka shiga wani kogo a tsaunin Saw'r suka zauna a ciki tsawon kwanaki uku, suka bar kogon a cikin daren Litinin. Bayan sun shafe mako guda suna tafiya, suka isa garin Kuba, wani ƙauyen Madina, a ranar ishirin ga watan Satumba; ranar Litinin, sai a ranar Jumu'a suka shiga Madina.

---

[1] Akwai cikakken bayani akan Mi'râj a babi na sittin a mujalladi na uku na littafin **Endless Bliss.**

An yi yaƙin Badar (Bedr ko Badr) a shekara ta biyu bayan hijira, a ranar Litinin cikin watan Ramadan. Tsakanin sojojin Musulmi ɗari uku da sha uku waɗanda takwas daga ciki sun je aiki a wani wuri, da sojojin ƙuraishawa dubu ɗaya. Sahabbai sha uku suka yi shahada a yaƙin. Yayin da aka kashe Abu Jahl da wasu kafirai guda saba'in.

An yi yaƙin Uhudu ('Uhud) a cikin watan Shawwal a shekara ta uku bayan Hijira. Sojojin Musulunci guda ɗari bakwai suka fafata da dakarun sojojin kafirai dubu uku. Sahabbai saba'in suka yi shahada. Watanni huɗu bayan yaƙin uhudu, aka aika da sahabbai matasa guda saba'in zuwa ga mazauna Najd domin su kira su zuwa Musulunci. Lokacin da suka isa wani wuri da ake kira **Bi'ri Me'una**, sai aka yi masu kwanton ɓauna, inda sahabbai biyu kaɗai suka tsira, sauran kuma suka yi shahada.

A shekara ta biyar bayan Hijira aka yi yaƙin Hendek (Handaƙ [Ganuwa]). Tsakanin sojojin kafirai dubu goma, da Musulmai dubu uku. Kafirai suka kewaye Madina. A lokacin Musulmi sun riga sun gina ganuwa suka zagaye garin Madina da ita. Shekara ɗaya kafin yaƙin Hayber (Haibar), wanda aka yi a shekara ta bakwai bayan Hijira, an ƙulla wata yarjejeniya da ake kira **Bi'at-ur-ridwan** a wani wuri da ake kira Hudeybiyya. Yaƙin Muta jihadi ne da aka yi shi da sarkin Romawa Hereƙla (Byzantine Caeser Heraclius). Sojoin Musulmi dubu uku ne suka fafata da sojoji dubu ɗari na Romawa. A wannan yaƙin ne Ja'far Tayyar 'radiyallâhu 'anh' ya yi shahada. Khalid bin Walid ne ya ci wannan yaƙin. An buɗe Makka ne a shekara ta takwas bayan hijira.

Yaƙin **Huneyn** (Hunaini) shahararren yaƙi ne, kuma Musulmi ne suka yi nasara.**Heyber** wani mashahurin yaƙi ne na Yahudawa, Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' ya tura sayyidina Ali 'Allah ya yarda da shi' ya ciwo yankin. A wannan wurin ne aka bai wa Annabi 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' abinci mai guba, wanda ya ƙi ci. A kan hanyarsu ta komawa gida ne daga yaƙi aka yi wa Nana Aisha ƙage, wanda ya sanya Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' cikin damuwa. An saukar da Ayar Alƙur'ani wadda ta tabbatar da cewa ƙagen tsagwaron ƙarya ce. Haka nan nasarar da aka samu a yaƙin Taif (Ɗa'ifa).

Idan kana son farin ciki, ya kai wannan ɗan saurayi,
Ka yi riko matuƙa ga Musulunci,ya kai ɗana, ba ƙaƙƙautawa.

Su ne farillai, wajibai, sunnoni da mustahabbai,
Haka nan ka yi amr-i-bi-l-ma'ruf kodayashe.

Ka aikata su kullum, kar ka bar ko ɗaya,
Manya da ƙananan su gaba ɗaya, yadda ya dace.

Kai! Dole ne ka ƙaurace wa makaruhi da haram,
Haƙƙin mutane a guje shi nesa ba kusa ba.

Ka yi koyi da karantarwar Ahl as-sunnat kai tsaye!
Ka yi aiki da abin da ka koya, nan take!

BAYANAI DA SUKA SHAFI IMANI

Akwai bayanai goma sha biyu da suka shafi imani: Ubangijina shi ne Allâhu ta'âlâ. Hujjata a nassi ita ce aya ta ɗari da sittin da uku ta suratul Baƙara. Annabina shi ne Muhammad 'alaihi-s-salam'. Hujjata a nassi ita ce ayoyi na ishirin da takwas da ishirin da tara na suratul Fat-h addinina shi ne Musulunci. Hujjata a nassi ita ce faɗar Allâhu ta'âlâ a aya ta goma sha tara ta suratu Al-i-'Imran. Littafina shi ne Alƙur'ani mai girma. Hujjata a nassi ita ce aya ta biyu ta suratul Baƙara. Ka'aba ita ce alƙiblata. Hujjata a nassi ita ce aya ta ɗari da arba'in da huɗu ta suratul Baƙara.

Mazhabata a i'tiƙad (iman) ita ce aƙidar **Ahl as-Sunnat wa-l-jama'at**. Hujjata a nassi ita ce aya ta ɗari da hamsin da uku ta suratul An'am.

Asalina (tsatsona) shi ne Annabi Adamu AS. Hujjata a nassi ita ce aya ta ɗari da saba'in da biyu ta suratul A'raf.

Millatina shi ne Millatil-Islam. Hujjata a nassi ita ce aya ta saba'in da takwas ta suratul Hajj.

Ina cikin al'ummar Annabi Muhammad 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam'. Hujjata a nassi ita ce aya ta ɗari da goma ta suratul Al-i-Imran.

Ni Mu'min (Mumini) ne, haƙƙan (da gaskiya). Hujjata a nassi ita ce aya ta huɗu ta suratul Anfal. Al-hamdu lillahi 'ala-t-tawfiƙihi wa-s-tagfirullaha min kulli taƙsirin.

Ilimi na sama da aiki bisa dalilai guda biyar: Ilimi ana dogaro da shi ne, yayin da aiki yake dogara gare shi. Ilimi wajibi ne, yayin da aiki ba ya iya rabuwa da shi. Ana amfana da ilimi shi kaɗai, yayin da aiki ba ya amfanarwa sai da ilimi.

Ilimi yana sama da hankali ('aƙl), domin shi yana dawwama, yayin da hankali yake gushewa.

Ƙawa/ado (zînat) ga mutum ya tsayu da ikhlas. Ado ga ikhlasi yana zama tare da imani. Adon imani yana kaiwa ga shiga Aljanna (Jannat). Adon Aljanna yana tare da huris da ghilmans, da ganin zatin Allâhu ta'âlâ, (wato ganin Allâhu ta'âlâ a wani yanayi da ba shi misaltuwa ko bayyanuwa).

Idan 'aiki ɓangare ne na imani, da ba a ɗauke wa mace mai al'ada (haila) salloli ba, domin shi imani ba a ɗauke shi.

Farilla ne mutum ya furta kalmar shahada, aƙalla sau ɗaya a rayuwar mutum. Hujjar haka a nassi ita ce aya ta goma sha tara ta suratul Muhammad.

Akwai sharuɗɗa guda huɗu da ya kamata mutum ya cika yayin furta kalmar shahada: ƙudurcewa a zuciya a lokacin da harshe yake furtawa. Sanin ma'anarta. ɗFaɗarta da gasgatawa. Faɗarta da ta'dhim (girmamawa).

Sannan akwai falala guda ɗari da talatin game da furta kalmar shahada. Sai dai samuwar wasu abubuwa huɗu za su iya ruguza dukkan wannan falalar. Waɗannan abubuwa su ne: Shirk, shek, teshbih da ta'til. Shirk na nufin haɗa Allâhu ta'âlâ da wani wajen bauta. Shek na nufin meks (dakatarwa, tsaidawa, ko kokwanto) a cikin addini. Teshbih na nufin kamanta Allâhu ta'âlâ da wani abu a cikin halittu. Ta'til kuma na nufin (mutum ya amince cewa) ko faɗar cewa Allah ba shi da hannu a samuwar halittu, suna samuwa ne kawai idan lokacin samuwarsu ya yi.

Za a kawo talatin daga cikin falalar kalmar shahada ɗari da talatin a cikin littafin nan. Ga talatin daga falalar, waɗanda biyar ana samunsu a duniya, biyar a lokacin mutuwa, sai biyar a cikin ƙabari da biyar a wani wuri da ake kira Arasat, sai kuma biyar a wutar jahannama da sauran biyar a cikin Aljanna.

Falala biyar da ake samu a duniya su ne:

1- Za a riƙa kiran sunan mutum cikin ƙyakkyawan lafazi.

2- Hukunce-hukuncen musulunci za su zama jiki ga mutum (farilla).

3- Za a kare wuyan mutum daga kaifin takobi.

4- Allahu 'adhim-us-shan zai yi farin ciki da mutum.

5- Dukkan Musulmi za su ƙaunaci mutum.

Falala biyar a lokacin mutuwa su ne:

1- Azra'ilu 'alaihis-salâm' (mala'ikan mutuwa) zai zo wa mutum cikin siffa mai kyau.

2- Mala'ikan zai zare ran mutum cikin sauƙi, kamar yadda ake zare gashi a cikin ɗanyen man shanu.

3- Mutum zai ji ƙamshin Aljanna.

4- Za a ɗaukaka ran mutum zuwa Illiyyin (Aljanna maɗaukakiya), kuma mala'ikun rahama za su zo wurin ɗaukar ran.

5- Wata murya za ta ce Marhaba (barka da zuwa) ya kai Mumini, kai ɗan Aljanna ne.

Falala biyar a cikin ƙabari su ne:

1- Za a yalwata ƙabarinsa.

2- Matambaya, wato mala'iku Munkar da Nakir za su zo wa mutum cikin siffa mai kyau.

3- Wani Mala'ika zai sanar da mutum abin da bai sani ba.

4- Allahu 'adhim-us-shan zai fahimtar da mutum abin da bai sani ba.

5- Mutum zai ga masaukinsa a gidan Aljanna.

Falala biyar a Arasat su ne:

1- Za a sauƙaƙa wa mutum amsa tambayoyi.

2- Za a bai wa mutum littafinsa na sakamako (abin da mutum ya aikata da wanda ya faɗa a duniya) da hannun dama.

3- Ladar mutum za ta rinjaya a cikin sikeli.

4- Mutum zai shiga ƙarƙashin inuwar Al'arshi.

5- Mutum zai tsallake siraɗi kamar walƙiya.

Falalar biyar ta wutar Jahannama su ne:

1- Idan mutum ya shiga wuta, idanunsa ba za su sauya zuwa launin irin na sauran 'yan wuta ba.

2- Mutum ba zai yi jayayya da shaiɗaninsa ba.

3- Ba za a ɗaure hannuwan mutum da sarƙoƙin wuta ba, haka nan ba za a rataya masa ita a wuyansa ba.

4- Ba za a shayar da mutum ruwan Hamin ba (ruwa masu azabar zafi).

5- Mutum ba zai dawwama a wuta ba.

Falala biyar a gidan Aljanna su ne:

1- Dukkan mala'iku za su gaishe shi.

2- Mutum zai yi abota da Siddiƙai.

3- Mutum zai dawwama a cikin Aljanna.

4- Allâhu ta'âlâ zai yi farin ciki da mutum

5- Mutum zai samu mafi ƙƙololuwar daraja ta gani zatin Allâhu ta'âlâ.

[Kadi-zada Ahmad Efendi (1133-1197 hijiriyya [1783 milladiyya.]) ya faɗa a **sharh of Amantu** mai suna **Faraid-ul-Fawaid** cewa: an halicci wuta

shimfiɗa bakwai, ɗaya saman ɗaya. Raɗaɗin kowace shimfiɗar wuta ta fi wadda take samanta. Musulmi da suke da zunubin da ba a yafe masu ba, za a yi masu azaba a shimfiɗa ta farko ta wuta, gwargwadon laifin da suka aikata; sai a fitar da su daga wutar a shigar da su Aljanna. Sauran shimfiɗar guda shida, za a yi wa kafirai daban-daban azaba da su. Munafukai za a yi wa azaba da shiɗar wuta ta bakwai, wadda ta fi kowace raɗaɗi. Sune Musulmai masu fuska biyu, waɗanda suke bayyana son Musulunci, suke ƙinsa a zuciya. Idan aka ƙona kafirai suka zama toka, za a sake masu sabuwar halitta a sake ƙona su, za a cigaba da yi masu haka har abada. Aljanna da Wutar Jahannama suna nan yanzu haka. Wasu manyan Malamai sun ce babu wanda ya san inda wuta take. Wasu kuma suka ce tana ƙarƙashin ƙasa ta bakwai. Wannan batun nasu ya nuna cewa ba ta bisa doron ƙasa. Domin ƙasa da rana da taurari suna tsakanin sama ta ɗaya ne, don haka akwai yanki na lahira a ƙarƙashin ƙasa. Ke nan wuta tana ɗaya daga cikin ƙassai bakwai.]

DALILAN DA KE HADDASA KAFIRCI (KUFR)

Akwai nau'in kafirci [wato ƙin Allah] guda uku: Kufr-i-inadi, da kufr-i- jahli da kufr-i-hukmi.

Kufr-i-inadi shi ne mutum ya bijire da kangare wa Musulunci da imani da gangan, misali: kafircin irin su Abu Jahl, da Fir'auna, da Lamarudu da (Shaddad bin Ad). Babu laifi idan aka kira su 'yan wuta kai tsaye.

Kufr-i-jahli: Idan kafiri a cikin al'umma ya san cewa Musulunci shi ne gaskiya, kuma ya ji da'awar Annabi Muhammad, kuma aka ce masu "Ku zo ku shiga Musulunci," sai su ce "Hanyar rayuwarmu ita ce wadda muka gada daga iyaye da kakanninmu, kuma a haka zamu cigaba".

Kufr-i-hukmi shi ne tahƙir (wulaƙantarwa) maimakon ta'dhim (mutuntawa) da ta'dhim mimakon tahƙir.

Haka nan kafirci ne wulaƙanta waliyyai da Annabawan Allahu 'adhim-us-shan da manyan malamai da maganganunsu a cikin litattafan Fiƙihu (Fiƙh) da Fatawa (Fatwa) maimakon mutunta su. Kazalika kafirci ne ƙaunar addinin kafirai da sanya zunnar (situra irin ta jagororin kafirai) ba tare da lalura ba, da sanya alamar gicciyewa ta (Cross).

Kafirci yana kawo illoli guda guda bakwai: Yana ɓata imani da aure. Ba za a ci yankan dabbobinsu ba (ko da ya yi yanka irin na Musulunci). Duk abin da ya yi da halaliyarsa ya zama saɓo. Ya zama wajibi a kashe shi. Aljanna ta nisanta a gare shi. Ya yi kusa da shiga wuta. Idan ya mutu a wannan hali na kafirci, ba za a yi masa sallar janaza ba.

Idan mutum ya faɗa a cikin son ransa cewa “Wane da wane suna da (ko ba su da) kaza da kaza. Na zama kafiri idan na yi kuskure,” to wannan mutum ya yi rantsuwar da za ta iya jefa shi cikin kafirci, ko da abin da ya yi ikirari ya tabbata ko akasin haka. Tajdid (sabuntawa) ta imani da aurensa ta wajaba gare shi.

Wani aikin na kafirci kuma shi ne misali ka yi fatan wani abu da Musulunci ya haramta irin su fasiƙanci da riba da ƙarya su zamo halal don ka aikata shi.

Idan misali mutum ya ce “Na yi imani da Annabi Muhammad ’sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’, amma ba ni tabbacin Annabi Adam ‘alaihis-salâm’ Annabi ne.” ya zama kafiri. Mutumin da bai san cewa Annabi Muhammad ’sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’ shi ne Annabin ƙarshe ba, ta ya zama kafiri.

Kamar yadda Malamai suka ambato: idan mutum ya ce: “Idan abin da Annabi Muhammad ’sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’ ya faɗa gaskiya ne, to mu mun tsira.” To ya zama kafiri. Birgiɓi ‘rahmatullâhi ’alaih’ ya ce “Idan mutum ya faɗi haka ta fuskar kokwanto, to ya zama kafiri. Amma bai zama kafiri ba idan ya faɗi haka da nufin ilzam (tabbatar da zance)”.

An ruwaito (Malaman Musulunci) suna cewa idan aka kira mutum domin yin sallar farilla cikin jam’i ya ce ba zai yi ba, ya zama kafiri. Amma bai zamo kafiri ba idan yana nufin ba zai yi sallar saboda gayyatarsa da suka yi ba, zai yi ta ne saboda Allah.

Idan jama’a suka ce da wani mutum: “Kada ka yanke gemunka ƙasa da kamu guda, ko kamar karamin kamu guda, ko ya yanke akaifarsa, saboda Sunnah ce ta Annabi ’sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’,” sai wannan mutumin ya ce, “Ba zan yi abin da kuka ce ba,” ya zama kafiri. Wannan ya shafi dukkan ayyuka na Sunnah, idan dai har an tabbatar da shi ta hanyar tawatur cewa wannan aikin Sunnah ne, misali: yin asiwaki (kafin mutum ya fara alwala). Hadrat Birgiɓi[1] ya yi ƙarin haske game da wannan batun:

“Kafirci ne idan ya faɗi haka bisa ƙudirin kore aikin Sunnah. Amma bai zama kafirci ba idan yana nufin: ba zai yi abin da suka faɗa ba saboda faɗarsu. Sai dai saboda Sunnar Manzon Allah ’sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’ ce.”

[Yusuf Kardawi ya ruwaito a cikin shafi na tamanin da ɗaya na mujalladi na huɗu na littafinsa mai suna **Al-halal wa-l-haram fi-l-islam:** a

[1] Zeyn-ud-dîn Muhammad Birgiɓî Efendi ‘rahmatullâhi ta’âlâ ’alaih’(928 [1521 A.D.], Balıkesir – 981 [1573], Birgi, ya rasu daga annoba.

cikin Hadisin da ya cirato daga littafin **Bukhari-i-sherif** (ko **Jami-i-Sahih**) [1] ya ce "**Ku saɓa wa mushirikai wajen aiki! Ku tsaida gemunku ku yanke gashin baki!**"] Wannan Hadisin ya hana aske gemu ko rage shi ya gaza kamu ɗaya. Masu bautar wuta suna rage gemunsu. Maganar gaskiya ma wasu daga ciki suna aske shi duka ne. Wannan Hadisi yana umartar mu a kan mu saɓa masu. Wasu Malaman Fiƙihu sun ce, wannan Hadisin yana nuna cewa wajibi ne a tsaida gemu, kuma haramun ne a aske shi. Ɗaya daga cikinsu mai suna Ibn Taymiyya, ya tsoratar sosai game da aske gemu. Wasu malaman kuma sun ce, tsaida gemu al'ada ce ba addini ba. A cikin littafin Fat-h an ruwaito Iyad yana cewa Makruhi ne aske gemu [ba tare da uziri ba]. Wannan shi ne gaskiyar zance. Wannan Hadisin ba ya nuna wajabcin tsaida gemu. Domin ya zo a Hadisi cewa: "**Yahudawa da Nasara ba sa rina gashinsu** [gashinsu da gemunsu] **ku saɓa masu a kan abin da suke yi!**" Haka nan hadisin da yake cewa a rina gashin kai da gemu ba ya nuna wajibi ne a rina gashin kai ko gemu. Yana nuna mustahabbancin yin haka ne. Sahabbai da yawa suna rina gashi da gemunsu. Mafi yawa daga cikin Sahabban kuma ba sa yin haka. Idan da wajibi ne da dukkansu sun aikata hakan. To haka abin yake a Hadisin tsaida gemu, ba yana nuna wajibi ne a tsaida gemu ba. Ba ruwaito wani daga cikin Malamai magabata suna aske gemunsa ba. Domin a wancan zamanin tsaida gemu al'adar al'umma ce. [Kaurin suna ga mutum ya saɓa wa al'adun al'ummar Musulmi. Makaruhi ne. Haramun ne mutum ya yi abin da zai tada fitina.] A nan muka kawo ƙarshen fassarar daga littafin Kardawi. A cikin gabatarwar wannan littafin, Kardawi ya rubuta cewa ya gwamutsa Fiƙihun dukkan Mazhabobi hudu, da kuma cewa ba adalci ba ne mutum ya tsaya ga Mazhaba guda ɗaya tak. Don haka ya saɓa da hanyar da Malaman Ahl as-sunnat 'Allah ya yi masu rahama' suka tsara. Malaman na Ahl as-sunnat sun ce wajibi ne ga Musulmi ya bi koyarwar Mazhaba ɗaya, mutumin da ya gwamutsa Mazhabobi zai zamo la-Mazhabi (marar Mazhaba) kuma Zindiƙi. Sai dai wancan zancen da Kardawi ya rubuta game da tsaida gemu yayi daidai da Mazhabar Imam Hanafi inda za kafa wa mai karatu hujja daga Mazhabar. Hadrat 'Abd-ul-Haƙƙ-i-Dahlawi 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' (958 [1551 milladiyya] – 1052 [1642], Delhi) ya bayyana a cikin mujalladi na uku na littafin **Eshi'at-ul-leme'at** cewa: "Malaman Musulunci suna bin al'adun al'umma da suke zaune a cikinsu a kan abin da ya shafi rina gashin kai da gemu. Saboda ƙin bin al'adun al'umma yana jawo fitina [a kan al'amurran da suke mustahabbi ne], wanda hakan makaruhi ne." Muhammad bin Mustafa Hadimi 'Allah ya yi masa Rahama (d. 1176 [1762 milladiyya],

[1] Wanda ya tattara bayanan shine, Muhammad bin Ismâ'îl Bukhârî 'rahmatullâhi ta'âlâ'alaih' (194 [810 A.D.], Bukhâra – 256 [870], a garin Samarkand).

Hadim, Konya, Turkiyya) ya faɗa a cikin littafinsa mai suna **Beriƙa** cewa: "An ruwato a wani Hadisi cewa: '**Ku rage gashin baki, ku tsaida gemu ya yi tsawo**' don haka an hana mutum ya aske gemunsa ko ya rage shi ƙasa da kamu ɗaya. Sunnah ne mutum ya tsaida gemu har ya kai kamu ɗaya. Haka nan Sunnah ne a rage shi idan tsawonsa ya wuce kamu ɗaya." Kamu ɗaya shi ne faɗin yatsun hannu idan aka damƙi gemu da su tun daga ƙarƙashin leɓen ƙasa na baki. Idan Sarkin Musulunci ya yi umarnni da abin da yake Sunnah, ko mustahabbi ne, daga lokacin ya zama wajibi a yi shi. Sarkin zai yi kuma sauran Musulmi ma haka. A irin wannan wurin wajibi ne a tsaida gemu gwargwadon kamun hannu ɗaya. Rage gemu ƙasa da kamu ɗaya ko aske shi gaba ɗaya, yana nufin watsi da aiki wanda yake wajibi. Makaruhi ne yin hakan (A duba babi na gaba domin sanin ma'anar kalmomi irin su wajib da makruh da sauransu). Bai halatta ba ga wanda ya aikata haka ya zamo limami a masallaci (ko a sallar Juma'a). A Dar-ul-harb, wajibi ne mutum ya aske gemu ko a hukunta shi, ko kuma ya rasa aikinsa da ya dogara a kansa, don ya samu damar yin amr-i-ma'ruf, da yi wa Musulunci da Musulmi hidima, da kare mutuncin kai. Idan babu uzuri, makaruhi ne askewa ko rage gemu. Haka nan bidi'a ne mutum ya dawwamar da gemunsa ƙasa da kamu ɗaya, da kuma ka riƙa jin cewa kana aikin Sunnah. Hakan na nufin ka canza Sunnah. Aikata bidi'a ya fi laifin kisan kai muni.]

Idan mace ko namiji suka kai shekarun balaga, sai aka ɗaura masu aure, amma suka gaza wajen amsa tambayoyi game da shika-shikan imani, wannan ya nuna cewa su ba Musulmi ba ne. auren da ke tsakaninsu zai zama sahihi ne kaɗai bayan an koyar da su game da shika-shikan imani, daga nan sun sabunta aurensu. A duba babin da yake magana a kan farillai hamsin da huɗu (fards ko faraid).

Idan mutum ya aske gashin bakinsa, sai wani da suke tare ya ce masa "yin haka babu kyau" to ana tsoron wannan mutumin ya rasa imaninsa. Saboda Sunnah ne aske gashin baki, shi kuma wannan mutumin bai ɗauki aikin Sunnah da muhimmanci ba.

Idan mutum ya sanya tufafi na siliki, wanda ya rufe baki ɗayan jikinsa daga sama har ƙasa, sai wani mutum ya gan shi, ya ce masa "madalla da wannan tufafin," Ana masa tsoron ya rasa imaninsa.

Idan mutum ya aikata makaruhi, kamar miƙe ƙafafu su kalli Alƙibla, ko tofar da yawu ko fitsari yana fuskantar Alƙibla, idan jama'a suka jawo hankalinsa a kan ya daina aikata makaruhin "Ina fatan dama a ce dukkan zunuban mu su zamo ƙanana kamar wannan" Ana masa tsoron ya na iya rasa imaninsa. Saboda ya yi zance a kan aikata makaruhi kamar babu laifi a ciki.

Haka nan idan bawan mutum ya shigo ɗakin da ubangidansa yake, sai ya gaishe shi da sallama (ta hanyar cewa “As-Salaamu ‘alaikum” cikin girmamawa), sai wani da yake zaune a wurin ya ce ma bawan “Yi mana shiru, marar tarbiyya kawai! Ba haka a ke gaishe da iyayen gidanka ba,” wannan mutum ya na iya zama kafiri. Amma idan mutumin yana nufin ya koyar da bawan tarbiyya ne, cewa ya sassauta muryarsa a wajen gaisuwar, to zancensa bai zamo aikin kafirci ba.

Idan wasu suna zancen wani a bayan idonsa, sai wani ya goya masu baya, ya zama kafiri, kamar yadda Malamai suka ce. Domin ya goyi bayan aikata haram maimakon hanawa.

Idan mutum ya ce “Idan Allâhu ta’âlâ ya ba ni Aljanna ba zan shiga ba sai tare da kai,” ko ya ce “Idan aka ce in shiga Aljanna tare da wane da wane, ba zan shiga ba,” ko “Idan Allâhu ta’âlâ ya ba ni Aljanna ba zan karɓa ba, na ƙwammace in ga didar ɗinsa (fuskar zatinsa),” waɗannan batutuwa duka aikin kafirci ne, kamar yadda malamai suka bayyana. Wani zancen kuma da malamai suka ce aikin kafirci ne, shi ne faɗar cewa imani zai ƙaru ko zai ragu. Birgiɓi ya ce kafirci ne a ce zai ƙaru ko zai ragu a kan abin da ya shafi **muminun bih**, amma ba kafirci ba ne a ce haka a kan abin da ya shafi yaƙin da ƙuwwat-i-sidƙ. Saboda mujtahidai da dama sun yi magana a kan tari da ƙaranci na imani.

Malamai sun ce kafirci ne a ce, “Akwai Alƙibla biyu. Ɗaya daga ciki ita ce Ka’aba, ɗaya kuma ita ce Jerusalem.” Birgiɓi ya ce, kafirci ne a ce akwai Alƙibla biyu a yanzu, amma ana iya cewa a da “Bait-i-muƙaddas ita ce Alƙibla. Amma daga baya Ka’aba ta zama Alƙibla.”

Idan mutum ya nuna tsana ko ya yi rantsuwa da wani Malamin Musulunci, ana masa tsoron zamowa kafiri, idan ya yi hakan ba tare da wani dalili ba.

Kafirci ne mutum ya ce ko ya yadda cewa ayyukan ibada da al’adun kafirai suna burge shi.

Malamai sun ce duk wanda ya ce yin shiru yayin cin abinci kyakkyawar al’ada ce ta maguzawa, ko ya ce yana daga kyawawan al’adun maguzawa mutum kar ya sadu da matarsa a lokacin da take jinin al’ada (haila) ko jinin haihuwa (biƙi) ya zama kafiri.

Idan aka tambayi mutum ko shi Musulmi ne, sai ya ce “Insha-Allah…” zai iya haddasa kafirci idan mutum ba iya yin cikakken bayani ba.

Malamai sun ce ida wani ya ce wa mutumin da ɗansa ya mutu “Ɗanka dole ne ga Allâhu ta’âlâ,” to ya kafirta.

Idan mace ta ɗaura ɗamara a ƙugunta, da aka tambaye ta sai ta ce zunnar ne, ta zama kafira, ta kuma haramta ga mijinta.

Sun ce duk mutumin da ya ce “Bismillah…” lokacin da zai ci abincin da yake haram, to ya zama kafiri. Birgiɓi ya ce: “Idan har mutumin ya san cewa abincin da zai ci haramun ne li-‘aynihi, [kamar giya da naman da aka haramta da mushen dabba.] ya zama kafiri. Sai dai wannan hukuncin yana hawa ne ga mutumin da ya san cewa abin da zai ci haramun ne li-‘aynihi, (wato abincin da Musulunci ya yi hani a ci.) yin hakan ya tozarta sunan Allâhu ta’âlâ. Domin waɗannan abubuwan haramun ne kai tsaye. Kamar yadda aka ruwaito daga manyan Imaman mu, idan mutum ya ce “Bismillah,” lokacin da zai ci abincin da ya samu ta hanyar zalunci.[1]

Abincin kansa ba haramunba ne. Zaluncin shi ne haramun. Idan mutum ya la’anci ɗan uwansa da cewa “Allah ya ɗauki ranka kana cikin kafirci,” An samu saɓanin Malamai a kan ko wannan mutumin (wanda ya yi la’antar) zai zama kafiri. Amma maganar gaskiya, kafirci ne mutum ya amince da yadda da kafircinsa, manyan Malamai sun haɗu a kan haka. Amma yadda da kafircin wani; wasu Malaman na ganin kafirci ne, wasu kuma suna ganin zai zama kafiri ne idan yaddar tasa tana nufin kafirci ne kai tsaye. Amma ba kafirci ba ne idan hakan ta faru ne sakamakon zalunci da fasiƙanci, sai dai zai fuskanci azaba mai ɗraɗaɗî. Birgiɓi ‘Allah ya yi masa rahama’ ya ce: “Mun fahimci wannan zancen (hukunce-hukuncen malamai) da muhimmanci. Saboda tarihin Annabi Musa ‘alaihis-salâm’ a cikin nassin Ƙur’an al-karim hujja ne a kan haka.”

Idan mutum ya ce “Allâhu ta’âlâ ya san cewa ban aikata kaza da kaza ba,” bayan kuma ya san cewa ya aikata hakan, to ya zama kafiri. Domin faɗar hakan ya danganta jahilci ga haƙƙin Allâhu ta’âlâ.

Idan mutum ya auri mace [ba tare da shaidu ba] sai mutumin da matar suka ce Allâhu ta’âlâ da Mazonsa ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ su ne shaidunsu, dukkansu sun zama kafirai. Saboda Annabinmu ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ bai san ghayb (gaibi) ba lokacin da yake raye. Don haka, kafirci ne a ce ya san gaibu.

Idan mutum ya ce ya san inda kayayyakin da aka sata ko suka ɓace suke, ya zama kafiri tare da waɗanda suka yadda da shi. Idan ya ce aljannu ne suke faɗa masa, ya ƙara zama kafiri kuma. Annabawa da aljannu ba su san gaibi ba, haka nan waɗanda suke samun bayanai daga wurinsu.

---

[1] Domin gujewa rashin fahimtar wannan madda, a karanta babi na farko a mujalladi na shida na Endless Bliss, wanda za’ a iya samunsa a maɗaba’ar Hakîkat Kitâbeɓi, da ke garin Fâtih, Istanbul, Turkiyya.

Kamar yadda Malamai suka faɗa, idan mutum yana son yin rantsuwa da Allâhu ta'âlâ, sai wani ya ce masa "Ba ni son ka rantse da Allâhu ta'âlâ, na fi son ka yi rantsuwa da sakin aure ko 'yanta bawa ko karimci ko mutunci," wannan mutum ya zama kafiri.

Idan mutum ya ce wa dan uwansa, "Yanayinka yana tuna mani da mala'ikan mutuwa," ya zama kafiri. Saboda Mala'ikan mutuwa yana daga cikin manyan Mala'iku.

Mutumin da ya ce "Akwai dadî mutum ya ƙi yin Sallar farilla," ya zama kafiri. Malamai su ce, idan aka ce wa mutum, "Zo ka yi Sallah," sai ya ce "Ina jin ƙmatuƙar wahalar yin sallah," to ya zama kafiri.

Idan mutum ya ce "Allâhu ta'âlâ ne shaidana a sama," ya zama kafiri, saboda ya ayyana bigire ga Allâhu ta'âlâ. Shi Allâhu ta'âlâ ba shi da bigire (makani). [Haka nan mutum da ya kira Allâhu ta'âlâ 'mahaifi' ya zama kafiri.]

Idan mutum ya ce "Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yana suɗe yatsunsa bayan ya gama cin abinci," sai wani ya ce mummunar ɗabi'a ce yin hakan, wannan mutumin ya zama kafiri.

Idan mutum ya ce, "Riz (abinci) yana zuwa ne daga Allâhu ta'âlâ, amma dole ne da sa hannun ƙul (bayi)" wannan zancen nasa ya zama shirka. Saboda Allâhu ta'âlâ shi ya halicci duk motsin da mutane suke yi. Idan mutum ya ce, zamowa Nasara ya fi mutum ya zama Bayahude, [ko ya ce, zamowa kafiri Ba'amurike ya fi zamowa mai bin aƙidar kwaminisancigurguzu,] ya zama kafiri. Abin da ya kamata mutum ya yi shi ne misali ya ce Yahudawa sun fi Nasara sharri ko [mai bin aƙidar kwaminisancigurguzu ya fi Kirista zalunci].

Idan mutum ya ce zamowa kafiri ya fi zamowa munafiki, ya zama kafiri.

Idan mutum ya ce, "Meye haɗina da harkar ilimi," ko ya ce "Wa zai iya yin abin da malamai suka ce," ko ya jefar da takardar da aka rubuta fatawa a ciki ƙasa, ko ya ce "maganar muhimman mutane a cikin addini ba ta da kyau," ya kafirta.

Idan mutane biyu suna jayayya, sai ɗaya ya ce "Mu je gaban shari'a (kotun Musulunci)," shi kuma ɗayan ya ce "ba zan je ba sai dai jami'an 'yan sanda ku kai ni," ko ya ce "Ban san Musulunci ba," to ya zama kafiri.

Idan mutum ya faɗi wani zance na kafirci, shi da wanda ya yi dariya a kan zancen sun zama kafirai. Amma wanda ya yi dariyar idan bisa lalura ne bai kafirta ba.

Idan mutum ya ce "Babu wani wuri da babu Allah," ko ya ce "Allâhu ta'âlâ yana sama," ya zama kafiri, kamar yadda Malamai suka ce.

Mutumin da ya ce ran Shehunnai suna nan a koda yaushe kuma sun sani, ya zama kafiri, amma ba kafirci ba ne idan ya ce za su bayyana.

Mutumin da ya ce “Ban san (ko ban son in san) Musulunci,” ya zama kafiri.

Idan mutum ya ce “Da Annabi Adamu bai ci itaciya ba, da ba mu zamo masu saɓo, ko zunubi ba,” ya zama kafiri. Amma akwai saɓanin Malamai game da kafircinsa idan ya ce “… da ba mu sauko duniya ba.”

Idan kuma mutum ya ce ina ma a ce Annabi Adamu ya saka sutura, sai wani ya ce “Da mun zama ‘ya’yan masaƙi,” to ya zama kafiri.

Idan mutum ya aikata ƙaramin zunubi, sai kuma ya mayar da martani ga wanda ya neme shi a kan ya tuba cewa: “Laifin me na yi da zan nemi tuba a kai” to ya zama kafiri.

Idan mutum ya ce da ɗan uwansa, “Zo mu karanta littafan Fiƙihu da ‘Ilm-i-hal domin mu koyi ilimi,” sai ɗan uwan ya amsa masa cewa: “Me ya shafe ni da ilimi,” to ya zama kafiri, don faɗar haka wulaƙanta ilimi ne. Mutumin da ya wulaƙanta ko ya musanta ko ya tozarta litattafan Tafsiri da Fiƙihu, ya zama kafiri. Kafiran da suke sukar muhimman litattafan Mazhabobi nan huɗu, ana kiransu ‘Zindiƙ’ ko ‘Zindiƙai’.

Idan mutum bai san yadda zai amsa tambayoyi kamar haka, “Su waye asalinka?” “A kan wace aƙida kake?” “A kan Mazhabar wane Imamin Aƙida kake?”, “A kan Mazhabar wane Imamin hukunce-hukuncen ibada kake?”, ya zama kafiri.

Kamar yadda manyan Malamai suka bayyana, idan mutum ya ce, “Halal” a kan abin da yake haram-i-ƙat’iyya (haramun kai tsaye) kamar su giya da naman alade, ko ya ce “haram” a kan halal-i-ƙat’iyya (halal na kai tsaye), ya zama kafiri. [Kuskure ne a ce taɓa sigari haramun ne.][1]

Haka nan kafirci ne mutum ya yi fatan cewa abin da aka haramta a dukkan addinai, kuma ya zamana ya saɓa wa hikima idan aka halatta abin. Misali: fasiƙanci, Luwaɗi, cin abinci bayan mutum ya ƙoshi da ci ko bayar da riba. Ba ya daga kafirci mutum ya yi fatan giya ta zama halal. Domin giya ba haramun ba ce a dukkan addinan da suka gabata. Kafirci ne a yi wasa ko raha da Alƙur’ani mai girma. Idan mutum ya ce da wani mai suna Yahaya, “**Ya Yahya! Huz-il-kitaba**,” ya zama kafiri. Domin ya yi wasa da ayar

[1] Acikin babi na huɗu a mujalladi na shida na littafin Endless Bliss and yi ƙarin bayani akan shan tabar sigari.

Alƙur'ani mai girma. Abin haka yake ga karanta Alƙur'ani mai girma tare da kayan kiɗa, ko ta hanyar rawa da waƙa.

Abu ne mai muni a ce "yanzu na iso, Bismillahi." Idan mutum ya ce "**Ma khalaƙallah**," idan ya ga wani abin al'ajabi, ya zama kafiri idan har bai san ma'anarta ba.

Abu ne mai muni a ce "Ba zan yi maka rantsuwa ba yanzu, domin sun mayar da rantsuwa 'saɓo'."

Haka nan abu ne mai muni a ce "ka zama tsirara kamar maraƙin Mala'ika Jibrilu." Faɗar haka kamar isgilanci ne ga ɗaya daga cikin manyan Mala'iku ne.

Haramun ne a yi rantsuwa da wani abu wanda ba Allâhu ta'âlâ ba. Mutum baya zama Murtad ko kafiri don ya aikata haramun. Amma mutum zai kafirta idan ya halatta haram wadda take masusun 'alaih, (wato wadda aka bayyana ƙarara a cikin nassin Alƙur'ani mai girma ko Hadisin Annabi 'sallallahu 'alaihi wa sallam').

Haka nan idan mutum ya yi rantsuwa da kan ɗansa ko kansa, tare da amfani da sunan Allâhu ta'âlâ, misali ya ce, Wallahi, ina rantsuwa da kan ɗana, to ana masa tsoron zama kafiri.

AHKAM-I-ISLAMIYYA

Umurni da hani na addinin Musulunci su ake kira **Ahkam-i-islamiyya** ko **Islam**. Ahkam-i-islamiyya yana da ginshiƙai guda takwas, su ne: **Fard** (koFarillai), da **wajib** da **sunnat** da **mustahabbai** da **mubah** da **haram** da **makruh** da **mufsid**.

Fard umarni ne na Allâhu ta'âlâ. Kuma umarni ne da aka tabbatar bisa ƙwararan hujjoji na nassi. Wato abin da aka bayyana ƙarara a ayar Alƙur'ani. Duk mutumin da ya musanta shi ko wanda bai ɗauke shi da muhimmanci ba ya zama kafiri. Misali (Umarnin Allâhu ta'âlâ da ake kira fard) su ne: Imani da Alƙur'ani mai girma da yin alwala da sallolin farilla da fitar da zakka da aikin hajji da wankan janaba, [wato wanke dukkan jiki (bisa koyarwar Musulunci)].

Fard sun kasu kashi uku: Fard-i-daim da fard-i-muwaƙƙat da fard-i-ala-l-kifaya. Fard-i-daim shi ne amincewa da dukkan (shika-shikan imani guda shida, da suka ƙunshi) **Amantu billah…,** saninsu tare da fahimtar ma'anarsu, da yadda da su babu shakka. Fard-i-muwaƙƙat su ne dukkan aikin ibada da muke yi a kan lokacinsa. Misali: sallolin farilla guda biyar, yin azumin a watan Ramadan, da sanin hukunce-hukuncen sana'o'i da cinikayya. Fard-i-'ala-kifaya umarni ne na Allâhu ta'âlâ wanda idan mutum ɗaya ko mutane

kaɗan a cikin al'umma suka yi, sun ɗauke wa sauran ayarin al'umma da yawa. Misalin wannan shi ne amsa gaisuwa. Wani misalin kuma shi ne sallar jana'iza, da wankan gawar Musulmi, da koyon nahawun larabci da ake kira "sarf da nahw" zamowa mahaddaci, da sanin (ilimin da ake kira) wujub ɗa zurfin ilimin addini da kimiyya, fiye da abinda mutum yake buƙata a sana'a ko kasuwancinsa.

Haka nan akwai wasu farillai a cikin aikin farilla. Waɗannan farillan su ne: 'Ilm-i-fard, da 'amal-i-fard, da miƙdar-i-fard, da i'tiƙad-i-fard, da ikhlas-i-fard, da inkar-i-fard. Inkar-i-fard kafirci ne.

Wajib shi ne abin da Allâhu ta'âlâ ya bayar da umarni. Sai dai an fahimci wannan umarnin bisa wani nassi da ya zo da harshen damo. Duk mutumin da ya musanta aikin ibada (wanda ya kasance wajibi ne) bai kafirta ba. Sai dai rashin aikata shi zai iya kai mutum zuwa wuta. Misalan irin waɗannan sun ƙunshi: Karanta Alƙunuti a cikin wutirin sallah, da yin (aikin ibada da ake kira) Kurban, (wato yanka dabba bisa umarnin Musulunci) a loakcin Idin Hajji, da bayar da (sadaka ko Zakka da ake kira) Fitra a ranar Idin ƙaramar sallah (Zakatul Fitr), da yin sujada (wadda ake kira) **Sajda-i-tilawar** idan mutum ya karanta ko ya ji an karanta ayar sujada a cikin Aƙur'ani mai girma. Akwai wajibai huɗu da farilla ɗaya a cikin Wajib: 'Ilm-i-wajib, da 'amal-i-wajib, da miƙdar-i-wajib, da i'tiƙad-i-wajib, da ikhlas-i-fard. Haramun ne yin wasa da ɗaya daga cikin farillai ko wajibai.

Sunnat aikin ibada ce wadda Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya taɓa tsallake aikatawa sau ɗaya ko sau biyu. Duk mutumin da yake tsallake aikatawa, ba za a yi masa azaba ba (ranar tashin ƙiyama). Sai dai idan mutum ya mayar da hakan ɗabi'arsa ba tare da wani 'udhr (uzuri ba) na tsallake aikin ibadar, ya cancanci 'itab (kunyata ranar lahira), baya ga asarar ladar aikata ibadar da ya yi. Misalin wannan shi ne: Yin miswak (asuwaki [mutum ya goge bakin sa da ɗan ƙaramin icce]), yin kiran sallah (azan ko adhan) da iƙama , da yin sallar juma'a, ciyar da abinci a walimar ɗaurin aure, da yi wa 'ya'ya maza kaciya . Akwai sunnoni guda uku, su ne: Sunnat-i-mu'akkada, da sunnat-ghayr-i-muakkada, da kuma sunnat-i-'ala-l-kifaya.

Misalin sunnat-i-muakkada su ne: Sunnar yin nafilolin safe da na hantsi da na yamma. Waɗannan su ake kira sunnat-i-mu'akkada. Akwai Malaman da suka ce sunnar sallolin nafila na safe wajibi ne. Ba za a bar wannan sunnar ba sai da uzuri. Duk mutumin da ya musanta su ya zama kafiri.

Misalan sunnat-i-ghayr-i-muakkada su ne: Sallolin nafila na rana da na farkon dare. Tsallake aikata su ko da ya yawaita babu laifi a ciki. Sai dai ƙin

aikata su baki ɗaya zai sa mutum ya kunyata, ya kuma gaza samun ceto a gobe ƙiyama.

[Kamar yadda aka rubuta a cikin **Habibi** da **Kuduri,** aikin ibada ya kasu kashi biyu: **Faraidh** da **Fadail.** Ayyukan ibada waɗanda ba farilla ba, ba kuma wajibi ba su ake kira **fadail** ko **nafila** (waɗanda ba dole ba). Sunnonin da ake yi a lokuttan sallolin farilla biyar suna daga cikin ayyukan ibada da ake kira nafila, kuma suna cike giɓin da aka bari ne a sallolin farilla. Wato suna zamowa kamar diyya ga kurakuran da aka yi a ɓangarorin sallolin farilla. Wannan ba yana nufin sallar nafila za ta iya maye gurbin sallar farillar da ba a yi ba ne. Haka kuma ba ya nufin cewa sallar nafila za ta iya hana a yi wa mutum azabar wuta da aka yi tanadi ga wanda ya bar sallar farilla. Sallar nafila ga wanda ya bar sallar farilla da gangan ba sahihiya ba ce. Niyyat (Niyya) wajiba ce a sallar nafila wadda take sahihiya, [wato wadda aka yi babu naƙasu]. Idan ba a yi niyya ba, to ba za a samu ladar aikin ibadar sunnah da aka yi ba. Kazalika mutanen da suka bar sallar farilla ta t'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam'on lokaci, dole ne su yi niyya biyu, ta ƙada (ramuwa) ta sallolin da suka kubce masu, sannan su yi niyyar nafila da ake yi a tsakanin sallolin farilla. Idan suka yi wannan niyyar, sun rama sallar da ake binsu, tare da sallolin nafila da suka saba a tsakanin sallolin farilla. Yin hakan ba ya nufin a bar yin sunnonin ba.]

Sunnat-i-ala-kifaya ita ce sunnar da idan mutum ɗaya ya aikata, ya ɗauke wa dukkan taron jama'a da suke tare. Kamar yin gaisuwa, da shiga i'tikaf (ittikafi), da yin Bisimilla (wato cewa: "Bismillah-ir-rahman-ir-rahim,") yayin fara wani abu da musulunci ya halatta a yi.

Idan mutum bai yi Bismillah ba yayin fara cin abinci, zai yi asara guda uku:

1- Zai ci abincin tare da Sheɗan.
2- Abincin da ya ci zai cutar da jikinsa.
3- Babu albarka a cikin abincin da ya ci.

Idan ya faɗi Bismillah kuwa, zai amfana da abincin ta fuskoki uku:

1- Sheɗan ba zai samu rabo a abincin ba.
2- Abincin da ya ci zai amfani lafiyar jikinsa.
3- Zai samu albarka a abincin. [Idan mutum ya manta bai yi Bismillah ba, sai bayan ya fara cin abincin sannan ya tuna, to ya yi Bismillar a wannan lokacin da ya tuna.]

Mustahab na nufin aikin da Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya yi sau ɗaya ko sau biyu a tsawon rayuwarsa. Duk mutumin da bai aikata shi ba, ba za a yi masa azaba ko kunyatar da shi a ranar lahira ba. Kuma ba

za a hana shi samun ceto ba. Misalan mustahab su ne: Yin sallolin nafila, da azumin nafila, da zuwa Umra, da aikin Hajji na nafila da bayar da sadaka.

Mubah ayyuka ne da aka amince a yi waɗanda ke kawo samun lada idan aka aikata su da kyakkyawar niyya, kuma suna jawo azaba (a ranar lahira) idan aka aikata su da mummunar niyya. Kin aikata su ba ya jawo azaba. Misali: Tafiya da zama da sayen gida, cin dukkan nau'in abinci da yake halal, da sanya dukkan nau'in sutura waɗanda suke halaliya ne.

Haram shi ne abubuwan da Allâhu ta'âlâ ya yi hani a kansu kai tsaye a cikin Alƙur'ani mai girma. Wato su ne abubuwan da ya yi gargaɗin kada a aikata a cikin Alƙur'ani mai girma. Duk mutumin da ke wasa da haram ko ya musanta haramci, ya kafirta. Amma mutumin da ya aikata haram, sannan ya yadda da haramcinta, to bai kafirta ba, sai dai ya zama fasiƙi. [Ibn 'Abidin 'Allah ya yi masa rahama' ya faɗa a cikin sharuɗɗansa na zamowa limami[1], cewa: "Kada mutum ya bi sallar jam'i bayan limamin da ya san fasiƙi ne. **Fasiƙi** shi ne Musulmin da yake aikata manyan zunubbai, kamar shan giya da zina da cin riba. [Aikata ƙananan zunubai na tsawon lokaci yana zama babban zunubi.] Idan akwai Masallatan Juma'a da yawa a wuri, wajibi ne mutum ya yi sallar a bayan limamin da ya tabbatar sahihi ne, maimakon wanda yake fasiƙin limami. Wajibi ne a bijire tare da la'antar fasiƙin mutum. Duk zurfin ilimin fasiƙi ba za a naɗa shi limami ba. Naɗa shi limamin zai nuna cewa ana daratta shi kuma ana girmama shi. Idan mutum fasiƙi ne, ko kuma baya bin ɗaya daga cikin Mazhabobi (huɗu) makruhi ne mai ƙarfi a naɗa shi ya zama limami. Guje wa aikata haram ana kiransa **taƙwa**. Guje wa aikata abubuwan da ake kokwanton halal ko haram shi ne **wara'**. Rayuwa ba tare da aikata abubuwan da suke halal ba domin gudun kada mutum ya faɗa wa ayyukan da ake kokwantonsu shi ake kira **zuhd.** Idan mutum ya musulunta lokacin da yake zama a Dar-ul-harb, to ya zama wajibi a gare shi ya yi hijira zuwa Dar-ul-islam."]

Haram ta kasu gida biyu: Daya daga ciki ana kiranta **haram li-'ainihi**, ɗayar kuma ana kiranta **haram li-ghayrihi**. Ta farkon asalinta haramun ce; a koda yaushe tana nan matsayinta na haram. Misalinta shi ne: Kisan kai, da zina da luwaɗi, da shan giya da caca da cin naman alade, da fita waje ga mata da 'yan mata alhali kansu da sandar hannuwansu da ƙafafunsu a buɗe.

---

[1] Imam, a nan shine, mutum musulmi da ke shugabantar yin sallah a cikin jam'i, wanda aka yi bayaninsa sosai a bagiri na ashirin a cikin littafi **Endless Bliss,** kashi na huɗu.

Idan mutum ya furta Bismillah yayin aikata waɗannan ayyukan saɓon, ko ya yadda cewa halal ne, wato bai ɗauki haramta su da Allâhu ta'âlâ ya yi a kansu da muhimmanci ba, wannan mutumin ya zama kafiri. Amma idan mutum ya aikata su tare da cewa ya yadda haramun ne, kuma yana tsoron azabar da Allâhu ta'âlâ zai yi ga waɗanda suka aikata hakan, to bai zamo kafiri ba, amma zai iya fuskantar azabar wuta a ranar lahira.

Haram li-ghayrihi na nufin abin da asalinsa halal ne, amma sai aka same shi ta hanyar haram. Misalan wannan su ne: Shiga lambun wani mutum a ɗebi kayan marmari na itacensa a ci ba tare da amincewar mai lambun ba, da satar kayan gidan mutum ko kuɗi kuma ya yi amfani da su.

Idan mutum ya ce Bismillah a lokacin da zai aikata laifin, ko ya ce halal ne, zai zama kafiri. Idan mutum ya ci kayan wani bisa zalunci ko da daidai da ƙwayar hatsi ne a nan duniya, Allâhu ta'âlâ zai ɗiba daga cikin ladar raka'a saba'in ta sallar farilla da ya yi a cikin jam'i na azzalumin (waɗanda Allâhu ta'âlâ ya karaɓa) ya saka wa wanda aka zalunta. Akwai lada mai yawa (wadda za a bayar a ranar lahira) ga wanda ya guji aika dukkan haramun, fiye da ladar yin aikin ibada.

Makruh na nufin abin da yake ɓata ladar da aka samu ta hanyar aikin ibada (kyakkyawan aikin da aka yi bisa tsoron Allah). Makaruhi ya kasu gida biyu, su ne: Karahat-i-tahrimiyya da karahat-i-tanzihiyya, (ko makruh tahrimi da makruh tanzihi.)

Karahat-i-tahrimiyya shi ne bari (wani da yake) wajibi. Ya fi kusa (ƙarib)da haram. Karahat-i-tanzihiyya shi ne barin (abin da yake) sunnah. Ya fi kusa da halal. Idan mutum ya aikata karahat-i-tahrimiyya ya zama mai saɓo, idan ya aikata hakan da gangan ne. ya cancanci shiga wuta. Idan ya aikata haka a cikin sallah zai sake sallah. Idan ya aikata ne a kan sahwy (wato kuskure) yi sujadar sahwy (rafkannuwabayan ya kammala sallar).[1] Mutumin da ya aikata (wani abu wanda yake) karahat-i-tanzihiyya ba za a yi masa azaba ba (a ranar lahira). Sai dai zai iya fuskantar jin kunya, ya kuma gaza samun ceto (a ranar lahira) idan ya mai da ita ɗabi'arsa. Misalin wanan shi ne: cin naman doki, cin abinci ragowar mage ko ɓera, da sayar da inabi ga masu yin giya.

[1] Anyi ƙarin bayani akan sajda-i-sahw acikin babi na goma sha shida a mujalladi na huɗu na littafin Endless Bliss.

Mufsid shi ne abin da yake ɓata ayyukan ibada (wato kyawawan ayyukan ibada da aka yi). Misalan wannan su ne: ɓata imani da salloli da aure da hajji da zakka da aka yi, ko saye da sayarwa da aka yi.

[Musulmin da ya aikata ibadar farilla da ta wajibi da ta sunnah, ya kuma guji aikata haramun da makaruhi zai samu **thawab**, wato za a ba shi lada a ranar lahira. Idan mutum ya aikata haramun da makaruhi ko ya ƙi aikata farilla da wajibi, za a sanya shi a matsayin mai **saɓo.** Ladar da ake samu saboda gudun aikata haramun ta fi ladar da ake samu saboda aikata farilla. Ladar aikata farilla ta fi ladar barin aikata makaruhi wanda ita kuma ta fi ladar aikata sunnah. A cikin mubah (abinda aka halatta), wadanda Allâhu ta'âlâ ya fi so ana kiransu **khayrat** da **hasanat** (kyawawa da ayyuka na ƙwarai) kuma ana bayar da lada ga mutumin da ya aikata su, ladar ba za ta kai ta aikata sunnah ba. Mutum ya aikata aikain da ya tabbatar cewa za a ba shi lada a kai ana kiranshi **ƙurbat.**

Saboda jin ƙai da Allâhu ta'âlâ yake wa bayinsa, ya turo masu addinai, wadanda su ne hanyoyin wadata da farin ciki. Addinin ƙarshe shi ne addinin (zamanin) Annabi Muhammad ''alaihis-salâm'. Sauran addinan wasu ɓata garin mutane ne suka gurɓata su. Idan wani mutum musulmi ko wanda ba musulmi ba, ya gudanar da rayuwarsa kamar yadda addini ya tanada, ko da aikata hakan a kan sani ko rashin sani ne, ba zai fuskanci matsala a rayuwarsa ta duniya ba. Misalin wannan su ne kafiran Turawa da Amurikawa da suke rayuwa bisa tsarin da addini ya shimfiɗa. Sai dai ba za a bayar da lada ga kafirai ba a ranar lahira. Idan mutum musulmi ya aikata hakan bisa ɗa'a ga Musulunci, zai samu albarka marar iyaka a ranar lahira.]

SHIKA-SHIKAN MUSULUNCI

Shikashikan Musulunci sun kasu kashi biyar, wato Musulunci ya ginu a kan wasu ginshiƙai guda biyar. Na farkonsu shi ne faɗar Kalima-i-shahada, da kuma fahimta da yadda da ma'anarta. Na biyu shi ne tsaida salloli (namaz ko salat) guda biyar a kowace rana a kan lokacinsu. Na uku shi ne azumtar kowace rana a watan Ramadan. Na huɗunsu kuma shi ne fitar da zakka da ushiri a kowace shekara, idan ta zama farilla. Na biyar kuma na ƙarshe shi ne zuwa aikin Hajji sau ɗaya a rayuwa, idan mutum ya samu iko. [Aikata wadannan horon na Allâhu ta'âlâ, tare da nisantar (abin da ya hana) haram shi ake kira **aikata ibada**. Nafila ce ga musulmin da bai cika sharuɗɗa ba a ɓangaren wujub da ada ya yi aikin Hajji, haka nan ga wanda ya riga ya yi aikin Hajji ya sake yin shi. Ba jaiz (hallata) ba ne mutum ya aikata nafila idan ya ƙunshi bidi'a ko haramun. Imam Rabbani 'ƙuddisa sirruh' ya faɗa a

babi na ishirin da tara da na ɗari da ishirin da uku, da na ɗari da ishirin da huɗu da (Abdullah Dahlawi ‘ƙuddisa sirruh) a babi na ishirin da shida na littafin **Maƙamat-i-Mazhariyya**, cewa kar ka bayar da dama ga nafilar Hajji ko Umra. (‘Afif-ud-din ‘Abdullah bin Es’ad Yafi’I ‘rahmatullahi ta’ala ‘alaihi’, 698 [1298 miladiyya], Yemen – 768 [1367], Makka, a kan bayaninsa game da matakan ‘zuhd’ (zuhudu), ya ce wasu matakan na zuhudu da ake kira maƙamat-i-‘ashara [matakai goma], a cikin littafinsa mai suna) **Nashr-ul-mahasin-il-ghaliyya**: “lokacin da aka tambayi Imam Nawawi, wanda shahararren malamin Musulunci ne kuma waliyyi: ‘kana aikata dukkan sunnah. Amma kana tsallake gida ɗaya, kuma babbar sunnah ce: shi ne aure,’ sai ya amsa da cewa, ‘Ina tsoron aikata haramun da yawa wajen ƙoƙarin aikata sunnah ɗaya.’” Imam Yahya Nawawi ya rasu a Dimashƙ a shekara ta 676 hijiriyya [1277 miladiyya]. Farfesa Habib-ur-Rahman, shugaban tsangaya a **Jami’a-i-habibiyya**, ya je Hajji a shekarar 1401 hijiriyya [1981 miladiyya]. Sai ya ga wani Imamina wahabiyya yana sallah (a cikin jam’i) yana amfani da na’urar shelanta magana ta lasifika, sai ya yi sallarsa shi kaɗai. Wanan ya sa aka kama shi, aka saka mashi ankwa, aka kai shi gidan yari, aka tuhume shi a kan meye dalilinsa na ƙin bin sallar jam’i. shi kuma ya ce ba hallata mutum ya yi sallah da lasifika ba, daga nan sai aka mayar da shi ƙasarsa, aka kuma hana shi zuwa aikin Hajji.

Abu na farko da ya wajaba a kan mutum, a ko’ina yake a duniya shi ne su fahimci aƙida da imaninsu. Abin da ya fi muhimmanci shi ne mutum ya koyi addini daga wajen manyan malamai magabata. Domin a wannan zamanin da muke ciki, babu malaman Musulunci a ko’ina. Jahilan mutane da wawaye da suka biye wa turawa, sun yaɗa gurɓataccen ilimi da sunan malaman addini. Hanya ɗaya tak ta fahimtar aƙida da imani ingantacciya a wannan zamanin shi ne karanta litattafan da Malaman Ahl as-sunnat suka rubuta. Samun waɗannan litattafan wani taimako ne daga Allâhu ta’âlâ. Maƙiyan Musuluci suna ta yaɗa litattafan addini na bogi, da nufin ɓatar da mutane, domin ya zamo abu mawuyaci a iya samun litattafan addini na gaskiya. Ana jan hankalin matasa da wasanni marasa ma’ana, wanda ke hana su neman litattafai da karanta su. Abin takaici ƙwarai yadda za ka ga matasa ba sa tunanin komai sai wasanni. Wannan mummunar cutar tana cigaba da yaɗuwa a tsakanin matasa. Wajibi ne ga iyaye Musulmai su kare ‘ya’yansu daga wannan annobar. Abin da za su yi shi ne, sanar da ‘ya’yansu game da aƙidunsu tare da horonsu su riƙa karanta litattafan addini. Hakan zai auku ne ta hanyar kare ‘ya’yan nasu daga halayyar shagala da wasanni. Za a ga cewa wasu daga cikin ‘ya’yanmu sun shagala da wasanni masu cutarwa, waɗanda suke sanyawa har su manta da cin abinci. Abu ne mawuyaci waɗannan yaran su iya karanta litattafansu har su iya cin jarabawa. Wajibi ne iyaye su lalubo

hanyar da za su tarbiyantar da ‘ya’yansu a kan karatun litattafai. Misali ya kamata su karanta ƊABI'O'IN MUSULUNCI. Mutumin da ya karanta wannan littafin, baya ga koyon aƙida da imani, zai kuma fahimci ƙulle-ƙullen maƙiyan Musulunci, da yadda suke aiki. Idan iyaye suka nuna halin ko’in kula a kan nauyin da ya rataya a wuyansu, za a samu matasa marasa addini da imani, waɗanda za su yi mummunar illa ga ƙasarsa da al’ummarsa.

Wani muhimmin abu kuma da ya wajaba iyaye su mayar da hankalinsu a kai shi ne sitr-i-awrat’, (wanda aka yi cikakken bayani a kai a babi na takwas, mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**). Muna ganin yadda matasa ke baiyana ƙwabri da guyawunsu har zuwa hantsarsu a cikin mutane masu wasanni. Yana daga cikin muhimman farillai mutum ya sitirta al’aurarsa. Mutanen da ba su ɗauki wannan da muhimmanci ba, za su iya rasa imaninsu. Musulmi suna zuwa masallatai ne da nufin samun lada mai yawa ta sallolin da suka yi da kuma sauraron wa’azi. Ko babu waɗannan dalilan, akwai lada ta musamman ga wanda yake zuwa masallaci. Duk wurin da mutane masu baiyana al’aura suke zuwa ba zai taɓa zama masallaci ba; taro ne kawai na fasiƙanci. An rubuta a cikin litattafan addinin (Musulunci) cewa haramun ne mutum ya halarci wurin da ake fasiƙanci. Mutanen da suke halartar waɗannan wurare da ake bayyana al’aura suna halartar wuri ne da ake fasiƙanci; suna aikata saɓo. Duk mutumin da ke halartar waɗannan masallatan da nufin samun lada da sauraren wa’azi, ya samu zunubi maimakon lada. Idan mutanen da suka bayyana al’aurarsu suka shiga masallaci, za su sanya Musulmi su zamo masu aikata saɓo. Saboda saɓo ne mai girman gaske baiyana al’aura (ga wasu mutane), haka nan saɓo ne mai girma mutum ya kalli al’aurar wani. Don haka Musulmin da ya halarci waɗannan irin wurare ya samu zunubi kuma zai haɗu da Ghadab-i-illah (fushin Allâhu ta’âlâ) maimakon samun thawab (lada).]

BABI A KAN SALLAH

Sallah tana da farillai guda goma sha biyu: Bakwai daga ciki suna wajen sallar (sharuɗɗa), yayin da sauran biyar suke cikinta.

Saruɗɗan sallah (farillai na wajen sallah) su ne: Taharat (tsarki) daga hadasi; tsarki daga najasa; sitirta al’aura; fuskantar alƙibla; shigar lokaci; niyya; kabbarar harama. Farillan da suke cikin sallah su ne: Tsayuwa; karatu; ruku’u guda ɗaya a kowace raka’a; sujada guda biyu a kowace raka’a; tsawaita zama (domin yin addu’a) bayan tahiya (tashahhud) a ƙa’ada-i-akhira (zaman ƙarshe). Farillan cikin sallah ana kiransu **rukns** (rukunnai). Farilla ne mutum ya sanya goshinsa da babban ɗan yatsa a ƙasa a lokacin sujada.

Tsarkin hadasi yana nufin yin alwala idan mutum ba shi da ita, da yin wanka ga wanda yake da janaba, da yin taimama idan babu ruwa ga wanda ke buƙatar yin alwala ko wanka. Akwai saruɗɗa guda uku da ya kamata a cika domin tsarkin hadasi ya inganta:

Kulawa da yin istinja da istibra, (za a yi bayaninsu nan gaba a littafin); a lokacin wanke gaɓɓai da shafar kai, kar a bar wani ɗigo na gaɓɓai da suke farilla ba a wanke ba.

Sharuɗɗan da za a cika na tsarkin najasa guda uku ne: tsarkake tufafin da za a yi sallah da su daga najasa. Tsarkake jiki kafin a fara sallah. Tsarkake bigiren da za a yi sallar. [A duba babin da yake magana a kan farillai guda hamsin da huɗu!]

Akwai sharuɗɗa guda uku na sitirta al'aura: A mazhabar Hanafiyya, maza za su sitirta daga cibiyarsu zuwa guiwarsu. Sunnah ne maza su rufe ƙafafunsu yayin da suke sallah.

Ga mata waɗanda ba bayi ba, za su sitirta dukkan jikinsu ban da fuskokinsu da tafukan hannuwansu. A cikin wata riwaya (riwayat) ta malamai, an ce za su iya bayyana tafukan ƙafafunsu.

Ga matan da suke jariyas (bayi) za su sitirta daga maɗaukakin ƙirji da bayansu zuwa guyawunsu. [Matan da suke yawo da gashinsu da cinyoyin hannunsu da ƙafafunsu a buɗe, ko suke sanya matsattsar situra, da mazan da suke kallonsu, suna aikata saɓo, saboda haramun ne yin hakan. Mutumin da ya san haka kuma yake aikatawa ya zama kafiri ko wanda ya yi ridda.]

Akwai sharuɗɗa guda uku da suka wajaba a cika domin tabbatar da istiƙbal-i-ƙibla: Fuskantar Alƙibla.

Kada mutum ya kawar da ƙirjinsa daga fuskantar Alƙibla har ya kammala sallah.

Mutum ya ƙanƙantar da kansa a diwan-i-ma'anawi na Allahu 'adhim-ush-shan.

Akwai sharuɗɗa guda uku na shigar waƙt (lokuttan sallah): Sanin farkon shigar lokacin sallah da fitar lokacin. Kar a jinkirta sallah har zuwa lokacin da makaruhi ne a yi sallar.

Ana kyautata niyya ne da sani, da ƙudircewa a zuciya cewa ko sallar da za a yi farilla ce ko wajibi ko sunnah ko mustahabbi, tare da kawar da tunanin duniya daga zuciya. Imam A'zam ya ce wajibi ne, amma sunnah ce inji Imamai biyu (wato Imam Abu Yusuf da Imam Muhammad), haka nan an faɗa a mazhabobin Malikiyya da shafi'iyya, yin sallar witr (witiri). [An amince wa wanda yake bin mazhabin Malikiyya ya bar sallar witiri idan akwai haraj (matsatsi kamar yadda Musulunci ya shar'anta).]

Ana yin Takbir-i-ifitah (kabbarar harama) ta hanyar ɗaga hannuwa daidai saitin kunnuwa, kuma da sani da kulawar zuciya.

Akwai sharuɗɗa uku na cikar Kiyam (tsayuwa): tsayuwa ana fuskantar alƙibla, kallon inda ake yin sujada, (wato inda ake sanya goshi da hanci a lokacin sujada). Kuma kada mutum ya riƙa waige-waige ko motsi mai ƙarfi daga nan zuwa can a cikin tsayuwar.

Akwai sharuɗɗa guda uku na cikar Kira'at (karatu): yin karatun sallah a bayyane a inda ake bayyanawa, da sassauta murya gwargwadon yadda mutum zai jiyar da kansa a inda ake sirranta karatu, da furta sautukan karatun daidai. Yin tunanin ma'anar ayoyin Alƙur'ani mai girma da kake karantawa. Bin ƙa'idojin tajwidi (tajwid) a lokacin da kake karanta ayoyin. Tun daga kabbarar harama da dukkan karatuttukan sallah da kiran sallah (azan ko adhan) wajibi a yi su da harshen Larabci. Wajibi ne a koyi yadda ake karanta su daga hafizi (hafid) wanda ya san Musulunci yake kuma bin dokokin da aka zayyana a littafin Ilmihal na Mazhabinsa. Ba za a iya furta ayoyin Alƙur'ani mai girma da baƙaƙen Turanci daidai ba. Karanta su a haka zai janyo kurakurai da dama. Amma ana iya yin Tafsir (fassarar) Alƙur'ani mai girma da shi.. Litattafan da ake fitarwa da sunan 'Alƙur'ani bugun Turkiyya wanda wasu marasa kishin addini marasa Mazhaba suke yi ba daidai ba ne. Ba su a kan daidai, suna da rauni. Wajibi ne ga dukkan Musulmi ya je ya koyi yadda ake karanta Alƙur'ani mai girma, ya koyi haruffan larabci, domin ya riƙa karatun Alƙur'ani da addu'o'i yadda suka dace. Ana karɓar sallar da aka yi karatun ayoyin Alƙur'ani da sauran addu'o'i daidai. An ruwaito a cikin littafin **Terghib-us-salat** cewa: "Idan ba a kyautata karatun ayoyin Alƙur'ani da addu'o'in cikin sallah ba, manyan malaman Musulunci guda tara tare da wani babban Malami sun ce ana iya cewa sallar shi ɓatatta ce ba."] (Aikin ibada wanda yake ɓatacce shi ne wanda ba a karɓa ba.)

Akwai sharuɗɗa guda uku na cikar ruku'u: yin ruku'a ta fuskar Alƙibla, duƙawa bisa daidaito (kamar an juya harafin 'L ya kalli sama') a daidaita kai da ƙugu su yi saiti da juna. Da natsuwa (tumaninat) a cikin ruku'un ta ɗan lokaci [wato har sai zuciyarka ta gamsu].

Akwai sharuɗɗa guda uku na cikar sujada: Duƙawa yin sujada kamar yadda sunnah ta tsara. Yin sujada ta fuskar Alƙibla yayin da goshi da hanci suke ɗamfare a kan ƙasa saiti da juna. Nutsuwa a cikin sujadar da wani ɗan lokaci. [An bayar da dama ga mutum mai lafiya ya yi sujada a kan wani abu da tsawonsa bai wuce santimita ishirin da biyar ba daga ƙasa, amma makaruhi ne yin hakan. Domin Annabi 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' bai taɓa yin sujada a kan wani abu maɗaukaki daga ƙasa ba, haka nan babu

ɗaya daga cikin sahabbai da ya aikata haka. Yin sujada bisa wani abu maɗaukaki da ya wuce santimita ishirin da biyar zai iya ɓata sallah.]

Akwai sharuɗɗa guda uku na cikar ƙa'da-i-akhira (zaman ƙarshe): 1- Ga maza su zauna a bisa ƙafarsu ta hagu, su kuma tokare ƙafarsu ta dama, ga mata kuma su zauna bisa sifar da ake kira tawarruk,wanda ke nufin su zauna a kan bisa ɗuwainiyarsu ta sashen hagu, su kwantar da ƙafar ta sashen dama. 2- karatun Tahiya (Tahiyyat) cikin ƙanƙantar da kai. 3- yin Salati da sauran addu'o'i a cikin ƙa'da-iakhira (zaman ƙarshe). Za a bayyana addu'o'in da ake yi a cikin sallah a nan gaba a cikin littafin.

BABI A KAN GHUSL (WANKA)

Akwai farillai uku da suka wajaba ga mai wanka a Mazhabar Hanafiyya, akwai guda biyar a Mazhabar Malikiyya, akwai guda biyu a Mazhabar Shafi'iyya, akwai guda ɗaya a Mazahabar Hambaliyya. A Mazhabar Hanafiyya:

1- Wanke baki da ruwa sau ɗaya. Farilla ne ruwa ya shiga tsakanin haƙora ko'ina. [A Mazhabar Hanafiyya, ba a yadda Musulmi ya sanya haƙorin Makka ba ko ya yi ma haƙori ciko sai in akwai lalura. Sai dai su yi wanda za a iya cirewa a duk lokacin da za a yi wanka, bayan an gama sai a mayar. Musulmin da aka yi wa ciko a haƙori, ko ya sanya haƙorin Makka saboda wani uzuri na haraj (tsanani) dole ne a gare shi; ya yi koyi da ɗaya daga cikin Mazhabobin Shafi'iyya da Malikiyya idan zai yi wanka. A kan haka sai sun ƙara da cewa "ina koyi da Mazhabin Shafi'iyya (ko Malikiyya)," a lokacin da suke ɗaura niyyar yin wanka ko alwala, da lokacin da za su yi sallah.]

2- Shaƙa ruwa a hanci sau ɗaya.

3- Game dukkan jiki da ruwa sau ɗaya. Farilla ne wanke dukkan jiki, inda babu haraj (tsanantawa) wajen wankewa. Idan ba za a iya wanke wata gaɓa ta jiki ba saboda dalili na lalura, wato wani abu da ya faru ga halitta wadda ba ƙirƙira aka yi ba, Allâhu ta'âlâ zai gafarta, kuma wanka zai inganta.

Kamar yadda aka faɗa a littafin **Durr-ul-mukhtar**, abincin da ya maƙale a cikin dasashi ba ya hana wanka ya inganta. Kamar yadda aka faɗa a cikin fatawa[1]. Domin ruwa zai jiƙa abincin ya shiga har ƙarƙashinsa. Amma idan

[1] Fatawa wani tabbataccen bayani ne inda wani shahararren malamin musulunci ke bayar da amsa ga musulmai game da lamarin addini. Sannan kuma ana rubuta silsila ta inda aka samo dalilan da aka gina wannan fatawar a ƙarƙashinta.

abincin daskararre ne, zai hana ruwa ya shiga ciki. Wannan shi ne gaskiyar zancen. **Ibni ‘Abidin** ‘Allah ya yi masa rahama’ ya yi bayanin mas’alar kamar haka: haka nan an ruwaito a cikin littafin **Khulasa-t-ul-fatawa** cewa ba zai hana ruwa ya shiga Tsakani ba, saboda ruwa ba daskararren abu ba ne, zai iya ratsa abincin (ya jika wurin da yake ƙarkashinsa). Idan aka fahimci cewa ruwa ba ya ratsa tsakanin abincin da ya mafale a dasashi, wankan bai inganta ba, kuma dukkan manyan Malamai sun yi ittifaki a kan haka.

Haka aka fada a littafin **Hilya-t-ul-mujalli**, (wanda Ibni Emir Hajj ya rubuta) Halabi ‘Allah ya yi masa rahama’, 879 hijiriyya [1474 miladiyya]. idan abincin ya daskare saboda matsatsi, ba zai bar ruwa ya ratsa ba, kuma wankan bai inganta ba. Domin babu lalura a nan. [wato ba abu ne da ya auku da kansa ba.] Sannan babu haraj [waken wanke wadannan sassan jikin.]

An ruwaito a cikin littafin **Halabi-i-saghir**: Idan mutum ya yi wanka da kingin biredi ko abinci ko wasu abubuwa a cikin dasashinsa, wannan wankan ya inganta, kamar yadda fatwar ta zo, ko da yana tunanin cewa ruwa (ruwan wankan) bai ratsa su ba. Fatawar ta yadda da hakan, kamar yadda aka rubuta a **Khulasa-t-ul-fatawa**.

Wasu malaman sun ce wankan bai inganta ba idan abincin daskararre ne. Wannan hukuncin na ƙarshe yana nan rubuce a littafin **Zahira-t-ul-fatawa**, (wanda Burhan-ad-din Mahmud bin Taj-ud-din Ahmad bin Abd-ul-‘Aziz Bukhari ‘Allah ya yi masa rahama ya rubuta’, 551 hijiriyya [1156 miladiyya.] Ya rasu a 616 hijiriyya [1219]). Shi ne zance mafi inganci game da batun. Domin ruwan da aka yi amfani da shi ba zai kai ƙarkashinsa ba. Sannan babu lalura ko tsanani game da hakan.

An fada a cikin littafin **Durr-ul-Muntaka**:[1] Game da wanka da abinci mafale a cikin dasashi, akwai Malaman da suke ganin wankan ya inganta, wasu kuma suka ce akasin haka. Abin da ya fi dacewa ga mutum shi ne ya cire abincin kafin ya yi wankan. An fada a cikin **Tahtawi**, Sharhin **Murak-il-falah**, idan akwai abinci mafale a cikin dasashi ko tsakanin hakora, wanka ya inganta. Saboda ruwa ba daskararre ba ne zai shiga ya jika ƙarkashi cikin sauki. Idan abincin da ya mafale ya daskare saboda tauna, zai hana ruwan wankan shiga. Haka abin yake a cikin littafin **Fat-h-ul-kadir**.

An fada a cikin littafin **Bahr-ur-raik** cewa wanka ya inganta ko da akwai abinci mafale a cikin dasashi ko tsakanin hakora. Domin ruwa tsinkakken abu ne da zai iya shiga ko’ina. Haka aka rubuta a littafin **Tajnis**. Sadr-ush-

[1] ’Alâ-ud-dîn Haskafî ‘rahmatullâhi ta’âlâ ’alaih’ (1021,Haskaf – 1088 [1677 A.D.]) ya rubutashi.

shehid Husamaddin ya ce wankan da aka yi a kan wannan mas'alar bai inganta ba, don haka dole a cire abincin ruwa ya ratsa ko'ina a cikin dasashin. Abin da ya fi dacewa shi ne a cire abincin da ya maƙale a wanke ƙarƙashin.

An bayyana a cikin littafin **Fatawa-i-Hindiyya**: Zancen da ya fi kusa da daidai shi ne wanda ya ce wankan da mutum ya yi da abinci maƙale a cikin dasashi ko tsakanin haƙora, ya inganta. Haka ya zo a cikin **Zahidi**. Sai dai ya fi dacewa idan aka cire abincin yadda ruwa zai shiga cikin dasashin. Haka nan ya zo a cikin littafin **Kadikhan**, an rubuta a cikin **Natifi** cewa wankan da aka yi da abinci a tsakanin haƙora bai cika ba, wajibi ne a cire abincin a wanke wurin.

An rubuta a cikin littafin **al-Mejmu'at-uz-zuhdiyya**: idan abincin da ya maƙale tsakanin haƙora ya daskare, ya toshe hanyar da ruwa zai shiga tsakani kome ƙanƙantarsa, to zai hana wanka. Haka batun yake a cikin **Halabi**. Babu tababa cewa "babu haraj, tsanani wajen cire abincin da ya maƙale, amma ciko da haƙorin makka suna da wahalar cirewa; a nan akwai haraj wajen." Idan mutum ya yi wani abu da ya zamo haraj, ya zama uzuri gare shi ya yi koyi da wata Mazhaba. Amma ba zai taɓa zama uzuri ba idan mutum ya bar farilla. Mutumin da za a iya ɗauke wa farilla, shi ne wanda ya zamana ba zai yiwu gare shi ya yi koyi da wata Mazhaba ba, hakan ya zame masa lalura da haraj. Idan aka tambaya, "Mutum ya sanya haƙorin Makka bisa dalilin kare shi daga ciwon haƙori ko cirewar haƙorin baki ɗaya. To yin hakan bai zamo lalura ba, (wato na ɗauke masa farilla, don haka zai iya yin wankan ba tare da wanke dasashin ba,)" to amsarmu ita ce "Zamowarsa lalura na buƙatar sai idan babu wata mafita idan ya yi koyi da wata Mazhaba."

Game da wannan batun, "Wajabcin wanke haƙora a wajen wanka, ya koma a kan ciko ko haƙorin makka da aka saka," bai dace ba a Musulunci. Tahtawi (Ahmad bin Muhammad bin Isma'il) ya faɗa a cikin sharhin da ya yi wa littafin (Shernbali) mai suna **Imdad-ul-Fattah**: idan alwalar mutumin da ya sa huffi bayan ya yi alwala ta karye, wannan karyewar ta shafi huffin ne ba ƙafarsa ba. Wannan zancen ya zo a litattafan Fiƙihu a matsayin abin da ya shafi alwala ne da kuma huffi. An danganta wannan hukuncin a kan mas'alar haƙorin makka da wanka yana nuna cewa mutum ya yi fatawa ta ƙashin kansa. Ko a ce za a kwatanta batun da gemu mai kauri idan ana alwala, domin ba wajibi ba ne a jiƙa fatar da take ƙarƙashin gemu a wajen alwala, amma farilla ne, (ya zama dole) a jiƙa fatar ƙarƙashin gemu wajen wanka. Mutumin da ya ce ba farilla ba ne "a jiƙa fatar da ke ƙarƙashin gemu a wajen wanka saboda ba farilla ba ne a jiƙa ta wajen alwala," don haka ba zai jiƙa fatar da ke ƙarƙashin gemu mai kauri a wajen wanka ba. Wankansa da sallarsa ba su inganta ba.

Haka nan ba abu ba ne tsayayye ga litattafan Fiƙihu su riƙa kwatanta hukuncin sanya haƙorin makka da huffi ko karan ɗori da aka sanya wa gaɓar jiki da ta karye, ko bandeji da aka rufe rauni. Domin idan akwai haraj ko matsala idan aka cire su daga rauni ko gaɓar da ta karye, ba zai yiwu ba su yi koyi da wata Mazhabar. Saboda waɗannan dalilai uku, an ɗauke wa mutum wajabcin wanke wurin.

Tun da kana da zaɓi na yin ciko ko sanya haƙorin makka a kan haƙorin da ya cinye ko yake ciwo, saboda baka son cire shi baki ɗaya a maye gurbinsa da na roba da za a iya cirewa, to ba zai zamo lalura ba idan an yi cikon ko an sanya haƙorin makka ba. Domin ko da ka ce lalura ce, ba zai ɗauke maka wajabcin wanke ƙarƙashinsu ba. Saboda akwai damar koyi da wata Mazhaba. Babu wanda yake da ikon amfani da wata dama ta zartar da wani hukunci ga mutanen da suke bin litattafan Fiƙihu da Mazhabobin Shafi'iyya da malikiyya a lokaci guda.

Darurat (lalura) na nufin dalilai na ƙaddara masu ƙarfi da za su tilastawa mutum yin wani abu (ko tilasta masa barin wani abu), wato abubuwan da ba a iya yin wani taimako a kai. Misalin lalura su ne hani da horo na Musulunci, tsananin zafin ciwo, matsalar da ka iya haifar da rasa wata gaɓa ko rayuwar mutum, da kuma halin ƙaƙa-nika-yi. **Haraj** (tsanani) shi kuwa yana nufin tsanani wajen kare wani abu da mutum ya yi da zai iya hana mutum aikin ibada na farilla, ko tilasta mutum ya aikata haramun. Horo da hani na Allâhu ta'âlâ su ake kira **Ahkam-i-islamiyya** a dunƙule. Idan mutum yana aikata ɗaya daga cikin dokokin Ahka-i-islamiyya, wato idan yana aikata abin da aka hore shi ko ya bar abin da aka hane shi, kuma yana bin hukunce-hukuncen Mazhabar da ya zaɓa game da horo ko hanin, sai ya zamana ya gamu da haraj wajen bin hukuncin wannan Mazhabar a kan abin da ka aikata, to mutum zai zaɓi hukuncin da ya fi rauni (wanda wasu malamai na wannan Mazhabar suka yi). Idan akwai haraj a nan ma, sai ya yi koyi da wata Mazhabar daban a kan wannan batun. Idan akwai haraj wajen koyi da wannan Mazahabar ita ma, to sai ya duba ya gani ko akwai darurat wajen yin wannan abin da ke haddasa haraj:

1- Idan akwai lalura wajen yin wani abu da yake (farilla kuma yake) kawo haraj, za a ɗauke wa mutum aikata wannan farillar.

2- Idan babu lalura wajen aikata wani abu da yake kawo haraj, [misali kankare akaifa], ko kuma akwai lalura da wasu hanyoyi kaɗan na aikata wannan abin da mutum ya zaɓi ya yi da yake kawo haraj, aikin ibadar da aka yi (ta hanyar da ke kawo haraj) ba zai inganta ba. Dole a yi wannan ibadar ta hanyar da ba za ta kawo haraj ba. Za a iya koyi da wata Mazhaba idan har an gamu da haraj, ko tsanani, (idan mutum ya zaɓi hanyar da take kawo haraj),

ko da akwai lalura ko babu, an ruwaito a cikin littafin **Fatawa-i-hadithiyya** (wanda Ibn-i-Hajar-i-Mekki ‘rahimahullâhu ta’âlâ’, 899 hijiriyya [1494 miladiyya] – 974 [1566], Mekka), da littafin **Khulasa-t-ut-tahƙiƙ** (na Abd-ul-Ghani Nablusi ‘rahimahullâhu ta’âlâ’, 1050 [1640 miladiyya], Damuscus – 1143 [1731]), a sharhin da Tahtawi ‘rahimahullâhu ta’âlâ’ ya yi wa littafin Sherblali ‘rahimahullâhu ta’âlâ’ mai suna **Meraƙ-il-felah** da littafin **Ma’fuwat** na Halil Es’irdi ‘Allah ya yi masa rahama’. Molla Halil (Es’irdi) ya rasu a shekarar 1259 [1843 miladiyya.]. Musulmi mai bin Mazhabar Hanafiyya wanda yake son a yi masa ciko ko ya saka haƙorin makka ga haƙorinsa mai ciwo maimakon a cire shi ya riƙa amfani da haƙorin roba da za a iya cirewa, ya zama wajibi gare shi ya yi koyi da Mazhabar Shafi’iyya ko Malikiyya a wajen wanka. Saboda bai zama farilla ba a wadanan Mazhabobin mutum ya wanke bakinsa da shaƙa ruwa a hancinsa a wajen wanka. Kuma ya fi sauƙi mutum ya yi koyi da Mazhabar Shafi’iyya ko Malkiyya wajen yin wanka ko alwala, da kuma lokacin da zai fara sallah ko idan ya manta, bayan kammala sallah ko lokacin da mutum ya tuna. A nan wanka da alwala da kuma sallolin da mutum ya yi sun inganta a ƙarƙashin Mazhabobin Shafi’iyya da Malikiyya. Mazhabar Shafiyya ta ce ingancinsu shi ne, wajibi ne a sake alwala idan fatar namiji ta taɓa fatar mace wadanda ba sa cikin mata goma sha takwas da aka haramta wa mutum ya aura[1] ko idan tafin hannun mutum ya taɓa al’aurarsa da tafin hannunsa (wato gaba da duburarsa) da mutum ya karanta suratul Fatiha a cikin zuciya a sallar jam’i da ake yi tare da liman. A duba babi na shida na mujalladi na hudu a littafin **Endless Bliss** domin sanin abin da ya kamata a yi idan ana koyi da Mazhabin Malikiyya! Koyi da wata Mazhaba ba ya nufin mutum ya sauya Mazhabarsa. Mabiyin Mazhabar Hanafiyya wanda ya yi koyi da wata Mazhaba bai fita daga Mazhabarsa ta Hanafiyya ba. Ya yi koyi da wata Mazhaba ne a kan farillai da mufsidai ne kadai. Zai cigaba da amfani da Mazhabarsa a fannin Wajibai da makaruhai da sunnoni.

Maganganun malaman Fiƙihu a kan wanka suna nan, an ji wasu maganganun na yunƙurin warware mas’alolin da suka shafe haƙori, har da rubuce-rubucen mutanen da ba su cancanta ba, wadanda ba sa bin wata Mazhaba. Sun ce an fada a cikin wata fatawa da aka rubuta a shekarar 1332 [1913 miladiyya] wadda aka wallafa a wani littafi mai suna Sabil-ur-rashad, cewa an yadda mutum ya yi ciko a haƙorinsa. Abin da muke cewa a nan shi

[1] A duba babi na goma sha biyu a mujalladi na biyar na littafin Endless Bliss domin sanin mata da su halatta mutum ya aura ba.

ne tun da farko waɗannan litattafan suna cike ne da rubuce-rubucen waɗanda suka yi sauye-sauye ne da sauran mutane waɗanda ba su da Mazhaba.

Ɗaya daga cikin marubutan mai suna Isma'il Hakiki daga Manastir (Bitola), riƙaƙƙen ɗan freemason ne. Wani kuma Isma'il Hakki na Izmir shi kan gaban waɗancan wawayen, waɗanda Mahmet Abduh ya karkatar da tunaninsu, wanda ake kira babban malamin freemason na Alƙahira (Birnin Cairo) kuma mai sauye-sauye a Musulunci. Ya samu ilimin sakandare a Izmar sannan ya halarci makarantar horar da Malamai ta Istambul. Yana da ƙarancin ilimin addini. Ya samu goyon bayan 'ya'yan jam'iyyar Union, ya zamo malamin makaranta, inda ya yi yunƙurin yaɗa aƙidar Abduh. A cikin yabon da ya rubuta a littafin **Talfiƙ-i-madhahib**, fassara daga Rashid Rida na ƙasar Misira (Egypt), wallafar Ahmed Hamdi Akseki, ɗaya daga cikin almajiransa da suka kurɓi gubar yaudararsa ya cutar da kansa.

Wannan mutum Isma'il Hakki a cikin waɗancan rubuce-rubuce game da maganganun Malaman Fiƙihu a kan ko ya halatta a ɗaure haƙora da waya ta zinari ya fitar da wasu littatafai, misali sharhin littafin (Muhammad Sheybani mai suna) **Siyar-i-kabir**, wanda yake magana a kan ijma'in Malamai waɗanda suke ganin akwai lalura wajen ɗaure haƙora da waya ta zinari maimakon ta azurfa, ya ce batun da ya shafi haƙoran lalura ce. Amma tambayar da aka yi masa ita ce shin ko wankan wanda aka yi wa ciko a haƙori ya inganta, ba batun ɗaure haƙora da waya ta zinari ko azurfa ba. Ya yi rubutu mai tsawo a kan abin da ba shi aka tambaye shi ba, wanda kuma an riga an sanshi, Isma'il Hakki na Izmar ya kammala da bayar da amsa da abin da aka tambaye shi. Abin da ya yi shi ne kusan gurɓata ilimi. Yunƙuri ne kawai na mutum ya bayyana ra'ayin kansa a matsayin cewa ya bayar da fatawa daga Manyan malaman Musulunci. Munin manufar tasa ya wuce haka. Ya yi ɗauko maganganun manyan Malaman Fiƙihu a kan wanka ya kawo su bisa ra'ayinsa. Misali ya ce, "Kamar yadda aka faɗa a Bahr, ba wajibi ba ne ruwa ya taɓa wuraren da suke da wahala ruwan ya kai ba." A ɗaya ɓangaren kuma, abin da aka rubuta a **Bahr** shi ne: "…sashen jiki inda yake da wahala ya kai." Don haka yake son abin da wani ya yi mai muhimmanci a kan abin da wani ya ji a jikinsa mai muhimmanci. Kuma ba a kan daidai yake ba wajen amfani da maganganunsa cewa, "idan wanke kai zai cutar da mace, to kada ta wanke kanta," wanda yake rubuce a cikin **Durr-ul-mukhtar**, a matsayin hujjar cewa mutumin da ya yi wanka da ciko a haƙorinsa ya zama jaiz (ya halatta). Jin zafi idan ruwa ta jiƙa kai yana faruwa ne sakamakon ciwo na sarari. Sanya haƙorin makka ko yin ciko wani abu ne da mutum ya zaɓi ya yi. Bisa wannan dalili aka tattauna batun maƙalewar abinci a cikin dasashi daban a cikin littafin **Durr-ul-mukhtar**.

Wannan yaudarar da aka bayyana ya nuna ƙarara irin mugunta da Isma'il Hakki na Izmar ya ƙulla. Idan an lura ya nuna ƙarancin aƙida bisa yunƙurin da yayi na ɗora dalilan Malamai a kansa ta hanyar cewa "Ba sharaɗi ba ne (na wanka) sai ruwa ya taɓa ƙarƙashin haƙorin makka na zinare ko na azurfa ko wanke ƙarƙashinsu. Malaman Fiƙihu sun yi ittifaƙi cewa akwai lalura a kan wannan haƙorin, don haka ba wajibi be ne sai ruwa ya jiƙa shi (wannan ɓangaren na jiki) a matsayin lalura." Babu wani Malamin Fiƙihu a Mazhabar Hanafiyya da ya ce lalura ne mutum ya sanya haƙorin makka ko a yi ciko. Asali ma a zamanin da Malaman Fiƙihun suka rayu, ba a fara sanya haƙorin makka ba. A cikin shafi sittin da huɗu na sharhin littafin **Siyar-i-kabir**, wanda ya kawo a matsayin hujja, an ruwaito Imam Muhammad Sheybani 'rahimahullâhu ta'âlâ' yana cewa ya halatta ga mutum ya sanya haƙorin zinari a inda haƙorinsa ya cire ko ya ɗaure haƙoransa da wayar zinari. Littafin bai yi magana kan sanya haƙorin makka ba. 'Yan ƙungiyar Firimason da suke cikin addini, waɗanda ba su da takamammiyar Mazhaba da aƙida, waɗanda suka bayyana daga baya, suna ɓugewa da yaudara domin cutar da Musulmi da nufin tunzura su. Suna rubuta maƙalu waɗanda ba su a kan daidai.

Imam Muhammad Sheybani 'rahimahullâhu ta'âlâ' ya ce haƙori da yake girgiɗi (rawa) ana iya ɗaure shi da wayar zinare ko azurfa. Bai ce ya halatta rufewa ko cike haƙori ba. Waɗannan maganganun Isma'il Hakki da ire-irensa suka cusa su.

Malamai masu fatawa da sauran muhimman mutane a cikin addini da suka yi zamani da Isma'il Hakki na Izmar, sun bayar da amsa domin tantance gaskiya da abin da ba gaskiya ba game da waɗannan rubuce-rubucen na yaudara, waɗanda aka zayyana a baya. Ɗaya daga cikin manyan Malaman shi ne Yunus-zade Ahmed Ɓahbi Efendi na Bolɓadin (ƙasar Turkiyya). 'Allah ya yi masa rahama'. Masani ne mai zurfin ilimin addini, ya tabbatar da cewa manyan Malaman Musulunci sun yi ittifaƙi game da batun wankan mutumin da wani abu ya maƙale a cikin dasashinsa cewa wankansa bai inganta ba.

Shugabannin mujallar mai suna **Sebil-ur-rashad** sun lura da ƙarancin hujja ga yaudarar da ke cikin rubuce-rubucen na Izmirer, don haka suka ga ya zama wajibi su agaza wa rubutun da ƙarin hujjoji ta hanyar sanya fatawar da ta kammala da cewa "…wankan ya inganta," a bugu na biyu na littafin fatawa mai suna **Majmu'a-i-Jadida** wanda aka buga a shekarar 1329H [1911 M.]. Sai dai wannan fatawar babu ita a bugu na farko na littafin, wanda aka yi a shekarar 1299 H. An cusa wannan ruɗani ne a cikin bugu na biyu, wanda Musa Kazim ya yi jagoranta, wato wani shaikh-ul-islam da jam'iyyar Union

ta nadַa. Saboda haka Mujallar Sebil-ur-Rashad suka yi yunkurin cusa maganganun da ‘yan firimason suka kirkira domin goyon baya ga rubutun wani malami ya yi. Babu wani Malamin Fiqihu ko dַaya da ya ce ‘lalura ne’ sanya hakorin makka ko yin ciko ga hakori. Mutanen da suke fadַa ko suka rubuta haka, ko dai ‘yan firimason ne na addini ko kuma Malaman zamani ko kuma wadַanda ba su da Mazhaba ko jahilan Musulmai wadַanda wahabiyawa suka yaudara.

Ahmad (bin Muhammad bin Isma’il) Tahtawi Allah ya yi masa rahama’ ya fadַa a cikin ta’aliqinsa na littafin Shernblali mai suna **Merak-il-falah**: “Idan mutum ya (bi jama’a, kuma ya) yi koyi da Liman (wajen gudanar da sallar jam’i, yake) bin dַaya daga cikin sauran Mazhabobi uku, to sallar da ya yi (a bayan wannan limamin) ta inganta, tare da cewa ba a samu wani abu tare da limamin ba wanda yake ɓata sallah a Mazhabarka (ko da abin baya ɓata sallah a Mazhabar Limamin) ko, kuma ya zamana abin da yake ɓata sallar a Mazhabarka bai fito fili ba a jikin Limamin a lokacin da kake bin shi. Wannan shi ne batun da ya fi shahara, idan sallar Limamin ta inganta a Mazhabarsa, to ya inganta a bi shi sallah ko da sallarsa ba ta inganta ba a Mazhabarka.” Haka hukuncin yake a cikin littafin Ibni ‘Abidin. Abin da aka fahimta daga wannan batun wanda aka rubuta a cikin ta’aliqin Tahtawi da littafinsa ‘Allah ya yi masa rahama’, akwai saɓanin malamai guda biyu game da ko sallah ta inganta ga Musulmi mai bin Hanafiyya wanda ba shi da hakorin makka ko ciko a hakori wadda ya yi cikin jam’i a bayan Limamin da yake da hakorin makka ko ciko a hakori: dַaya zancen ya nuna cewa bai inganta ba ga mabiyin Hanafiyya marar hakorin makka ko ciko a hakori ya bi Limamin da yake da ciko ko hakorin makka. Dַaya kaulin kuma ya nuna cewa idan Limamin da yake bi mabiyin Mazhabin Shafi’iyya ko Malikiyya ne ya inganta mabiyin Hanafiyya da ba shi da hakorin makka ko ciko a hakori ya bi shi sallah. Wannan shi ne ijtihadin Imam Hinduwani ‘rahmatullâhi ’alaih’. Wannan hukuncin ya shafi har wanda yake koyi da Mazhabar Shafi’iyya. Sai dai idan an san cewa salihin Limamin baya koyi da Mazhabar Malikiyya ko Shafi’iyya, mabiyin Hanafiyya wanda ba shi da hakorin makka ko ciko a hakori zai iya bin sallar jam’i bayan wannan Limamin. Bai halatta a tambaye shi ko yana koyi da Mazhabar Malikiyya ne ko Shafi’iyya a wajen sallah. Wannan zancen na karshe shine mai rauni. Amma kamar yadda muka bayyana a baya a cikin littafin, idan akwai haraj (tsanani) wajibi ne a yi aiki da zance mai rauni (da’if). Wajibi ne a yi amfani da kauli mai rauni don guje wa afkawa cikin fitina, an ruwaito a cikin **Hadika** ma. Idan mutum baya koyi da dַaya daga cikin wadַannan Mazhabobin hudu, kuma ba ya aikata ibada bisa koyarwar litattafan Fiqihu, ya tabbata cewa shi ba Ahl as-sunnat ba ne. mutumin da ba Ahl as-sunnat ba, ko dai ya zamo dַan

bidi'a ko marar alƙibla, ko kuma ya rasa imaninsa gaba ɗaya, ya zama murtad (wanda ya yi ridda). Ba a ce kar mutum ya yi ciko a haƙori ko kada ya saka haƙorin makka ba. Illa muna nuna wa 'yan uwa maza da mata da suka yi hakan yadda za su yi ibada karɓaɓɓa. Muna nuna masu hanyoyi masu sauƙi.

Akwai ire-iren wanka guda goma sha biyar: Biyar daga ciki farilla ne, biyar kuma wajibai ne, sai guda huɗu kuma sunnah ne, sannan guda ɗaya mustahabbi. Wankan da yake farilla su ne: wankan haila ga mace ('yan mata) idan jini ya ɗauke mata, da bayan saduwa, wato jima'i, da bayan fitar maniyyi ta hanyar jin daɗi, da idan an ga maniyyi a wajen kwanciya ko a wando bayan yin mafarki, farilla ne a yi wanka kafin lokacin sallar da ta riske ka ya fita.

Wanka da yake wajibi shi ne: Yi wa Musulmi wanka idan ya mutu, da yin wanka ga yaro idan ya balaga. Idan mata da miji suka kwana a gado ɗaya, suka ga maniyyi a tsakaninsu, kuma ba su san na waye a cikinsu ba, wajibi ne su duka su yi wanka. Haka nan idan mutum ya ga maniyyi kuma bai san tun lokacin da ya fito ba, shi ma wajibi ne a yi wanka. Kazalika idan mace ta haihu ko da jini bai fito ba wajibi ne ta yi wanka. (Farilla ne yin wanka idan jini ya fito.)

Wankan da yake sunnah shi ne: Yin wanka domin sallar Juma'a, da ranar sallar Idi, da lokacin ɗaukar Ihiramin Hajji a kan kowace niyya mutum yake, da ranar tsayuwar Arfa[1] Wankan da yake mustahabbi:

Idan kafiri ya Musulunta, amma farilla ne ya yi (ko ta yi) wanka idan ya zamana a lokacin da ya (ko ta) musulunta yana (ko tana) tare da janaba, (wanda hakan yana wajabta wanka.) Idan ba haka ba Mustahabbi ne a gare su yin wakan.

Akwai abubuwa uku da aka haramta a wanka:

1-Bayyana sashen jiki ga maza da mata daga ƙasan cibiya zuwa ƙasan guiwa a gaban wasu mutane da suke jinsi ɗaya idan suna wanka; (wato haramun ne maza su bayyana jikinsu daga cibiya zuwa guiwa ga 'yan uwansu maza, haka nan mata su bayyana wannan sashen jikin ga 'yan uwansu mata sa'ilin da suke wanka).

2- Wani ƙaulin ya ce haramun ne mata Musulmi su nuna jikinsu ga mata kafirai idan suna wanka. (Wannan hukuncin ya shafi kowane lokaci, ba wanka kaɗai ba).

---

[1] A duba cikin babi na huɗu a mujalladi na huɗu na littafin Endless Bliss, Wanka kuma a dubabbi na bakwai a mujalladi na biyar domin ƙarin bayani akan 'Hajj.'

3- Ɗarnar ruwa; (wato haramun ne a yi amfani da ruwan da ya wuce kima a lokacin wanka).

A Mazhabar Hanafiyya, akwai sunnoni guda goma sha uku da ya kamata a aikata yayin da mutum yake wanka:

1- Yin istinja da ruwa. Wato wanke dubura da al'aura.

2- wanke hannuwa zuwa ku'i (wuyan hannu).

3- Idan akwai wata najasa a jiki, a kawar da ita.

4- Kai maƙura wajen yin mazmaza da istinshaƙ. (Mazmaza shi ne kurkurar baki da ruwa, istinshaƙ kuma yana nufin shaƙa ruwa a hanci.) Wanka ba zai inganta ba idan akwai wani ɗigo da ruwa bai taɓa ba a cikin baki ko hanci. Da yin alwalar sallah idan mutum zai fara wanka.

5- Ɗaura niyyar yin wanka.

6- Cuɗa dukkan gaɓɓai da hannu idan ana zuba ruwa a kai.

7- Farawa da zuba ruwa a kai, sannan a zuba a kafaɗar dama da ta hagu sau uku-uku.

8- Tsattsefe yatsun hannu da na ƙafa.

9- Kar a fuskanci, ko bayar da baya ga Alƙibla.

10- Kar a yi magana da shafi duniya idan ana wanka.

11- Kurkure baki da shaƙa ruwa sau uku-uku.

12- Fara wanke kowace gaɓa daga ɓangaren dama.

13- Kar a yi fitsari a wajen da ake wanka, idan ruwa na kwanciya a inda ake wankan. Akwai wasu sunnonin baya ga waɗannan da aka lissafa.

ADDU'AR TAUHIDI

Ya Allah, ya Allah. La ilaha il-l-Allah Muhammadun Rasulullah. Ya Rahman, ya 'afuwwu ya Karim, fa'fu'anni wa-r-hamni ya arham-ar-rahimin! Tawaffani Musliman wa al-hiƙni bi-s-salihin. Allahummagfirli wa li-abai wa ummahati wa li aba-i wa ummahat-i-zawjati wa li-ajdadi wa l-abnai wa banati wa li-ihwati wa ahawati wa li-a'mami wa ammati wa li ahwali wa halati wa li ustazi 'Abd-ul-Hakim-i-Arwasi wa li-kaffa-t-il-mu'minina wa-l-mu'minat. 'Rahmatullahi ta'ala 'alaihim ajma'in'.

BABI KAN HAIDH DA NIFAS

(Jinin Al'ada da na Haihuwa)

Ƙarancin wa'adin jinin al'ada kwanaki uku ne, yawanci kuma kwanaki goma ne. Babu ƙaranci kwanaki ga jinin Haihuwa. Idan jinin ya ɗauke wajibi

ne a gaggauta yin wanka a cigaba da sallah da azumi. Yawancin wa'adin kwanakinsa arba'in ne. Idan jinin al'ada ya ɗauke kafin kwanaki uku, mace za ta rama sallolin da suka kubce, saboda ba jinin al'ada[1] ba ne kamar yadda take tunani. Wanka bai wajaba ba a irin wanna lamarin. Idan jinin ya ɗauke bayan kwanaki uku, sai ta yi wanka ta cigaba da sallah a lokacin da ta tabbatar jinin ya ɗauke. Idan kwanaki goma suka cika, za ta yi wanka ta cigaba da ibada ba tare da la'akari da jinin ya ɗauke ko yana zuba ba. Idan kwanaki arba'in suka cika ga mai jinin haihuwa, za ta yi wanka ta cigaba da sallah ba tare da la'akari da ko jinin ya ɗauke ko yana zuba ba. Duk wani abin da yake fita a lokacin jinin al'ada ko na haihuwa, an ɗauke shi matsayin jinin ne, (ko a wane irin launi ya zo).

Idan jini ya ɗauke cikin wasu kwanaki tsakanin kwanaki goma na al'ada ko kwanaki arba'in na haihuwa, sai ta yi wanka ta cigaba da azumi, saboda tana zaton jinin ya ɗauke, daga baya sai jini ya sake dawo mata a tsakanin waɗannan kwanakin, za ta rama azumin da ta yi a wannan lokacin. Sannan za ta sake yin wanka idan jinin ya ɗauke. Idan jini ya ɗauke mata ba kamar yadda ta saba ba, amma bayan kwanaki uku da farawa, sai ta yi wanka ta cigaba da sallah. Sai ba za ta sadu da mijinta ba har sai kwanakinta na al'ada sun cika. Haka hukuncin yake har a jinin haihuwa. Idan jinin ya ɗauke bayan kwanakinta na al'ada[2] kuma tsakanin kwanaki goma na shari'a ko kafin haka, to wannan lokacin gaba ɗaya na halarta ne. idan jinin bai ɗauke ba, ya cigaba har bayan kwanaki goma, to jinin da ya zuba bayan kwanakinta na al'ada ba na haila ba ne, za ta rama sallolinta na kwanakin da ta ƙara, (wato bayan kwanakinta na al'ada). Haka hukuncin yake ga kwanaki arba'in na jinin haihuwa.

Idan haid (jinin al'ada) ko nifas (jinin haihuwa) ya ɗauke kafin lokacin shan ruwa a cikin watan azumin Ramadan, za ta kame bakinta daga cin abinci da shan abin sha kamar mai azumi. Amma ba zai zamo matsayin azumi ba. Za ta rama azumin wannan ranar, (wato za ta yi azumi ɗaya bayan sallah). Idan jinin ya zo mata kafin faɗuwar rana, ko da ya zamo da rana ne, za ta cigaba da cin abinci a ɓoye. Zance na gama gari shi ne idan mace ta ga jini

---

[1] Ramu wata ibada ta farilla na nufin aikata wannan abun bayan lokacin ya wuce.

[2] Tazarar dake tsakanin lokacin da mace taga jini zuwa lokacin da ya tsaya mata shi ake kira 'âdat. A mazhabar Hanafi ƙarancinta kwana uku ne mafi tsawonsu kuma kwana goma, A mazhabar Shafi'i da Hanbali mafi ƙarancinta kwana ɗaya ne mafi tsawonta kuma kwana goma sha biyar. A duba shafi na hamsin wallafa goma sha huɗu a 2008 a mujalladi na na huɗu na littafin Endless Bliss domin cikakken ƙarin bayani.

ya zo mata za ta dakatar da sallah da azumi. Amma idan ya ɗauke kafin rana ta uku ta ƙare, za ta jira har sai lokacin sallar da ya riske ta ya kusa fita a, idan jinin ya dawo, ba za ta yi sallar ba, idan jinin bai dawo ba, za ta yi alwala ta yi sallah, idan aka ƙara ɗaukar lokaci jinin bai dawo ba, za ta yi alwala ta cigaba da sallolinta, idan jinin ya dawo sai ta dakatar da yin sallah. Idan jinin ya sake ɗauke wa, za ta sake jira har sai lokacin sallah ya kusa fita, sai ta sake alwala ta yi sallah, idan jinin bai sake dawowa ba. Za ta cigaba da haka har kwanaki uku su cika, amma ba za ta yi wanka ba kafin kwanaki ukun.

Alwala kaɗai ta isar mata. Idan jinin ya ɗauke bayan kwanaki uku za ta sake jira har sai lokacin sallah ya kusa fita sai ta yi wanka ta cigaba da sallah, idan jinin bai sake dawowa ba, idan ya sake dawowa, sai ta dakatar da sallah, haka za ta cigaba har kwanaki goma sannan ta yi wanka ta cigaba da ibada, ko da jinin bai yanke ba. Haka hukuncin yake a jinin haihuwa. Amma wanka ya wajaba a duk lokacin da jinin ya ɗauke, ko da a ranar farko ya ɗauke. A watan Ramadan idan jinin ya ɗauke kafin fitowar alfijir, za ta ɗauki azumin wannan ranar. Idan jinin ya dawo mata da rana ko da almuru, azuminta ya kare. Za ta rama wannan azumin (bayan sallah).

Idan mace ta yi ɓarin ciki, hukuncin daidai yake da haihuwar jaririn da bai zo da rai ba, idan har halittar wata gaɓa ta bayyana a jikinsa, wato gashi ko baki ko hanci. Idan babu wata gaɓa da ta bayyana, to ba zai zamo hukuncin jinin haihuwa ba. Amma idan jinin ya cigaba da zuba har tsawon kwanaki uku, zai zamo hukuncin jinin al'ada (haila). Amma jinin bai zamo na al'ada ba idan tsakanin ɓarin cikin da lokacin da jinin al'ada ya ɗauke mata ya kai kwanaki goma sha biyar ko fiye da haka, kuma wa'adin jinin bai kai kwanaki uku ba, ko kuma ba a ƙarasa kwanaki goma sha biyar ba da jinin al'adarta ya ɗauke. Hukuncinsa kamar jini ne da yake fitowa daga hanci. Za ta yi sallolinta. Za ta yi azuminta. Wanka bai wajaba a kanta ba kafin ta kwanta da mijinta.

[Wani Shahararren Malamin Musulunci (Zeyn-ud-din) Muhammad Birgiɓi (bin 'Ali) 'rahmatullâhi 'alaih' (928 [1521 Miladiyya.], Balikesir – na annoba a 981 [1573], Birgi, Aydin, Ƙasar Turkiyya), ya rubuta wani littafi mai daraja mai suna **Zuhr-ul-mutaahhilin** inda ya yi bayani game da jinin al'ada da na haihuwa. An rubuta littafin ne da harshen Larabci. 'Allama Shami Sayyid Muhammad Emin (ko Amin) bin 'Umar bin 'Abd-ul-'Aziz Ibni 'Abidin 'rahmatullâhi 'alaih' (1198 [1784 miladiyya], Dimashƙ – 1252 [1836], Dimashƙ) ya faɗaɗa littafin ya sanya masa suna **Menhel-ul-waridun**. Ga (kaɗan daga) abin da aka rubuta a littafin na **Menhel** (-ul-waridun): Malaman Fiƙhu sun yi ittifaƙin cewa farilla ne ga dukkan Musulmi mace da namiji, su koyi (ilimin Musulunci da ake kira) 'ilm-i-hal. Wato mata da

mazajensu na aure wajibi ne su san hukunce-hukuncen jinin al'ada da na haihuwa. Maza su koyar da matansu, idan ba su sani ba, su bar matan nasu su koya daga wajen wasu 'yan uwansu mata da suka sani. Macen da mijinta ya hana ta fita ta koya, wajibi ta fita ba tare da izininsa ba domin ta koya. Waɗannan hukunce-hukuncen da suka shafi mata, ba a ba su kulawar da ta dace ba, yanzu kusan masana addini da daman gaske ba su san su ba. Malaman wanna zamanin ba su da ilimi sosai a kan bambancin da ke tsakanin jinin al'ada (haid) da na haihuwa (nifas) da cuta (istihadha). Ba su da litattafai da suka yi cikakken bayani a kan haka. Waɗanda kuma suke da litattafan ba sa iya karantawa su fahimce su. Saboda hukunce-hukuncen suna da matuƙar wahalar fahimta. Yayin da sauran al'amurran addini da suka shafi alwala da sallah da karatun Alƙur'ani mai girma, da azumi da ittikafi da hajji, da balaga da aure da saki da wa'adin lokacin idda da istibra'i da makamantansu, suna buƙatar a samu ilimi game da waɗannan jinin. Ni ma ya ɗauke ni kusan rabin rayuwata kafin in fahimci hukunce-hukuncensu. Zan yi ƙoƙari in yi cikakken bayani a taƙaice game da abin da na sani domin amfanin 'yan uwana mata Musulmi:

Haid (Haila) shi ne jinin da yake fitowa daga farjin mace lafiyayya (aƙalla) da zarar ta shekara takwas, ko ga mace da ta cika kwanakinta na tsarki bayan jini ya ɗauke mata, wanda ya haura kwanaki uku. Wannan jinin ana kiransa **ingantaccen jini**, (ko ingantaccen jinin al'ada). Idan jinin bai zo ba tsawon kwanaki goma sha biyar ko fiye, bayan kammala kwanakin al'ada, waɗanda ke tsakanin jinin al'ada biyu, wannan lokacin ana kiransa **ingantaccen lokacin tsarki**. Idan aka samu kwanakin fasid kafin ko bayan kwanaki sha biyar na ingantaccen lokacin tsarki, dukkan waɗannan kwanakin (da aka samu jinin fasid) ana kiransu **lokacin tsarkin hukmi** ko **lokacin tsarkin fasid**. Lokacin da mace ta shafe batare da jini ba, wato cikin tsarki wanda ba su kai kwanaki sha biyar ba su ake kira tsarkin fasid. Ingantaccen lokacin tsarki da lokacin tsarkin hukmi ana kiransu **cikakkun lokuttan tsarki**. Jinin da ya zo kafin ko bayan cikakken lokacin tsarki suka kuma kai kwanaki uku, to jini biyu ne daban-daban na haila.

Duk nau'in kalar da jinin ya zo da ita idan ba fari ba ne sal, ko da ya yi kalar giza-gizai, to jinin al'ada ne.

Idan yarinya ta fara jinin al'ada, to ta zamo **baligha**, (wato ta kai munzalin balaga). Ta zama cikakkar mace ke nan. Kwanakin da aka shafe daga lokacin da jini ya zo zuwa lokacin da jinin ya ɗauke, shi ne lokacin **'adat** (al'ada ko haila). Lokacin al'ada kwanaki goma ne tsanani. Ƙaranci kuma kwanaki uku. A Mazhabar Shafi'iyya da ta Hambaliyya kwanaki sha biyar ne tsanani, ƙaranci kuma kwana ɗaya.

Ba dole ba ne jinin al'ada ya zamo mai kwarara ba ƙaƙƙautawa ba. Idan jinin ya zo, kuma ya ɗauke, sannan ya sake dawowa bayan kwana ɗaya ko biyu, lokacin da aka ɗauka jinin bai zo ba ƙasa da kwanaki uku, za a haɗa da su cikin kwanakin al'ada, kamar cewa jinin yana zuba ne koda yause, bisa ittifaƙin manyan Malamai. Idan ɗaukewar jinin ta kai kwanaki uku ko ta wuce haka, amma ya ɗauke baki ɗaya kafin kwanaki goma, shi ma za ɗauka cewa jinin yana ta zuba ne kullum, kamar yadda aka ruwaito daga Imam Muhammad 'Allah ya yi masa rahama' ya karɓo daga Imam A'zam Abu Hanifa 'Allah ya yi masa rahama'. Akwai wani zancen na Malamai wanda Imam Muhammad ya ruwaito. A ɗayan ɓangaren kuma, Imam Abu Yusuf 'Allah ya yi masa rahama' ya ce, dukkan kwanakin da jini ya ɗauke kafin kwanaki sha biyar, za a ɗauke su ne a matsayin kamar jinin yana fita kullum. Idan jini ya ɗauke wa yarinya bayan kwana ɗaya, sai bayan kwanaki sha huɗu jinin ya sake dawowa; ko idan jini ya ɗauke wa mace bayan kwana ɗaya, bayan kwanaki goma ya sake dawowa na kwana ɗaya, ko kuma jinin ya ɗauke bayan kwanaki uku, sannan ya sake dawowa bayan kwanaki biyar; kwanaki goman farko da yarinyar ta yi su ne kwanakinta na al'ada, inji Imam Abu Yusuf. Ita kuma macen kwanakinta da ta saba su ne na al'ada, duk sauran kwanakin da suka biyo baya sun zamo na Istihada (rashin lafiya). Dukkan kwanaki taran da ta yi na al'ada ne. bisa ruwayar Imam Muhammad 'Allah ya yi masa rahama' ta farko, kwanaki taran kaɗai ne na al'ada (haila) ga macen.

A ruwayar Imam Muhammad ta biyu, ya ce kwanaki uku na farko ga macen, su ne kwanakinta na al'ada amma ban da sauran. An fassara daga littafin **Multeƙa** (ko Multaƙa) a cikin wannan littafin, mun rubuta dukkan waɗannan bayanai ne akan turbar ruwayar Imam Muhammad ta farko. Kwana ɗaya (a ma'ana) yana nufin sa'o'i ishirin da huɗu. Mustahabbi ne sanya kaɗa (auduga, pad ko ƙyalle) da ake kira kursuf, ga macen da ba ta taɓa aure ba a lokacin da take al'ada, ga matar aure kuma a kowane lokaci ta saka auduga ko ƙyalle a ƙofar farjinsu, tare da sanya turare a kai. Makaruhi ne mace ta tura audugar gaba ɗaya a cikin farjinta. Idan budurwa ta riƙa ganin jini a audugar tsawon wata guda, a nan sai ta ɗauki kwanaki goman farko a matsayin na al'ada, sauran kwnaki ishirin kuma su zama na rashin lafiya. Wannan hukuncin zai cigaba har sai lokacin da wannan zubar jinin mai suna **istimrar** ya ɗauke. Idan jini ya zo wa budurwa tsawon kwnaki uku, ya ɗauke na kwana ɗaya, ya dawo na kwana ɗaya, sannan ya ɗauke na kwanaki biyu jere, ya sake dawowa na kwana ɗaya, ya sake ɗaukewa na kwana ɗaya, har kwanaki a haka, to dukkan kwanaki goman na al'ada ne. Idan jini ya zo mata na kwana ɗaya, ya ɗauke kwana ɗaya, ya sake dawowa kwana ɗaya, ya cigaba da haka har kwanaki goma a kowane wata, za ta dakatar da sallah ta

ajiye azumi a duk ranakun da jinin ya zo, a ranakun da bai zo ba kuma za ta yi wanka ta cigaba da ibadarta [Mesail-i-sharh-i-wikaya][1]. Idan jini ya zuba ƙasa da kwanaki uku, wanda ya yi daidai da sa'o'i saba'in da biyu, ko da ya gaza da mintuna biyar ne, ko ga yarinyar da ta fara jinin al'ada, wanda ya cigaba har bayan kwanaki goma, idan ya cigaba har bayan kwanaki goma, ko ga macen da ta saba, wanda ya cigaba da fitowa bayan kwanakinta na al'ada, har ya wuce kwanaki goma na shari'a, ko wanda ke zo wa mace mai ciki ko aisa [tsohuwa] ko ga ƙaramar yarinya da ba ta shekara tara ba, ba jinin al'ada ba ne, na **istihada** (rashin lafiya) ne ko jinin fasid. Mace tana zama aisa ne daga shekaru hamsin da biyar. Idan al'adar mace ta zamanto kwanaki biyar ne, jini ya zo mata a lokacin da rana ta ɓullo kaɗan, sannan ya ɗauke bayan ranar ta ƙara ɗagowa, a safiyar rana ta sha ɗaya, to jinin da ya zuba bayan kwanaki biyar na al'adarta ya zamo na istihada (rashin lafiya). Domin saboda jinin ya wuce yini goma da dare goma na shari'a da ɓullowar rana. Idan kwanaki goman suka wuce sai ta yi wanka, kuma ta rama sallolin da suka kuɓuce mata a bayan kwanakinta na al'ada.

Macen da take fama da matsalar istihada tana cikin mutane masu 'udhr (lalura), kamar wanda yake fama da matsalar yoyon fitsari ko haɓo ne. Za ta yi salloli da azuminta, da saduwar aure.

A wani ƙauli na Imam Muhammad, ya ce idan budurwa ta fara ganin jini a karon farko a rayuwarta, sai ya ɗauke bayan kwana ɗaya, ya sake dawowa bayan kwanaki tara, to dukkan kwanaki goman na al'adarta ne. Amma idan jinin ya ɗauke bayan kwana ɗaya, ya kuma dawo bayan kwanaki goma sha ɗaya, to duka biyun ba jinin al'ada ba ne. Duka jinin na kwanakin biyu sun zama istihada.

Kamar yadda aka faɗa da farko, kwanakin da jini ya ɗauke har zuwa waɗanda wani jinin ya dawo bayan kwanaki goma na shari'a, ba a lissafa su cikin kwanakin al'ada. Idan jinin ya zo a rana ta goma da rana ta sha ɗaya to za a lissafa waɗancan kwanakin da jinin bai zo ba a tsakani a matsayin na al'ada, wato kwanaki goma za su zama na al'ada, kwana na sha ɗaya kuma ya zama na istihada.

Jinin da ake kira istihada, alamu ne na rashin lafiya. Idan zubar jinin ta yi yawa, ta kan iya zama haɗari. Wajibi a je wajen likita ya duba. Akwai wani sinadari da ake kira dragon's blood yana tsayar da zubar jinin, idan aka sha da ruwa sau biyu a rana, giram ɗaya da safe, ɗaya da yamma. A shawarce

[1] Wannan littafin a yarin Farisanci aka rubuta shi, na 'Abd-ul-Haƙƙ Sujâdil Serhendî 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih'.

dai kada a wuce giram biyar a kowace rana. Kwanakin jinin al'ada na mace da kwanakinta na tsarki duk ɗaya ne a kowane wata. Wata ɗaya a nan ana nufin tsawon kwanakin da mace ta fara jinin al'ada zuwa ranar da za ta sake wata al'adar.

Wajibi ne ga kowace mace ta hardace kwanaki da sa'o'in da take al'ada, da na lokacin da take cikin tsarki. Al'adar mace ba ta cika sauyawa ba tsawon shekaru. Idan ta sauya, wajibi ta hardace sabon tsarin kwanakin nata na al'ada da na tsarki.

A cikin littafin **Menhel** (ul-waridin) an kawo wannan sharaɗin ga macen da kwnakin al'adarta suka sauya: Idan mace tana jinin al'ada daidai da kwanakin da ta saba a baya, to an tabbatar da cewa kwanakin al'adar ba su sauya ba. Idan kwanakin ba su zo daidai ba, to al'adarta ta sauya, don haka za a yi bayanin sauyin a nan gaba kaɗan. Idan kwanakin suka sauya sau ɗaya, to an amince da cewa al'adarta ta sauya. Akwai wannan hukuncin a cikin fatwa. Macen da take kwanaki biyar na jinin al'ada, ta ga jini ya zo mata a rana ta shida bayar ingantaccen tsarki, waɗannan kwanaki shidan su ne sababbin kwanakinta na al'ada. Haka nan a karo ɗaya kwanakin tsarki ma suna sauyawa. Idan suka sauya, kwanakin al'ada ma za su sauya. Misalin idan kwana biyar mace take yi na al'ada, sannan ta yi kawanki ishirin da biyar na tsarki; sai jinin ya koma kwanaki uku a sabuwar al'adarta, kwanaki ishirin da biyar na tsarki, ko kwanaki biyar na al'ada, kwanaki ishirin da uku na tsarki, to adadin kwanakin al'adarta da na tsarki duka sun sauya. Haka nan idan jinin ya wuce kwanaki goma na shari'a, ta fara jinin fasid, kuma kwanaki uku ko fiye na ƙarshe na jinin fasid suka yi daidai da kwanakin al'adarta na baya, sannan sauran kwana na ƙarshe na al'adarta ya daidaita da sababbin kwanakin tsarkinta, kwanakin da suka yi daidai da na al'adarta ta baya, su ne sababbin kwanakinta na al'ada. Daga lokacin kwanakin al'adarta sun sauya. Idan al'adarta kwanaki biyar ne, sai jinin ya zo kwanaki bakwai kafin ƙarewar lokacin tsarkinta, kuma jinin ya cigaba da fitowa har kwanaki sha ɗaya, wannan jinin fasid ne, domin ya zarce kwanaki goma. Wato kwanaki huɗun suna cikin kwanakinta na al'ada, wannan kwana ɗayan ya faɗa cikin sababbin kwanakinta na ingantacciyar al'ada. Al'adarta ta koma kwanaki huɗu, duk da cewa wa'adin lokacin da jinin ya zo bai sauya ba. Bari mu yi ƙarin haske game da wannan mas'alar ta sauyi a jinin al'ada:

Idan sababbin kwanakin na al'ada da adadinsu ya sauya, suka bambanta da waɗanda suka gabace su, suka cigaba fiye da kwanaki goma, kuma kwanaki uku ko huɗu ba su yi daidai da na al'adar da ta gabata ba, wa'adin lokacin da jinin ya zo ya sauya. Adadin kwanakin (na al'ada) bai ƙaru ba, kuma sun fara ne daga ranar da jinin ya zo. Idan jini bai zo wa mace a

kwanaki biyar da ta saba al'ada ba a wata, ko jinin bai zo ba a cikin kwanaki uku na farko, daga nan kuma jinin ya zo har tsawon kwanaki sha ɗaya, kwanaki biyar ne kaɗai na al'adarta, daga ranar da jinin ya zo; amma kwanakin al'adarta sun sauya. Idan kwanaki uku ko fiye na sabuwar al'adar suka yi daidai da kwanakin da ta saba, waɗannan kwanaki ukun ko fiye kaɗai su ne na al'ada, sauran kwanakin na istihada (rashin lafiya) ne. idan jinin ya zo kwanaki biyar kafin lokacin da ta saba, sannan ba ta ga jini ba a kwanakin da ta saba, sai kuma jinin ya zo kwana ɗaya bayan kwanakin da ta saba, Imam Abu Yusuf ya ce waɗannan kwanakin biyar da jinin bai zo ba su ne na al'adarta, kwanakinta ba su sauya ba. Idan jinin ya zo a cikin kwanaki uku na al'adarta da ta saba, da kuma kwanaki takwas bayan haka, to kwanaki ukun na farko na al'adarta ne, lakacin al'adar ya sauya. Idan kwanakin da ta ƙara kaɗan ne da jimillarsu ba ta wuce kwanaki goma ba (wato kwanaki uku da ƙasa da kwanaki takwas), to na al'ada ne. Idan kwanakin da suka biyo baya na tsarki suka zama fasid, to al'adarta ba ta sauya ba. Idan al'adarta kwanaki biyar ne, sai jinin ya cigaba a kwana na shida, sannan ta yi tsarki tsawon kwanaki sha huɗu, sai kuma jinin ya zo na kwana ɗaya, al'adarta ba ta sauya ba. Bari mu bayar da misalai goma sha ɗaya a kan macen da take jinin al'ada kwanaki biyar, sannan ta yi kwanaki ishirin da biyar na tsarki, domin ƙarin haske a kan bayanin da aka yi a sama.

1- Idan mace ta yi kwanaki biyar na jinin al'ada, ta kuma yi kwanaki sha biyar na tsarki, sai kuma jini ya zo mata tsawon kwanaki goma sha ɗaya, sannan ya zamana jinin bai zo mata ba a lokacin da ta saba, wanda hakan zai ɗauke kwanaki hamsin da biyar (bayan kammala al'adarta da ta saba ta kwanaki biyar). To kwanakin al'adarta sun sauya, amma adadin kwanakin ba su sauya ba. Kwanaki biyar na farkon kwanaki sha ɗayan nan sun zama na al'adarta.

2- Idan mace ta shafe kwanaki biyar tana al'ada, sannan kwanaki arba'in da shida suka biyo baya na tsarki, sai kuma ta yi kwanaki goma sha ɗaya tana jini, a nan kwanaki biyu na ƙarshe a cikin kwanaki sha ɗayan sun faɗa cikin kwanakinta da ta saba na al'ada. Tun da kwanakin ba su kai uku ba, adadin kwanakinta na al'ada ba su sauya ba, amma lokacinta ya sauya. Don haka kwanakin biyar na farko a cikin sha ɗayan su ne na al'adarta.

3- Macen da ta yi kwanaki biyar na jinin al'ada, sannan ta yi kwanaki arba'in da shida na tsarki, sai ta yi kwanaki sha biyu tana jini, kwanaki biyar daga cikin sha biyun suna cikin kwanakin hamsin da biyar na tsarki da ta saba, kwanaki biyar kuma na al'ada ne, babu wani sauyi a nan.

4- Idan kuma ta kwashe kwanaki biyar tana al'ada, sannan ta yi kwanaki hamsin da huɗu na tsarki, sai jini ya zo mata na kwana ɗaya, sannan jinin ya

ɗauke tsawon kwanaki sha huɗu, sai kuma jini ya zo na kwana ɗaya, kwana ɗaya tsakanin kwanakinta na al'ada da ta saba. Tun da kwanaki sha huɗun tsarkin naƙis ne (bai cika ba), (wato saboda sun gaza da kwanaki biyar na cikar kwanakin tsarki), to sun zama na jini, kuma biyar na farko a ciki su ne na al'ada. Adadin kwanakin da lokacin ba su sauya ba.

5- Idan aka samu kwanaki biyar na al'ada, sannan kwanaki hamsin da bakwai na tsarki, sai kuma aka samu kwanaki uku na jini, sannan jinin ya ɗauke tsawon kwanaki sha huɗu, sai kuma wani jinin ya zo na kwana ɗaya, kwanaki ukun sun yi daidai da kwanakin al'adarta. Kwanaki sha huɗun kuwa suna cikin kwanakin jini, amma tun da kwanakin sun wuce sha ɗaya, al'adar ta sauya da adadin kwanaki kaɗai.

6- Macen da ta fuskanci kwanaki biyar na al'ada da kwanaki hamsin da biyar na tsarki, sai kuma jinin ya zo na kwanaki tara, daga nan kuma aka samu ingantaccen tsarki, kwanaki tara na ƙarshe, na al'ada ne. adadin kwanakin al'adar kaɗai suka sauya. Akwai kwanaki fiye da uku a lokacin al'adar da bayansa.

7- idan aka samu kwanaki biyar na jinin al'ada, aka kuma samu kwanaki hamsin na tsarki a bayansu, sannan jinin ya sake zuwa tsawon kwanaki goma. Kwanaki goman na al'ada ne. kwanakin tsarkin sun sauya zuwa kwanaki hamsin. Kwanakiin jini suna zuwa ne a lokacin al'ada, haka nan ma adadinsu.

8- Idan kuma aka yi kwanaki biyar na al'ada, sannan aka yi kwanaki hamsin da huɗu na tsarki, sannan jinin ya sake zuwa tsawon kwanaki takwas, kwanaki takwas ɗin na al'ada ne, fiye da kwanaki uku a ciki su ne waɗanda ta saba. Adadin kwanakin al'ada da na tsarki duka sun sauya da kwana ɗaya.

9- Idan aka samu kwanaki biyar na al'ada, da kuma kwanaki hamsin na tsarki, sannan aka samu kwanaki bakwai na jini, kwanaki bakwan na al'ada ne, kwanakin adadin nisabi suna zuwa ne kafin lokacin da aka saba, wato kwanakin da ba su kai uku ba su ne nisab. To a nan adadin kwanakin al'adar da lokacin sun sauya, yayin da adadin kwanaki kaɗai ya sauya na lokacin tsarki.

10- Idan aka samu kwanaki biyar na al'ada, da kwanaki hamsin da takwas na tsarki, sai jini ya zo tsawon kwanaki uku, to kwanaki ukun sun zama na jinin al'ada, kwanaki biyu na lokacin da ta saba, kwana ɗaya kuma ƙari a kai. Al'adarta ta sauya ta fuskar adadin kwanaki da kuma lokaci, yayin da adadin kwanaki kaɗai suka sauya a lokacin tsarkinta.

11- Idan kuwa aka samu kwanaki biyar na al'ada, kwanaki sittin da huɗu na tsarki, sannan kwanaki bakwai ko sha ɗaya na jini suka biyo baya, idan

na farkon ne, kwanaki bakwan na al'ada ne, sai dai an samu sauyin adadin kwanaki da lokaci. A batu na biyu kuwa, kwanaki biyar na farko daga cikin sha ɗayan su ne na al'ada, sauran kwanaki shida kuma na istihada ne. lokacin al'adar kaɗai ya sauya. Tun da yake jinin ya zarce kwanaki goma na shari'a, adadin kwanakin bai sauya ba. Adadin kwanakin tsarkinta ya sauya.

Imam Fakhr-ud-din 'Uthman Zeyla'i 'Allah ya yi masa rahama' (d. 743 H [1343 M.], Egypt) ya faɗa a cikin littafinsa **Tebyin-ul-haƙaiƙ**, da kuma Ahmad bin Muhammad Shelbi 'rahimahullâhu ta'âlâ' (d. 1031 H [1621 M.], Egypt), a sharhin littafin: idan jini ya zo mata kwana ɗaya kafin lokacin da ta saba, da kwanaki goma na tsarki, sai kuma kwana ɗaya na jini, Imam Abu Yusuf 'rahimahullâhu ta'âlâ' ya ce al'adarta ta fara ne a cikin kwanaki goman na tsarki, kuma za ta cigaba zuwa adadin kwanakin da ta saba. Jini bai fito mata ba a ranar farko da ta ƙarshe na al'adarta. Al'adar ta fara ne kafin lokacin da ta saba, kuma bayan kwanki goma, wanda ke nufin za a ƙirga kwanakin tsarkin fasid a cikin ranakun hailarta. Imam Muhammad 'rahimahullâhu ta'âlâ' ya ce dukkan wannan lokacin ba na al'ada ba ne. Idan ya zamana kwanakin da ta saba na al'ada kwana biyar ne sannan ta yi kwanaki ishirin da biyar na tsarki:

1- Idan jini ya zo wa mace kwana ɗaya kafin lokaci, sai ya ɗauke bayan kwana ɗayan, sai kuma jinin ya dawo, ya cigaba a kan abin da ake kira 'istimrar' (ba ƙaƙƙautawa) har ya zarce kwanaki goma, Imam Abu Yusuf ya ce kwanaki biyar ne na al'adarta kamar yadda ta saba. Jinin da ya zuba kafin nan da kuma bayan kwankin biyar, na rashin lafiya ne (istihada). Imam Muhammad ya ce kwanaki uku na zubar jinin, wato waɗanda suka tare da kwanakin da ta saba na al'ada ne. Kwanaki ukun su ne na biyu da na uku da na huɗu na kwanakin da ta saba. Domin jinin bai zo ba a ranar farko ta al'adarta. Kwana na biyar da jinin ya zuba shi kuma ba ya cikin kwanakin al'adarta.

2- Idan jini ya zo a ranar farko ta al'adarta, ya kuma ɗauke a rana ta biyu, sannan jinin ya cigaba da zuba ba ƙaƙƙautawa (istimrar) har ya wuce kwanaki goma, to kwanaki biyar da ta saba, su ne na al'adarta, kamar yadda ittifaƙin Malamai ya nuna. Saboda jinin ya zuba a ranar farko da ta ƙarshe na al'adarta.

3- Idan jini ya zo wa mace tsawon kwanaki uku na al'adarta, sai ya ɗauke na tsawonkwanaki biyu, daga nan kuma ya cigaba da zuba ba ƙaƙƙautawa har ya zarce kwanaki goma, kwanaki biyar na farko su ne na al'adarta, inji Imam Abu Yusuf. Imam Muhammad ya ce kwanaki uku na farkon su ne na al'adarta. Domin a ijtihadinsa ya ce wajibi ne a samu zubar jini a ranar farko da ta ƙarshe na al'ada.

A ruwaito a cikin litattafan **Bahr** da **Durr-ul-muntekа**: “Idan jini ya wuce kwanakin al’ada, ya ɗauke kafin cikar kwanaki goma, kuma bai sake dawowa ba har aka yi kwanaki goma sha biyar bayan ya ɗauke, waɗannan ƙarin kwanakin da jinin ya zuba duk na al’ada ne bisa ittifaƙin Malamai. A nan kwanakinta na al’ada sun sauya. Idan kuma jinin ya zuba ko da sau ɗaya ne a tsakanin kwanakin sha biyar, dare da yini, waɗannan kwanakin da suka ƙaru ba na al’adarta ba ne; na istihada ne. za ta rama sallolin da ba ta yi ba a waɗannan kwanakin.” Mustahabbi ne gare ta, ta jira har sai lokacin sallah ya kusa fita a lokacin da jinin ya ɗauke, idan jinin ya ɗauke bayan kwanakin al’adarta kuma kafin kwanaki goma, sai ta yi wanka da yi sallar wannan lokacin. Saduwa ta halatta a wannan lokacin. Idan ta yi jinkiri har lokaci ya fita ba ta yi wanka da sallar ba, in dai har lokacin sallar ya fita, saduwa ta halatta ko da ba ta yi wankan ba.

Idan jini ya zo wa budurwa a karon farko, da macen da jini ya zo mata bayan kwanaki sha biyar da kammala al’adarta, kuma dukkansu jinin ya ɗauke kafin kwanaki uku, za su jira har sai lokacin sallah ya kusa fita (a lokacin da jinin ya ɗauke). Sai su yi alwala kaɗai su yi wannan sallar su kuma rama sauran sallolin da suka kuɓuce masu (a lokacin da jinin yake zuba). Idan jinin ya dawo bayan sun yi sallar, to sallar ba ta yi ba. Idan ya sake ɗaukewa, sai su yi alwala a ƙarshen lokacin sallar da ta riske su, sai su yi alwala su yi sallar, su kuma rama sauran sallolin da suka kuɓuce masu idan akwai. Za su cigaba da haka har kwanaki uku su cika. Amma saduwa ba ta halatta ba ko da an yi wanka.

Idan jinin ya wuce kwanaki uku, ya kuma ɗauke kafin cikar kwanakin da ta saba, saduwa ba ta halatta ba ko da ta yi wanka, har sai kwanakinta na al’ada sun cika. Haka nan idan ba ta ga jini ba ko kaɗan har lokacin sallah ya kusa fita, sai ta yi wanka ta yi wannan sallar. Ba za ta rama waɗanda suka kuɓuce mata ba. Za ta yi azumi. Idan jinin ba sake fitowa ba tsawon kwanaki sha biyar bayan ya ɗauke, ranar da ya ɗauken ita ce ta ƙarshe a sababbin kwanakin al’adarta. Amma idan jinin ya dawo, za ta dakatar da sallah. Za ta rama azumin da ya kuɓuce mata bayan sallah. Idan jinin ya sake ɗaukewa, za ta yi wanka gab da fitar lokacin sallah, sannan ta yi wannan sallar. Za ta yi azumi. Za ta cigaba da yin haka zuwa cikar kwanaki goma. Bayan kwanaki goma, za ta cigaba da sallah ba tare da yin wanka ba, ko da jinin ya cigaba da zuba, haka nan saduwa ta halatta ko da ba ta yi wanka ba. Amma Mustahabbi ne yin wanka kafin saduwa. Idan jinin ya ɗauke kafin fitar alfijir, kuma akwai lokaci da za ta iya yin wanka ta sa situra, ta iya faɗar “Allahu Akbar” kafin alfijir ya fito, za ta ɗauki azumin wannan ranar. Amma ba za ta rama sallar wannan daren ba. Idan akwai isashshen lokacin da za ta iya cewa “Allahu Akbar” (wato ta yi kabbara), za ta rama sallar wannan daren.

Idan jini ya zo mata kafin lokacin shan ruwa (buɗa baki wato faɗuwar rana) azuminta ya kare (kai tsaye). Za ta rama shi bayan sallah. Idan jinin ya zo mata a lokacin da take sallah, to wannan sallar ta ɓaci. Idan ta yi tsarki (wanka bayan kammala al'adarta) ba za ta rama wannan sallar ba idan sallar farilla ce. Idan nafila ce, za ta rama ta. Idan ta ga jini a jikin audugarta (kursuf) bayan fitar alfijir, lokacin da ta farka daga bacci, al'adarta ta fara ne daga wannan lokacin. Idan kuma ta farka daga bacci ba ta ga ɗigon jini a jikin audugar ba, to jininta ya ɗauke ne a lokacin da take bacci. Don haka za ta rama sallar wannan daren. Domin sallah tana zama farilla ne da zarar ta yi tsarki (ɗaukewar jinin al'ada), har zuwa ƙarshen lokacinta. Idan jini ya zo wa mace kafin ta yi sallah, ba za ta rama wannan sallar ba.

Wajibi ne a samu **cikakken lokacin tsarki** tsakanin lokacin jinin al'ada biyu. Idan lokacin tsarkin ya zamo **ingantaccen lokacin tsarki**, jinin da ya zo kafin, da bayan shi, jinin al'ada biyu ne daban-daban, bisa ittifaƙin manyan Malamai. Kwanakin da jini ya ɗauke a cikin kwanakin al'ada goma na shari'a duk ana lissafa su a matsayin kwanakin al'ada (haid), yayin da kwanakin da jinin istihada ya zo a bayan kwanaki goman, ana lissafa su a matsayin kwanakin tsarki. Idan budurwa ta yi kwanaki uku tana jini, sannan jinin ya ɗauke tsawon kwanaki sha biyar, sai kuma jinin ya zo na kwana ɗaya, ya ɗauke kuma na kwana ɗaya, ya sake dawowa na kanaki uku, to kwanaki uku na farko da na ƙarshen su ne kwanakinta na al'ada biyu daban-daban. Saboda kwanakin al'adarta sun zamo kwanaki uku ke nan, al'adarta ta biyu ba za ta fara daga wannan jinin da ya zo na kwana ɗaya a tsakani ba. Wannan jinin na kwana ɗaya ya mayar da cikakkiyar al'adarta zuwa fasid. An ruwaito Molla Husraw 'Allah ya yi masa rahama' (d. 855 H [1480 M.]) yana faɗa a cikin sharhin Shernbalali na littafin **Ghurer**: "Idan jini ya zo wa budurwa na kwana ɗaya, ya ɗauke na kwanaki sha huɗu, ya dawo na kwana ɗaya, ya sake ɗauke wana kwanaki takwas, sannan ya sake zuwa na kwana ɗaya, ya ƙara ɗaukewa na kwanaki bakwai, sai jinin ya sake dawowa na kwanaki biyu, sannan ya ɗauke na kwanaki uku, ya sake dawowa na kwana ɗaya, sai kuma ya ɗauke na kwanaki uku, ya sake dawowa na kwana ɗaya, sannan ya ɗauke na kwanaki biyu, ya dawo kuma na kwana ɗaya, a cikin waɗannan kwanakin arba'in da biyar, kwanaki goman da suka biyo bayan kwanakin goma sha huɗu kaɗai ne na jinin al'ada, sauran kwanakin na jinin rashin lafiya ne (istihada), inji Imam Muhammad 'rahimahullâhu ta'âlâ',." Domin sababbin kwanakin al'ada ba sa farawa bayan waɗannan kwanakin goma, tun da ba a samu cikakken lokacin tsarki ba. Kwanakin tsarkin da suka biyo baya, ba a ɗauke su a matsayin kwanakin jinin al'ada ba, domin jinin bai zo a lokacin kwanakin al'ada ba. "Inji Imam Abu Yusuf 'rahimahullâhu ta'âlâ', a ɗaya ɓangaren, kwanaki goma na al'ada na farko, da kwanaki goma

sha hudù na tsarki, kwanakin al'ada biyu ne da kwanakin tsarki a tsakaninsu." Kamar yadda Imam Abu Yusuf ya fadà, cewa lokacin tsarki na fasid da ya biyo bayansu, an yadda cewa jinin ne ya riƙa fitowa ba ƙaƙƙautawa. Bisa la'akari da hukuncin farko, bayan kwanaki goma na al'ada, kwanaki ishirin da suka biyo baya na tsarki ne, yayin da kwanaki goma na ƙarshe na al'ada ne.

Idan jini ya cigaba da zuba har zuwa kwanaki goma sha biyar ba tare da ya ɗauke ko sau ɗaya ba, wato babu ƙaƙƙautawa '**istimrar**' za ta yi lissafi ne a kan yadda ta saba. Wato za ta fara daga lokacin da jini ya ɗauke mata, da adadin kwanakin tsarki da ta yi a watan da ya gabata, daga nan kuma za ta cigaba da lissafi daidai da kwanakin da ta saba.

Idan istimrar ya auku ga budurwa, an fadà a cikin littafin **Menhel-ul-waridun** cewa za a iya ɗaukar hukunci ta waɗannan fuskokin hudù:

1- Idan jinin ya zuba a tsakanin kwanaki goma na shari'a za a ɗauke shi a matsayin na al'ada, kwanaki ishirin kuma su zama na tsarki.

2- Idan Budurwa ta fuskanci istimrar bayan ingantacciyar al'ada, sai kuma ingantaccen lokacin tsarki ya biyo baya, wannan ya zamo mata lokacin da ta saba. Misali, idan jini ya zo mata na kwanaki biyar, sannan ta yi kwanaki arba'in na tsarki, kwanakin nan biyar na istimrar sun zame mata kwanakin al'ada, kwanaki arba'in da suka biyo baya sun zame mata kwanakin tsarki. Wannan hukuncin zai cigaba har lokacin da jini ya ɗauke mata.

3- Idan jinin fasid ya zo mata, sannan lokacin tsarki na fasid ya biyo baya, ba za a karɓi ko ɗaya ba a matsayin lokacin al'ada. Idan lokacin tsarkin na fasid ne, saboda bai kai kwanaki goma sha biyar ba, jinin da ya zuba a farko za a karɓe shi a matsayin na istimrar. Idan jinin ya kai kwanaki goma sha ɗaya, sannan kwanaki goma sha hudù natsarki suka biyo baya, sannan aka samu jini (babu ƙaƙƙautawa) na istimrar, jinin na farko ya zama fasid, saboda ya zarce kwanaki goma na shari'a. Wannan kwanan na goma sha ɗaya da kwanaki biyar, kwanaki goma na farkon istimrar za a ɗauke su a matsayin kwanakin tsarki, yayin da ƙarin kwanakin biyar za su zamo cikin kwanaki goma na al'ada, da kuma kwanaki ishirin na tsarki da ke biye masu da makamantansu. Idan aka samu cikakkun kwanakin tsarki, amma ya zamo fasid saboda an samu zubar jini a ciki, a nan ma za a ɗauki kwanakin farko a matsayin istimrar, idan kwanakin na tsarkin fasid da na zubar jinin ba su wuce kwanaki talatin ba. Haka abin yake idan aka samu kwanaki goma sha ɗaya na zubar jini, sannan kwanakin tsarki goma sha biyar suka biyo baya, kuma aka samu istimrar bayansu. Kwanakin goma sha shida na tsarkin fasid ne, domin ranar farkon jini ya zuba. Kwanaki hudù na istimrar ɗin sun zama

kwanakin tsarki. Idan jimillar kwanakin suka zarce kwana talatin, kwanaki goma na farko su ne na al'ada, sauran kwanakin har zuwa lokacin istimrar, su kuma suna matsayin kwanakin tsarki, daga nan za a ɗauki tsarin kwanaki goma na al'ada da kwanaki ishirin na tsarki. Wannan hukuncin za a yi amfani da shi idan aka samu kwanaki goma sha ɗaya na jini, sannan aka samu kwanaki ishirin na tsarki na biye masu, sannan kuma aka samu istimrar.

4- Idan aka samu ingantaccen lokacin jinin al'ada, sannan aka samu lokacin tsarki na fasid, kwanakin jinin na al'ada ne, sannan a samu har zuwa kwanaki talatin da za a ɗauka a matsayin kwanakin tsarki. Misali, idan aka samu istimrar bayan kwanaki biyar na jini, sannan aka samu kwanaki goma sha huɗu na tsarki, kwanaki biyar na farkon na al'ada ne, kwanaki ishirin da biyar kuma na tsarki ne. Kwanaki goma sha ɗaya na farko na istimrar ana ɗaukarsu a matsayin kwanakin tsarki, za su shiga cikin kwanaki ishirin da biyar ɗin nan. Daga nan kuma za a cigaba da amfani tsarin da kwanaki biyar na al'ada, da kwanaki ishirin da biyar na tsarki. Haka nan idan aka samu istimrar bayan kwanaki uku na jini, sannan kwanaki goma sha biyar na tsarki suka biyo baya, jinin ya dawo na kwana ɗaya, aka kuma sake samun kwanaki goma sha biyar na tsarki, za a karɓi kwanaki ukun farko na jinin a matsayin na ingantacciyar al'ada, sauran kwanakin har zuwa istimrar za su zamo na tsarkin fasid, don haka jininta zai zamo kwanaki uku na al'ada, kwanaki talatin da ɗaya na tsarki. A lokacin istimrar, za a samu kwanaki uku na al'ada, da kwanaki ishirin da bakwai na tsarki. Idan kwanakin tsarki na biyun suka zamo kwanaki goma sha huɗu, za a karbi jinin a matsayin wanda ba ƙaƙƙautawa inji Imam Abu Yusuf, duka dai, kwanaki biyu na farko (na kwanakin goma sha huɗun nan) za a haɗa su da wannan kwanan ɗaya (kafin kwanaki sha huɗun) domin su yi daidai da kwanakin al'ada da kuma kwanaki goma sha biyar na tsarki. A kan kwanaki ukun farko na jini, da kuma kwanaki goma sha biyar na tsarki da suka biyo baya a matsayin ingantattun kwanakin tsarki, za a karɓe su a matsayin kwanakin da ta saba.

Macen da ta mance kwanakin da ta saba yin al'ada, ana kiranta **muhayyira** ko **dalla**.

Nifas na nufin jinin haihuwa. Jinin da yake fita idan aka samu ɓarin ciki na nifas (jinin biƙi) ne, idan halittar hannu da ƙafa da kai sun bayyana a jikin jinjirin. Babu ƙayyadajjen lokaci ga jinin haihuwa (biƙi). Duk lokacin da jinin ya yanke (ko ya ɗauke) sai ta yi wanka, ta cigaba da sallolinta. Amma ba za ta cigaba da saduwa da mijinta ba sai lokacin da kwanakin jinin da ta saba suka cika. Mafi yawan adadin kwanakin jinin su ne kwana arba'in. Idan kwanaki arba'in suka cika, sai ta yi wanka ta cigaba da sallolinta ko da jinin bai tsaya ba. Jinin da ya zuba bayan kwanaki arba'in, na istihada (rashin

lafiya) ne. Idan jini ya ɗauke wa mace bayan kwanaki ishirin da biyar da haihuwa, kwanakin jininta sun zama kwanaki ishirin da biyar. Idan kuma mace ta yi kwanaki arba'in da biyar tana jini bayan ta yi haihuwa ta biyu, za a lissafa kwanaki ishirin da biyar a matsayin kwanakin ta na jinin biki, sauran kwanaki ishirin kuma za a ɗauke su a matsayin na istihada. Za ta rama sallolin da suka kubce mata na kwanakin ishirin. Kuma wajibi ne ta hardace kwanakin jinin biƙinta. Idan jinin ya ɗauke, misali a cikin kwanaki talatin da biyar maimakon kwanaki arba'in da biyar, dukkan kwanaki talatin da biyar ɗin na jinin bikinta ne, daga lokacin kuma tsarin kwanakinta na jinin biƙi sun sauya daga ishirin da biyar zuwa talatin da biyar.

Idan a watan azumin Ramadan ne jinin mace ya ɗauke na al'ada ko na biƙi, bayan lokacin sahur ya fita, ba za ta ci abinci ko ta sha abin sha ba a wannan yinin, za ta rama azumin wannan ranar bayan sallah. Idan jinin al'ada ko na biƙi suka zo wa mace bayan lokacin sahur, ko da safe ko da yamma, za ta cigaba da cin abincinta.

A lokacin da mace ke jinin al'ada ko na biƙi, haramun ne a dukkan Mazhabobin nan hudu ta yi sallah ko azumi ko ta shiga masallaci, ko ta ɗauki Alƙur'ani mai girma ko ta karanta shi ko ta yi ɗawafi (zagayen ɗakin Ka'aba) ko saduwa da mijinta. Za ta rama azumi, amma ba za ta rama sallolin da suka kuɓuce mata ba. An yafe mata sallolin. Idan ta yi alwala a lokcin sallah ta zauna a kan sallayarta gwargwadon lokacin da ta saba yin sallah, ta yi zikiri da tasbihi, za ta samu lada kamar wanda ya yi sallah ingantacciya.

An faɗa a cikin littafin **Jawhara-t-un-neyyira**[1] cewa: "Ya kamata mace ta riƙa sanar da mijinta idan ta fara jinin al'ada. Idan mijin ya tambaya, saɓo ne mai girman gaske ta ƙi faɗa mashi. Haka nan saɓo ne mai girma ta ce mashi ta fara al'ada alhalin tana cikin tsarki. Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' ya ce: '**Macen da ta ɓoye farawa da kammala jinin al'adarta ga mijinta tana cikin tsinuwar Allah**.' Haramun ne mutum ya sadu da matarsa ta dubura, a lokacin da take al'ada ko lokacin da take cikin tsarki. Saɓo ne mai girman gaske." Allah ya la'anci duk mutumin da ya aikata wannan saɓon da matarsa. Zunubin ya fi muni matuƙa ida ya aikata da ƙaramin yaro ko saurayi. Ana kiransa **Liwadi**, an bayyana shi a matsayin

[1] Taƙitaccen Littafin nan mai suna **Sirâj-ulwahhâj**, wanda ke da mujalladi uku na Abû Bakr bin Alî Haddâd-i-Yemenî 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' (ya rasu a shekarar 800 H. [1397 A.D.]) an rubuta shi a matsayin sharhin littafin Mukhtasar-i-Kudûrî, wanda Abul-Huseyn Ahmad bin Muhammad Baghdâdî 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' (362 [973 A.D.] – 428 [1037], Baghdâd). Ya rubuta.

mummuna aikin saɓo a cikin suratul Anbiya. Kamar yadda aka faɗa a cikin sharhin **Birgiɓi** Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' ya ce: '**Idan aka kama mutane biyu suna liwaɗi kamar yadda ake yi a zamanin Annabi Lut, a kashe dukkansu**!' Wasu manyan Malamai sun ce a ƙona su duka biyun. Dukkansu biyun sun zamo masu janaba idan suka aikata zunubin. Yin bututu ba ya haddasa janaba, amma yana karya azumi (Feyziyya).

Idan jini ya zo wa mace a lokacin sallar da ba ta kai ga yi ba, ba za ta rama wannan sallar ba idan jinin ya ɗauke mata. [A karanta babi na huɗu na mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**!]

BAYANI AKAN ALWALA

Alwala tana da farillai guda huɗu a Mazhabar Hanafiyya, guda bakkwai a Mazhabar Malikiyya, guda shida a Mazhabar Shafi'iyya da Mazhabar Hambaliyya. Na Mazhabar Hanafiyya su ne:

1- Wanke fuska.

2- Wanke hannuwa zuwa murafiƙai (guiwar hannu).

3- Shafar kashi ɗaya bisa huɗu na kai.

4- Wake ƙafafu zuwa idon sawu.

Alwala ta kasu kashi huɗu: Kashi na farko farilla ne, kashi na biyu wajibi, kashi na uku sunnah ne, yayin da kashi na huɗu kuma mustahabbi ne.

Akwai wurare guda huɗu da alwala take zama farilla: Yin alwala domin ɗaukar Alƙur'ani mai girma, da yin alwala domin sallolin farilla biyar, ko domin yin sallar jana'iza (an yi cikakken bayani a kai, a babi na goma sha biyar na mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**) ko yin sujadar tilawa (an yi cikakken bayaninta a babi na goma sha shida na mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**).

Alwala da take wajibi ita ce wadda ake yi idan za a yi ɗawafi (tawaf-i-ziyarat) an yi cikakken bayani a babi na bakwai na mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss**.

Alwala da take sunnah ita ce wadda ake yi idan za a yi karatun Alƙur'ani mai girma ba tare da an ɗauke shi ba, ko idan za a ziyarci maƙabartar Musulmi, ko yin alwala kafin wanka.

Alwala da ta ke mustahabbi kuwa ita ce wadda ake yi kafin a kwanta bacci ko bayan farkawa daga bacci. Idan mutum ya yi ƙarya ko gulmar wani, ko ya saurari kaɗe-kaɗe na banza, mustahabbi ne mutum ya tuba da yin istigifari a kan saɓon da ya aikata, sannan ya yi alwala.

Haka nan mustahabbi ne mutum ya yi alwala idan zai je wajen neman ilimi, ko ƙara yin alwala bayan kana da ita, amma bayan ka yi wani abu da ba a yi sai da alwala, [misali bayan ka yi sallar farilla.] Idan ba ka yi wani aikin ibada ba (da alwalar da kake da ita) makaruhi ne ka ƙara yin wata alwala a kan wadda kake da ita.

BAYANI AKAN RUWA

Ruwa ya kasu kashi huɗu: Ma-i-mutlaƙ; da ma-i-muƙayyad; da ma-i-mashkuk; da kuma ma-i-musta'mal.[1]

1- Misalan ma-i-mutlaƙ su ne ruwan sama, da ruwan teku, da ruwa mai gudana, da ruwan rijiya. Waɗannan irin ruwa suna da tsarki kuma suna tsarkakewa. Ana iya kowane irin amfani da su.

2- Misalan ma-i-muƙayyad su ne ruwan lemu da kankana da inabi da sauran 'ya'yan itace da makamantansu.

Irin waɗannan ruwan masu tsarki ne, amma ba sa tsarkakewa, ba za iya alwala ko wanka da su ba.

3- Ruwan da jaki ko alfadari da jaka ta Haifa suka sha suka rage shi ake kira ma-i-mashkuk.

Ya halatta a yi alwala ko wanka da irin waɗannan ruwan. Mutum yana da zaɓin ya fara yin kowane daga ciki.

4- Shin ruwa yana zama ma-i-musta'mal ne idan ya zuba ƙasa ko ya bar jiki, (wato ya bar gaɓar da ake wankewa) batu ne da manyan malamai suka yi saɓani a kai. Tun da farko ruwan ya zamo musta'mal idan ya bar jiki, (wato an yadda da fatawa a kan wannan ijtihadin).[2] Bisa haka, akwai maganganun Malamai guda uku (wato bayanan da mujtahidai suka yi a kai). Imam A'zam (Abu Hanifa) 'Allah ya yi masa rahama' ya ce najasat-i-ghaliza (ƙazanta ce) [3] Imam Abu Yusuf 'Allah ya yi masa rahama' ya ce najasat-i-khafifa ce (najasa ce mai sauƙi). Imam Muhammad 'Allah ya yi masa rahama' ya ce ruwan tsarkakakke ne. zance na ƙarshe shi ne ya fi inganci (bisa cikakkar fatawa).

---

[1] 'Ma' na nufin 'ruwa'.

[2] Ita Kalmar 'Ijtihad' an yi bayaninta a wurare daban daban a cikin mujalladi na shida na littafin Endless Bliss, Misali a babi na ishirin: da biyar, da shida da bakwai a mujalladi na farko da kuma babi na goma, na ishirin datara a mujalladi na uku.

[3] Najasa, tare da ire-irenta anyi bayaninta a babi na shida a mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss.**

Akwai sharuɗɗa tara da suka wajaba a cika ga alwala (wato alwala ta inganta):

1- Mutum ya zamo Musulmi.

2- Mutum ya kai munzalin balaga.

3- Mutum ya zamo mai nutsuwa.

4- Idan mutum ba shi da alwala.

5- Ruwan alwalar su zamo masu tsarki.

6- Mutum ya zamo yana iya yin alwala.

7- Ga mace ta zamo ba ta cikin jinin al'ada.

8- Ga mace ta zamo ba ta cikin jinin biƙi.

9- A dukkan salloli biyar na farilla, wato duk sallar da lokacinta ya shiga.

[Wannan sharaɗin na tara yana kan har nutumin da ke da uziri, (wanda aka yi cikakken bayani a kai, a sakin layi na shida a ƙarshen babi na uku, a mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**.)]

SUNNONIN ALWALA: Guda ishirin da biyar ne:

1- Yin ta'awizi (a ce "A'uthu billah-imin-ash-shaytan-ir rajim.")

2- Yin Basmala (wato cewa "Bismillah-ir-Rahman-ir-Rahim.")

3- Wanke hannuwa.

4- Tsats-tsefe yatsun hannu, (wato cuccuɗa tsakanin yatsu ta hanyar amfani da yatsun ɗayan hannun kamar haƙoran masharci a tsakanin yatsun ɗaya hannun.)

5- Kurkurar baki da ruwa.

6- Shaƙa ruwa a hanci.

7- Ɗaura niyya. A Mazhabar Hanafiyya, sunnah ne ba farilla ba, amma yin niyya yayin kurkurar baki farilla ne a Mazhabar Shafi'iyya. A Mazhabar Malikiyya farilla ne yin niyya idan mutum zai wanke hannunsa.

8- Fuskantar Alƙibla.

9- Tsefe gemu (ta hanyar amfani da hannu kamar masharci) [idan yana da kauri].

10- Shafar gemu.

11- Farawa da ɓangaren dama.

12- Tsefe yatsun ƙafa da ƙaramin ɗan yatsa na hannun hagu, ta hanyar farawa da ƙaramin yatsa na ƙafar dama.

13- Shafar kai, ta hanyar game dukkan faɗin kan.

14- Shafar fatun kunnuwa da bayan kai da sauran ruwan da suka rage a kan.

15- Da Jerantawa (wanke gaɓoɓin alwala a kan yadda aka tsara).

16- Gaggautawa, wato wanke gaɓoɓin alwala ɗaya bayan ɗaya ba tare da tsayawa ba.

17- Fara shafar kai daga goshi.

18- Yin asawaki.

19- Tabbatar da ruwa ya jiƙa ƙwarin idanu da gira.

20- Cuccuɗawa, wato cuɗa gaɓoɓin alwala da hannu cikin nutsuwa.

21- Mutum ya yi al'awala bisa maɗaukakin bigire.

22- Wanke gaɓɓai sau uku-uku.

23- Sake cika buta idan an kammala alwala da ita.

24- Kar mutum ya riƙa zancen duniya idan yana alwala.

25- Yin riƙo da niyya.

YIN ASUWAKI

Akwai amfani guda goma sha biyar da ake samu daga yin asuwaki. An ruwaito waɗannan amfanin ne daga littafin **Siraj-ul-wahhaj** (Mujalladi uku na sharhin da Abu Bakr bin 'Ali Haddad Yemeni 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' ya rubuta, (ya rasu 800 H. [1397 M.]) na littafin **Mukhasar-i-Kudiri**, wanda Abul Hueyn Ahmad bin Muhammad Baghdadi 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' ya rubuta, (362 H. [973 M.] – 428 H. [1037 M.], Baghdadi), cewa:

1- Zai sa mutum ya cika da kalmar Shahada lokacin da zai mutu.

2- Yana ƙara ƙarfin dasashi.

3- Yana taimakawa wajen rage majina a ƙirji. (magani ne mai kyau).

4- Yana taimakawa wajen narkar da abinci.

5- Yana maganin cututtukan cikin baki.

6- Yana hana warin baki.

7- Allâhu ta'âlâ yana farin ciki da mai yin asuwaki.

8- Yana ƙarfafa jijiyoyin haƙora.

9- Yana sa Shedan baƙin ciki (idan mutum na yin asuwaki).

10- Yana ƙara hasken idanu. (idan mutum na yin asuwaki).

11- Ana ɗaga darajar ayyukan mutum na ibada (alkhairi da kyawawa).

12- Mutum ya aikata sunnah (idan ya yi asuwaki)

13- Yana tsarkake baki.

14- Yana ƙara fasahar magana.

15- Yin raka'a biyu na sallah tare da (alwalar da aka yi bayan yin) asuwaki ta fi lada fiye da raka'a saba'in da aka yi ba tare da (amfani) da asuwaki ba.

MUSTAHABBAN ALWALA

Guda shida ne kamar haka:

1- Niyyar da mutum ya ɗaura a zuciyarsa, kar ya furta ta a fili.

2- Shafar bayan wuya da sauran ruwan da aka shafi kunne.

3- Kar mutum ya fuskanci Alƙibla da ƙafarsa lokacin da yake wanke ta.

4- Shan sauran ruwan alwala yayin da ake fuskantar Alƙibla.

5- Yayyafa ruwa kaɗan a jikin situra bayan kammala alwala.

6- Tsane jiki da tsumma mai tsafta.

Ibn 'Abidin ya faɗa a bayaninsa na kan abubuwan da suka shafi alwala cewa: "Idan wani abu ya zamo ba makaruhi ba a Mazhabarka, amma farilla ne wata Mazhaba, (a ɗaya daga cikin Mazhabobi uku), to mustahabbi ne ka 'aikata shi." Imam Rabbani ya faɗa a cikin bayaninsa na ɗari biyu da tamanin da shida (286) cewa: "Saboda farilla ne a Mazhabar Malikiyya a cuɗa gaɓoɓin alwala da hannu cikin nutsuwa, mu, (a Mazhabar Hanafiyya) ya kamata mu cuɗa gaɓoɓinmu idan muna alwala." Ibn 'Abidin ya faɗa a lokacin da yake bayani a kan talaƙ-i-rij'i cewa. "Abin yabo ne matuƙa ga Musulmi mabiyin Mazhabar Hanafiyya ya yi koyi da Mazhabar Malikiyya. Domin Imam Malik (jagoran Mazhabar Malikiyya) kamar ɗalibi yake a wajen Imam A'zam Abu Hanifa (jagoran Mazhabar Hanafiyya). Idan Malaman Mazhabar Hanafiyya suka gaza samun wani zance a Mazhabarsu, (domin yin hukunci a kan wata mas'ala), suna bayar da fatawarsu ne a kan

Mazhabar Malikiyya. A cikin duk sauran Mazhabobi ukun nan, Mazhabar Malikiyya ita ta fi kusa da Mazhabar Hanafiyya."

MAKARUHAN ALWALA

Guda goma sha takwas ne kamar haka:

1- Watsa ruwa da sosai a fuska.

2- Yin numfashi a cikin ruwan alwala.

3- Wanke gaɓɓai ƙasa da sau uku (waɗanda ya kamata a riƙa wankewa sau uku).

4- Da wankewa fiye da sau uku.

5- Yin tofi a cikin ruwan alwala.

6- Fyacewa a cikin ruwan alwala.

7- Haɗiye ruwa a lokacin buɗa baki.

8- Bai wa aƙibla baya (yayin alwala).

9- Da rumtse idanu da ƙarfi yayin alwala.

10- Buɗe idanu sosai yayin alwala.

11- Fara wankewa daga sashen hagu.

12- Yin amfani da hannun dama wajen fyacewa.

13- Yin amfani da hannun hagu wajen kuɓar ruwa a baki.

14- Yin amfani da hannun hagu wajen shaƙa ruwa a hanci.

15- Ajiye tafin ƙafa a ƙasa.

16- Yin alwala da ruwan da suka yi zafi saboda daɗewa a cikin rana.

17- Kin gujewa amfani da ma-i-musta'mal (a duba bayanin a kan irin wannan ruwa a sama).

18- Yin maganganu da suka shafi duniya idan ana alwala.

ABUBUWAN DA KE WARWARE ALWALA

Guda ishirin da hudu ne kamar haka:

1- Abubuwan da ke fita daga dubura.

2- Abubuwan da ke fita daga gaba (al'aura).

3- Tsutsa da tsakuwa da suke fitowa daga dubura ko gaban mutum.

4- Yin bututu.

5- Idan mace ta yi matsi na magani a cikin farjinta sai ya fito.

6- Idan maganin da aka ɗura a kunne ya dawo ta baki, alwala ta warware [idan ya fito ta kunne ko ta hanci bai warware alwala ba (**Fatawa-i-Hindiyya**).]

7- Da audugar da namiji ya sanya a hudar mafitsararsa, idan ta jiƙe ta faɗo. [idan ya zamana wani sashe na audugar a waje yake, kuma wanda ke cikin hudar a bushe yake, to alwala ba ta warware ba matuƙar ba ta faɗo ba.]

8- Idan audugar ta faɗo kuma sashen da ke waje ya zamo a jiƙe.

9- Amai mai yawa. Idan mutum ya yi aman majina komi yawansa, alwala bata warware ba. Miyan bacci mai tsarki ne, ko da ya yi launin ɗorowa-ɗorowa.

10- Zubar hawaye sakamakon rashin lafiya yana warware alwala. Amma ba ya warware alwala idan ya zuba saboda kuka ko kusantar abubuwa masu yaji irin su albasa.

11- Haɓo ko fitar da ɗorowan ruwa daga hanci suna warware alwala ko da bai fito daga cikin hancin ba. Majina ba najasa ba ce. Ba ta warware alwala idan ta fito daga hanci.

12- Haka nan miyau da mutum ya tofar wanda ya gauraya da jini.

13- Idan mutum ya ga jini a jikin wani abu da ya ciza, zai warware alwala idan jinin ya watsu a cikin baki ko a haƙora.

14- Idan mutum ya ga jini ya fito daga wani sashe na jikinsa, ya kuma watsu a wannan sashen ko da kaɗan ne, alwala ta warware ga wanda yake bin mazhabin Hanafiyya, amma ba ta warware ba ga waɗanda suke bin Mazhabin Malikiyya ko Shafi'iyya.

15- Mutumin da yake tafiya a kan doki ba tare da sirdi ba, idan bacci ya ɗauke shi a yayin da dokin yake gangarawa daga tudu, alwala ta warware.

16- Idan kana kokwanto ko ka yi alwala ko baka yi ba, dhann-i-ghalib (tunani mafi rinyaje) a gare ka shi ne, ba ka da alwala.

17- Idan mutum ya rungumi matarsa alhalin suna tsirara, alwalarsu ta warware.

18- Idan Mutum ya manta bai wanke wata gaɓar alwala ta jikinsa ba, kuma ya manta ko wace gaɓa ce, alwalarsa ta warware.

19- Idan farin ruwa ko jini ko ɗorowan ruwa suka fito daga bororon (maruru) da ya fashe da kansa ko aka matse shi a wani sashe na jiki, alwala ta warware.

20- Misali a ce mutum yana da ƙurji, wanda yake da ruwan najasa da suka ƙunshi ɗorowa ruwa ko jini ko farin ruwa a tsakiyarsa a jikin mutum, alwalarsa za ta iya warwarewa idan akwai auduga ko bandeji a jikin mutum da wannan ruwan najasar ya jiƙa. Akwai wani zance na Malamai cewa, ruwan ciwo ko ƙurji da ba shi da kala ba ya warware alwala. Ya halatta ga waɗanda suke da rashin lafiya da ta ƙunshi ƙaiƙayi ko ƙurajen ado ko kyasfi su lura da wannan zancen.

21- Misali bacci ya ɗauki mutum yana jingine da wani abu; (alwala ta warware) idan gyangaydinsa ya yi nauyi, har ya zamana zai iya faɗuwa idan aka janye abin da ya jingina da shi.

22- Yin dariya da ƙarfi a cikin sallah mai ruku'u da sujada har mutum ya ji sautinta ko wani da ke kusa da shi ya ji sautin, alwala ta warware. Idan mutum ya yi dariya mai sauti amma wanda yake kusa da shi bai ji sautin ba, to alwala ba ta warware ba, sai dai sallar ta ɓaci. (Wato idan mutum ya yi dariyar da shi kadai ya ji sautinta, sallarsa ta ɓaci amma alwalarsa ba ta warware ba.)

23- Farfaɗiya ko suma suna warware alwala.

24- Idan fari ko ɗorowan ruwa ko jini suka fito daga kunnen mutum, har ya taɓa ɗaya daga cikin wuraren da ya wajaba a wanke a wajen wanka (alwala ta warware).

Daga gare mu ne Turawa suka koyi yadda ake wanka a makewayi.
Kafin nan gidajensu suna cike da ɗoyi idan ka kusance su.
Musulmai ne suka yaɗa tsafta a duniya baki ɗaya,
Suka ceto al'umma daga mummunan maƙiy (ɗabi'a)i.

ADDU'O'IN DA AKE YI LOKACIN ALWALA

Idan mutum zai fara alwala, zai ce: "**Bismillah-il-'adhim wa-l-hamd-u-li-l-lahi 'ala din-il-islami wa 'ala tawfiƙ-il-imani al-hamd-u-li-l-lah-il-ladhi ja'al-al-maa tahuran wa ja'al-al-islama nuran**."

Idan ka kurɓi ruwa a bakinka, sai ka ce: "**Allahum-masƙini min hawdi nabiyy-ika ka'san la'azmau ba'dahu abadan**."

Yayin shaƙa ruwa a hanki sai ka ce: "**Allahumma arihni rayiha-t-al Jannati wa-r-zuƙni min naimiha wa la turihni rayihat-an-nari**."

Lokacin da kake wanke fuska, zaka ce: "**Allahumma Bayyid wajhi binurika yawma tabyaddu wujuhu awliya-ika wala tasawwid wajhi bizunubi yawma taswaddu wujuhu a'da-ika**."

Haka nan yayin wanke hannun dama (zuwa guiwar hannun), za ka ce: "**Allahumma a'tini kitabi bi-yamini wa hasibni hisaban yasiran**."

Idan kana wanke hannun hagu (zuwa guiwar hannu) za ka ce: "**Allahumma la tu'tini kitabi bishimali wa la min warai zahri wala tuhasibni hisaban shadidan**."

A lokacin da kake shafar kai, za ka ce: "**Allahumma harrim sha'ri wa bashari 'alannari wa azillani tahta dhilli 'Arshika yawma la dhilla illa dhilluka**."

Yayin shafar kunuwa za ka ce: "**Allahumma-j'alni minalla-dhina yastami'una-l-ƙaula fa yattabi'una ahsanah**."

Idan kana shafar bayan wuyanka, za ka ce: "**Allahumma a'tik raƙabati min-an-nari wahfaz min-as-salasili wa-l-aghlal**."

Lokacin da kake wake ƙafar dama, sai ka ce: "**Allahumma thabbit ƙadamayya 'ala-s-sirati yawma tazillu fihil-aƙadam**."

Yayin wanke ƙafar hagu, za ka ce: "**Allahumma la-tatrud ƙadamayya 'ala-s-sirati yawma tatrudu kullu aƙdami a'daika. Allahumma-j'al sa'yi mashkuran wa zanbi maghfuran wa 'amali maƙbulan wa tijarati lan'tabura**."

Idan ka kammala alwala, sai ka ce: "**Allahumma-j'alni min-at-tawwabina wa-j'alni min-al-muta-dah-hirina wa-j'alni min ibadika-s-salihina wa-j'alni min-al-ladhina la khaufun 'alaihim wala hum yahzanun**."

Daga nan mutum zai kalli sama, sai ya ce: "**Subhanakallahumma wa bihamdika ash-hadu an la ilaha illa Anta wahdaka la sharika laka wa anna Muhammadan 'abdika wa rasuluka**."

Bayan nan sai a karanta suratul (Kadr) **Inna anzalna** sau ɗaya ko sau biyu ko sau uku, a fara karatun da **Basmala**, itace; "Bism-illah-ir-Rahman-ir-Rahim," kafin karanta surar.

Wajibi ne mutum ya koyi ilimin addini wanda iyalansa za su buƙata domin ya koyar da su. Domin za a tambayi mutum a kan matansa a ranar tashin ƙiyama.

BAYANI AKAN TAIMAMA

A Mazhabar Hanafiyya taimama tana inganta idan aka yi ta kafin lokacin sallah ya shiga. Amma ba ta inganta ba a sauran Mazhabobi uku. Taimama tana da farillai (fards) guda uku: Taimamar da ake yi a madadin alwala irinta ce ake yi a madadin wanka. Inda suka bambanta shi ne wajen ɗaura niyya. Don haka, ba za a iya amfani da ɗaya taimamar a madadin ɗaya ba.

1- Ɗaura niyya, wanda yake wajibi ne.

2- Buga ƙasa da tafukan hannuwa biyu, daga nan sai a yi shafa a dukkan fuska da tafukan hannuwan.

3- Buga ƙasa na biyu da tafukan hannuwa, sannan a fara da shafar hannun dama zuwa guiwar hannu ta amfani da hannun hagu, sai a shafi hannun hagu zuwa guiwar hannu da amfani da hannun dama, (har da guiwar hannun). Waɗannan ayyukan dukkansu rukunnai ne, (wato farillai ne na taimama. Idan aka bar ɗaya daga cikinsu, taimama ta ɓaci).

Hujjoji daga nassi da ke nuna taimama farilla ce su ne aya ta arba'in da uku ta suratun Nisa, da kuma aya ta shida ta suratul Maida. A Mazhabobin Malikiyya da Shafi'iyya, bai halatta ba a yi taimama (wadda za a yi sallah da ita) kafin shigar lokacin sallar, kuma ba a yin sallah fiye da ɗaya da taimama ɗaya. (Wato dole ne yin taimama ga kowace sallah, kuma dole a jira har sai lokacin sallar ya shiga.)

Akwai abubuwa guda shida waɗanda ba a yin taimama da su, sai dai idan akwai kakkaɓin turɓaya a jikinsu. Abubuwan shida su ne: ƙarfe, da jan ƙarfe, da tagulla, da ma'adanin tin, da zinare da azurfa da sauran dukkan ƙarafuna da suke narkewa idan sun sha wuta; da gilassai da suke yin laushi idan sun sha zafi; da tangaram. Amma ya zamo asalinsu daga ƙasa ne.

Za a iya yin sallah a kan ƙasar da aka yi fitsari a kai idan ya bushe. Amma ba za a iya yin taimama da ita ba.

Taimama tana halatta ne idan an nemi ruwa ba a samu ba, an kuma tambayi adali ko sahihin Musulmi. (Adalin Musulmi shi ne wanda ba ya aikata manyan zunubai, kuma ba ɗabi'arsa ce aikata ƙananan zunubai ba. Sahihin Musulmi shi ne wanda yake guje wa aikata ba haram kaɗai ba har ma da abubuwan da ake kokwanto a kai, balle ya aikata saɓo ba da gangan ba. A duba babi na farko na mujalladi na shida na littafin **Endless Bliss** domin samun bayani a kan abubuwan da ake kokwanto.

Akwai sharuɗɗa wajibai biyar da ya kamata a cika idan za a yi taimama:

1- Ɗaura niyya. 2- Yin shafa. 3- Dukkan abin da za a yi taimama a kai, ya zamo yana da alaƙa da ƙasa, idan ya zamo ba abin da aka yi daga ƙasa ba ne, to wajibi ya zamo a kwai kakkaɓin ƙasa a kai. 4- Ƙasar ko kakkaɓinta da za a yi taimamar da su, wajibi ne su zamo masu tsarki. 5- Ya zamo tabbas mutum ba zai iya yin amfani da ruwa ba (wajen yin alwala). [Nauyin jiki bayan warkewa daga rashin lafiya shi ma uzuri ne, (na yin taimama maimakon alwala da ruwa). Haka nan ma nauyin jiki sakamakon tsufa. Wani rangwamen kuma da aka yi wa irin waɗannan mutanen shi ne, za su iya yin sallah daga zaune.]

Akwai sunnoni bakwai da suka kamata a yi a wajen yin taimama:

1- Yin Basmala (wato faɗar "Bismillah-ir-Rahman-ir-Rahim," idan za a fara taimama). 2- Bugun ƙasa mai tsarki a hankali da tafukan hannuwa. 3- Goga tafukan hannuwan kwan-gaba kwan-baya a hankali a kan ƙasar da aka buga sau ɗaya. 4- Ware `yan yatsu. 5- Karkaɗa hannuwa suna dukan juna da nufin cire datti. 6- Farawa da shafar fuska. 7- Shafar dukkan sandar hannu har zuwa guiwar hannu.

Akwai sharuɗɗa huɗu na neman ruwa da ya kamata a cika:

1- Idan ya zamana akwai al'umma mazauna yankin da kake.

2- Idan aka faɗa maka inda ruwa suke.

3- Idan kana da tabbacin cewa akwai ruwa.

4- Idan ba ka wurin da ke halin fargaba.

Idan mutum ya samu ruwa, amma nisan wurin da ruwan yake ya haura mil guda, to ya halatta a gare shi ya yi taimama (maimakon sai ya je can ya yi alwala). Idan nisan wurin bai kai mil guda ba, kuma akwai sauran lokacin sallah kafin ya fita, to a nan bai halatta ya yi taimama ba. [Tsawon mil ɗaya shi daidai da zra' (zira'i) dubu huɗu, wato 0.48×4000=mita 1920 a Mazhabar Hanafiyya.]

A wani ƙaulin kuma, idan ya nemi ruwa bai samu ba, sai ya yi taimama ya yi sallah, sannan ya samu ruwa, zai sake wannan sallar? Wannan batu an tattauna shi (tsakanin manyan malamai). Zance mafi dacewa shi ne, mutum ba zai sake wannan sallar ba.

Idan mutum ya jiƙe, sannan bai samu ruwan da zai yi alwala ba, kuma bai samu wani abu da zai yi taimama da shi ba, sai ya ɗebi taɓo ya shanya, sannan ya yi taimama da shi. Idan gungun jama'a suka yi taimama; sai ɗaya daga cikinsu ya ga ruwa, to dukkansu taimamar tasu ta ɓaci.

Idan wani mutum ya kawo ruwa ga gungun jama'a, ya ce ɗaya daga cikinsu ne zai yi amfani da ruwan ya yi alwala, su duk mutanen taimamarsu ta ɓaci, (wato ta warware). Amma kuma idan ya ce ya kawo ruwan ga dukkan gungun jama'ar su yi alwala, amma ruwan daidai na mutum ɗaya ne, taimamarsu tana nan (ingantacciya).

Idan mutum ya samu janaba[1], bai samu ruwa ko'ina ba sai a masallaci; da farko zai yi taimama ta wanka, sannan ya shiga masallaci ya ɗebo ruwan.

[1] Junub na nufin wanda ke buƙatar yin alwala ta dalilin yin saduwa ko fitar da maniyyi cikin mafarki, A duba babin dake magana akan ghusl.

Amma idan bai samu ruwa a masallacin ba, sai ya sake yin wata taimamar ta yin sallah.

Idan mutumin da ke zaune a masallaci ya yi mafarki da dare har ya fitar da maniyyi, sai ya yi taimama sannan ya fita daga masallacin.

Mutumin da ba shi da hannuwa, zai an ɗauke masa taimama. Amma ba a ɗauke masa yin tsarki (istinja)[1] ba, idan yana da wanda zai taimake shi. Idan babu, an ɗauke masa.

Idan mutum ba shi da hannu da ƙafa, an ɗauke masa yin sallah, inji Tarafeyn, (wato Imam A'zam Abu Hanifa da Almajirinsa Imam Muhammad Sheybani). Shi kuma Imam Abu Yusuf ya ce wannan mutumin wajibi ne ya yi sallah.

Haka nan bai halatta mutum ya yi taimama domin sallar Juma'a ba. Wato idan mutum ba shi da isash-shen lokacin yin alwala (domin sallar Juma'a), bai halatta ya yi taimama ba domin gaugawa, ko da kuwa zai rasa sallar. [Sai dai ya yi sallar Azahar (domin wadanda ba su samu sallar Juma'a ba, wajibi ne su yi sallar Azahar).] An ruwaito a cikin littafin **Durr-ul-mukhtar** cewa bai halatta a yi alwala da narkakken dabino ba mai suna 'nebidh'. (A duba sakin layi na goma sha ɗaya a babi na uku a mujalladi na shida na littafin **Endless Bliss** a kan 'nebidh'.)

Idan mutum ya yi mafarki alhali yana matafiyi, sai ya yi taimama ya yi sallar Asuba. Daga nan sai ya cigaba da tafiyarsa, har sai rana ta yi. Idan lokacin La'asar ya kusa shiga, sannan lokacin sallar Azahar ya kusa fita, sai ya yi taimama ya yi sallar Azahar. Misali idan wannan mutimin ya samu ruwa bayan La'asar, shin zai sake sallolin Asuba da Azahar da ya yi? Manyan Malaman Musulunci ba su haɗu ba a wannan mas'alar. Wani ƙaulin ya ce sai ya sake sallolin, wani ƙaulin kuma ya ce ba zai sake su ba. Kamata ya yi wannan batun ya biyo bayan 'tertib', (wanda aka yi bayaninsa a sakin layi na bakwai na babi na 23 a mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**).

Alal misali idan mutum yana tare da jakinsa ɗauke da ruwa a kai, sai jakin ya ɓace; wannan mutumin (idan lokacin sallah ya yi, yana buƙatar yin alwala), zai yi taimama ya yi sallah. Idan yana cikin sallah ya ji kukan jakin nasa, taimamarsa ta warware.

---

[1] Istinja na nufin mutum ya wanke gabansa bayan fitsari ko bayan gida. A duba sashe na ƙarshe a babi na shida na mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss** domin ƙarin bayani.

Haka nan mutumin da yake tafiya a kan doki, kuma ya tabbatar cewa abokan tafiyarsa ba za su jira shi ba idan ya sauka daga kan dokin; sai ya yi taimamarsa a kan dokin ya yi sallarsa ta hanyar ima (ima'i ko alamu).

Idan mutum yana tafiya mai cike da haɗari, da kuma tsananin sanyi, ta yadda yin wanka zai iya cutar da shi, zai cigaba da yin taimama yana sallolinsa.

Idan mutum zai yi tafiya, wajibi ya samu ɓungu ko tubali ya saka a kayayyakinsa na tafiya. Idan buƙatar taimama ta riske shi a wajen da yake da taɓo, sai ya fito da wannan ɓungun ko tubalin ya yi taimama a kai ya yi sallah.

Mutumin da yake sallar Idi, sai alwalarsa ta warware (ana cikin sallah); sai ya yi taimama ya cigaba da sallarsa, idan ya ga lokaci zai ƙure masa ya samu sauran sallar ta Idi, ko ya ji tsoron zai maƙale a cikin cinkoson jama'a, sai ya yi taimama ya cigaba da sallarsa. Wannan zancen Imam A'zam (Abu Hanifa) ne. Amma a zancen Imamyni[1], sai ya sake alwala.

[An faɗa a cikin sharhin da (Ahmad bin Muhammad ibn Isma'il) Yahtawi ya yi wa littafin **Meraƙ-il-felah** na (Abul-Ikhlas Hassan bin Ammar) Sherblali cewa: "Rashin lafiya uziri ne, (wato dalili ne da Musulunci ya yadda da shi), wanda (ya halatta) yin taimama (a madadin alwala). Ba a yi uzuri ba ga mai lafiya ya yi fargabar cewa zai iya kamuwa da rashin lafiya idan ya yi alwala. Malaman da suka ce ya halatta ga mutum lafiyayye ya ajiye azumi ya zama ƙada (wato ya ajiye azumin sai daga baya ya yi ramuwa) idan ya yi fargabar cewa zai iya kamuwa da rashin lafiya idan ya yi azumin (na watan Ramadan), sun kuma ce ya halatta ga mutumin da yake fargabar kamuwa da rashin lafiya ya yi taimama (maimakon alwala). Abubuwa huɗu ake nufi da kamuwa da rashin lafiyar: Ruwa na iya zama cutarwa (ga lafiyar mutum). Motsawa na iya zama cutarwa. Zai iya kasancewa mutum ba ya iya taɓa ruwa. Yana iya kasancewa mutum ba zai iya yin taimama ba kuma.

Ana iya tabbatar da cutarwar ko ta hanyar mutum ya gano da kansa ko kuma daga gargaɗi daga adalin likita Musulmi kuma ƙwararre. Idan ba a samu adalin likita ba, za a iya amfani da likitan da saɓonsa bai bayyana a fili ba. Mutumin da ba zai iya amfani da ruwa da kansa ba, yana iya yin taimama idan bai samu wanda zai taimake shi ya yi alwala ba. Idan yana da `ya`ya ko bayi ko wani abokin arziki wanda zai iya taimakonsa ya yi alwala, to ɗaya daga cikinsu zai taimake shi ya yi alwala. Idan ya zamana babu ko ɗaya daga cikin waɗannan mutanen, to sai ya yi taimama. Imam A'zam ya ce, ba zai

[1] Imamayni: Ana nufin Imâm Abû Yûsuf da Imâm Muhammad Sheybânî, manyan ɗaliban Imâm A'zam Abû Hanîfa.

ɗauki mutum aiki ba yana biyansa albashi don ya taimake shi ba. Mutumin da ba zai iya yin taimama ba, yana da zaɓin ko dai ya bar sallar ta zama ƙada (wato ya jinkirta sallar sai ya samu lafiya). Haka nan mata da miji ba lallai ba ne su taimaki juna wajen yin alwala ko sallah ba, amma miji zai iya neman taimakon matarsa. Misali mutum ne ba ya kusa da gari ko ƙauye, kuma bai samu ruwan zafi ba; zai iya yin taimama idan ya yi fargabar cewa zai iya kamuwa da rashin lafiya idan ya yi wanka da ruwan sanyi. An bayar da fatawar cewa wannan hukuncin ya shafi har da birane. Idan mutum yana da rauni a fiye da rabin gaɓarsa ta alwala ko wanka, sai ya yi taimama (a madadin alwala ko wankan). Idan ya zamanto wurin da raunin yake bai wuce rabin gaɓar ba (ta alwala ko wanka), to zai wanke daidai inda babu raunin; idan ya kasance shafa zai iya matsala ga raunin, sai ya yi shafa a kan bandejin. Idan hakan zai kawo matsala shi ma, to ba zai yi shafa ba a kan dukkansu. Idan akwai rauni a kansa, ya kasance shafa a kai zai iya kawo wata matsala, an ɗauke masa (yin) shafar. Alal misali akwai raunuka a wuraren da suke farilla ne a wanke su (idan ana alwala ko wanka) a hannuwa biyu, sannan ga wani raunin a fuska; wannan mutumin ba zai iya yin taimama ba; sai ya yi sallolinsa babu alwala da taimama, kuma ba zai rama sallolin da ya riga ya yi ba daga baya. Idan fuskarsa tana da lafiya, zai wanke fuskar. Idan babu wanda zai taimake shi, sai ya goga fuskarsa kasa a hankali. Idan hannu ɗaya na mutum mai lafiya ya samu rauni ko aka yanke ko babu `yan yatsu, sai ya yi alwala da ɗayan hannun. Idan duka hannuwan ne, sai ya goga fuskarsa a kasa. Idan ya zamana bandeji ko karan ɗori ko magani ko ɗori na filasta da aka rufe raunin ko kariya a kan wata gaɓa da nufin yin magani ko bayar da kariya ba za'a iya cirewa ba, ta yadda za a iya wankewa ko yin shafa a gaɓar ba, sai a yi shafa a gwargwadon inda yake waje da sauran wurin da babu raunin a jikin gaɓar. Idan zai yiwu, wajibi ne a cire bandejin ko karan ɗori ko maganin da aka shafa ko kuma ɗorin filastar. A yi shafa a inda matsalar take, sai a wanke inda wajen yake da lafiya. Waɗannan abubuwan ba wajibi ba ne a yi aiki da su bayan an yi alwala ba; kuma babu wa'adin lokacin amfani da su. Ya halatta a wanke ƙafa mai lafiya, a yi shafa a kan bandeji da ke ɗaya ƙafar. Idan abin da yake a kai ya faɗi kafin raunin ya warke, ba zai warware alwala ba. Kuma ba ta warware ba idan aka sauya bandejin da yake a kai bayan an yi shafa a kansa. Idan aka shafa magani a kan akaifa da ta kare ko ta ji rauni ko raunin da aka ji a ƙafa, ba za a cire shi ba, domin cirewar zai iya cutarwa, idan mutum yana da gyambo, mutum zai wanke saman maganin da aka shafa, idan hakan zai iya cutarwa, sai ya yi shafa a kai. Idan shafar za ta iya cutarwa, to ba sai ya yi shafar ba ita ma. [Wannan hukuncin shi ne sauran Mazhabobi uku suka tafi a kai, don haka babu dalilin yin koyi da wata Mazhaba.] Wannan maganin kamar abun yin

ɗori ne, wanda aka rubuta a littafin Ibni ‘Abidin. Amma mas’alar yin ciko a haƙori ko sanya haƙorin makka ta sha bamban da wannan. Saboda akwai damar yin koyi da ɗaya daga cikin Mazhabobin Malikiyya ko Shafi’iyya. Idan mutum ya fita daga hayyacinsa ko ya suma ba da gangan ba, har tsawon lokacin salloli shida, ba zai rama sallolin da suka kuɓuce masa ba (a wannan lokacin na salloli shida da ya rasa. Wato ba zai sake yin wasu salloli a madadinsu ba). Wannan mutumin ba zai bayar da wasiyya cewa a yi masa isƙat ba ga sallolin da bai samu damar yi ta hanyar Ima (ima’i ko alama). Zai rama su ne gaba ɗaya idan ya warke.” (A duba babi na ishirin da ɗaya a mujalladi na littafin **Endless Bliss** domin samun bayani a kan ‘isƙat’ da dawr.)

Ibni ‘Abidin ‘Allah ya yi masa rahama’ ya ce: Makaruhi ne mutum mai lafiya ya sanya wani ya wanke masa gaɓar alwala ko yin shafa a kai. Amma ya halatta wani ya kawo masa ruwa ko ya zuba masa shi kuma ya riƙa wankewa (gaɓoɓin alwalar) da kansa. Idan mara lafiya yana yawan ɓata kayansa ko gadon da yake kwance a kai da najasa, ko idan ya zamo akwai tsanani wajen canza kayan, sai ya yi sallarsa da kayan masu najasa. Idan ƙaran ɗorin ko filasta ko magani da aka shafa suka faɗi bayan rauni ya warke, to alwalar marar lafiyar ta warware. Idan raunin ya warke amma abubuwan ba su faɗi ba, alwalarsa ta warware idan har ana iya cire su ba tare da cutarwa ko tsanani ba.

Allâhu ta’âlâ ya sanya raɗaɗi da rashin lafiya ne ga bayinsa domin ya gafarta masu zunubansu ko ya ɗaukaka darajar da za a ba su a cikin Aljanna. An sanya cikas tsanani a gudanar da ibadarsu. A madadin haka, sai ya ba su sauƙi da rangwame wajen harkokinsu na duniya, da sanya albarka a dukiyarsu (abinci, abin sha da sauran abubuwan buƙata da Allâhu ta’âlâ ya tanadar wa bayinsa. Akwai bayani cikakke a kan rizƙ a gaba a ɗayan mujalladi na shida na littafin **Endless Bliss**). Baya bayar da wannan sauƙin da albarkar ga waɗanda suka yi watsi da ibada. Waɗannan mutane suna samu ne cikin tsanani da yaudara da cin amana da yin rayuwa ta shagala da baɗala, wadda ba ta ɗorewa. Bayan ɗan lokaci zai ƙare a asibiti ko gidajen yari, cikin wulaƙanta har ƙarshen rayuwarsu. sannan su fuskanci azaba mafi tsananin gaske a gobe ƙiyama.]

ISTINJÂ, ISTIBRÂ DA ISTINKÂ

Istinja yana nufin wanke al’aura da ruwa, istibra kuma yana nufin, bayan mutum ya gama fitsari, ya jira ta hanyar kai-komo ko ta yin wani abu har sai mafitsararsa ta bushe (kafin ya yi alwala). Istinƙa na nufin zuciya ta samu yaƙinin cewa jiki ya samu tsarki.

Istinja ya kasu kashi huɗu:

Akwai wanda yake farilla ne; idan akwai najasa da ta fi nauyin dirhami ɗaya a situra ko a jiki, ko a bigiren da za a yi sallah, farilla ne a kawar da wannan najasar da ruwa. Haka nan istinja na zama farilla a yayin wanka. [Girman dirhami ɗaya na daidai da girman mithƙal, wanda yake daidai da nauyin giran huɗu da santigram 80.]

Wanda yake wajibi shi ne; idan aka samu najasa mai nauyin dirhami ɗaya a situra ko a bigiren da za a yi sallah. Wajibi ne a kawar da ita.

Idan ba ta kai nauyin dirhami ba, sunnah ne a gusar da ita.

Wanda yake mustahabbi kuma ita ce; idan akwai najasa `yar kaɗan, mustahabbi ne gusar da ita. Wanda yake mandubi kuma idan mutum ya yi tusa, yayin da duburarsa take a jiƙe, mandubi ne wanke ta.

Idan mutum ya yi tusa yayin da duburarsa take a bushe, bidi'a ne wanke ta.

Sunnonin istinja: Sunnah ne yin tsarki da duwatsu ko ƙasa, sannan a sake wankewa da ruwa.

Idan aka gaza gusar da najasa baki ɗaya kuma wadda ta ragen ta zarce dirhami ɗaya, kuma ta zamo wajen dubura ne, farilla ne a wanke da ruwa. Sannan a tsane wurin da kyalle, ko hannu idan babu kyallen.

Akwai abu ɗaya da yake mustahabbi a yi yayin istinja: riƙe duwatsu mara. Wato duwatsun (da mutum zai riƙe) su zamo uku ko biyar ko bakwai.

[Idan mutum yana fama da matsalar yoyon fitsari, dole ne ya samu ƙyalle mai faɗi da tsayin santimita sha biyu ya ɗaure kusurwa guda da maɗauri mai tsawon rabin mita. Zai naɗe kan azzakarinsa da ƙyallen sannan ya naɗe ƙarshen ƙyallen da maɗaurin, wato a jikin azzakarinsa sau ɗaya. Zai ruɓanya a jikin ƙyallen, ƙarshen inda aka ruɓanya ɗin zai bi ta ƙasan naɗin kyallen sannan a ja shi yadda zai tsuke ƙyallen. Sai a ɗaure sauran kusurwar a zagayen, wanda za a haɗe shi da bante da abin matsewa mai sauƙi. Idan buƙatar yin fitsari ta taso, sai a cire abin matsewar a zare a cire ƙullin, ta hanyar jan maɗaurin. Idan ya zamana akwai matsala wajen kwance ƙullin daga abin matsewar, sai a haɗe ƙullin da waya mai laushi ita kuma sai a haɗa ta da abin matsewar. Ga tsofaffin da azzakarinsu ya ƙanƙance, ba zai yiwu a naɗe shi da kyalle ba, za su sanya azzakari da marainansu a cikin leda ƙarama sai su ɗaure bakinta. Mutumin da yake bin Mazhabar Hanafiyya kuma yake fama da matsalar yoyon fitsari, wanda bai samu uzuri ba, sai ya yi niyya ya yi koyi da Mazhabar Malikiyya idan zai yi alwala ko wanka a lokacin da zai yi sallah. An faɗa a cikin littafin **Kitab-ul-fiƙh 'ala-l-madhahib-il-arba'a** kuma Malaman Misira suka rinjayar ƙarƙashin jagorancin 'Abd-ur-Rahman

Jeziri ‘rahmatullâhi ’alaih’ (ya rasu 1384 H.) ɗaya daga cikin shehunnan Malamai na jami’ar Azhar: “A ƙauli na biyu an ce, a Mazhabar Malikiyya idan marar lafiya ko tsoho suka tsinci kansu a wani yanayi na warwarewar alwala, sun zamo mutane masu uzuri nan take, wanda zai ɗauke masu warwarewar alwalar. Musulmi mabiya Hanafiyya ko Safi’iyya da fuskantar (tsanani) haraj, zai yi amfani da wannan ƙaulin (ijtihad).” [Mabiyin Mazhabar Hanafiyya wanda yake yoyon fitsari a lokacin da yake sallah, zai yi koyi da Mazhabar Malikiyya idan abin ya tsananta. Ya yi niyya, ya cigaba da sallarsa a matsayin mutum mai uzuri.]

YADDA AKE YIN SALLAH

Akwai abubuwa huɗu da ake yi a cikin sallah: Akwai farillah da wajibai da sunnoni da mustahabbai. A Mazhabar Hanafiyya, sunnah ne ɗaga hannuwa sama zuwa saitin kunnuwa. Sunnah ne a juya tafukan hannu su kalli alƙibla. Mustahabbi ne ga maza, taɓa fatun kunnuwa da babban ɗan yatsa, ga mata kuma su ɗaga hannuwansu zuwa saitin kafaɗunsu; sannan farilla ne a ce “**Allahu Akbar**.” Sunnah ne linke hannuwa bayan kabbara, wato cewa, “Allahu Akbar.” Sunnah ne a ɗora hannun dama a kan na hagu. Sunnah ne ga maza su ajiye hannuwan ƙasan cibiyarsu, mata kuma su ɗora su a kan mamansu. Mustahabbi ne ga maza su riƙe wuyan hannun hagunsu da hannun dama, wato da yatsunsu.

A cikin sallah, sunnah ne ga limami da mamu da mai sallah shi kaɗai, su yi addu’ar ‘Subhanaka’[1]. (Bayan addu’ar) sunnah ne su ce, “A’udhu billah-im-ash-shaytan-ir-rajim,” wanda limamin da yake jan sallah zai faɗa (a sallar jam’i), da kuma wanda yake sallah shi kaɗai, (ban da mamu da yake bin sallar jam’i.) Sunnah ne yin Basmala (bayan ta’awizi). Wajibi ne karatun Fatiha (sura ta farko a cikin Alƙur’ani mai girma); farilla ne karanta aƙalla ayoyi uku ko ayoyi masu yawa bayan Fatiha; farilla ne karanta ayoyin Alƙur’ani mai girma yayin tsayuwa a dukkan raka’o’in salloli na sunnah da sallolin Witiri, da lokacin da mutum yake shi kaɗai, a raka’o’i biyu na ƙarshen sallolin farilla (waɗanda suke da raka’o’i huɗu).

Farilla ne duƙawa (ta hanyar lanƙwasa jiki) daga ƙugu domin yin ruku’u; wajibi ne tsayawa a duƙa gwargwadon lokacin da mutun zai ce, “**Subhanallah**,” sau uku. Sunnah ne a ce, “**Subhana Rabb-iy-al ‘adhim**.” Sau uku (duk a duƙe). Mustahabbi ne faɗar waɗannan addu’o’in sau biyar ko bakwai. Idan ka taso daga ruku’u, da tsakanin sujadu biyu, za ka tsaya a natse

[1] ‘Subhânaka’ ana ambatonta kamar haka: “Subhânaka Allâhumma wa bi hamdik wa tabâraka-s-muk wa ta’âlâ jad-duk wa lâ ilâha ghayruk.”

gawargwadon lokacin da za ka ce, "**Subhanallah,**" amma, farilla ne inji Imam Abu Yusuf; su kuma Tarafeyn, (wato Imam A'zam Abu Hanifa da almajirinsa Imam Muhammad) sun ce wajibi ne. Duk da cewa wasu manyan Malamai sun ce sunnah ne, amma mafi rinjayen zance, an ce wajibi ne.

A sujada, farilla ne mutun ya sanya goshinsa a ƙasa. Wajibi ne a tsaya haka a natse gwargwadon lokacin da za ka ce, "**Subhanallah.**" Sunnah ne ka ce, "**Subhana Rabb-iy-al-a'la**," sau uku, sannan mustahabbi ne a maimaita sau biyar ko bakwai.

Ibn 'Abidin 'Allah ya yi masa rahama' ya ce: "Idan za a yi sujada, abu na farko guyawu biyu, sai hannuwa biyu, sai hanci, sannan na ƙarshe goshi, duk za a ɗora su a kan ƙasa. Za a ajiye babban ɗan yatsa saitin kunnuwa. A Mazhabar Shafi'iyya, wajibi ne hannuwa su yi saiti da kafaɗa. Farilla ne aƙalla yatsan ƙafa ɗaya ya taɓa ƙasa. Ya kamata ƙasa ta zamo mai ƙarfi yadda kai ba zai nutse a cikinta ba. Shimfiɗa ko tabarma ko ciyawar alkama ko turɓaya duk za su yi aiki a nan. Teburi ko doguwar kujera ko tarragon da aka girke a ƙasa, suna madadin ƙasa ne. Shillo ko sutura ko falle zani ko shimfiɗa da aka ɗaure a jikin icce ko ginshiƙi wanda yake rataye a kan iska (wato shiɗar da ba kafe take da ƙasa ba), ba sa zamowa madadin ƙasa. Sujadar da aka yi a kan kayan amfanin gona da suka ƙunshi shinkafa da gero da makamatansu, ba ta inganta ba. Amma ta inganta idan acikin buhu suke. Idan tudun wurin sujadar ya kai rabin zira'i ba, wato tsawon yatsu goma sha biyu [santimita ishirin da biyar] tsakaninsa da wurin da mutum ya ajiye gwiwarsa, sallah ta inganta; amma makaruhi ne. A yayin sujada, ya kamata mutum ya raba guiwar hannunsa da jikinsa, ya kuma raba cikinsa da cinyoyinsa. Wajibi ne yatsunka su kalli Alƙibla. Sunnah ne mutum ya haɗe dugaduginsa yayin ruku'u, haka nan ma yayin sujada.

Ga mace idan za ta fara sallah, za ta ɗaukaka hannuwanta sama zuwa kafaɗunta. Hannuwan nata kada su fito daga hannun rigarta. Za ta ɗora hannuwanta a kan ƙirjinta, tafin hannunta na dama a kan na hagu. Za ta lanƙwasa jikinta daidai a lokacin ruku'u. Amma ba za ta daidaita saitin kanta da ƙugunta ba. Ba za ta ware yatsunta ba yayin da take ruku'u ko sujada. Za ta matse su da juna. Za ta ɗora hannuwanta a kan guiwa, ta lanƙwasa su kaɗan. Ba za ta haɗe guiwowinta ba. Yayin sujada za ta ajiye hannunta a ƙasa, ta matse guiwar hannunta kusa da cikinta, cikin nata kuma ya taɓa cinyoyinta. A wajen tashahhud (zaman tahiya) za ta zauna a ƙasa, ta shimfiɗa ƙafarta ta hagu zuwa sashenta na dama. Yatsunta su kalli saitin guyawunta. [Maza ma ba za su haɗe guyawunsu ba, (a yayin da suke zaman tahiya.)] Za ta dunƙule yatsunta matse da juna. Makaruhi ne mace ta yi sallar jam'i a tsakanin 'yan uwanta mata, ko ta bi maza idan zuna sallar jam'i. ba farilla ba

ne a gare su halartar sallar juma'a ko sallar Idi. (Wato Allâhu ta'âlâ bai umarce su a kan su halarci wadanan salloli ba). (Za a samu cikakken bayanin wadannan salloli biyu a babi na ishirin da daya da na ishirin da biyu a mujalladi na hudu na littafin **Endless Bliss**.) Za su rika yi **Takbir-i-tashrik** a asirce bayan sallolin farilla a kwanakin idin babbar sallah. Mustahabbi ne su yi sallar asuba farkon lokacinta. Ba za su bayyana karatun da ake yi ba a cikin sallah." A nan muka kammala fassarar littafin Ibni 'Abidin. Sayyid Ahmad Hamawi bin Muhammad Mekki 'Allah ya y masa rahama' (d. 1098 H. [1686 M.]) ya dfada a cikin littafinsa **Uyun-ul-besir**, wanda sharhi ne na littafin **Eshbah** (wanda Zey-al-'abidin bin Nujaym-i-Misri 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih', 926 H. – 970 [1562 M.], Egypt) cewa: Makaruhi ne mace ta sake gashin kanta, ta hanyar askewa ko datsewa ko ta amfani da sinadari. [Amma ya halatta su rage gashin kan nasu ya zuwa daidai kunuwa, muddin dai ba za su yi kama da maza ba.] Mkaruhi ne ga mace ta yi kiran sallah ko tada ikama, (wadanda aka yi cikakken bayani a kai a babi na goma sha daya na mujalladi na hudu na littafin **Endless Bliss**). Ba za ta yi (doguwar tafiya da ake kira) safar ba, sai tare da rakiyar mijinta ko daya daga cikin muharramanta maza. Ba za ta bude gashin kanta ba a lokacin aikin hajji. Za ta yi (aikin ibada na) sa'y (sa'ayi) daga dutsen Safa zuwa dutsen Marwa (a lokacin aikin hajji), ko da tana jinin al'ada. Za ta yi dawafi nesa da dakin Ka'aba. Ba za ta yi hudduba ba. Saboda ya inganta cewa muryarta al'aura ce. Mace ba za ta bi taron jana'iza ba. Ba za a kashe ta ba idan ta yi ridda. Ba za a karbi shedarta ba a shari'ar (da ta shafi) haddi ko kisasi, (wadanda aka yi cikakken bayani a kai a babi na goma zuwa na sha biyar a Mujalladi na shida na littafin **Endless Bliss**). Ba za ta yi ittikafi ba a masallaci. Ya halatta ta yi kunshin lalle a hannuwa da kafafunta. [Ba za ta sa jan farce ba.] Tana da rabin hakkin namiji a al'amurran da suka shafi gado da shaida da bayar da nafaka ga 'yan uwa mabukata. Ba a kiran mace muhsina zuwa kotu. Alkali ko mataimakinsa ne za su je gidanta. (Mace muhsina ko muhsana ita ce wadda ta yi aure kuma ba ta sadu da mijinta ba. A duba sakin layi na biyar da na shida a babi na goma da sakin layi karkashin kan bayani kamar haka 'HADD FOR KAZF' a wannan babin, na mujalladi na shida a littafin **Endless Bliss**). Budurwa ba za ta gaishe da namijin da ba muharramin ta ba, ko yi masa ta'aziyya ko gaishe da shi idan ya yi atishawa (idan ya ce "Al-hamd-u-lillah,") Ko ta mayar masa da jawabi. Ba za ta kadaita da mutumin da ba muharramin ta ba a cikin daki. A nan muka kawo karshen bayani daga Hamawi.

Wajibi ne a yi zaman ka'da-i-ula (zaman farko a cikin sallah), sannan farilla ne yin ka'da-i-akhira (zaman karshe). Wajibi ne yin (addu'ar da ake kira) tahiya a zaman karshe na sallah.

Sunnah ne yin addu'ar da ake kira Salawat a zaman ƙarshe na sallar farilla, da na wajibi, da nafilolin farko na sallar Azahar da nafilolin farko da na ƙarshe na sallar Juma'a, da zaman tahiya na sauran salloli [da suka ƙunshi raka'o'i hudu na nafila lokacin sallar la'asar, da sallar isha'i]. Wajibi ne furta sallama, (wato cewa "As-salamu 'alaikum wa rahmatullah), (a yayin sallama, za a juya kai dama da hagu). Sunnah ne a juya kai ya kalli kafadu biyu a yayin sallamar. Sannan mustahabbi ne a sanya nutsuwa.

Ingancin sallah ya dogara ne ga [mutum ya guje wa haram da] sanya khushu' da taƙwa da guje wa malaya'ni da terk-i-kesel da ibdad. Khushu' na nufin tsoron Allah 'adhim-ush-shan; taƙwa na nufin mutum ya kare gaɓoɓinsa daga aikata haram da makaruhi; guje wa malaya'ni na nufin barin zantuka da ba za su amfani mutum ba duniya da lahira; terk-i-kesel na nufin guje wa kasala wajen gudanar da sallah; sannan ibdad na nufin barin duk wani aiki da mutum yake yi da gaggauta halartar Juma'a da zarar mutum ya ji kiran sallah, kuma mutum ya ɗore a haka.

Akwai abubuwa guda shida waɗanda suke da muhimmanci a yi riƙo da su a sallah: ikhlas; tafakkur; khawf; raja; ru'yat-i-taƙsir da mujahada.

Ikhlas na nufin a samu khulus (gaskiya) wajen aikin ibada, wanda ke nufin a yi (sallah) saboda Allah; tafakkur na nufin yin tunanin abin da ya shafi sallar da kake yi; khauf na nufin tsoron Allah 'adhim-ush-shan ; raja na nufin sanya rai ga samun rahamar Allah 'adhim-ush-shan; ru'yat-i-taƙsir na nufin mutum ya san cewa yana da rauni; mujahada na nufin mutum ya yi yaƙi da son zuciya da kuma shedan.

Idan aka yi kiran sallah, mutum ya hararo Mala'ika Israfil 'alaihis-salâm' yana busa ƙaho (a ranar tashin ƙiyama); idan mutum ya tashi zai yi alwala, ya hararo cewa ya taso ne daga ƙabarinsa; idan mutum ya nufi masallaci, ya hararo cewa yana tafiya ne zuwa Mahsher (filin tsayuwar hisabi); idan ladan ya fara tayar da iƙama, mamu suka jera sahu, mutum ya hararo cewa da'ira ce guda ɗari da ishirin ta jama'a a filin hisabi, tamanin daga cikin da'irar ta al'ummar Annabinmu ce 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam', yayin da sauran arba'in kuma ta sauran Annabawa ce; idan kayi kabbara ka bi liman, yayin da limamin ya fara karatun fatiha, mutum ya hararo Aljanna a hannunsa na dama, wuta kuma a hannunsa na hagu, Mala'ika Azrail 'alaihis-salâm' yana bayansa; Beytullah kuma a gabansa da kabarinsa kusa da shi, siradi kuma a ƙarƙashin ƙafafunsa. Mutum ya riƙa fargabar ko hisabin da za a yi masa (a ranar tsayuwa) zai zo masa da sauƙi, ko ibadarsa za ta zamo hular sarauta a kansa, ta zamo jagora a gare shi a hanyarsa ta zuwa lahira, ta zamo haske a gare shi a ciki ƙabarinsa, ko kuma za ta zame masa tsumman da za a cusa masa a cikin haƙora.

Rashin gaskiya duk amfaninki ne, ya, ke, duniya, ke ƙaskantacciya ce!
Guguwar mutuwa tana lalata dukkan abin da kike bayarwa da sunan nasara.

AZAN-I-MUHAMMADI (KIRAN SALLAH)

Wannan bayanin an cirato shi daga littafin **Durr-ul-mukhtar** da sharhinsa mai suna **Ibni 'Abidin**:

Furucin kalmomin Musulmi na musamman da ke cikin litattafan koyon ibadu na Musulunci, da Musulmi na musamman ke aikatawa, shi ake kira **Azan-i-Muhammadi** (kiran sallah). Wato mutumin da zai yi kiran sallah (Azan ko Adhan) zai hau saman mimbari ya tsaya ya karanta kalmomin larabcin. Idan aka furta shi da wani harshe daban bai zamo kiran sallah ba, ko da kuwa ma'anar ta fita. Ana yin kiran sallah ne domin sanar da shigar lokuttan sallolin farilla biyar da ake yi a yini. Sunnah ce muakkada ga maza su hau mimbari a wajen masallaci su yi kiran sallar. Makaruhi ne mata su yi kiran sallah ko tada iƙama. Haramun ne a gare su namiji (wanda ba muharraminsu ba) ya ji muryarsu.

Ladan (mutumin da yake yin kiran sallah), zai hau saman mimbari a wajen masallaci, ya yi kiran sallah da ƙarfi gwargwadon yadda maƙabta za su ji. Bai halatta ya ɗaga murya ƙwarai ba. Idan ya ce "**Akbr**," yana da zaɓin dakatawa a ƙarshe abin da ake kira jazm ko ya cigaba ta hanyar furta (wasalin harshen Larabci da ke nuna 'a' ana kiran shi) ustun. Kar ya furta wasalin Larabci na 'u' ana kiran shi) oetra. Bai halatta ba a ƙara wasali ko sauti domin tsawaita tsarin sautin da aka amince da shi, ko a gurɓata shi zuwa tsarin waƙe, ko sauraren wannan gurɓataccen tsarin. Sunnah ne a waiwaya dama da hagu yayin da ake faɗar 'salat' da 'falah'. Ba za a kawar da ƙirji da ƙafafu daga fuskantar Alƙibla ba. Ko idan ana kiran sallar a kan hasumiyya; (Ladanin) ya juya a cikin hasumiyyar. An gina hasumiyyar farko bisa umarnin Sayyidina Mu'awuyya 'radiyallâhu 'anh' (19 H. [680 M.]) Akwai mimbarin da aka gina a Masjid (Masallacin) Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam'. Bilal Habashi 'Allah ya yarda da shi' (ya rasu 20 H. Damascus) yana hawa a kai ya kira sallah. Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' ya umarci Bilal ya riƙa sanya ɗan yatsansa a kan kunnuwansa (a lokacin da yake kiran sallah). Yin magana yayin da mutum yake kiran sallah yana wajabta sake kiran sallar. Ya halatta mutum fiye da ɗaya su kira sallah a tare lokaci guda. Amma kiran sallar ba zai inganta ba idan wasu daga ciki ba sa faɗar wasu kalmomi da ɗaya daga ciki yake furtawa. Makaruhi ne tahrimi a yi kiran sallah daga zaune. Sunnah ne Ladani ya zamo sahihin Musulmi, ya san sunnonin kiran sallah, da lokuttan kiran sallah, ya riƙa kiran sallar kowace rana ba ƙaƙƙautawa, ya ƙriƙa yi saboda

Allah ba domin a biya shi ba. Amma ya halatta (a riƙa biyan shi ladar aikinsa) ya kuma karɓa idan an biya shi. Kiran sallar yaro ƙarami da bai balaga ba, bai inganta ba. Saboda muryarsa tana yanayi da kukan tsuntsaye ko kayan kaɗe-kaɗe. [Don haka amfani da lasifika wajen kiran sallah da tada iƙama ba su inganta ba. Bai kamata fasiƙi ya yi kiran sallah ba, da kabbarorin da ya yi a matsayin Limamin sallar jam'i. Makaruhi ne ya yi kiran sallah. Yana da muhimmanci Ladan ya san cewa ana yin kiran sallah ne bayan shigar lokacin sallah, domin sauran Musulmi su san cewa za su yi sallah ne a kan lokacinta. Idan mutum ya kabbara sallah yana kokwanton shigar lokacinta, sallarsa ba ta inganta ba, ko da daga baya ya gano cewa lokacinta ya shiga. Sallar da aka yi bisa tsarin lokaci na kafirai ko fasiƙai ba ta inganta ba. Game da sahihancin tsarin lokaci da ake amfani da shi (a wata ƙasa mai suna) Dar-ul-harb, mutum zai tambayi sahihan Musulmi da ya yadda da su suna da ilimi, domin ya san gaskiya daga gare su.] Idan misali Mutum ya ji kiraye-kirayen sallah a wurare daban-daban waɗanda suka dace da sunnah a lokaci guda; za ya maimaita wanda ya fara ji ne kaɗai, idan daga Masallacin da yake sallah ne, sai ya halarce shi domin samun jam'i. Mutum zai maimata kiran sallar ko da yana cikin karatun Alƙur'ani mai girma. Ba dole ba ne ga mutum ya maimata idan yana sallar jam'i ko yana cikin makewayi ko yana cin abinci ko yana cikin masallaci ko kuma yana koyarwa ko koyon ilimin addini. Kiran sallah da wani harshe da ba larabci ba ko yin sa da tsarin waƙe ya saɓa wa sunnah. Mustahabbi ne ga mutumin da ya ji kiran sallah ya miƙe tsaye idan a zaune yake, idan kuma yana tafiya ne, sai ya dakata. An faɗa cewa ana yi wa shan alwashi hukunci ɗaya da alƙawari: "Wajibi ne ga gwamnatin (Musulunci) ta gina masallaci a kowace unguwa. Ana gina Masallatai ne da dukiyar Bayt-ul-mal. Wajibi ne ga Musulmi su gina wa kansu Masallaci idan gwamnati ba ta gina masu ba.

[Kamar yadda aka gani, idan ana yin ɗa'a ga dokokin Musulunci, za a gina Masallaci a kowace shiyya ta gari, Za a riƙa yin kiran sallah a kowane gari kuma kowa zai ji kiran sallah a shiyyarsu. Ba a buƙatar sai Ladan ya ɗaga murya ko ya yi amfani da lasifika. Amfani da lasifika bidi'a ne da ke kai wa ga saɓa wa sunnonin kiran sallah. Yana sanya wa sunnah ta rasa kyaunta. Wannan dalili ne a sakin layi na goma sha biyar na doka ta ɗari bakwai da talatin da bakwai da hukuma ta amince da ita aka kuma sa hannu a kai, game da neman ilimin addini, bisa umarnin hukumar kula da harkokin addini (a ƙasar Turkiyya) a kwanan watan 1.12.1954 ya bayyana cewa: "An haramta sanya lasifika a kan mimbari (a Masallatai). Idan jama'a (mamu da suka halarci sallar jam'i) suka yi yawan da ba za su iya jiwo kabbara da karatun Liman ba, to ɗaya daga cikin Ladanai ko wani da yake nesa kaɗan da Limamin zai riƙa karɓa kabbarar domin isarwa ga jama'ar da ke nesa."

An yi cikakken bayani mai tsayi game da sajda-i-tilawat a cikin littafin **al-Fiƙh-u-‘alal madhahib-ul-arba’a** haka nan a kashi na biyu na babi na goma sha shida a mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss** cewa karatun Alƙur’ani mai girma ko kiran sallah a radiyo, ko a naɗa a kaset ko a yi amfani da lasifika, ba muryar mutum ba ce ta asali, sauti ne da ake samarwa ta hanyar na’ura wanda wani ya yi, duk da muryar mutum ce ga ainihi, amma ba shi ne yake fitar da ita ba a wannan lokacin. **Azan-i-Muhammadi** (kiran sallah) wanda Musulunci ya bayar da umarni dole ne a samu sahihin Musulmi ya yi kiran. Sautin da yake fita daga bututu ba kiran sallah ba ne. Hamdi Efendi na Elmali ‘Allah ya masa rahama’ ɗaya daga cikin manyan Malamai na farko, ya faɗa a shafi ɗari da ishirin da uku da na sittin da ɗaya na mujalladi na uku na littafin Tafsir: [Kamar yadda aka gani, hukunce-hukuncen da suka shafi ‘saurare da yin shiru’ sun zamo wajibi a fannin ƙira’at, wanda zaɓi ne na ayyukan harshe da ake yi ta hanyar kulawa da wasu gaɓoɓi na furuci da sauti tare da niyya da fahimta. Batu na gaskiya, ko aikin da Jibril (Mala’ika Jibrilu), (a lokacin da yake saukar da Alƙur’ani ga Annabi Muhammad ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’) ya riƙa sanya (Annabi ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’) yana yin ƙira’at (tilawa) maimakon ya riƙa yin tilawar da kansa. Aikin da Allâhu ta’âlâ ya yi kuma shi ne tanzil (saukarwa) da kuma halittar (aikin) tilawa. Don haka muryoyin na abin ƙerawa da ba su da hankali, ba za a kira su tilawa ba; ko kuma wani sauti da ke bayyana a matsayin tilawa. Bisa wannan dalili ne malaman Fiƙihu (wato manyan Malaman Musulunci da suka ƙware wajen ilimin **Fiƙihu**) suka ce amsa kuwwar tilawar da ake yi ba za a kira shi tilawa ba, kuma ba zai wajabta yin wasu ayyuka da suka shafi tilawa ba, kamar misalin sujadar tilawa,[1] wadda ta wajaba ga Musulmi wanda (yake karatu ko tilawa) ya ji ayar sujada. Karatun wasu litattafai ma ba za a kira shi tilawa ba, haka nan sauraren amsa kuwwar sautuka da suka fito daga wani abin kiɗa da ake bugawa ba zai zamo tilawa ba. Don haka sautuka ko muryoyi da suke fita daga rediyo ko rikoda (ko talabijin ko DVD) da suke fitar da muryar wani mutum yana karatu ko tilawar Alkur’ani mai girma, to amsa kuwwa ko kwaikwayo na tilawa, ba tilawar ba ce da kanta, don haka wannan ba zai wajabta saurare ko yin shiru (ga Musulmin da suka ji ko sauraren ta ba). Wato (ayoyin) Alƙur’ani mai girma da suka wajaba a saurara, su ne ayoyin da aka karanta bisa tsarin tilawa, maimakon (sautukan) ayoyin da aka kunna. Amma faɗar cewa ba wajibi ba ne ko mustahabbi, ba wai ana nufin bai halatta ba ne, ko kuma

[1] A duba sashe na baya a babi na goma shida a mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss.**

wajibi ne kada a saurari karatun ba. Domin kunna (ayoyin) Alkur'ani mai girma (a radiyo da makamantanta) da sauraren (ayoyin daga) Alkur'ani maigirma ayyuka ne mabambanta. Abu ne da aka riga aka sani cewa ba abu ne da ya dace ba a sanya karatun (ayoyin) Alƙur'ani (a rediyo da makamantansu) ko yin sa ta amfani da wani abin kiɗa. Batun gaskiya ma, aikata ƙurbat, wato a yi karatu (Alƙur'ani mai girma, laifi ne yin hakan a wuraren da za su iya cutarwa ne ga darajar da ya kamata a bayar wajen karatun. Amma idan wani ya aikata laifin, ƙin sauraren, maimakon sauraren shi ma wani laifin ne. Misali, laifi ne yin karatu (wato karatu ko tilawar Alƙur'ani mai girma) a cikin makewayi. Idan wasu suka aikata hakan, ƙin saurarensu ba zai samar da thawab (lada a lahira) ba. Haka nan zancen cewa ba ibada ba ne sauraren amsa kuwwar karatun Alƙur'ani mai girma ko kuma sanya su a na'urorin da suka ƙunshi rikoda ko a radiyo, bai kamata a ce ba a sauraren shi ba. Saboda wani abu ne da yake kama da tilawar. Kuma wani abu ne da yake nuni da Kalam-i-nafsi, (Kalmomin Allâhu ta'âlâ). Don haka duk da cewa ba wajibi ba ne ko mustahabbi sauraren tilawar, amma ba wai kawai ya hallata ba, abin yabo ne matuƙa; wato bai kamata a ce ba a girmama shi ba yadda ya dace. Irin wannan batun daidai yake da mutum Musulmi ya ga takardar Alƙur'ani mai girma a wurin da bai dace ba, wajibinsa ne ya ɗauke ta ya mayar da ita inda ya dace, maimakon wucewa kawai."]

An rubuta a litattafan Fiƙihu, misali a littafin **Kadikhan**: "Sunnah ne yin kiran salah. Saboda wani hatimi ne ko tambari na Addinin Musulunci, idan mazauna gari ko unguwa a cikin birni suka daina yin kiran sallah, wajibi ne gwamnati ta tilasta masu su cigaba da yin kiran sallar. Ladani (Musulmin da aka ɗora wa alhakin kiran sallah), wajibi ne ya san Alƙibla da kuma lokuttan sallolin farilla biyar. Saboda sunnah ne yin kiran sallah a tsaye ana fuskantar Alƙibla daga farko har zuwa ƙarshe. Ana yin kiran sallah ne domin sanar da mutane shigar lokuttan sallolin farilla biyar da kuma lokacin iftar, (wato lokacin da Musulmi ke shan ruwa [buɗa baki] a cikin azumi). Sanya mutumin da bai san lokuttan sallah ko fasiƙi su yi kiran sallah yana jawo fitina. Makaruhi ne ga yaro maras nutsuwa da mashayin giya ko mai taɓin hankali da mai janaba ko mace su kira sallah. Ladan ne ya kamata ya riƙa yin kiran sallah. [Akwai lada ƙwarai yin Mawlid, mutum ya yi da kansa da zuwa inda ake yi. Amma haramun ne ga mace ta bari mazan da ba muharramanta ba su ji muryarta ta hanyar yin maulidi ko kiran sallah, ko kuma yin waƙa da magana da ƙarfi fiye da kima, haka nan haramun ne ga namiji ya ji muryar matar da ba muharramarsa ba. Macen da za ta yi wannan, za ta yi ga `yan uwanta mata kawai, sannan kar ta bari a naɗi muryarta a kaset ko a saka a rediyo ko talabijin.] Kazalika makaruhi ne ga mutumin da yake zaune ko ba shi da alwala ko yake kan dabba (kamar doki) da suke cikin

birane su yi kiran sallah, amma ba za a sake kiran sallar ba idan sun riga sun yi. Ana yin kiran sallah ne a kan minbari ko kuma wani bigire a wajen masallaci. Ba a yi a cikin masallaci. Makaruhi ne yin kiran sallah bisa tsarin 'telhin' wato rerewa ko tsawaitawa wajen furuci wanda zai iya sauya ma'anar kalma. Ba a yin kiran sallah da wani yare idan ba Larabci ba" an faɗa a cikin littafin **Fatawa-i-Hindiyya** cewa: "Makaruhi ne ga Ladani ya buɗe murya ƙwarai ta yadda zai iya suƙewa (a lokacin da yake kiran sallah). **Ibni 'Abidin** 'Allah ya yi masa rahama' ya ce "Sunnah ne ga Ladan ya hau kan wani abu mai tudu idan zai yi kiran sallah, domin a ji shi daga nesa. Ya halatta ga Ladanai biyu su yi kiran sallah a lokaci guda." Idan an fahimci waɗannan zantukan na malamai, bidi'a ne yin kiran sallah ko tada iƙama ko yin sallah ta amfani da lasifika. Aikata bidi'a laifi ne mai girma. Wani Hadisin Annabi 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya ce: "**Idan mutum ya aikata bidi'a ba za a karɓi sauran ayyukansa na ibada ba**." Duk da cewa muryar da ake ji daga lasifikar ta yi kama da ta mutane, amma ba muryar mutum ba ce. Sauti ne da yake fita daga na'ura mai maganaɗisu. Ba ɗaya take da muryar mutumin dake kan wani abu mai tudu ba. Laifin ya fi tsananta idan aka sanya lasifikar a hagu ko dama ko bayan mimbarin ko saman rufi, ta yadda sautin zai riƙa fita ba ta fuskar alƙibla ba. Ba wajibi ba ne sai murya ta isa nesa ba, ko mu dogara da sautin da ke fita daga na'urar ba. Domin wajibi ne a gina masallaci a kowace unguwa, ta yadda mutane za su riƙa jin kiran salla a ko'ina. Haka nan an halatta **Azan-i-jawƙ**. Ladanai fiye da ɗaya su kira sallah tare shi ake kira **Azan-i-jawƙ**.

Za a ji muryar mutum mai cike da shauƙi daga nesa, da take sanyaya zuciya da rai, ta kuma tsarkake imanin mutane. [Ladan zai yi kiran sallah, shi kuma Liman ya yi karatu da muryoyin su na asali da sauti daidai da yadda Musulmin da ke ciki da wajen Masallaci za su ji. Makaruhi ne su ƙure muryarsu domin wanda ke nesa da Masallacin ya ji. Wannan shi yake nuna amfani da lasifika ba dole bane.] A taƙaice, sautin da yake fita daga bututun magana da ake kira lasifika ba kiran sallah ba ne. **Azan-i-Muhammadi** (kiran sallah) shi ne sautin da yake fita daga bakin Ladan. Hadisi ya zo a cikin littafin **Hilya-t-Awliya** wanda babban Malami Abu Nuaym Isfahani (Ahmad bin Abdullah) 'rahmatullâhi 'alaih' (336 H. [948 M.) – 430 [1039]) ya rubuta, cewa: "**Muryar kiran sallah da aka yi amfani da wani abin kiɗa, muryar Sheɗan ce. Mutanen da suke** (amfani da lasifika) **wajen yin sa, sheɗanun Ladanai ne**."

An faɗa a cikin wani Hadisi cewa: "**Alamu ne na kusantowar tashin ƙiyama a riƙa karatun Alƙur'ani mai girma ta hanyar mizmars. Za a riƙa karanta shi ba don Allah ba, sai don jin daɗi**," "**Akwai mutane da dama da**

suke karatun (da tilawar) **Alƙur'ani mai girma, amma Alƙur'anin yana la'antarsu**," "**Zamani zai zo wanda Ladanai su zamo marasa kirki a cikin al'ummar Musulmi**," "**Zamani zai zo wanda za a riƙa karanta Alƙur'ani mai girma** (da tilawa) **ta hanyar mizmars. Allâhu ta'âlâ zai la'ance su** (waɗanda suka aikata haka)." Mizmars na nufin dukkan wasu kayan kaɗe-kaɗe da bushe-bushe. Lasifika mizmars ce ita ma. Ya kamata Ladanai su ji tsoron wannan Hadisin, su guji yin (aikin ibadarsu) ta amfani da lasifika. Wasu marasa ilimin addini ƙwarai suna cewa lasifika tana da amfani, domin tana kai murya zuwa wurare masu nisa. Manzon Allah ya ce: "**Ku yi aikin ibada kamar yadda kuka ga ni da Sahabbaina muna yi! Mutanen da suke kawo sauye-sauye a aikin ibada su ake kira 'ahl-i-bid'at'** (mutane masu aikata bidi'a) **masu aikata bidi'a shakka babu 'yan wuta ne. Ba za a karɓi ayyukansu na ibada ba**." Ba daidai ba ne a riƙa cewa "Muna ƙara abubuwa masu amfani ga ayyukan ibada." Irin waɗannan zantukan, ƙarairayi ne da maƙiyan Musulunci suke ƙagawa. Manyan Malaman Musulunci kaɗai suka san ko ya kawo sauyin yana da amfani. Waɗannan muhimman Malaman su ake kira **Mujtahidai**. Mujtahidai ba kawo sauyi bisa ra'ayin kansu. Sun san irin ƙari ko sauyin da yake zama bidi'a. Akwai ittifaƙin cewa bidi'a ne yin amfani da 'mizmar' wajen kiran sallah. Zukatan mutane ne za su sanya su samu albarka da ƙaunar Allâhu ta'âlâ. Ita zuciya kamar madubi take. Ayyukan ibada suna wankewa da tsarkake zuciya. Bidi'a da saɓo suna sanya duhu a zuciya, ta yadda ba za ta iya samun haske da annuri da suke zuwa wurinta ta hanyar ƙauna ba. Ingantattun Musulmi suna fargabar haka. Ba sa son aikata zunubi. Suna son yawaita ayyukan ibada. Baya ga sallolin farilla biyar na yini, suna kwaɗayin ƙari. Zukatan mutane na jin daɗin aikata saɓo; za su ji kamar wani abu ne mai amfani. Dukkan bidi'a da saɓo suna kawo jin daɗi da ƙarfafawa ga zukatan mutane, wanda saɓa wa Allâhu ta'âlâ ne. Ɗaya daga cikin waɗannan shi ne yin kiran sallah da lasikifa. Ra'uf Ahmad, ɗaya daga cikin waɗanda suka gaji 'Abdullah Dahlawi, ya faɗa a cikin muƙaddimar **Durr-ul-ma'arif** cewa: "Haramun ne yin karatun Alƙur'ani mai girma ko yin wasu ayyukan ibada ta amfani da kayayyakin kaɗe-kaɗe da ake kira 'mazmars'." Misalin wannan shi ne kiran sallah da lasifika.

[An faɗa a cikin littafan Shafi'iyya mai suna **al-Muƙaddima-t-ul-hadramiyya** (wanda 'Abdullah bin 'Abd-ur-rahaman ya rubuta) da **al-Anwar li-a'mal-il-ebrar** (na Yusuf Erdebili, ya rasu 799 H.) cewa: "Akwai sharuɗɗa uku da Musulmi zai cika kafin ya zama sahihi a Mazhabar shafi'iyya na yin koyi da Limami (a sallar jam'i) a masallaci ko a wajen masallacin: 1) wajib ya tsaya (wurin da zai iya) ganin Liman 2) wajibi ne ya riƙa jiwo muryar Liman; 3) Kar ya kasance a samu zira'I ɗari uku (300×0.42 =mita 126) tsakaninsa da sahu (na jama'a)." Ko a Mazhabar Hanafiyya ko Shafi'iyya,

babu inda sallah ta inganta ta hanyar bin Limamin da ke nesa wanda ake gani da kafar talabijin. **Bidi'a** ne gurɓata ayyukan ibada da irin waɗannan abubuwa da babu su a zamanin Salaf-i-salihin. Kamar yadda muka fahimta a aya ta ɗari da huɗu ta suratun Nisa'i, mutanen da suke yin bidi'a ta hanyar yin kiran sallah (adhan) da sallah a rediyo ko talabijin ko lasifika za su shiga wuta. Muryar da ke fita daga lasifika ko rediyo ba kiran sallah ba ne da kansa, kawai dai wani abu ne mai kama da shi. Kamar misalin mutum ya ga kansa a madubi ko hoto, ba mutumin ba ne da kansa, sai wani abu ne mai kama da haka, duk da tsananin kamance-ceniyar da ke akwai.]

WAJIBAN SALLAH: wajiban sallah a Mazhabar Hanafiyya su ne: Kar a karanta komai bayan an ce "Subhanaka.." (idan kana sallar jam'i) a bayan Liman. Ga Liman kuma (idan yana jan sallah (ta jam'i) da mutumin da yake sallah shi kaɗai, su karanta suratul Fatiha sau ɗaya a (kowace) raka'a biyu ta sallar farilla da kowace raka'a ta kowace irin sallah. Karatun surah (ƙarin sura da ake kira) Dhamm-i-Sura sau ɗaya a raka'o'i biyu na farko na sallar farilla da suke da raka'o'i huɗu ko uku, da kowace raka'a ta kowace irin sallah. Yin karatun Fatiha a raka'o'i biyu na farko ga salloli masu raka'o'i huɗu ko uku. Daga sallar farilla zuwa wata sallar farilla. Karatun Fatiha ya zo kafin karatun sura. Da zama a Ƙa'da-i-ula (zaman farko). Yin sujudu biyu, ɗaya bayan ɗaya. Yin (karatun) tahiyyat (tahiya) a Ƙa'da-i-akhira (zama na ƙarshe). Ƙare sallah da yin sallama, (wato cewa "As-salam-u-'alaikum wa rahmatullah.") Yin karatun Ƙunut (alƙunut) a sallar witiri. Yin ƙarin kabbarori a yayin sallar Idi. Yin karatuttukan (cikin sallah) da ikhfa', (wato cikin sirrantawa) a inda ake sirrantawa, da jahr (wato bayyanawa) a inda ake bayyanawa. Yin Ta'dil-i-arkan a yayin da kake sallah, [wanda ke nufin, kamar yadda aka bayyana a baya, tsayawa cikin nutsuwa gwargwadon yadda mutum zai ce "Subhanallah" yayin ruku'u da ɗaukakowa, wato tsayuwa bayan kammala ruku'u, da lokacin sujada da yayin da mutum ya zauna, wato zaman da ke tsakanin sujudu biyu.) wannan tsayawar ita ake kira 'tumaninat'.] Yin sujadar Tilawa idan ka karanta ayar Tilawa a yayin da kake sallah, ko ka ji Liman ya faɗa (a cikin sallar jam'i). Yin sujadar rafkannuwa (idan buƙatar hakan ta taso). (An yi bayanin sujadar tilawa da ta rafkannuwa a babi na goma sha shida na mujalladi na huɗu a littafin **Endless Bliss**.) Miƙewa tsaye cikin gaugawa a zaman farko bayan kammala karatun tahiya a sallolin farilla masu raka'o'i huɗu. Koyi da Liman a kowane lokaci. Wani ƙaulin an ce yin sallar farilla a cikin jam'i, sai dai idan akwai uzuri (wato dalili mai ƙarfi da Musulunci ya shardanta) da zai hana yin hakan. Bayan kowaɗanne sallolin farilla ishirin da uku da ka yi bayan sallar asuba ta ranar arfa, (wadda ita ce ranar daren) babbar sallar idi, har zuwa sallar la'asar ta rana ta huɗu ta babbar sallar, za a karanta **takbir-i-tashrik**, (wadda aka yi

cikakken bayaninta a babi na ishirin da biyu na mujalladi na huɗu a littafin **Endless Bliss**).

SUNNONIN SALLAH: Sunnonin sallah a mazhabar Hanafiyya sun ƙunshi:

A wajen kabbarar harama, (wato kabbarar da ake yi idan za a fara sallah) haka nan a wajen kabbarar Kunut, (wato lokacin da za ka ce "Allahu Akbar" kafin ka fara karatun Alƙunut a yayin tsayuwa ta ƙarshe) a sallar witiri, ga maza, su ɗaga tafukan hannayensu zuwa saitin kunnuwansu, ga mata kuma, su ɗaga tafukan hannuwansu zuwa saitin kafaɗunsu, kuma (dukkansu maza da mata) su fuskantar da tafukan hannuwansu su kalli Alƙibla. A yayin tsayuwa a cikin sallah, a riƙe hannun hagu ta amfani da babban ɗan yatsa na hannun dama. Mata kuma su ɗora hannunsu na dama a kan na hagu. Maza za su ɗora hannuwansu a ƙasan cibiyarsu, mata kuma su ɗora hannuwansu a ƙasan mamansu. Karanta addu'ar "**Subhanaka…**" a raka'a ta farko ta kowace sallah, ga Liman da mamu da mai sallar shi kaɗai. Ga Liman da mai sallah shi kaɗai, za su faɗi ta'awizi da Basmala bayan addu'ar Subhanaka a raka'a ta farko. Haka nan ga Liman da mai sallah shi kaɗai su furta Basmala kafin su fara karatun Fatiha a kowace raka'a. faɗar "Ameen – a asirce" (a ƙarshen karatun fatiha) wanda ya shafi Liman (da yake jan sallah) da (jama'ar da suke bin sa a sallar jam'i) wato mamu, da Liman ya faɗi "**…wa la-d-dallin**," (waɗannan su ne kalmomi biyu na ƙarshen sura ta farko ta Alƙur'ani mai girma da ake kira suratul Fatiha, haka abin yake ga mai sallah shi kaɗai[1] idan ya kammala karatun Fatiha. Wajen yin kabbara (wato cewa "Allahu Akbar") yayin duƙawa yin ruku'u (daga tsayuwa). Sai kuma a ɗora hannuwa a kan guiwa tare da wawware 'yan yatsu, a yayin ruku'u. Sai a ce "Subhâna Rabb-iy-al 'adhîm," sau uku acikin ruku'u. Yayin ruku'u, kafaɗu da ƙugu za su yi saiti da juna.[2] Ga Liman kuma, (wanda yake jan sallar jam'i) da wanda yake sallah shi kaɗai sai a ce "**Sami-Allahu liman hamidah**," yayin ɗaukakowa daga ruku'u. Ga mamu da ke sallah cikin jama'a, ko wanda yake shi kaɗai ya ce "**Rabbana laka-l-hamd**," yayin ɗaukakowa daga ruku'u. Faɗar "**Allahu akbar**" yayin duƙawa zuwa sujada daga (tsayuwa) Kiyam. Faɗar "Subhana Rabb-iy-al-'a'la" a cikin sujada, da faɗar "**Allahu akbar**" yayin (ɗago kai da) zama daga sujada ta farko. Faɗar "**Allahu akbar**" yayin komawa (sujada ta biyu). Game 'yan yatsu waje guda a yayin sujada. A yayin sujadar, maza za su ɗora guyawunsu a kan ƙasa, su raba cikinsu da

[1] Ga mai sallah shi kaɗai' wato muna nufin mai sallah shiɗai.

[2] A nan mafi yawancin dokokin sun shafi maza ne kawai, Muna ba mata shawara idan suna neman cikakken ƙarin bayani akan sallar mata su duba sakin layi na ƙarshe a rarrabewa na goma sha huɗu na mujalladi na hudu a littafin **Endless Bliss.**

cinyoyinsu, yayin da mata za su haɗe cikinsu da cinyoyinsu, faɗar "**Allahu akbar**" yayin ɗagowa daga sujada ta biyu. Maza su zauna a kan ƙafarsu ta hagu, su tokare ƙafarsu ta dama. Karanta salati a Ka'da-i-akhira (zaman ƙarshe). Juya kai (dama da hagu) yayin sallama. Yayin (zaman farko da na biyu za a yi karatun) Tahiyyat (tahiya) za a ɗora hannuwa bisa cinyoyi a miƙe ɗan yatsa manuniya ya yi saiti da guiwa, sauran yatsun kuma a dunƙule su. Saita hannu da yatsun ƙafa su kalli Alƙibla yayin sujada, sannan tafukan hannuwan su yi saiti da kunnuwa. Yin sujada da gaɓoɓi bakwai a kan ƙasa a lokaci guda. Karatun fatiha kaɗai a lokacin (tsayuwa) ta raka'o'i biyu na ƙarshen sallar farilla mai raka'o'i huɗu. Yin kiran sallah bisa koyarwar Sunnah. Yin iƙama ga maza (kafin su kabbara) sallar farilla, ko da suna cikin sallar jam'i ko suna sallah su kaɗai.

MUSTAHABBAN SALLAH: Mustahabban sallah a Mazhabar Hanafiyya su ne:

Mamu kada su zauna, su miƙe tsaye da zarar Ladan ya ce "**Hay-ya-'ala-s-salah**," yayin da yake tayar da Iƙama, (wadda ke nuna yin kira ga Musulmi su yi sallah cikin jam'i). Ga maza su taɓa fatun kunnuwansu yayin da suke yin kabbarar harama da kabbara yayin Alƙunuti ta sallar witiri. Yayin naɗe hannuwa lokacin tsayuwa, mutum ya matse hannunsa (na hagu). Kallon bigiren da ake sanya goshi yayin sujada a lokacin da mutum yake tsaye. Yin tasbihi a yayin ruku'u da sujada, (wato mutum ya ce "**Rabb-iy-al 'adhim**," a cikin ruku'u, da "**Rabb-iy-al-a'la**," a cikin sujada) sau biyar ko sau bakwai. Kallon ƙafafu yayin ruku'u. haɗe ƙafafu yayin tanƙwarawa zuwa ruku'u. Raba ƙafar dama da ta hagu yayin ɗaukakowa daga ruku'u zuwa tsayuwa. Fara sanya hanci a ƙasa kafin goshi a lokacin sujada. Kallon hanci da idaniya biyu yayin sujada. Kallon kafaɗu yayin Sallama. Ga mutumin da yake hagun Liman (a sallar jam'i) ya yi niyyar cewa yana gaishe da Liman da Mala'iku Hafaza[1] (masu rubutu) da (al'ummar Musulmi da ke) sallar jam'in. Ga mutumin da yake daman Liman, ya yi niyyar cewa yana gaishe da Liman da mala'ikun rubutu, da sauran mamu. Ga mutumin da babu kowa a hagunsa da damansa, ya yi niyyar cewa yana gaishe da mala'ikun rubutu kaɗai. Kar mutum ya riƙa share gumi (zufa) idan yana sallah. Guje wa yin tari. Guje wa yin hamma. Kallon cinyoyi yayin da mutum yake zaman tahiya. Liman ya juyo ya kalli mamu bayan sallame sallar jam'i.

[1] A duba sakin layi na ishirin da ɗaya na babin da ake kira 'Shika-shikan Imani' na littafin Imani da Musulunci, ɗayane daga cikin wallafar Hakîkat Kitâbeɓi, Fâtih, Istanbul, akan mala'ikun da ake kira Hafaza, ana kuma kiransu da Kirâman Kâtibîn.

ADAB (LADUBBAN) SALLAH

1- Ga wanda yake sallah shi kaɗai da kuma wanda (ya bi jam'i) ya bi Liman, ya karanta wannan addu'ar bayan sallama: "**Allahumma anta-s-salam-u-wa minka-s-salam tabarakta ya dhal-jalali wa-l-ikram**." Sannan ya karanta wannan sau uku: "**As tagfirullah-al 'adhim al-ladhi la ilaha illa Huw-al-Kayyuma wa atubu ilaih**." Wannan addu'ar ita ce **Istigfar**. Ya halatta a karanta ta ko da mutum ba shi da alwala.

2- Daga nan sai ya karata (ayar Alƙur'ani, wato) **Ayat-al-kursi**.

3- Karanta "**Subhanallah**" sau talatin da uku.

4- Karanta "**Al-hamd-u-li-llah**" sau talatin da uku.

5- Karanta "**Allahu akbar**" sau talatin da uku.

6- Sai a Karanta wannan addu'ar sau ɗaya: "**La ilaha il-l-Allahu wahdahu la sharikalah lahul mulku wa lahul hamdu wa Huwa 'ala kulli shay'in ƙadir**."

7- Ɗaga hannuwa da buɗe tafukan hannuwa ta fuskar 'Arshi, wanda nan ne Alƙibla domin yin addu'a, sai mutum ya roƙi Allah bisa yaƙini da tsarkin zuciya.

8- Idan ka yi sallah tare da jama'a (wato idan ka yi sallah cikin jam'i) ka tsaya a yi addu'a (ta gama gari).

9- Faɗar Amin a ƙarshen addu'a.

10- Shafa hannuwa a hankali a kan fuska.

11- Sannan a karanta suratul **Ikhlas** sau goma sha ɗaya, kowace da Bisimillah, kamar yadda ya tabbata a Hadisi da aka ruwaito a shafi na ƙarshe na mujalladi na ɗaya na littafin **Beriƙa**. Bayan nan sai a karanta surori biyu na Alƙur'ani da suka fara da "**Kul-a'udhu…**" sau ɗaiɗaya, sannan a karanta "**astaghfirullah**," sau sittin da bakwai, sannan a cika da cikakkar addu'ar istigifari sau uku ya zamo saba'in, daga nan sai a ce "**Subhanallahi wa bihamdihi subhanallah-il 'adhim**," sau goma. Bayan nan sai a karanta ayar Alƙur'ani da ta fara da "**Subhana Rabbika…**" Waɗannan ladubban an rubuta su a cikin littafin **Meraƙ-il-felah**. An ruwaito a cikin Hadisi cewa: "**Duk addu'ar da aka yi** (a kowace sallar farillah) **guda biyar, za a karɓe ta** (Allâhu ta'âlâ zai karɓa)." Idan za a yi addu'ar bayan sallah (da kowace irin addu'a) za a yi ta ne da nutsuwa kuma a sirrance. Makaruhi ne yin addu'ar bayan sallah (da sauran addu'o'i) a lokacin da mutum ya kammala sallolin farilla kaɗai, ko a wasu lokutta na musamman kaɗai, ko rera waƙe a madadin addu'ar. Idan aka kammala addu'o'in, sunnah ne mutum ya shafa tafukan hannuwansa a fuskarsa. Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam'

yana yin addu'a idan ya kammala ɗawafi da bayan cin abinci da kafin kwanciya bacci. Yayin da yake addu'ar ba ya ɗaga hannuwansa, kuma ba ya shafawa a fuskarsa. Ya kamata a riƙa yin addu'o'in da zikiri a cikin sirranta murya. (A duba babi arba'in da shida da na arba'in da takwas na mujalladi na biyu, da babi na hamsin da bakwai na mujalladi na uku, da kuma babi na ishirin da biyar na mujalladi na shida na littafin **Endless Bliss**, a kan zikiri). Mustahabbi ne zama da alwala yayin addu'ar bayan sallah da sauran addu'o'i irin su istigfari. Haramun ne yin rawa ko jujjuyawa ko tafi ko amfani da kayan kiɗa da suka ƙunshi mandiri da ganguna da mabusa, ko kayan kiɗa na karkaɗawa; irin waɗannan ayyuka ne na masu (ƙaryar) sufanci; amma manyan Malaman Musulunci sun yi ittifaƙi wajen haramta su. Kamar yadda muka gani, yana da kyau (Musulmi da suka yi) sallar jam'i da Liman su yi addu'o'insu a cikin sirrantawa. Haka nan ya halatta ga ɗaiɗaikun mutane su yi addu'o'insu su kaɗai, sannan suna iya fita ba tare da sun yi addu'a ba. An faɗa a cikin littafin **Fatawa-i-Hindiyya** (wanda wani ayarin malamai suka haɗa ƙarƙashin jagorancin Sheikh Nizam Mu'in-ud-din Naƙshibandi) cewa: "A sallolin da ake yin nafilolin ƙarshe (misali sallar Azahar da La'asar da Isha'i) makaruhi ne ga Limamin (da ya jagoranci sallar farillar ta jam'i) ya zauna bayan sallama. Zai tashi da gaugawa ya yi sallar nafila bayan ya matsa zuwa damansa ko hagunsa ko baya kaɗan. Yana kuma iya tafiya gida sannan ya yi sallar nafilar a gida. Musulman da (suka yi sallar) jam'i da wanda ya yi sallah shi kaɗai su zauna su yi addu'a a wajen da suke. Sannan ya halatta su tashi su yi nafila a wurin da suke zaune, ko su matsa gefen dama ko hagu ko baya. A sallolin da ba a yi masu nafilar ƙarshe, makaruhi ne ga Liman ya zauna yana kallon Alƙibla bayan sallama; batun gaskiya ma, bidi'a ne. Zai iya tashi tsaye ya fita, ko ya juyo ya kalli jama'a, ko ya juya dama ko hagu sannan ya sake zama."

ADDU'O'IN DA AKE YI (ko zikiri da ake yi), BAYAN SALLAH

"Al-hamd-u-li-l-lahi Rabb-il-alamin. As-salatu wa-s-salamu 'ala Rasulina Muhammadin wa 'ala Alihi wa Sahabihi ajma'in. Ya Rabbi (Ya Ubangijina, Allah)! Ka karɓi wannan sallar da na yi! Ka sad ani da khayr (alheri) a lahira (ƙiyama) da 'aƙibat (ƙarshe). Ka sa in cika da kalmar shahada idan ajalina ya zo, (wato mutuwa). Ka yi 'afw da maghfirat (gafara da afuwa) wa 'yan uwana da suka rasu. Allahum-maghfir warham wa anta khayr-ur-rahimin. Tawaffani Musliman wa-al-hiƙni bis-s-salihin. Allahummaghfirli wa-li-walidayya wa-li-ustaziyya wa-li-l-mu'minina wa-l-mu'minat yawma yaƙum-ul-hisab. Ya Rabbi! Ka kare ni daga sharrin

shedanu da sharrin maƙiya da sharrin kaina! Ka yi wa gidanmu albarka da kyakkyawa da halal, da wadata (abinci da sauransu). Ina roƙo ka yi albarka ga ahl-i-islam, (wato Musulmi) da salamat (aminci da tsaro)! Ka ƙasƙantar da watsa a'da-yi-muslimin, (wato maƙiyan Musulmi)! Ka taimaki Musulmin da suke yaƙi da kafirai, ka taimake su da imdad-i-ilahi! Allahumma innaka 'afuwwun karimun tuhib-b-ul-'afwa fa'fu 'anni. Ya Rabbi! Ka warkar da marassa lafiyarmu, Ka kawo sauƙi ga waɗanda ke cikin tsanani! Allahumma inni as'aluka sihhata wa-l-afiyata wa-l-amanata wa husn-al-khulƙi wa-r-ridaa bi-l-ƙadari bi-rahmatika ya arham-ar-rahimin. Ina roƙon Ka yi albarka ga iyaye da 'ya'yana da 'yan uwana da abokaina da sauran 'yan uwa musulmi da rayuwa mai cike da alkhairi da kyawawan ɗabi'u da cikakkar lafiya da shiriya da istiƙamat, ya Rabbi! Amin. Wa-l-hamd-u-li-l-lahi Rabb-il-'alamin. Allahumma salli 'ala sayyidina Muhammadin wa 'ala Al-i-Muhammad kama sall-ay-ta 'ala Ibrahima wa 'ala Al-i-Ibrahim innaka Hamid-un-Majid. Allahumma barik 'ala Muhammadin wa 'ala Al-i-Muhammad kama barakta 'ala Ibrahim wa 'ala Al-i-Ibrahim innaka hamid-un-majid. Allahumma Rabbana atina fi-d-dunya hasanatan wa ƙina 'adhab-an-nar birahamatika ya-Arham-ar-rahimin. Wal-l-hamd-u-li-l-lahi Rabb-il-'alamin. Astaghfirullah, astaghfirullah, astaghfirullah, astaghfirullah-al-'adhim al-karim al-ladhi la ilaha illa Huw-al-Hayy-al-Ƙayyuma wa atubu ilaih."

MAKARUHAN SALLAH

1- Waiwayawa kowane gefe, yayin da wuya yake duƙe.

2- Yin wasa da wani abu a jikinka.

3- Share wajen da ake yin sujada da hannu (cikin sallah) ba tare da uzuri ba (wato dalili mai ƙarfi).

4- Ga maza su ɗora hannuwansu a ƙirji yayin tsayuwa (a cikin sallah) da ajiye su saitin ƙirji a yayin sujada.

5- Raƙwarƙwasa 'yan yatsu.

6- Hardɛ ƙafafu ba tare da uzuri ba.

7- Ɗage ɗaya daga cikin ƙafafu a lokacin sujada.

8- Sanya wani abu a cikin sallah wanda mutum ba zai iya sanya shi ba a gaban manyansa (magabatansa).

9- Yin sallah kana kallon fuskar wani.

10- Yin Sallah a gaban wuta.

11- Sanya hoto a jiki ko a jikin sutura.

12- Yin hamma ba tare da wani uzuri ba.

13- Yin sallah da hannuwa a cikin hannun riga.

14- Zama tare da tsaida ƙwabri, kamar kare.

15- Rufe idanu.

16- Juya hannuwa daga kallon Alƙibla.

17- Yayin sallar jam'i, komawa bayan sahu, alhali akwai wuri a sahu da ke gabanka (na aƙalla mutum ɗaya). Idan ya zama akwai wani tare da kai a wannan sahun, to ya zama tanzihi karhat (makruh), yayin da babu kowa kuma ya zama tahrimi karahat. A nan ka bar wani abu wanda yake wajibi; don haka babu abin da zai gyara sallarka sai dai ka sake wata sallar.

18- Yin sallah a gaban kabari ba tare da wani abu ya yi maka shinge tsakaninka da shi ba.

19- Yin sallah a gaban najasa. (An yi cikakken bayani a kan najasa a babi na shida a mujalladi na huɗu na littafin Endless Bliss.)

20- Mace da namiji su yi sallah daban-daban jere da juna.

21- Yin sallah a cikin matsin buƙatar zuwa makewayi.

22- Bayan ɗagowa daga ruku'u, fara sanya hannu a ƙasa yayin sujada, kafin (sanya guiwa a ƙasa) ba tare da wani uzuri ba.

23- Yin susar ƙaiƙayi a kowane ɓangare na jiki sau biyu a rukuni ɗaya na sallah (wanda ya fara daga tsayuwa zuwa wata tsayuwar. Sallar mutum tana ɓaci idan ya ɗaga hannunsa sau uku ya yi susa sau uku, don haka sai ya sake sallah).

24- Rigan Liman yin ruku'u (a cikin sallar jam'i).

25- Ɗagowa daga ruku'u kafin Liman ya ɗago.

26- Rigan Liman yin sujada.

27- Ɗagowa daga sujada kafin Liman ya ɗago.

28- Dogara ga wani abu da ke kusa da kai, sai dai idan akwai uzuri da ya wajabta haka.

29- Yayin ɗagowa daga sujada, fara tasowa da guyawu kafin hannuwa daga ƙasa (ko shimfiɗar sallah).

30- Goge ƙura a fuska da idanu.

31- Araka'a ta biyu, mutum ya tsallake surar (da ke kusa) da wadda ya karanta a raka'a ta farko.

32- Karanta sura ɗaya a raka'o'i biyu da ke jere, ko karanta sura ɗaya sau biyu a raka'a ɗaya. (Ya halatta a yi a sallar nafila).

33- Karanta sura a raka'a ta biyu wadda take sama da wadda aka karanta a raka'a ta farko.

34- Karanta sura a raka'a ta biyu wadda ta ɗara wadda aka karanta a raka'a ta farko da ayoyi uku.

35- Duƙawa ko miƙewa tsaye ta hanyar dafa wani abu da ke kusa da kai, sai dai idan akwai wani uzuri, (wato dalili mai ƙarfi na yin haka wanda Musulunci ya yadda da shi) da ya wajabta yin hakan.

36- Korar ƙwari da hannu.

37- Naɗe hannun riga ko bayyana kafaɗa ko ƙafafu a cikin sallah.

38- Nuna halin ko in kula da rufe jiki a waje.

39- Yin sallah a kan hanyar da ake wucewa.

40- Kirga tasbihi da yatsun hannu a yayin ruku'u ko sujada.

41- Ga Liman ya shige can cikin kusurwar liman ta yadda zai faku idan da za a saki labule.

42- Haka nan Liman ya zamo a kan wani bigire da ya yi sama ko ƙasa da zira'i ɗaya tsakaninsa da mamu, idan shi kaɗai ne (a bigiren). (Zira'i ɗaya yana daidai da rabin mita).

43- Ga Limami ya yi sallah a wani sashe wanda ba kusurwar liman ba.

44- Furta Amin a cikin sallah da murya mai ƙarfi.

45- Kammala dukkan karatun da aka fara a yayin tsayuwa, (wato suratul Fatiha da sauran surori) kafin yin ruku'u.

46- Kammala dukkan tazbihi a cikin ruku'u (wato "Subhana Rabb-iy-al 'adhim") kafin miƙewa tsaye.

47- Tsayuwa a kan ƙafa ɗɗaya ba tare da (wani ƙwaƙƙwaran dalili ba) Uzuri ba.

48- Motsawa gefe da gefe yayin da ake sallah.

49- Kashe ƙwari waɗanda ba sa cizo.

50- Sunsuna wani abu yayin da mutum yake sallah.

51- Yin sallah da kai a buɗe. Mahajjata suna yi da kai a buɗe ne saboda suna cikin ihirami. (A duba babi na bakwai na mujalladi na biyar a littafin Endless Bliss a kan 'ihirami').

52- Yin Sallah da cinyoyin hannu a buɗe.

53- Fara Sallah da ƙafafu a buɗe (a wani ƙaulin makaruhi ne mace ta yi sallah da ƙafafu a buɗe. Wani ƙaulin ya ce sallarta ta ɓaci). An rubuta a cikin shafi na ɗari huɗu da talatin da tara na Ibn 'Abidin cewa idan ka shiga

masallaci, makaruhi ne ka bar takalminka da wani abu makanatansu a wani wuri a bayanka. An rubuta a ƙarshen littafin **Berika** cewa sunnah ne a ajiye su a wani wuri da ke hagunka, maimakon a gabanka ko damanka.

An rubuta a cikin littafin **Terghib-us-salat** cewa makaruhi ne karanta addu'a, irin addu'ar da ake kira 'ɛɓrad' tsakanin sallar farilla da ta sunnah.

ABUBUWAN da ke BATA SALLAH: A Mazhabar Hanafiyya, an bayyana abubuwa hamsin da biyar da ke ɓata sallah, waɗanda suke sanya sallar mutum ta zama ɓatatta, ko da gangan ko a kan kuskure:

1- Yin faɗar wata kalma.

2- Kyalƙyata dariya wadda mutum zai ji da kansa.

3- Yin wani abu da za a iya kira 'amal-i-kathir (aiki mai yawa).

4- Tsallake wani abu na farilla (a cikin sallah) ba tare da uzuri ba.

5- Tsallake ɗaya daga cikin farillai ba da niyya ba.

6- Ɗarkewa da kuka a kan wani lamari na duniya.

7- Yin gyaran murya ko tari ba tare da uzuri ba.

8- Cin cingam.

9- Yin susa a wata gaɓa ta jikin mutum sau uku da hannu ɗaya, ko ɗaga hannuwa a yi tafi a cikin rukuni ɗaya.

10- Gaisawa (da wani).

11- Kin bayyanawa kabbarar harma gwargwadon yadda mutum zai jiyar da kansa.

12- Kin yin karatun (sura da addu'o'in sallah) a bayyane gwargwadon yadda za ka jiyar da kanka.

13- Faɗar "**La hawla wala ƙuwwata il-la billah-il-'aliy-yil 'adhim**," ko "**Subhanallah**," ko "**La ilaha il-l-Allah**," yayin da wani ya kira ka. Sallah ba za ta ɓaci ba, idan niyyarka ta sanar da su ce cewa kana sallah. Amma sallah ta ɓaci idan niyyarka ta amsa wannan kiran ce.

14- Amsa gaisuwa da gangan. (A duba babi na sittin da biyu na mujalladi na 3 a littafin **Endless Bliss**).

15- Ɗandana wani abu mai zaƙi da baki, har ya kai ga hadiyewa a maƙoshi.

16- Yayin da mutum yake sallah a waje, ya buɗe bakinsa a sama, ruwan sama ko wani abu ya faɗa masa a maƙoshi.

17- Jan linzamin dabbar da mutum yake a kai sau uku.

18- Ɗaga hannuwa sau uku, ko a kashe ƙwaro da makamantansa ta hanyar murje su.

19- Cire gashi har sau uku a rukuni ɗaya.

20- Furta kalma mai sautin furuci uku, kamar kash, humn, da makamantansu.

21- Yayin da mutum yake sallah a kan doki bisa tsarin da Musulunci ya amince, ya yi wa dokin ƙaimi sau uku da ƙafa ɗaya.

22- Yin ƙaimi da ƙafa biyu a lokaci guda sau ɗaya.

23- Shiga gaban liman (Yayin sallar jam'i).

24- Yin tafiya gawargwadon sahu biyu ba tare da uzuri ba, (wato, yin wani abu na dole da Musulunci ya yarda da ingancin dalilinsa).

25- Tsefe (sharce) gashin kai ko gemu.

26- Ga mace da namiji su yi sallah jere da juna a bayan Liman a sallar jam'I da niyyar jagorantar sallah ga maza da mata. (Ya halatta idan ba jere da juna suke ba, ko akwai shamaki (labulai) a tsakaninsu. Haramun ne ga mace da 'yan mata su fita waje ba tare da rufe kansu da hannuwansu ba, wato su fita wani sashe na al'aurarsu a waje, ko da wane irin dalili ne, da ya ƙunshi zuwa Masallaci da sauransu. Duk aikin ibadar da suka yi a wannan halin zai janyo masu zunubi maimakon lada, (wato sakamako a gobe ƙiyama).)

27- Yin gyara ga Limamin da ba naka ba, (wato taimakon Limamin da yake jan sallar jam'i daban wanda ya yi kuskure ko ya kakare wajen yayin da yake karatun Alƙur'ani a cikin sallah).

28- Misali idan mace ta samu wurin da babu kowa ta kabbara sallah ta bi Liman, daga baya wasu maza suka zo suka shiga sahu har suka tarad da inda wannan matar take da ke bin wannan sallar, to sallar mutane uku, da suka ƙunshi wanda yake kusa da ita a gefen dama, da wanda yake kusa da ita a gefen hagu, da wanda yake bayanta, duk sallarsu ta ɓaci.

29- Rungumar yaro ƙarami.

30- Cin abinci ko shan abin sha.

31- Hadiye wani abu dan ƙanƙane wanda ya maƙale a hakori.

32- Jawo gefe biyu na wuyan riga da hannu biyu, ko cire hula da hannu ɗaya, ko cire ta da sake mayarwa.

33- Faɗar "**Inna lilla wa inna ilaihi raji'un**," idan mutum ya ji mummunan labari yana cikin sallah.

34- Faɗar "**Al-hamd-u-lillah**," sakamakon jin labarin farin ciki.

35- Wani ƙaulin an ce, Faɗar "**Al-hamd-u-lillah**" bayan yin atishawa.

36- Faɗar “**Yarhamukallah**” ga mutumin da ya yi atishawa kusa da kai.

37- Faɗar “**Yahdikumullah**” ga wanda ya yi atishawar.

38- Namiji ya sumbaci macen da take sallah.

39- Yayin addu’a a cikin sallah, mutum ya roƙi abubuwan da suka shafi duniya, kamar zinare da azurfa.

40- Mutum ya juya gabansa daga fuskantar Alƙibla. Akwai hanyoyi biyu na gano Alƙibla. 1– Ta hanyar kusurwar da Alƙiblar take. 2– Ta hanyar sa’o’in Alƙibla. 1- Idan aka ja layi miƙe tsakanin wani birni zuwa Makka a kan taswira, wannan layin shi ne (saitin Alƙibla daga birnin, ana kiransa) **layin Alƙibla**. Bambancinsa da kudanci shi ne **kusurwar Alƙibla**. 2- Duk wanda ya kalli rana a lokacin Alƙibla wanda aka rubuta a matsayin **sa’o’in Alƙibla** (ko lokacin Alƙibla) a jikin kalanda ya fuskanci saitin Alƙibla. Kadusi ya yi bayani a sharhinsa (na Rub’-i-daira) cewa: “Idan kibiyar rub-i-daira da ke tsaida alƙibla, ya motsa zuwa saitin alƙibla, kusurwar da (zaren da ake kira) khayt ya kalla sama shi ne Fadl-i-dair (H) na lokacin Alƙibla na Istanbul.” Idan aka tsaida na’urar (Agogo) ya kalli sama, kuma kibiyar da take nuna sa’a ta kalli rana, to ita ce marabar kusurwar da ke tsakanin sa’a da lamba sha biyu da ke kallon kudu. A duba babi na tara na mujalladi na huɗu a littafin **Endless Bliss!**

41- Ɗage ƙafafu biyu daga ƙasa a lokacin sujada.

42- Gurɓata karatun ayoyin Alƙur’ani mai girma ta yadda ma’anarsu za ta sauya.

43- Ga mace ta shayar da ɗanta nono.

44- Mutum ya sauya wuri bisa buƙatar wani.

45- Dukan dabbar da mutum yake a kai sau uku.

46- Buɗe ƙofa da take rufe.

47- Rubuta wani abu da ƙalla kalmomi uku.

48- Mutum ya sanya riga.

49- Tuna wata sallolin farilla da suka kuɓuce (wato wasu daga cikin sallolin farilla biyar na yini da mutum bai yi ba) idan ba su kai shida ba.

50- Yayin sallar farilla tare da uziri a [cikin jirgin ruwa ko jirgin ƙasa] ko a kan dabba (kamar doki) mutum ya juya zuwa wani gefe da ba Alƙibla ba.

51- Ɗora kaya a kan dabbar da mutum yake a kai.

52- Yin ridda (fita daga addini) a cikin zuciya.

53- Mutum ya samu janaba, ko mace ta fara jinin al’ada.

54- Ga Limamin (da yake jagorantar sallar jam'i) ya jawo wani ya maye gurbinsa saboda yana zaton alwalarsa ta warware.

55- Karanta ayoyin Ƙur'an al-karim tare da gurɓata sautukansu har ya kai ga ɓata ma'anarsu. [Ibni 'Abidin 'rahimahullahu ta'ala' ya faɗa a lokacin da yake tattaunawa game da sunnonin sallah cewa: "Sallar da aka yi tare da bin wani wanda ba cikin sallar yake ba, ba ta inganta ba. Makaruhi ne ga Liman ko Ladan su ɗaga muryarsu da ƙarfi fiye da yadda waɗanda ke cikin sallar za su ji. Idan Liman da Ladan suka yi kabbarar harama yayin fara sallah (a cikin jam'i) za su yi niyyar fara sallah. Sallarsu ba za ta inganta ba idan suka yi niyya har mamu suka ji muryarsu. Haka nan sallar mamun ita ma ba ta inganta ba. Makaruhi ne Ladan ya ɗaga murya wajen yin Kabbara idan muryar Liman tana da ƙarfin da kowa zai ji. Bidi'a ne yin hakan. Amma mustahabbi ne yin hakan idan buƙatar hakan ta taso, sai dai sallar Ladan ne za ta ɓaci idan ya mayar da abin kamar waƙe." Don haka Liman da Ladan da suke fitar da muryarsu ta amfani da lasifika, baya ga ɓata sallar mamu, kuma sun hana sallarsu ta zama ingantatta. Bidi'a ce mai muni a tsakaninsu. Kuma saɓo ne aikata bidi'a. Bai inganta ba ga mutum ya bi Limamin da ke jan sallah a wani wuri nesa sallah ba ko wanda yake gani da ji a talabijin, an rubuta bayanai da ƙwararan hujjoji a cikin wata maƙala game da batu na goma sha biyu a watan Rabi'ul-awwal, 1406, daidai da Disamba 1985, a cikin mujallar **al-Mu'allim**, wadda malaman ƙasar Indiya suka buga a Malappulam.]

Abubuwan da ba sa ɓata sallah: Idan akwai kafa a sahun da ke gabanka, ka taka zuwa wurin da taƙi ɗaya ko biyu, ko ka ce "Amin," ba da nufin karɓa wa wani ba, ko ka karɓa gaisuwar wani (wato mutum ya ce maka "Salamu 'alaikum")[1] ta hanyar yin ishara da girar ido ko idanu, ko idan wani ya tambaye ka ta raka'a nawa kake, ka yi masa ishara da yatsunka; dukkan waɗannan abubuwan ba sa ɓata sallah.

Ma'anar kalmar 'sallah' ita ce 'jin ƙai daga Allah 'adhim-ush-shan da istigfari daga mala'iku, da addu'a daga muminai'. Ma'anarta ta fannu kuwa ita ce 'ef'al-i-ma'luma da erkan-i-mahsusa', wato 'namaz' a Turkanci (ko 'prayer' da ingilishi. Ef'al-i-ma'luma na nufin ayyukan da ake yi a wajen sallah', shi kuma arkan-i-mahsusa na nufin 'rukns (tsayuwa kamar yadda aka tsara, da zama da sujada da ruku'u da addu'o'i) a cikin sallah, dukkan waɗannan suna da muhimmanci ƙwarai a cikin sallah.

Wata rana Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' a wata girmamawa da ya yi ga masoyinsa, ya shaida wa sayyidina Ali 'karramallahu wajhahu wa radiyallahu 'anh' cewa: **Ya Ali! Ka aikata farillai da wajibai da sunnoni da kuma mustahabban sallah**." Sai wani sahabi daga cikin mutanen

Ansar[1] (Madina) ya ce: Ya Manzon Allah! Sayyidina Ali ya san dukkan waɗannan abubuwan. Ka faɗa mana albarkar da ke tattare da aikata farillai da wajibai da sunnoni da mustahabban sallar, domin mu riƙa yin su yadda suka kamata." Sai Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya ce "**Ya ku al'ummata kuma sahabbaina! Sallah ita ce ibadar da Allahu 'adhim-ush-shan yake farin ciki da ita. Ita ce Mala'iku suke ƙauna. Sunnah ce ta Annabawa. Haske ce ta ma'rifat. Ita ce mafificiyar ibada** (ayyukan addini). **Karfi ce ga gangar jiki. Karin kumallo ce ga arziki. Haske ce ga zuciya. tana sa Karbar addu'a. Tana saukin fitar rai daga Mala'ikan mutuwa. Fitila ce a cikin ƙabari. Ansa ce ga** (tambayoyin Mala'ikun da ake kira) **Munkar da Nakir. Rumfa ce a ranar tashin Alƙiyama. Shamaki ce tsakaninka da wuta. Tana sa a tsallake siraɗi kamar walƙiya. Hular alfarma ce a cikin Aljanna sannan kuma ita Mabuɗi ce ta shiga Aljanna**."

FALALAR SALLAR JAM'I

Misali idan mutun ya yi salla cikin jam'i raka'a biyu, sannan ya yi wasu raka'o'i ishirin da bakwai shi kaɗai, sallar da ya yi raka'a biyu a cikin jam'i ta fi waɗancan ishirin da bakwan lada.

A wata riwayar, ko da sallar ta kai raka'a dubu, raka'o'in biyu da aka yi a cikin jam'i ta fi lada. Akwai lada mai yawa cikin yin sallah a jam'i. Ga wasu daga cikin falalarta:

1- Idan Musulmi suka haɗu wuri ɗaya, yana gadar da soyayya a tsakaninsu.

2- Marasa Ilimi a cikinsu za su koyi abubuwan da suka shafi sallah daga waɗanda suke da ilimi.

3- Idan aka karɓi sallar wasu daga cikinsu, wasu kuma ba a karɓi tasu ba, to za a karɓi sallar waɗannan saboda albarkar sallar waɗancan na farkon da aka karɓa.

Wani Hadisi yana cewa: "**Ya ku Al'ummata kuma Sahabbaina! Na samar maku da hanyoyi biyu: Daya daga cikinsu ita ce Alƙur'ani mai girma, ɗaya kuma Sunnata. Duk wanda ya wata hanya ba ɗwaɗannan ba, ba ya cikin Al'ummata!**" ['Abd-ul-Ghani Nablusi 'Allah ya yi masa rahama' (1050 [1640 M.], Damascus – 1143 [1731]) ya faɗa a cikin shafi na casa'in da tara na littafinsa mai suna **Hadiƙa** (wanda sharhi ne na littafin **Tariƙat-i-**

[1] A yayin da fiyayyen halitta Rasûlullah 'sallallâhu 'alaihi wa sallam' yayi hijira zuwa Madina (daga Makkah) a 622 A.D. Muslimai dake zama a Madania suka yimu tarba babba tare da sahabbansa. Waɗanda suka zo daga makka ana kiransu 'Muhajirun' sannan musulman Madina ana kiran su da 'Ansar'.

Muhammadiyya na Imam Birgiɓi) cewa: Bayan Allâhu ta'âlâ ya sanar da wani ɓangare na addini a Alƙur'ani mai girma, sai ya sanar da sauran ɓangaren ta Sunnar Annabinsa 'sallallahu 'alaihi wa sallam'. Sunnar Annabi 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ta ƙunshi abubuwan da ya yarda da su da waɗanda ya faɗa da waɗanda ya aikata da kyawawan ɗabi'unsa da amincewa da aiki ko furucin wani, [wanda ke nuna yardarsa (ga abin da aka aikata ko aka faɗa).]" Hadisi shi ne na biyu (a cikin madogarar addini huɗu da ake kira) **Adilla-i-Shar'iyya**.]

LIMANCI A CIKIN SALLAH (ta jam'i)

Akwai nau'in mutane huɗu da suke bin Liman (wanda yake jan sallar jam'i): Mudrik, da Muƙtedi, da Masbuƙ, da Lahiƙ.

1- Mudrik shi ne Musulmin da ya yi kabbarar harma tare da Liman. (Wato, ya ce "Allahu Akbar" (kusan) lokaci ɗaya da Liman, wanda ke nufin ya fara sallar jam'i tare da Limamin da yake jan sallar jam'in).

2- Musulmin da bai samu kabbarar harma tare da Liman ba shi ne Muƙtadi.

3- Masbuƙ shi ne Musulmin da ya (bi sallar jam'i amma) ya fara bin Liman bayan ya ƙulla raka'a ɗaya ko biyu.

4- Lahiƙ shi ne wanda ya yi kabbarar harama tare da Liman; sai hadasi ya same shi (alwalarsa ta warware) ya sake alwala, ya koma ya cigaba da sallah a bayan Liman. Ya samu sallar kamar yadda ya bar ta a bayan wannan Limamin, (wato bai yi karatu ba, amma ya yi ruku'u da sujada da tasbihi a cikinsu). Idan bai yi wata magana da ta shafi duniya ba (sa'ilin da ya bar masallacin domin sake alwala), to kamar ya samu cikakkar sallar ce tun farkonta a bayan Liman kuma tare da Liman. Amma bayan ya bar masallacin (domin sake alwala) kamata ya yi ya sake alwalar a kusa da masallacin. Akwai malaman da suka ce sallarsa ta ɓaci idan ya yi nisa ƙwarai da masallacin.

Idan mutum ya samu Liman ya yi ruku'u lokacin da ya shiga masallaci, a ƙoƙarin da yake yi na riskar Limamin, sai ya yi kabbarar harma a lokacin da yake duƙawa zuwa ruku'u, to bai bi Liman ba, (wato, bai samu wannan sallar jam'i ba). Idan ya riski Liman yana tafiya ruku'u, ya yi niyyar bin Liman sannan ya yi kabbarar harama daga tsaye sosai, kana ya duƙa zuwa ruku'u, ya yi tasbihi a yayin da Limamin yake cikin ruku'un, ya riski Liman (ya samu jam'i) a wannan raka'ar. Haka nan idan ya zamana Liman yana ɗaukakowa a daidai lokacin da yake duƙawa, bai samu wannan raka'ar ba.

NUTSUWA (TA'DIL-I-ARKAN) A CIKIN RUKUNAN SALLAH

Idan mutun ya bar (riƙo) da ta'dil-i-arkan a wurare biyar na sallah, da gangan ba a kan mantuwa ba, sallarsa ta ɓaci. Imam Abu Yusuf 'Allah ya yi masa rahama' kamar yadda Tarafeyn (Imam A'zam Abu Hanifa da Imam Muhammad) suka faɗa, ba ta ɓaci ba, amma wajibi ne ya sake yin wata sallar domin cike giɓin da ya bari saboda sakaci ga abin da yake wajibi. Wajibi ne a yi **Sajda-i-sahw** (sujadar rafkannuwa) idan a kan mantuwa ne ka yi. [A duba sashin wannan littafin da yake bayani game da abubuwan da suke sa mutum ya rasa imaninsa!]

Barin ta'dil-i-arkan yana jawo wasu matsaloli ishirin da shida:

1- Yana jawo talauci.

2- 'Ulama (bayi) na ranar lahira za su tsani mutum.

3- Mutum zai fita daga cikin adalai, ya zamo ba za a riƙa karɓar shedarsa ba.

4- Wuraren da mutum ya yi rashin nutsuwar (a cikin sallah) za su zamo sheda a kansa a ranar lahira.

5- Mutum zai zamo mai saɓo saboda ƙin gargaɗi (cikin hikima da girmamawa) ga mutumin da ya gani yana sallah ba tare da ta'dil-i-arkan ba.

6- Dole a sake sallah (wadda aka yi ba tare da ta'dil-i-arkan ba).

7- Yana sa mutuwa babu imani.

8- Yana mayar da mutum ɓarawo wanda ke yin sata daga sallah.

9- Za a cusa sallar da mutum ya yi a cikin haƙoransa kamar tsumma a ranar Lahira.

10- Mutum ba zai samu rahamar Allâhu ta'âlâ ba.

11- Ka yi abin da ba daidai ba wajen bautar Allâhu ta'âlâ.

12- Mutum ba zai samu tarin ladar da ake bayarwa ga masallata ba.

13- Yana sa a hana mutum samun ladar sauran ayyukansa na ibada.

14- Yana sa a shiga wutar Jahannama.

15- Yana sa jahilai da suka ga abin da kake yi (su yi koyi da kai) su yi watsi da ta'dil-i-arkan. A kan haka ne, yin saɓo ga mutum mai muhimmanci a addini yake haddasa tsananin azaba.

16- Mutum ya saɓa wa imaninsa.

17- Mutum ya bar sunnah a Intiƙalat (jerantawa).

18- Mutum zai hadu da fushin Allah 'adhim-ush-shan.

19- Shedan zai yi farin ciki.

20- Mutum zai nisanta kansa daga Aljanna.

21- Zai kusanta da wutar Jahannama.

22- Mutum ya cutar da rayuwarsa.

23- Ya sanya datti a zuciyarsa.

24- Mutum ya cutar da Mala'ikun da ke dama da hagunsa.

25- Mutum ya baƙanta ran Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam'.

26- Mutum ya cutar da dukkan halittu. Saboda saɓonka zai haddasa ƙarancin ruwan sama ga tsirrai, ko ya haddasa ruwan sama kamar da bakin ƙwarya da zai cutar da tsirrai maimakon ya amfane su.

SALLAH YAYIN DOGUWAR TAFIYA

An rubuta a cikin littafin **Ni'mat-i-islam** (wanda Hadji Muhammad Zihni 'rahmatullahi ta'ala 'alaih,' ya rubuta, 1262–1332 [1914 M.] Kupluce-Beglerbegi, Istanbul) cewa: Ya halatta yin nafila daga zaune a koyaushe a ko'ina, ko da mutum yana da ikon yin ta daga tsaye. Idan kana sallah daga zaune, za ka duƙa kaɗan domin yin ruku'u. A yayin sujada, mutum zai kai goshinsa ƙasa (ko bisa dardumar sallah). Amma idan mutum ya yi sallah daga zaune ba tare da wani uzuri ba (dalili mai ƙarfi da Musulunci ya amnce da shi) zai samu rabin ladar wanda ya yi sallar a tsaye. Sallolin sunnah da ake yi a lokacin sallolin farilla biyar da Tarawih suna cikin sallolin nafila. (A duba babi na 19 a mujalladi na hudu na littafin **Endless Bliss** game da bayani kan Tarawih). A yayin tafiye-tafiye, wato fita daga yankin birane, ya halatta a yi sallolin nafila a bisa dabba (kamar doki). Ba wajibi ba ne kallon Alƙibla ko yin ruku'u ko sujada. Mutum zai yi ima'i ne (wato alamu). Haka nan mutum na iya ɗan lanƙwasa da jikinsa. A sujada kuma zai iya duƙawa sosai. Samuwar najasa da yawa a jikin dabbar ba zai yi wani tasiri a sallar ba. Ya halatta ga mutumin da ke cikin tsananin gajiya a cikin sallah ya dogara da sandarsa ko wani mutum, ko kuma ya jingina a jikin bango. Bai inganta ba mutum ya yi sallah yana tafiya da ƙafafunsa. (Wato sallar da aka yi a wannan yanayin ba karɓaɓɓa ba ce). A sallolin farilla da na wajibi; sai akwai uzuri ne kaɗai za a iya yin su a kan dabba a wajen birane. Uzuri a nan ya ƙunshi: Idan mutum ya ji tsoron ayarinsu na matafiya za su iya barinsa a baya idan ya sauka daga kan dabbar; ko ya ji tsoron 'yan fashi da za su iya salwantar da rayuwa ko dukiyarsa ko dabbarsa; ko kuma wuri mai taɓo ko ba zai iya komawa kan dabbar ba idan ya sauka; da makamantansu. Idan zai yiwu, mutum ya sa dabbarsa ta kalli Alƙibla sannan ya yi sallar. Idan ba zai

yiwu ba, sai ya yi sallar yana fuskantar inda dabbar take tafiya. Haka hukuncin yake ga wanda yake cikin sundukin da ake ɗorawa a kan dabba. Idan aka tsayar da dabbar, aka sanya ginshiƙai a kan sundukin, ya sauya zuwa **serir**, wato kamar wani teburi ko kujera, ta yadda sallah a kai zai zama kamar sallah ne a ƙasa. A nan wajibi ne a yi sallah daga tsaye ana kallon Alƙibla.

Yin sallah a cikin jirgin ruwa kamar yadda Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya koyar da sayyidina Ja'far Tayyar[1] sa'ilin da zai tafi Habasha (Ethiopia), kamar haka: Za a iya yin sallolin farilla da na wajibi a cikin jirgin ruwa, babu buƙatar uzuri na yin hakan. Za a iya yin sallar jam'i a cikin jirgin ruwa. Bai halatta ba yin sallar ima'i a cikin jirgin, (ta hanyar ishara); dole a yi ruku'u da sujada. Haka nan wajibi ne a kalli Alƙibla. Idan mutum zai kabbara sallar zai fuskanci Alƙibla, idan jirgin ya yi ƙwana, dole ne mutum ya juya ya sake fuskantar Alƙibla. Kazalika wajibi ne a yi tsarkin najasa a cikin jirgin ruwan. (A duba babi na shida na mujalladi na huɗu a littafin **Endless Bliss** game da bayani a kan tsarki da najasa). A mazahabar Hanafiyya, ya halatta a yi sallar farilla daga zaune a ƙasan cikin jirgin ruwan da yake tafiya ba tare da wani uzuri na yin hakan ba.

Jirgin ruwan da aka riƙe da ƙugiya a cikin ruwa kamar jirgin da yake tafiya ne, idan ya zamana yana injin dînsa yana juyawa da ƙarfi. Idan yana juyawa a hankali ne, to kamar jirgin da yake bakin gaɓa ne. Ba za a yi sallar farilla daga zaune ba a jirgin da yake ɗaure a bakin gaɓa ba. Bai inganta ba a yi sallar daga tsaye ba, idan ya zamana za a iya fitowa zuwa gaɓa. Wajibi ne a je zuwa gaɓar a yi sallar a kan ƙƙasa. Idan mutum ya yi fargabar asarar dukiyarsa, ko rayuwarsa, ko kuma jirgin ya tafi ya bar shi, to ya halatta ya yi sallar daga tsaye a cikin jirgin ruwan. A nan muka kawo ƙarshen ruwaya daga **Ni'mat-i-islam**.

Ibni 'Abidin ya faɗa cewa: "Yin sallah a kan keken dawaki mai ƙafa biyu wanda ba zai iya tsayuwa da kansa ba sai an ɗaura shi a jikin dabba, a tsaye ko a tafiya, kamar yin sallar ne a kan dabbar. Keken mai ƙafa huɗu, idan yana tsaye wuri guda kamar serir ne (teburi ko kujera). Idan yana tafiya,

---

[1] Ja'far Tayyâr 'radiyallâhu 'anh' ɗaya ne daga cikin yaran baffan Rasulullah mai suna Abu Talib. Ya girme sayyidina Ali da shekara goma sannan shi kuma 'Uƙyl ya girme shi da shekara goma. Yayi Hijira zuwa ƙasar Habasha sannan ya dawo ranar Haibara. A shekara ta takwas na Hijra ya na yaƙar Byzantines tare da dakaru dubu uku a wani wuri mai suna Mu'ta a farfajiyar garin Damascus, yayin da yayi shahada a fagen yaƙi bayan ya kai farmaki masu yawa sannan yaji raunuku har guda saba'in a rana ɗaya. Yana da shekaru araba'in da ɗaya. Ya na ɗaya daga cikin mutane bakwai masu kamanni da manzon Allah.

za a iya yin sallar farilla a kai bisa dalilin uzuri irin na wanda yake a kan dabba kamar yadda aka yi bayani a baya; a tsayar da keken a fuskanci Alƙibla. Idan aka gaza tsayar da shi, sai a yi sallar kamar wanda yake cikin jirgin ruwa." Idan mutumin da ke (kan doguwar tafiya wadda ake kira) safari ba zai iya zama a ƙasa ba ko ya juya ya kalli Alƙibla ba a kan abin hawan da yake a kai, zai yi koyi da Mazhabar Shafi'iyya ko Malikiyya, ya yi jam'in salloli biyu da ke kusa da juna idan ya sauka a kan abin hawan. Bai halatta ba ga mutumin da wanda zai iya zama a ƙasa ya zauna a kan kujera ko a kan hannun kujera ya yi sallah ta hanyar ima'i. yin sallah a kan motar safa (bus) ko jirgin sama, kamar yin sallah ne a kan keken dawaki. Mutumin da ya fita doguwar tafiya, ya kuma yi niyyar tafiya ta tsawon kwanaki uku, wato fersah goma sha takwas = mil 54 [54×0.48×4 = kilomita 104] daga wajen birni ko ƙauye, ya zama (mutumin da yake) safari da zarar ya fita gari. Ibni 'Abdin ya ce, mil ɗaya shi ne daidai da zira'i 4000, zira'i kuma yana daidai da taƙin yatsu ishirin da huɗu [24]. [Taƙin yatsu shi ne tsawon santimita biyu. A Mazhabar Shafi'iyya da Malikiyya fersah 16 = mil 48 = 48 × 0.42 × 4000 = 80 km.]

Kai, ku zo mu yi sallah, mu goge tsatsar da kezuciyarmu,
Ba za ka kusanci Allah ba, sai ka gudanar da sallah!

Duk a inda ake sallah, ana kankare dukkan
Ba za ka taɓa samun kamala ba, sai ka yi sallah!

A Alƙur'ani mai girma da gaskiya an yabi sallah sosai,
Ya ce "Ba zan so ka ba, sai ka yi sallah!"

A hadisi tsarkakakke: Imani ba shi cika,
Gaba ɗai ga mutum, sai ya yi sallah!

Kin yin sallah, a dukkan zunubbai shi ne gaba,
Nadama ba ta isa, har sai ka rama rankon sallah!

Ko wa ya wulƙanta sallah, zai rasa imaninsa nan take,
Musuluncinsa ba zai inganta ba, har sai ya yi sallah!

Sallah na wanke zuciya, da hana ta saɓo,
Ba ka taɓa samun haske da wayewa ba, har sai ka yi sallah!

FALALAR KABBARAR HARAMA

Idan mutum ya yi kabbarar harama tare da liman, zunubansa za su riƙa zuba kamar yadda iskan bazara mai ƙarfi ke kakkaɓe ganye.

Wata rana da asuba, Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana sallah, sai wani ya zo, amma ya makara bai samu kabbarar harama ta sallar asuba ba (wato bai samu yin kabbarar harama tare da liman ba). Sai ya ‘yanta bawa. Bayan nan ya tambayi Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’: “Ya Rasulallah (Ya Manzon Allah!) Yau ban samu kabbarar harama ba a sallar asuba. Na ‘yanta bawa. Ina tunanin ko zan iya samun ladar da na rasa a kabbarar haramar?” Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya tambayi sayyidina Abubakar ‘radiyallâhu ta’âlâ ‘anh’: “**Me za ka ce game da wannan kabbarar haramar?**” Sayyidina Abubakar ‘Allah ya yarda da shi’ ya amsa: “Ya Manzon Allah ’sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’! Idan ina da raƙuma arba’in ɗauke da dukiya ta alfarma, na bayar da su sadaka ga mabuƙata, ba zan samu ladar yin kabbarar harama tare da liman ba.” Bayan nan, sai shugaban halitta ya tambaya: “**Ya Umar! Me za ka ce game da wannan kabbarar haramar**?” Sayyidina Umar ‘Allah ya yarda da shi’ ya ce: “Ya Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’! Idan ina da raƙuma da yawansu ya kai nisan tsakanin Makka da Madina, kuma dukkansu ɗauke da dukiya ta alfarma, na bayar da su sadaka ga mabuƙata, ba zan samu kwatankwacin ladar samun kabbarar harama tare da Liman ba.” Bayan nan Annabi ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya tambaya: “**Ya Uthman, me za ka ce game da wannan kabbarar haramar**?” Sayyidina Uthman zin-nurayn ‘radiyallâhu ta’âlâ ‘anh’ ya ce “Ya Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’! Idan na yi sallah raka’a biyu a cikin dare, na sauke Alƙur’ani mai girma a kowace ɗaya daga cikin raka’o’in, ba zan samu kwatankwacin ladar kabbarar harama tare da Liman ba.” Daga nan kuma Ya tambayi sayyidina Ali ‘karramallahu wajhah’: “**Ya Ali! Me za ka ce game da wannan kabbarar haramar**?” Sai ya amsa da cewa: “Ya Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’! Idan kafirai da ke tsakanin gabas da yamma, suka kawo hari da nufin kawar da Musulmi, sai Allâhu ta’âlâ ya ba ni ƙarfi da iko na yi jihadi a kan kafiran nan, na kawar da su gaba ɗaya, ba zan samu gwargwadon ladar yin kabbarar harama tare da Liman ba.”

Daga nan Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ce: “**Ya ku Al’ummata kuma Sahabbaina! Idan da ace ƙassai bakwai da sammai bakwai takardu ne, kuma dukkan takun duniya tawada ne, sannan dukkan itacen dunya alƙalumma ne, haka nan dukkan Mala’iku marubuta ne, su yi ta rubutu** (ba ƙaƙƙautawa) **har zuwa ranar tashin ƙiyama, ba za su iya rubuta ladar yin kabbarar harama tare da Liman ba**.”

Idan ka ce “Shin Mala’ikun da Allâhu ta’âlâ ya halitta sun kai yawan haka?” (Ga amsarka): a daren Mi’raj, lokacin da aka ɗauki Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ zuwa sama, Mala’iku suna ziyartar Aljanna da Wuta da Bayt-i-ma’amur (Ka’ba) suna tafiya. Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya tambaya: “**Ya ɗan uwana Jibril! Mala’ikun da suke ziyarar Bayt-i-ma’amur ba sa komawa. Ina suke tafiya ne**?” Jibril ‘Allaihis-salam’ ya ce: “Ya Habibullah (ya masoyin Allah)! Tun daga lokacin da aka halicce ni, ban taɓa ganin wani Mala’ika da ya ziyarci Bayt-i-ma’amur ya koma ba. Idan Mala’ika ya yi ɗawafi a Bayt-i-ma’mur ya tafi, ba zai sake dawowa ba har ranar tashin Alƙiyama.”

Idan mutum ya karanta A’udhu (ta’awizi) da Basmala a lokacin sallah, Allahu ‘adhim-ush-shan zai ba wannan bawan lada gwargwadon yawan gashin da ke jikinsa. Idan wannan bawan ya karanta suratul Fatiha, Allâhu ta’âlâ zai ba shi lada gwargwadon ta aikin hajjin da aka karɓa. Idan wannan bawan ya yi ruku’u, Allahu ‘adhim-ush-shan zai ba shi lada gwargwadon da zai bai shi idan ya yi sadaka da dubban sulallan zinare, idan ya yi tasbihi, (wato idan ya ce “Subhana Rabbiy-al-‘adhim”) sau uku kamar yadda aka koyar a sunnah, Allahu ‘adhim-ush-shan zai ba wannan bawan lada kamar ya karanta litattafan huɗu da aka saukar daga sama, da ƙananan litattafan (suhuf) da aka saukar guda ɗari. Idan ya ce “**Sami’ Allahu liman hamidah**,” (yayin da ya ɗaukako daga ruku’u) Allahu ‘adhim-ush-shan zai lulluɓe wannan bawan da rahamarsa. Idan ya tafi zuwa sujada, Allâhu ta’âlâ zai bai wa wannan bawan lada kwatankwacin yawan mutane da aljannu. Idan ya yi tasbihi (wato ya ce “Subhana Rabbiy-al-a’la”) sau uku, kamar yadda yake a sunnah, akwai falala da dama da Allahu ‘adhim-ush-shan yake bai wa bayinsa. Kaɗan daga cikinsu (daga malaman Musulunci) kamar haka:

Falala ta farko ita ce zai ba shi lada da nauyinta ya kai na Al’arshi da Kursi. Ta biyu, Allah ‘adhim-ush-shan zai ba shi maghfirat (gafara). Falala ta uku ita ce, idan wannan mutumin ya mutu Mala’ika Mika’il ‘Amincin Allah ya tabbata a gare shi’ zai riƙa ziyartar kabarinsa (a-kai a-kai) har ranar tashin ƙiyama. Ta huɗu, a ranar tashin ƙiyama, Mika’il ‘alaihis salam’ zai ɗauki wannan bawan, a kan fiffikensa, ya nema masa ceto, sannan ya wuce da shi Jannat-i-a’la (Aljanna).

Idan wannan bawan ya yi Ƙa’da-i-akhira (zaman tahiya na ƙarshe), Allahu ‘adhim-ush-shan zai ba shi lada kwatankwacin wadda yake bai wa fuƙaray-i-sabirin (Musulman da suke mabuƙata kuma masu haƙuri).

Su fuƙaray-i-sabirin za su shiga Aljanna da shekaru ɗari biyar kafin aghniyay-i-shakirin (mawadata musulmai masu godiya). Idan aghniyay-i-

shakirin suka gansu, sai su ce: “Ina ma a ce muna cikin fuƙaray-i-sabirin a duniya!)

A cikin kabari, mala’iku masu tambaya za su zo gare ka;
Za su ce, “Ka yi sallah yadda ya kamata,”

“Ka aminta cewa mutuwa ta zo a matsayin ceto gareka?
Za su ce, Azaba mai raɗaɗi tana jiranka.”

GAME DA JANNAT-I-ALIYYAT
(Dausayin Gidan Aljanna)

Akwai ƙofofi takwas da mabuɗi takwas na dausayin Alajanna. Na farkonsu shi ne iman (imani) ga Musulmin da suke yin (sallolin farilla biyar) sallah. Na biyunsu shi ne yin Basmala (wato cewa “Bismillah-ir-Rahman-ir-Rahim”). Sauran shida suna cikin (sura ta farko ta Alƙur’ani mai girma da ake kira) Fatiha. Jannat (Dausayin Aljanna) guda takwas su ne:

1- Dar-i-jalal. 2- Dar-i-ƙarar. 3- Dar-i-salam. 4- Jannat-ul-khuld. 5- Jannat-ul-ma’wa. 6- Jannat-ul-‘adn. 7- Jannat-ul-firdaus. 8- Jannat-ul-na’im.

1- Dar-i-jalal an yi shi da farin haske.

2- Dar-i-ƙarar an yi shi da jan Yaƙutu.

3- Dar-i-salam an yi shi da koren duwatsun murjani.

4- Jannat-ul-khuld an yi ta da murjani.

5- Jannat-ul-ma’wa an yi ta da azurfa.

6- Jannat-ul-‘adn (Eden) an yi ta da zinare.

7- Jannat-ul-firdaus an yi ta da zinare da azurfa.

8- Jannat-ul-na’im an yi ta ne da jan Yaƙutu.

Muninai da suka shige su, za su rayu ciki har abada; ba za su taɓa fita ba. Matan da suke can ba sa yin jinin al’ada ko na haihuwa; ba su da wata matsala. Mutum zai ci duk irin abinci ko abin sha da yake so, duk lokacin da yake buƙata. Za a nisanta su daga damuwa ta yin girki da shara. Tsuntsaye za su riƙa shawagi a saman kawunansu. Muminai za su riƙa ganinsu yayin da suke zaune a gida jensu na Aljanna. Yayin da suka yi tunani a ransu, suka ce “Idan da a duniya ne kuka zo kusa da ni da na kama ɗaya na gasa” gasashshen tsuntsu zai bayyana a gabansu a cikin wani faranti da aka halitta da haske. (Bayan sun gama cin naman tsuntsun) Mumini zai tattara ƙasusuwan wuri guda, sai ya raya a zuciyarsa cewa ƙasusuwan su sake

komawa tsuntsu kamar a da, sai tsuntsun ya mayar da jikinsa ya tashi ya tafi abinsa.

An halicci ƙasar Aljanna da almiski, sannan gine-ginenta an yi su ne da tubalan azurfa da zinare.

Kowane ɗan Aljanna za a ba shi ƙarfin maza ɗari. Kowanne za a ba shi aƙalla matan Aljanna (Huril Aini) guda saba'in da mata na duniya guda biyu.

Akwai ƙoramu guda huɗu a Aljanna. Waɗanda suke fitowa daga maɓuɓɓuga guda, suna bambanta ta yadda suke gudana da kuma ɗandanonsu. Ɗaya daga cikinsu ita ce ƙoramar ruwa, ta biyunsu ita ce ƙoramar madara, ta ukun su ita ƙoramar abin sha, ta huɗun su ita ce ƙoramar zuma.

Akwai dogayen gine-gine na alfarma a Aljanna. Za su riƙa duƙawa ga mumini domin ya shiga, ya ɗauke shi zuwa duk inda yake so. (kwatankwacinsu a duniya su ne matattakala mai motsi da jiragen sama).

Akwai wata bishiya da ake kira 'Tuba' a Aljanna. Saiwar wannan bishiyar tana daga sama, yayin da rassanta da 'ya'yanta suna kallon ƙasa a sagale. Kwatankwacinsu a duniya kamar rana da wata.

'Yan Aljanna na cin abinci da shan abin sha, kuma suna jin daɗin abincin da abin shan; amma ba sa jin fitsari ko bayan gida; an nisanta su daga dukkan lalurorin na ɗan adam.

Allâhu ta'âlâ zai yi magana da bayinsa Muminai da suke cikin Aljanna: "**Ya ku bayina! Me kuma kuke buƙata daga gare ni? Ku cigaba da jin daɗin rayuwa cikin farin ciki da annushuwa!**" Sai bayin su amsa: "Ya Ubangiji! Ka kare mu daga wuta, ka sanya mu Aljannarka, ka bamu matan Aljanna da yawa da masu yi mana hidima. Abin kunya ne a gare mu a ce mu roƙe ka ƙarin wani abu." Daga nan Rabb-ul-alamin zai sake yi masu magana ya ce: "**Ya ku bayina! Akwai abin da ya kamata ku roƙe ni baya ga waɗannan abubuwan**." Sai bayin su amsa: "Ya Ubangiji, muna jin kunyar mu tambayi ƙari. Sannan ba mu san abin da za mu roƙa ba," Rabb-ul-alamin zai tambaye su: "**Ya ku bayina! Me kuke yi idan wata mas'ala ta same ku a duniya**?" Sai su amsa cewa: "Muna tambayar Malamai (Malaman Musulunci) sai su warware masu matsalarsu. Daga nan Allâhu ta'âlâ zai ce: "**Ku aikata haka yanzu ma, ku tammbayi Malamai**." Sai Malaman su ce da muminai: "Kun manta da Jamalullah? Lokacin da kuke duniya kuna kwaɗayin (ganin Allâhu ta'âlâ) kuka ce: "A ranar tashin ƙiyama, Ubangijinmu wanda ba shi da makani zai ba mu ikon ganin Jamalinsa (zati).' Abin da za su roƙa ke nan yanzu." Sannan za su roƙi ru'yat-i-jamalullah (ganin zatin Allah), sai Allah 'adhim-ush-shan wanda ba shi da makani, zai nuna masu jamal-i-bakemal

ɗinsa. Idan suka ga zatin Allâhu ta'âlâ ƙaunarsu za ta ƙara daɗuwa har tsawon dubban shekaru.

A lokacin da Mumini yake zaune a gidansa na Aljanna, akwai 'ya'yan itatuwa kewaye da shi da bakin tagoginsa. Idan ya yi tunanin cewa, "Bari in miƙa hannuna in kamo wancan reshen, in ciri ɗan iccen in ci," ba ya buƙatar ya motsa daga mazauninsa ya kamo reshen. Reshen da yake buƙata zai ƙaraso inda yake zaune, ya ciri ɗan iccen, ya saka a bakinsa, kafin ya haɗiye, wani sabon ɗa zai sake fitowa a inda ya ciri wannan. Idan ya saka ɗan iccen a bakinsa, zai narke ya ƙara dadi. Haka Rabb-ul-izza zai ta sake halittar sababbi.

Idan kana da wayo, ka zamanto mai yin sallah, saboda kallabi ce na farin ciki,

Iliminka na sallah ya zamo cewa ita ce Mi'raj ga mumini.

SALLOLIN DA BA A YI A KANLOKACIN SU BA
(Ramuwar Salla)

Akwai falala ƙwarai da gaske ga sallar da aka yi a kan lokacinta. (Manyan Malamai) sun bayyana wasu daga cikinsu:

1- Na farko fuskar mutum za ta yi haske baki ɗaya.

2- Mutum zai samu albarkar rayuwa.

3- (Allâhu ta'âlâ) zai karɓi addu'o'in da mutum ya yi.

4- Mutum zai zamo mai alkhairi.

5- Muminai za su so mutum.

Barin sallah ba tare da wani uzuri ba, wato yin ta bayan fitar lokacinta ba tare da dalili mai ƙarfi da Musulunci ya yarda da shi ba, yana jawo matsaloli guda goma sha biyar. Biyar daga ciki a nan duniya; uku daga ciki a lokacin mutuwa; uku daga ciki a cikin kabari; huɗu daga ciki a filin Arasat (hisabi).

Matsaloli biyar da mutum zai fuskanta a duniya su ne:

1- Mutum zai zamo babu haske a fuskarsa.

2- Zai zamo babu albarka a rayuwarsa.

3- Ba za a karɓi addu'o'insa ba.

4- (Allâhu ta'âlâ) Ba zai a karɓi albarkar da ya sanya wa 'yan uwansa Musulmi ba.

5- Ba zai samu ladar sauran ayyukansa na ibada ba.

Matsaloli uku da mutum zai fuskanta a yayin sakarat-i-mawt (fitar rai) su ne:

1- Zai mutu da Yunwa.

2- Zai mutu da ƙishin ruwa.

3- Zai mutu cikin ƙunci. Komai yawan abinci ba zai kosar da shi ba, haka nan komai yawan ruwa ba zai kawar masa da ƙishirwa ba.

Matsaloli uku a cikin kabari su ne:

1- Kabarinsa zai matse shi, har ƙasusuwansa su shige cikin juna.

2- Wuta za ta mamaye kabarinsa gaba ɗaya.

3- Wata mummunar halitta za ta bayyana gare shi. Sunanta Aƙra. Za ta riƙe bulala a hannu ɗaya. Duk duka ɗaya da bulala da zai yi wa mutum sai ya nutse can ƙarƙashin ƙasa. Sannan ya sake dawowa, shi kuma ya sake dukansa da bulalar. Haka zai yi ta dukansa har ranar tashin Alƙiyama. Za a yi ta yi wa mutum azaba har ranar lahira.

Matsaloli huɗu na filin arasat (filin hisabi) su ne:

1- Za a yi masa hisabi mai tsanani.

2- Zai fuskanci azabar Allahu ‘adhim-ush-shan.

3- Zai shiga wuta.

4- Za a yi masa rubutu iri uku a goshinsa:

Na farko shi ne: Wannan mutumin ya cancanci azabar Allah.

Na biyu shi ne: Wannan mutumin ya yi watsi da haƙƙin Allâhu ta’âlâ.

Na uku shi ne: Yadda ka yi watsi da haƙƙin Allahu ‘adhim-ush-shan, babu kai babu rahamar Allâhu ta’âlâ.

Sallah ita ce ginshiƙin addinin Musulunci. Idan mutum ya yi sallah (salloli biyar na farilla) ya tsayar da ginshiƙin addininsa. Don haka ya yi wa kansa rumfar da za ta yi masa inuwa.

Idan mutum ya bar sallah guda ɗaya ta wuce shi da gangan, kuma bai rama ta ba, (wato bai yi ta daga baya ba) a Mazhabobi uku sun bayar da fatawar cewa a kashe shi. A Mazhabar Hanafiyya, ba dole ba ne a kashe shi. Amma, ya aikata babban saɓo da ake kira ‘akbar-i-kaba’ir’. Wajibi ne a rufe shi (a gidan fursuna) a tsare a gidan yari har sai ya fara sallah (salloli biyar na farilla). Mutumin da ya bar sallah saboda ba ya ɗaukar ta da muhimmanci, kuma bai yarda cewa sallah ita ce mafificiyar ibada (ga Musulmi ba), ya zama kafiri.

Idan mutum ya bar ɗaya daga cikin salloli (sallolin farilla biyar) da gangan, sai ya rama ta nan take, (wato idan ya biya bashin sallar daga baya)

za a ƙona shi a jahannama tsawon lokacin da ake kira ‘huƙba’, wato shekaru tamanin. Ba zai tsira daga wannan azabar ba har sai ya tuba tare da yin istigfari.

(Kwana ɗaya na lahira daidai yake da shekaru dubu na duniya. Za a lissafa shekarun na lahira daidai wa daida.)

[Muhammad Amin Ibn ‘Abidin ‘rahmatullahi alaihi’ ya faɗa a cikin littafinsa mai suna **Radd-ul-muhtar** cewa: Kamar yadda (Malamai) suka faɗa. Annabi Adamu ‘alaihis-salâm’ ya yi sallah (ta yini) a lokacin la’asar, Annabi Yaƙub ‘alaihis-salâm’ ya yi sallah (ta yini) a lokaci magariba (bayan faɗuwar rana), haka nan Annabi Yunus ‘alaihis-salâm ya yi ta (ta yini) da dare. Ɗaya daga cikin rukunan imani shi ne yadda da ayyukan ibada farillai da waɗanda aka haramta, haka nan rukuni ne na imani a yadda cewa aiki ne na bautar Allah wajibi yin sallah (sallolin farilla biyar a yini). Amma ba ya daga cikin rukunnan imani yin (waɗannan) sallolin.

Farilla ne ga Musulmin ƙwarai baligi, namiji ko mace, ya yi salloli biyar na yini, sai dai idan yana da wani uzuri, (wato, wani abu da zai ɗauke masu wannan nauyin). Salloli biyar na yini sun zamo farilla (wato umurni na Musulunci) ne a daren mi’raj (mi’iraji). An kawo Hadisai a cikin littafin **Muƙaddima-us-salat** da **Tafsir-i-Mazhari** da **Halabiy-i-kabir** cewa: “**Mala’ika Jibril ‘’alaihis-salâm’** (Na yi sallah tare da Jibril ‘alahis-salam) **Ya jagorance mu sallah ni da shi mu biyu, a gefen ƙofar ɗakin Kaba, yini biyu a jere. Ni da shi muka yi sallar Asuba yayin da alfijir ya keto; muka yi sallar Azahar yayin da rana ta karkata daga tsakiya; muka yi sallar La’asar yayin da inuwar abu ta gota tsawonsa; muka yi sallar Magriba yayin da rana ta faɗi,** [wato yayin da ƙwallon rana ya ɓace baki ɗaya;] **muka yi sallar Isha’i yayin da duhu ya bayyana daga hasken maraice. A rana ta biyu, muka yi sallar Asuba yayin da gari ya fara wayewa; muka yi sallar Azahar yayin da inuwar abu ta zo daidai da tsawonsa; muka yi sallar La’asar nan take bayan sallar Azahar; muka yi sallar Magriba a daidai lokacin da ake shan ruwa (buɗa baki) idan an kai azumi; sannan muka yi sallar Isha’i a ƙarshen silusin dare. Sai ya ce ‘Ya Muhammad, waɗannan su ne lokuttan sallah** (salloli biyar na farilla) **a gare ka da sauran Annabawa da suka gabace ka. Lallai Al’ummarka su yi sallah a tsakanin lokuttan nan biyu da muka yi kowace sallah**.’” Ya kamata mu yi sallolin sau biyar a yini. Wajbi ne ga iyaye su hori ‘ya’yansu da suka kai shekaru bakwai a kan yin sallah, sannan a doke shi da hannu idan ya kai shekaru goma ba ya yin sallar. Bai halatta mutum ya doki wani da yake ƙarƙashinsa ya wuce sau uku ba, ko ya doke shi da sanda. Haka nan za a doki yaro idan ya ƙi yin azumi (a watan Ramadan) ko domin hana shi shan giya. Mutumin da ya musanta cewa farilla ne yin sallah, kuma ba

ita ba ce babbar ibada ga Musulmi, to ya kafirta. Amma idan ya ƙi yin sallar saboda ganda, amma ya yarda farilla ce, to ya zama **fasiƙin** Musulmi. Za a kulle shi a gidan yari har sai ya fara sallah. Za a yi masa haka ba tare da tausayi ko yafiya ba. Idan bai cigaba (da yin sallolin farillar biyar) ba, za a cigaba da tsare shi a gidan yarin yar ƙƙarshen rayuwarsa. Akwai wasu malaman da suka ce, a yi ta dukansa da bulala har sai jini ya fito. A Mazhabobin Shafi'iyya da Malikiyya, mutumin da ya bar sallah ɗaya bai kafirta ba, amma za a yanke masa hukuncin kisa. An faɗa (malamai) a Mazhabar Hambaliyya cewa ya kafirta, kuma za a kashe shi. Akwai malamai da suke da irin wannan ijtihadin a Mazhabar Shafi'i. Idan Mutum ya yi sallah a cikin jam'i, za a yi masa hukunci da cewa Musulmi ne, domin wancan hukuncin bai shafi sallah a cikin jam'i ba; Musulmi na iya yin sallah shi kaɗai. Wani aikin ibadar da suka yi shi ne aikin Hajji. Saboda sallah ibada ce wadda mutum ke yi da kansa, wani Musulmi ba ya iya yi wa wani sallah. Saboda zakka ibada ce wadda ake iya yi da dukiya kaɗai, mutumin da ba shi da wani uzuri, zai iya wakiltar wani mutum wajen biyan zakka a madadinsa ta amfani da dukiyar (wancan) mutumin. Saboda aikin hajji ibada ne wanda ake yi da jiki da dukiya, mutumin da yake da uzuri (wato, wani abu da ya hana shi zuwa aikin hajji), yana iya wakiltar wani ya je aikin hajjin ta amfani da dukiyarsa. Tsoho da ya tsufa tuguf! Da ba ya iya azumi gaba ɗaya a rayuwarsa ba, zai iya ciyar da Musulmi faƙirai da ake kira fidya, a duk ranar da aka yi azumi (wanda bai samu ikon yi ba). Bai halatta ba a bayar da fidya a madadin sallah. Idan mutum ba ya iya yin sallah, idan ya yi wasiyya, yana da kyau bayan rasuwarsa a yi masa fidya ta sallolin da ake binsa daga cikin dukiyar da ya bari. Idan dukiyar da ya bari ba za ta isa ba, ya halatta a yi masa **dawr**. A kan azumi kuma, wajibi ne a yi masa sadaka a kai. (A duba babi na ishirin da ɗaya a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss** domin ƙarin bayani).

A lokacin bazara a ƙasashen arewa, a wuraren da alfijir ke wucewa kafin dare ya shiga, wanda ke nufin lokacin sallar Isha'i da sallar Asuba ba su yi ba, ba wajibi ba ne yin waɗannan sallolin biyu bisa hukuncin Mazhabar Hanafiyya. Babban mujtahidi Imam Shafi'i 'rahmatullahi 'alaih' ya lalubo wani ijtihadin cewa wajibi ne a yi sallolin biyu. Amma wasu manyan Malaman (wato, cikin waɗanda ke fuskantar irin wannan mas'alar) sun ce ba za a yi sallolin na Asuba da Isha'i ba, kuma ba za a rama su ba. (Wato, ba za su yi sallolin daga baya ba). Saboda lokuttan sallolin biyu bai shiga ba. Ba farilla ba ne yin sallar da lokacinta bai yi ba. Ba haka abin yake ga azumi ba. Idan sabon wata ya tsaya a wata Kasa, to watan Ramadan ya tsaya a dukkan sauran ƙasashe.

Idan aka samu **haraj** (tsanani) wajen aikata farilla, ko guje wa aikata haram, sai a yi koyi da wata Mazhabar, (wato ɗaya daga cikin Mazhabobi uku) inda babu wannan haraj ɗin. Haraj na nufin yin wani abu cikin tsanani, ko babu ikon aikata shi gaba ɗaya. Idan babu wata Mazhaba a cikin ukun da ta kawo sauƙi ga wannan Haraj ɗin, kuma haraj ɗin ya faru ne saboda wata lalura,[1] ta an ɗauke maka aikata wannan farillar ko guje wa aikata wannan haramun ɗin. Idan kuma babu lalura a ciki, to sai ka yi ƙoƙarin kawar da haraj ɗin, ta hanyar yin ibadar ba tare da dalilin da ya haddasa shi ba. A duba babi na huɗu na mujalladi na huɗu na littain **Endless Bliss!**

Musulmin da ya makara wajen (nafila) a sallar Asuba, zai bar sallar nafilar domin gudun kada (sallar Asuba ta ƙubuce masa cikin) jam'i. Wajibi ne gare shi ya bar nafilar (ta lokacin sallar asuba) don gudun kada ya rasa lokacin (da ya kamata a yi sallar Asuba). Idan (ya yi hasashen) zai iya samun jam'i, sai ya yi nafilar a wajen masallaci ko bayan ɗaya daga cikin ginshiƙan masallaci. Idan babu wuri (da zai iya yin nafilar) sai ya bar nafilar maimakon yin ta a kusa da sahun jam'i. Domin ana barin aikata sunnah da nufin guje wa aikata makaruhi.

Sallolin farilla da suka kuɓuce sakamakon uzuri ana kiransu **fawait**, wadda ke nufin sallolin (farilla) da suka kuɓuce ba a samu damar yin su (a kan lokacinsu) ba. Sallolin da suka kubce saboda sakaci ba tare da wani uzuri ba, ana kiransu **matrukat**, wanda ke nufin waɗanda suka kuɓuce ba tare da wani uzuri ba. Malaman Fiƙihu sun kira sallolin (da suka kuɓuce saboda uzuri) aka rama su da suna 'faitas (fawait)', maimakon kiransu 'sallolin da suka kubce.' Saboda zunubi ne mai girma ƙin yin sallah a kan lokacinta ba tare da uzuri ba. Ba a yafe wannan laifin ta hanyar rama sallar, (wato, yin ta daga baya, kamar biyan bashi). Haka nan wajibi ne yin tuba da yin hajj-i-mabrur. Idan aka yi ramuwa, (wato, aka yi sallar daga baya, aka biya bashi) zunubin da aka samu shi ne na barin sallar (har lokacinta ya fita) aka yi ta daga baya. Tuba ba tare da rama sallar ba (wato, ba tare da biyan bashi ba,) bai inganta ba, (wato, tubar ba ta yi ba). Domin tuba (a kan wani saɓo) ta ta'allaƙa ne da barin aikata wannan saɓon.

Akwai uzuri biyar (dalilai masu inganci da Musulunci ya yarda da su) na barin sallah har lokacinta ya fita: Idan abokan gaba suka kawo hari, mutum ba zai iya yin sallah ba, ko a zaune ko fuskantar inda ba Alƙibla ba, ko a kan dabba; idan musafir (wato, mutumin da yake kan doguwar tafiya da ake kira 'safar') ya yi fargabar haɗuwa da ɓarayi, ko 'yan fashi ko miyagun

[1] Lalura (Darurat) wani dalili ne dakan sa kayi wani abu ko ya hanaka aiwatar da wani abu. Wato wani abu da ya fi ƙarfinka.

dabbobi a kan hanya; Idan ungozoma (mace mai amsar haihuwa) ta ga akwai haɗarin mutuwar uwa ko jaririnta; to akwai uzuri ga waɗannan mutanen uku su dakatar da yin sallah. na huɗu shi ne mantuwa, sai na biyar kuma bacci ya kwashe mutum. **Adâ**[1] wato a Mazhabar Hanafiyya a yi ƙoƙarin yin kabbarar harama, sannan a Mazhabar Shafi'iyya a samu yin raka'a ɗaya (ta sallah) kafin lokacinta ya fita.

Farilla ne yin ramuwar sallolin farilla, haka nan wajibi ne rama sallolin da suke wajibi. Idan mutum ya rama sallar da take sunnah, zai samu ladar (sallar da take) sunnah. Wajibi ne bin tsarin muhimmanci wajen yin ramuwar ɓangaren farillar witirin sallolin farilla biyar na yini, haka nan a lokacin da ake ramuwarsu. Wannan hukuncin bai shafi idan lokacin sallah ya ƙure ba. Wato, ba za abar sallah ta zama ƙara'i ba a ƙoƙarin rama sallar da ta kuɓuce, (wato, yin sallar da ta kuɓuce a lokacin da ake yin ta). Wani abin kuma da ya kawar da wannan hukuncin shi ne, mutum ya manta yana da faita ta sallah, (wato, sallar da ta kuɓuce), ko yawan sallolin da suka kubcen su kai shida. Jerantawa (wato, tsarin salloli biyar), ba zai yiwu ba idan sallolin ba su kai shida ba. Amma sallolin farilla da aka yi ba bisa tsari ba, sun ɓaci, (wanda ke nufin ba a karɓe su ba) idan yawan su ya kai shida, dukkansu sun inganta, idan lokacin sallah ta biyar ya fita. Misali, mutum ne bai yi sallar Asuba ba, sai ya yi sallar Azahar da La'asar da Magriba da isha'i da witiri (ba tare da ya yi sallar ta Asuba ba) sai ya tuna bai yi sallar Asuba ba, sallolin nasa ba su inganta ba; amma za su inganta idan rana ta riga ta fito (washe gari).

Ana rama sallolin da suka kuɓuce cikin gaugawa. Amma ya halatta a dakatar da su har sai mutum ya samo wa iyalansa abinci da yin sallolin nafila na lokacin sallolin farilla, da sallar duha da ta tasbihi da tahiyyat-ul-masjid.[2] Ibni 'Abidin ya faɗa a sashen da ya yi bayani a kan sunnonin alwala: 'ya halatta' na nufin 'ba a hana ba'. Aiki wanda yake makaruhi tanzihi, (Malaman Musulunci) sun ce 'ya halatta'." Don haka wajibi ne kada a aikata aka ce 'sun halatta (jaiz)', haka nan ba za a jinkirta rama sallah ba da nufin yin waɗannan sallolin na sunnah. Ba lallai ba ne a rama azumin kwanakin watan Ramadan da suka kubce cikin gaugawa.

Mutumin da ya shiga Musulunci (a ƙasar kafirai, da ake kira) Dar-ul-harb, ba lallai ba ne sai ya rama (ayyukan ibada na farilla kamar) sallah da azumi da zakka waɗanda bai yi ba a kan lokacinsu, domin bai san komai ba a kan su. Amma rashin sanin ayyukan ibada na farilla da waɗanda suke

---

[1] Yin adâ na wata sallah shine yin sallar acikin lokacinta. Yin ƙadâ na wata sallah shine aikata ta bayan lokacinta ya wuce.

[2] Duk waɗannan kalmomi anyi bayaninsu a wurare daban-daban a mujalladi na shida na littafin **Endless Bliss.**

haramun ba uzuri ba ne ga mutanen da suke zaune (a ƙasar Musulunci da ake kira) Dar-i-islam ba. Idan wanda ya yi ridda, (wato, ya bar Musulunci) ya sake dawowa Musulunci, ba zai rama sallolin da bai yi ba a lokacin da ya fita. Domin Musulunci ba ya magana da waɗanda ba Musulmi ba. Idan sabiy (yaron da bai balaga ba, wanda shari'a ba ta hau kansa ba) ya yi sallar Isha'i (sannan ya kwanta bacci) sai ya yi mafarki, yayin da ya farka bayan ƙetowar alfijir na washe gari, sai ya rama wannan sallar ta Isha'i (wato, sallar Isha'in da ya riga ya yi). Domin sallar da ya yi (a wancan daren) nafila ce. Ta zama farilla a gare shi a lokacin da yake bacci. Idan akwai sallolin da mutum bai yi ba lokacin da yake da lafiya, ya halatta ya rama su da taimama [1] ko ima'i[2] a lokacin da yake cikin tsananin ciwo. Sallar da ta kubce mai raka'o'i huɗu, za a rama ta ne da raka'o'inta huɗu a yayin safar (doguwar tafiya). Raka'o'i huɗu na farilla a sallar azahar, wadda ta zamo ƙara'i a yayin (doguwar tafiya da ake kira) safar, za a rama ta ne a ta hanyar yin raka'o'i biyu, ko da mutum na muƙim (zaman gida). Idan mutum zai fara sallar La'asar, zai yi niyya ta yin sallar La'asar ta yau, ko ya "yi ta sallar Azahar." Idan ya zamana akwai salloli fiye da ɗaya da suka kuɓuce (waɗanda zai rama ɗaya bayan ɗaya), zai yi niyyar cewa "sallar farillah ta Azahar da ta kuɓuce (wato, ba a kan lokacinta ba ne)" ko "sallar farilla ta La'asar da ta kuɓuce," yayin da za ka fara ramuwar sallolin; ko kuma yayin rama azumin Ramadan da suka kuɓuce ɗaya bayan ɗaya, ba wajibi ba ne jerantawa a tsakaninsu.

Idan mutum yana ramuwar sallah (wadda bai yi ba a lokacinta, ba tare da wani ƙwaƙƙwaran dalili ba da ake kira uzuri, ramuwar sallar da) ake kira matruk, kar ya bari mutane su sani. Saboda zunubi ne mai girma mutum ya bar sallah har lokacinta ya fita. Haka nan saɓo ne ya bari mutane su san zunubinka. Wani aikin saɓon kuma shi ne sanar da mutane zunubin da mutum ya aikata jiya da dare. Nan muka kawo ƙarshen bayanin Ibni 'Abidin.

Kamar yadda aka gani ana gaggauta rama sallolin da suka kuɓuce, a Mazhabar Hanafiyya. Haka hukuncin yake a Mazhabar Shafi'iyya. Shams-ud-din Muhammad Remli 'rahmatullahi 'alaih' malami ne a Mazhabar Shafi'iyya, ya faɗa a cikin littafinsa na fatawa cewa: "Idan sallah ta kubce wa mutum saboda wani uzuri, ba laifi ba ne ya yi sallolin tarawihi a cikin watan Ramadan, sai ya rama sallar bayan Ramadan ɗin. Sai dai saɓo ne ga mutumin da ya bar sallah ta kuɓuce masa ba tare da uzuri ba ya aikata hakan. Domin ana rama sallar da ta kuɓuce ne nan take." Malaman Mazhabar Shafi'iyya sun faɗa a fili cewa saɓo ne mutum ya yi sallolin nafila irin su

[1] Akwai cikakken bayani game da taimama a babi na biyar na mujalladi na huɗu a littafin Endless Bliss.

[2] Wato mutum yayi sallah ta hanyar ishara ko alama.

sallar tarawihi maimakon ya fara rama sallar da ta kubce masa ba tare da wani uzuri ba. Haka hukuncin yake a Mazhabar Hanafiyya. Hukuncin Mazhabar Hanafiyya cewa ya halatta a jinkirta ramuwar sallar da ta kuɓuce (daga kan lokacinta) saboda uzuri, yana nuna cewa ya fi dacewa a rama ta ba tare da ɓata lokaci ba. Abin da ya halatta (jaiz) na nufin wanda ba a hana ba. Ibni 'Abidin 'rahmatullahi 'alaih' ya yi bayanin cewa, "… ya halatta (jaiz) yin ɓarnar ruwa," cewa "makaruhi tanzihi ne….." A lokacin da ya fi dacewa a gaggauta rama sallolin da suka kuɓuce sakamakon wani uzuri, wajibi ne a rama sallolin da suka kuɓuce ba tare da uzuri ba maimakon yin sallolin nafila (na salloli biyar na yini). Ibni 'Abidin 'rahmatullahi 'alaih' ya ce: "Idan mutum yana alwala, sunnah mu'akkada ce wanke (dukkan gaɓoɓin alwala) sau uku-uku. Ba makaruhi ba ne barin wannan sunnar saboda uzuri, da ya shafi ƙarancin ruwa, ko sanyin ruwa da ruwan da ake buƙata." Wannan yana ƙara nuna cewa domin guje wa aikata saɓo, a rama sallolin da suka kubce, wajibi ne a rama sallolin maimakon yin nafila (na lokacin salloli biyar na yini) ban da sallar Asuba. An yi bayanin yadda za a rama sallolin a ƙarshe babin da ke bayani a kan muhimmancin sallah.]

BIYAN BASHIN SALLAH GA MAMACI

['Isƙat na sallah na nufin 'biya wa mamaci bashin sallolin da ake bin sa.' A nan za a yi masa kaffara na sallolin (da suka kuɓuce). Idan za a yi kaffarar, wajibi ne ya zamana mamacin ya bayar da umarni a cikin wasiyyarsa cewa a yi masa, ya zamo ya bar isassar dukiyar da za a yi masa. Wato kashi ɗaya bisa uku na dukiyar da ya bari ta zamo za ta isa a yi masa kaffarar da ita. Waliyyan mamacin ne za su yi masa kaffarar, wanda ya kasance shi ne wanda mamacin ya aminta da shi, ko ɗaya daga cikin magadansa. Waliyyai a nan iri huɗu ne a Musulunci. Waliyyin mamaci (mayyit); da waliyyin yatim (maraya); da waliyyin mace (da za a yi wa aure da ake kira) nikah, (wanda aka yi cikakken bayani a kai, a babi na goma sha biyu na mujalladi na biyar a littafin **Endless Bliss**), da waliyyin bawa ko baiwa ana kiransu **mawla**. Akwai wasu waliyyan bayan waɗannan: Waliyyan Allâhu ta'âlâ waɗanda ake kira **Awliya**. Su ne mutanen da Allâhu ta'âlâ yake so sosai. Samun wannan muƙamin na soyayya yana buƙatar cika dukkan sharuɗɗa da suka shafi kalmomi da aiki da kyawawan ɗabi'u da Annabi Muhammad 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' ya koyar. Za a iya koyon waɗannan abubuwan cikin sauƙi daga wurin malamai bayin Allah na ƙwarai. Mutumin da bai samu Malaman ba, sai ya koya daga littatafai da malaman Ahl as-sunnat. **Ibni 'Abidin** 'Allah ya yi masa rahama' ya ce: "Mutumin da yake da faitas, wato sallolin da suka kuɓuce masa bisa wani uzuri, ya bayar da umarni (a cikin wasiyyarsa) cewa a yi masa kaffara da rabin sa' [lita 2.1],

ko dirhami 520 [1750 gr] na alkama ko garin alkama za a bayar ga mabuƙata ga duk sallah ɗaya ta farilla ko ta wajibi. Ana iya bayar da duka ga mabuƙaci ɗaya. Ya fi dacewa a ƙiyasta darajarsu [da zinare ko azurfa] sai a bayar. Idan mamacin bai bar dukiya ba, ko kashi ɗaya bisa uku na dukiyar ba za ta isa a yi masa kaffarar ba, ko bai yi wasiyya ba, sai waliyyinsa ya yi masa kaffara ta hanyar bayar da kuɗi kaɗan, tun da ya zamana abin da ake buƙata a kowace rana shi ne: 1750 × 6 = 10500 gr. Ko kilogiram goma da rabi [10.5]kg. na alkama, – sai ya ranto na shekara guda = 3780kg. na alkama [ko, – tun da darajar kg. goma da rabi na alkama ya kusa nauyin giram ɗaya na zinare –, kwabon zinare ya yi daidai da ita a daraja, wato 52.5 na kwabon zinare, ko kwabon zinare 60, bisa ƙididdiga, ko wasu abubuwa na zinare da nauyinsu ya zo daidai [432 gr] da suka ƙunshi su awarwaro, da zobukba, da makamantan su.] Bisa la'akari da cewa sallolin (da mamacin ya yi) suna iya zamowa masu rauni, sai ya cire lokacin ƙuruciya, – shekaru goma sha biyu ga namiji, da shekaru tara ga mace, – daga nan sai ya nemo adadin shekarun balaga na mamacin, (wato, lokacin da ya isa yin sallah.) Saboda adadin sallolin na rana ɗaya da suka wajaba a yi wa kaffara su ne guda shida, zai ranto [3780 kg.] na alkama, ko kwabon zinare guda sittin, – wanda ake buƙata domin yin kaffarar na sallolin shekara guda. Ya bayar da su ga mabuƙata a cikin Musulmi tare da niyyar isƙat na kaffara ga salloli (na mamacin). Mabuƙacin ya zamo mai nagarta da nutsuwa, kuma sahihi (mai tsoron Allah) sannan namiji musulmi. Mabuƙacin zai ce "Na karɓa" sannan ya amsa. Sai ya bayar da ita kyauta ga Magajin. Sai magajin ya karɓa ya sake bayar da ita ga wannan mabuƙacin, ko wani mabuƙacin daban. Haka za a yi ta maimaitawa har na adadin lokacin da mamacin ya balaga (sallah ta wajaba gare shi). Idan zinaren da ya ranto ya zarce (adadin da ake buƙata) adadin bayarwar da karɓa zai sauya daban. Idan ya zamanto babu kwabban zinaren, waliyyi zai karɓo aron kayan ado na zinare da suka ƙunshi awarwaro da zobuk a daga wajen mace, ya auna su, sai ya rarraba (shekarun da ba a yi sallar ba × giram 7.2) ya ƙulle a tsumma, kamar kwabban zinaren adadin shekarun da mamacin bai yi sallah ba. Za a ruɓanya wannan adadin sau sittin [60] sai a raba abin zuwa yawan mabuƙatan da za a bai wa sadakar, hakan shi zai ba da adadin zagayen da za a yi. Idan zinaren kaɗan ne, kamar rabin wanda aka ambata a baya. Za a ƙara adadin sadakar da aka yi a baya. Ga mutumin da ya mutu yana da shekaru sittin [60], 60×48×7.2=20736 gr. na zinare za a bai wa mabuƙaci ɗaya. Saboda isƙat na sallah na shekara ɗaya shi daidai da kwabon zinare sittin [60]. Za a yi sadaka sau talatin [30] da 100 gr. na zinare ga mabuƙata bakwai. Idan aka kai ƙarshen sadakar, mabuƙacin na ƙarshe zai bayar da kyauta ga waliyyin mamacin, wanda shi kuma zai mayar ga wanda ya karɓo aron a hannunsa. Haka nan za a yi kaffara ga azumi

da ta yanka da ta rantsuwa. Amma ana buƙatar aƙalla mabuƙata goma ga kaffarar rantsuwa, kuma ba za a bayar da fiye da sa' ɗaya ba a rana guda ga mutum ɗaya, amma za a iya bayar da kaffarar salloli da dama ga mutum ɗaya a rana guda, kuma a lokaci ɗaya. Ba za a bayar da kaffarar zakka ba idan mamaci bai yi wasiyya a kai ba. Amma tun da ba shardanta haka ga azumi ba, ya kamata waliyyi ya aikata hakan ga zakka ita ma, ta hanyar bayarwa daga dukiyarsa. Idan aka kammala dukkan kaffara, magajin zai bayar da dukiya ko kuɗi a matsayin kyauta ga mabuƙatan (waɗanda aka bai wa sadakar kaffarar).

"Idan ya kasance kashi ɗaya bisa uku na dukiyar da mamacin ya bari wanda ya yi wasiyya da kaffara ba za ta isa a yi masa kaffarar ba, waliyyin ba zai iya ɗibar abin da ya fi kashi ɗaya bisa ukun ba ya yi masa kaffarar sai da izinin magadansa. Idan kuma kashi ɗaya bisa ukun ya isa a yi masa kaffarar, amma kuma ana bin sa bashi, to za a fara biya masa bashin kafin kaffarar, ko da wanda ke bin bashin ya bayar da ita ga isƙat. Bayan an biya bashin, wanda ke bin bashin ba zai mayar ba a matsayin kyauta domin a yi masa kaffara. Domin (kammaluwar) kaffara na cika ne da dukiyar da magada suka bayar. Idan mamaci ya bar wasiyya a masa kaffarar sallolin duka rayuwarsa, amma ya zamo ba a san adadin shekarun da ya rayu ba, (wannan ɓangaren) wasiyyarsa ta zama baɗil (ɓatatta). Idan ya kasance kashi ɗaya bisa uku na dukiyarsa bai kai adadin abin da ake buƙata na kaffarar sallolinsa na baki ɗayan rayuwarsa, sai ya yi umarnin a bayar da kashi ɗaya bisa ukun, a nan (wannan ɓangaren na) wasiyyarsa an yi shi ne bisa wani adadi, don haka (wannan ɓangaren na) wasiyyarsa ya zama ingantacce.

"Idan mamaci ya bayar da umarni a wasiyyarsa (a yi masa kaffara), wajibi ne ga waliyyinsa, [wato, magajinsa da zai zartar da wasiyyarsa] ya bayar da wannan kaffarar. Wajibi ne ga mamacin ya bar adadin dukiyar da ta kai kashi ɗaya bisa uku da za a fitar a matsayin kaffara, kuma ya bayar da umarni a cikin wasiyyarsa cewa za a yi masa kaffara da wannan kashi ɗaya bisa ukun. Idan ya bayar da umarnin cewa a yi masa kaffara da wani ɓangare na kashi ɗaya bisa ukun, sauran kuma a bai wa magadansa ko wasu mutane, to yayi shish-shigi ga wajibi wanda yin hakan saɓo ne. Game da wannan batun, bai halatta ba a yi umarnin cewa a yi amfani da wani ɓangare na kashi ɗaya bisa ukun da za a yi kaffarar, wajen yin khatms na Alƙur'ani mai girma da tahlils. Haka nan bai halatta ba a karanta Alƙur'ani mai girma domin a biya mutum. Duka wanda ya biya da wanda aka biya sun yi tarayya wajen aikata saɓo. Wasu (Malaman) sun ce ya halatta mutum ya koyar da Kur'an al-karim don a biya shi, amma babu ko ɗaya (daga cikin Malamai) da ya ce ya halatta a karanta shi domin a biya mutum.

“Idan mamaci ya bayar da umarni a cikin wasiyyarsa cewa magadansa su yi masa sallolinsa (wato, wadanda suka kuɓuce masa), bai halatta ba ga ma Magadan su rama masa sallolin (ga mamacin). Amma ya halatta mutum ya yi sallah ko azumi ya kyautar da ladar da ya samu ga mamacin. Bai halatta ba ga mutum a lokacin da yake gargarar mutuwa, ya bayar da fidya na sallolinsa.” Nan muka kawo ƙarshen bayani daga Ibni ‘Abidin.

Ahmad Tahtawi ‘rahmatullahi ‘alaih’ ya fadà a cikin sharhinsa na littafin **Merafk-il-felah**: An fadà a cikin Nassin ayoyin Alƙur’ani da Hadissai a bayyane, ana yin isƙat na azumin da ya kuɓuce (a lokacinsa) ta hanyar yin masu fidya. “Tun da sallah ta fi azumi muhimmanci, hukuncin zai iya hawa kan sallar,” wannan zance ne da manyan Malaman Musulunci suka hadù a kai.

Don haka, batun “Isƙat ga sallah abu ne da ba shi da tushe,” a ɓangaren (mutanen da suka yarda) mutum mai addini alamu ne na jahilci. Batu ne da ya saɓa wa hadùwar Malamai.

Idan marar lafiya ba ya iya yin sallah, ko da ta hanyar ishara ne da kansa a lokacin da yake kwance, ba zai bayar da umarni a wasiyyarsa ba, ko da sallolin ba su kai guda biyar (na yini) ba. Haka nan, idan mutum ba ya iya yin azumi (sakamakon doguwar tafiya da ake kira) safar ko rashin lafiya, bai samu wajen iƙamat ba, (wato, wurin da zai yada zango) ko bai samu lafiya ta tsawon lokacin da zai iya yin ramuwa ba, ba zai bayar da umarnin isƙat a cikin wasiyyarsa ba. Wasiyyat (wato, umarni a cikin wasiyyar mutum) tana ɗaukar har da (gazawa kan abin da ya shafi) sadaƙa-i-fitr[1], dukiyar mata[2], karya dokokin aikin hajji[3] bayan mutum ya sanya ihrami, sadakar da ake bayarwa ga cika alƙawari[4]. Idan mutum ya mutu ba tare da ya bar wasiyya ba, insha-Allah ya halatta ga magadansa ko wani mutum ya yi masa sadakar. Idan mutum (mamaci) ya yi umarni da hajji a cikin wasiyyarsa, wakilinsa zai je hajjin daga garin mamacin, ko daga wani wuri da kashi ɗaya bisa uku na dukiyarsa za su isa, amma wanda zai je hajjin zai zaɓi daga inda yake so ya tafi aikin hajjin. Bai inganta ba ga kowane mutum ya yi azumi ko sallah a madadin mamaci, ko a kan kudi ko kyauta. Hadisin da ya zo a kan wannan mas’alar Mansukh[5] ne. Game da batun sadakar da ake bayar wa ta kaffara,

---

[1] A duba a babi na uku na mujalladi na biyar a littafin Endless Bliss

[2] A duba a babi na takwas na mujalladi na shida a littafin **Endless Bliss**

[3] A duba a babi na bakwai na mujalladi na biyar a littafin **Endless Bliss**

[4] A duba a babi na biyar na mujalladi na biyar a littafin **Endless Bliss**

[5] Hadisi sharif na goma sha biyar a babi na shida na mujalladi na biyu a littafin **Endless Bliss**

Allâhu ta'âlâ zai yafe bashin mamacin (da ya shafi ayyukan ibada). An faɗa a cikin littafin Shafi'iyya mai suna **Anwar**: "Ba wajibi ba ne ga mamaci ya bayar da fidya a kan sallolin da bai yi ba. Idan aka bayar, ba za ta zamo isƙat ba." Musulmi mabiya Mazhabobin Malikiyya da Shafi'iyya suna bayar da sadakar ne bisa koyi da Mazhabar Hanafiyya.

Idan yawan dukiyar da mamaci ya bayar da umarni ba ta isa a yi kaffarar ba, ko idan kashi ɗaya bisa uku na dukiyar da ya bari ba zai isa ba, ko ya mutu ba tare da ya yi wasiyya ba, za a bayar da sadakar, ta yadda za a yi isƙat na dukkan bashin da ake binsa da dukiya kaɗan da wani ya bayar. Za a bayar da dukiyar ga mabuƙaci da niyyar isƙat. Bayan mabuƙacin ya karɓa sai ya bayar da ita kyauta ga waliyyin ko wani mabuƙacin, wanda zai karɓa, wato ya karɓa da hannunsa; sannan ya miƙa wa wani mabuƙacin ta hanyar sadaka da niyyar isƙat ga bashin da ake bin mamacin (na ayyukan ibada kamar sallah da azumi da bai yi ba). Nan muka kawo ƙarshen bayani daga sharhin Tahtawi.]

BAYANI AKAN JUMA'A

Akwai sharuɗɗa bakwai da za a cika kafin juma'a ta zama ingantacciya:

1. Wurin da za a yi sallar Juma'a ya zama mai girman da za a iya kiran shi gari.

2. Yin (Jawabin da ake kira) Khutba (huɗuba).

3. Yin huɗuba kafin sallah.

4. Yana nufin samun wakilta a wurin daga liman ko kuma shugaban ƙasa.

5. Za a yi sallar juma'ar a lokacin da aka ƙayyade na sallar Juma'a.

6. Kafin sallar Juma'a ta tabbata. (cewa, wajibi ne a samu adadin mutane da za su yi sallar jam'i [mamu, Musulmi], domin sallar Juma'a wajibi ne a yi ta cikin jam'i.) Imam A'zam da Imam Muhammad 'rahmatullahi 'alaih' sun ce, baya ga Liman, wanda dole ya kasance baligi natsattse, dole ya zamo akwai aƙalla mutane uku; wato, da Limamin da mutane biyu, Imam Abu Yusuf 'rahatullahi 'alaih' ya ce zancen na Tarafeyn yana da ƙarfi. (Imam A'zam Abu Hanifa da almajirinsa Imam Muhammad su ake kira 'Tarafayn').

7- An bai wa mutane dama su halarci sallar Juma'a.

An faɗa a cikin littafin fatawa mai suna **Hindiyya** cewa: [Farz-i-'ayn ne ga mutane masu 'yanci lafiyayyu waɗanda ba matafiya ba su halarci sallar Juma'a. Ba farilla ba ne ga (wanda yake doguwar tafiya da ake kira) safar ko marar lafiya, ko mata su halarci sallar juma'a. Haka nan ba farilla ba ne ga

namiji da yake jin tsoron fita saboda ruwan sama ko fargabar haɗuwa da jami'an gwamnati. Bai kamata mahukunta ko jagorori ko shugabannin ma'aikatu, su hana jama'a halartar sallar Juma'a ba. Suna iya cire wani yanki na albashinsu. Idan Limamin Juma'a ya zamo fasiƙi[1], kuma ba ka da ikon hana shi, shawarar Malamai ita ce ka yi sallar Juma'ar a bayansa ya fi dacewa fiye da ƙin halartarta. Wani lokacin, (misali salloli biyar na yini) sai ka tafi wani masallacin inda ke da Liman nagartacce ka yi sallah a cikin jam'i maimakon yin sallar a bayan Liman fasiƙi. Makaruhi ne ga mace ta je masallaci domin halartar sallar jam'i ko da bisa wane dalili ne, ko da wace sallah ce za ta yi.]

Idan mutum ya riski Liman ya yi ruku'u a raka'a ta biyu ta sallar Juma'a, ya yi sallar Azahar ne (ta ranar) inji Imam Muhammad 'rahmatullahi 'alaih'. Imam A'zam da Imam Abu Yusuf 'Allah ya yi masu rahama' ya samu sallar Juma'a ko da ya samu (Liman a makare yayin da yake) tashah-hud (zaman tahiya na ƙarshe). Idan mutum yana sallar nafila, yayin da Liman yake huɗuba, zai yi raka'a biyu ne kaɗai, kar ya zarta haka. Idan sallar da ya yi ta kafin sallar Juma'a ce, babu haɗuwar Malamai game da ko zai yi raka'o'i biyu ne kaɗai ya yi sallama ko kuma ya yi duka raka'o'in huɗu. Yana da muhimmanci ya yi duka raka'o'in huɗu.

Akwai wajibai guda biyar na sallar Juma'a da dole ne a yi riƙo da su:

1- Barin kowane irin aiki da zarar an kira sallah (na lokacin sallar juma'a).

2- Tafiya zuwa masallaci a tsarin tafiyar da ake kira 'sa'i', (wato, yin koyi da irin tafiyar da ake yi tsakanin duwatsun safa da Marwa a lokacin aikin hajji, wanda aka yi cikakken bayani a kai a babi na bakwai na mujalladi na biyar a littafin **Endless Bliss**).

3- Kar a yi sallar nafila yayin da Liman (wato, Khatib) yake khutba (huɗuba).

4- Barin zantuttuka na duniya.

5- Yin shiru.

Akwai mustahabbai shida na sallar Juma'a da ya kamata a yi riƙo da su:

1- Rayiha-i-tayyiba, (wadda ke nufin sanya turare).

[1] Mutumin da tabbas yana aikata ɣaya daga cikin aiyukan haram kamar shan giya, zina da dai sauransu shine 'fasiƙ'.

2- Yin asuwaki (wanda gutsiren icce ne da ake kira araƙ)[1]

3- Sanya tufafi masu kyau.

4- Tabkir, [wanda ke nufin tafiya zuwa Masallaci da wuri domin halartar sallar Juma'a. A zamanin (da ake kira) Zaman-i-Sa'adat, (wato a lokaci mai albarka wanda fiyayyen halitta, Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya rayu da lokacin Khalifofinsa guda huɗu, sayyidina Abu Bakr da sayyidina Umar da sayyidina Uthman da sayyidina 'Ali 'radiyallâhu ta'âlâ 'anhum ajma'in') Sahabbai 'radiyallâhu ta'âlâ 'anhum ajma'in' ba sa fita daga Masallaci bayan sallar asuba a ranar Juma'a har sai an kammala sallar Juma'a. Al'ummar wannan zamanin sun yi watsi da wannan kyakkyawar ɗabi'ar, wadda take sunnah ce da ake kira tabkir.]

5- Yin wanka, (wanda aka yi bayaninsa a babi na huɗu a mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**).

6- Karanta azkar da ake kira salawat, (wanda ake yi wa Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' kamar haka: "**Allahumma salli 'ala sayyidina Muhammadin wa 'ala [alihi wa sahabihi] ajma'in**.")

Akwai Makaruhai guda biyar da ya kamata a guji aikatawa a ranar Juma'a:

1- Yin sallama, (wato, gaisuwa da addinin Musulunci ya tanada) yayin da Liman yake huɗuba (An yi cikakken bayanin gaisuwa a addinin Musulunci a babi na sittin da biyu a mujalladi na uku na littafin **Endless Bliss**.)

2- Karanta Alƙur'ani mai girma (yayin da Liman yake huɗuba).

3- Cewa "**Yarhamukallah**," ga mutumin da ya yi atishawa (ya ce "Al-hamd-u-li-llah"), (yayin da Liman yake huɗuba).

4- Ci ko shan wani abu (yayin sallar Juma'a da huɗubarta).

5- Yin aikin da yake makaruhi. [Aiki da yake makaruhi ya ƙunshi Liman ya ja dogon bayani da sunan huɗuba.]

Bayan kiran sallar Juma'a na farko, wanda za a yi a kan mimbari (da ke wajen Masallaci) Liman zai yi nafila ta farko ta sallar Juma'a kusa da mimbari. Daga nan zai zo gaban minbarin ya yi gajerar addu'a yana kallon

[1] A daure a duba sakin layi na goma sha uku a ƙarƙashin 'Ladubban alwala' a babi na biyu a mujalladi na huɗu na littafin Endless Bliss, ko kuma a shiga Google a bincika kalmar 'Miswak' domin ganin yadda musulunci ya koyar damu tsaftace hakora, baki da abinda ya shafi jikin mu sama da shekaru dubu da ɗari huɗu.

Alƙibla, sai ya hau minbarin ya zauna yana fuskantar jama'a, ya saurari kiran sallah na biyu. Daga nan zai miƙe ya fara hudubba.

[Mutanen da ake kira Wahhabis ba sa kan Mazhabar Ahl as-sunnat. Ba su da wata tsayayyar Mazhaba. Ana kiransu **Wahhabis ko Hajdis**. Wasu munafukan Turawan Ingila ne suka ƙirƙiro Wahabiyanci. Sun yi amfani da wani jahilin Malami daga Nejd mai suna Muhammad ɗan 'Abd-ul-wahhab wajen ƙirƙiro shi. Suna kiran waɗanda ba sa bin Wahabiyanci kafirai a litattafansu. Sun rubuta cewa ya halatta a kashe mutanen da ba sa bin Wahabiyancin, a ƙwace matansu da 'ya'yansu mata da dukiyarsu a matsayin ganima. Suka riƙa jan hankalin jahilai da mutanen da ba su da Mazhaba da dukiya suna yaudararsu, suna mayar da su Wahabiyawa suna tura su cibiyoyinsu da suke kira **Rabita-t-ul 'alam-il-islam** waɗanda suka kafa a ƙasashen duniya da dama. Suna yaɗa rubuce-rubucensu na ƙin Musulunci a matsayin 'Fatawowin da Malaman duniya suka bayar' sun yaɗa su a dukkan ƙasashen Musulmi na duniya. Yayin aikin hajji, suna rarraba su ga hadjis (Musulmi mahajjata). A wani rubutu da suka yi, sun ce: "Farilla ne ga mace ta halarci sallar Juma'a." Suna amfani da ƙarfi wajen tirsasa wa mata fita zuwa sallar Juma'a. Suna yin sallah cakuɗe tsakanin maza da mata, a sallar jam'i lokaci guda. Haka nan a wani rubutunsu sun ce: "Wajibi ne a karata hudubar Juma'a da ta Idi a harshen (yare) da mutanen (da suka halarci sallar) suke ji. Ba za a karanta da Larabci ba." Malaman Musulunci na gaskiya sun kore wannan fatawar tasu ta hanyar bayar da hujja ta nassi. Ɗaya daga cikin waɗannan bayanan su ne fatawowin da Malaman Ahl as-sunnat na wurare daban-daban na ƙasar Indiya suka bayar. Misali, 'Allama hibr-un-nihrin wa-l-fehhama sahib-ut-taƙrir wa-t-tahrir Mawlana Muhammad Temimi bin Muhammad Madrasi 'neɓɓerallahu merƙadehu', Mufti na Madras, ya ambato kamar haka:

Makaruhi ne yin (karanta) hudubba da wani harshe da ba Larabci ba, ko gwama harshen Larabci da fassara ta a wani harshen daban. Wajibi ne yin baki ɗayan hudubba da Larabci. Domin Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' ya yi dukkan hudubobinsa da harshen Larabci ne. An faɗa a cikin babin da yake bayani a kan sallar Idi a cikin littafin **Bahr-ur-rasiƙ** cewa: "Ba a yin sallolin nafila cikin jam'i ban da sallar Tarawihi (asham) da ta Kusufi. Tun da sallar Idi a kodayaushe ana yin su ne a cikin jam'i, sun zama wajibi ke nan ba nafila ba." Kamar yadda aka gani, aikin ibada wanda Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yake yi a kodayaushe wajibi ne. Allama Zebidi 'rahmatullahu alaihi' ya faɗa a cikin sharhin littafin **Ihya-ul-'ulum** cewa: "Aikin ibada wanda Annabi 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yake yi a koda yaushe wajibi ne. Ba lallai ba ne sai aikin ibada na farilla. 'Allama

Mufti Abu-s-su'ud Efendi 'rahmatullahi 'alaih' ya faɗa a cikin littafinsa mai suna **Fet-h-ullah-il-mu'in** cewa: "Aikata ta da Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yake yi a-kai a-kai ya nuna cewa aiki ne na ibada da yake wajibi." Ibni 'Abidin 'Allah ya yi masa rahama' ya faɗa a cikin rubutunsa a kan bayani game da sunnonin alwala cewa: "Aikin ibadar da Mazon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yake yawan aikatawa sunnah muakkada ne, idan dai har ba ya bari ya kuɓuce masa. Baya ga ba ya bari ya kuɓuce masa, kuma yana kwaɓar duk wani mutum da yake barin sa, to wajibi ne. Idan bai kwaɓi (mutumin da ya bar aikin ibadar ba) yana nuna amincewarsa a kan barin shi. A kan haka, Abu-s-su'ud Efendi ya ce "Aikin ibada wanda Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yake aikatawa koda yaushe ba tare da barinsa ba wajibi ne." An faɗa a ƙarshen sashen da aka yi bayani a kan makaruhan sallah cewa makaruhi ne tahrimi barin ɗaya daga cikinsu.] Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yana yin huɗubarsa a kowane lokaci da harshen Larabci, wannan ya nuna cewa wajibi ne yin huɗuba da Larabci. Don haka makaruhi ne tahrimi yin huɗuba da wani harshen da ba Larabci ba ko gwama su a tare, wato Larabci da wani harshen daban. Bisa la'akari da hukuncin farko, an karya ƙa'idar cewa wajibi ne a yi ta da Larabci; haka nan a hukunci na biyu, an karya ƙa'idar cewa dole ne a yi ta da harshen Larabci kaɗai. A dukkan hukunce-hukuncen biyu, an saɓa a kan dukkan abin da Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yake aikatawa kodayaushe. Haka nan, furta kabbara (ta harama, wato faɗar "Allahu akbar") a harshen Larabci yayin fara sallah, da faɗar "Allahu akbar a tsakani, abubuwa biyu ne mabambanta. Makaruhi ne tahrimi barin kowane ɗaya daga cikinsu. Domin ya zama wajibi yin hakan, saboda Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yana faɗar "Allahu akbar" kodayaushe, don haka makaruhi ne tahrimi ƙin aikata hakan. Ibni 'Abidin Allah ya yi masa rahama' ya faɗa a cikin **Radd-ul-muhtar** cewa: "Makaruhi na nufin wai abu (misali, aiki ko ɗabi'a) wanda idan aka yi shi an saɓa wa sunnah. Hukuncin farko (wato, saɓa wa wani abu da yake wajibi) shi ne makaruhi tahrimi; yayin da hukunci na biyu (wato, saɓa wa wani abu da yake sunnah) shi ne (makaruhi) tanzih ." An rubuta a cikin littafin **Halabi-i-kabir** (na Ibrahim bin Muhammad Halabi (886, Haleb [Aleppo] – 956 [1549 M.]) cewa: "Makaruhi tanzihi barin (ko watsi) da abin da yake sunnah. Makaruhi ne taharimi barin abin da yake wajibi." An ruwaito a cikin littafin **Fatawa-i-Sirajiyya** (na 'Ali 'Ushi bin 'Uthman 'rahmatullahi 'alaih' (d. 575 [1180 M.]) cewa: "Ya halatta a yi huɗuba da harshe Farisanci (Persian)." Ya zamo baɗil (ɓatacce) a bayar da wannan batun a matsayin hujja, a bayar da fatawa cewa ya halatta a yi huɗuba da wani Harshe da ba Larabci ba, kuma ba makaruhi tanzihi ko taharimi ba ne. A batun na Sirajiyya ana nufin "Sahih ne (ya inganta)", ba ya

nufin “ba makaruhi ba ne”. Ibni ‘Abidin ‘Allah ya yi masa rahama’ ya faɗa a cikin **Radd-ul-muhtar** cewa: Maganarsa (wato ‘Ali ‘Ushi) cewa ya inganta ba ya nufin cewa ba makaruhi ba ne.” Muhammad ‘Abd-ul-Hayy Luƙneɓi ‘rahmatullahi ‘alaih’ ya faɗa a littafinsa mai suna **‘Umdat-ur-riaya** cewa: “Maganar yin huɗuba da harshen Larabci ba sharaɗi ba ne na cikar sallar Juma’a; ya halatta a yi ta da harshen Farisanci ko wani Harshen daban,” ya nuna idan aka yi sallar juma’ar ta yi. Wato, an cika sharaɗin yin huɗuba domin sallar Juma’a ta inganta. Ba ya nuna cewa huɗubar da aka yi makaruhi ce. Domin Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ da sahabbansa ‘radiyallahu ‘anhum’ suna yin huɗuba ne da Larabci kaɗai a kodayaushe kuma a ko’ina. Makaruhi taharimi ne a saɓa masu.” Haka nan, Tabi’ai da Tabi’ut Tabi’in ‘Allah ya yi masu rahama’ duk sun yi huɗuba ne da Larabci, a kodayaushe kuma a ko’ina. Baya ga cewa ba su yi ta wani Harshe bayan Larabci ba, kuma ba su gwama Larabcin (da wani Harshe ba) suna fassara ta ba. [Haka abin yake a wasu ƙasashe kamar Asiya da Afrika, inda mutanen da ke sauraren huɗuba ba sa fahimtar abin da ake faɗa a huɗubar saboda ba sa jin Larabci. Duk da cewa dole ta sa ake fassarar huɗubar, domin a koyar da sababbin Musulmi, ba su halatta cewa a yi amfani da wani Harshe da ba Larabci ba a yayin huɗubar. Sai su sanar da su Musulunci ta wata hanyar da ba huɗuba ba. Su ba su shawarar su koyi Larabci domin fahimtar huɗuba da Musulunci baki ɗaya. Mu yi koyi da waɗannan bayin Allan a wannan batun.]

Bidi’a ne saɓa masu ta hanyar yin huɗuba da wani Harshe da ba Larabci ba. Makaruhi ne taharimi yin hakan. Bai inganta ba a kira batun na farko ‘tahrimi’ na bayan kuma kira shi ‘tenzihi’. Domin makaruhi tanzihi na nufin barin wani abu da yake sunnah. Saboda Manzon Allah ’sallallâhu ta’âlâ ’alaihi wa sallam’ ya yi dukkan huɗubobinsa ne da Larabci kaɗai, don haka wajibi ne yin huɗuba baki ɗayanta da harshen Larabci. Ta yaya zai zama tanzihi idan aka bar wannan wajibin? Wajibi ne a bar aikata duk wani abu da yake makaruhi taharimi. Mawlana Bahr-ul-‘ulum ‘rahmatullahi ‘alaih’ ya faɗa a cikin **Arkan-ul-arba’a**: “Wajibi a guji aikata wani abu da yake makaruhi taharimi. Aikata makaruhi na nufin saɓa wa (umarni da yake) wajibi.”

Mutumin da yake yawan aikata makaruhi taharimi ba adalin Musulmi ba ne. Ibni ‘Abidin ‘Allah ya yi masa rahama’ ya faɗa bisa ruwayar Ibni Nujaym ‘Allah ya yi masa rahama’ yayin da ya fara tattaunawa a kan wajiban alwala a littafinsa **Radd-ul-muhtar** cewa: “Karamin zunubi ne aikata makaruhi tahrimi. Dawwama a kan aikata ƙananan zunubai yana raba mutum da zama adali. (Wato yawan aikata ƙananan zunubai suna taruwa su zamo manyan zunubai. Kuma yawan aikata manyan zunubai yana raba mutum da zama adali, wato zai kasance ba adalin Musulmi ba). Bisa wannan batun,

Limamin da ya fassara hudùba ya rabu da zama adali, ya zama fasiƙin Musulmi. (Fasiƙi shi ne wanda yake aikata manyan zunubai a fili. Misalan manyan zunubai su ne: Kin aikata dàya daga cikin shikashikan Musulunci ba tare da wani uzuri ba, ko aikata abubuwan da aka haramta a fili). Makaruhi taharimi ne bin irin wadannan mutanen sallah, (wato, bin sallar jam'in da suke jagoranta). An rubuta a cikin littafin **Nur-ul-idhan**, (na Abul-Ikhlas Hasan bin 'Ammar Shernblali 'rahmatullahi 'alaih', 994 – 1069 [1658 M.] Egypt,) da **Ibni 'Abidin** cewa: "Makaruhi ne ga bawa ko mutumin ƙauye, ko shege, idan ba su da ilimi, da dan bidi'a, ko da yana da ilimi su yi limanci (su jagoranci sallar jam'i). saɓo ne a ba su limanci (har su jagoranci sallar jam'i)." 'Allama Ibrahim Halabi 'rahmatullahi 'alaih' ya fadà a cikin **Halabi-i-kabir** cewa: "Musulmin da suka bar fasiƙi ya zamo Limaminsu (yana jan su sallar jam'i) sun aikata zunubi (bisa yin haka). Domin makaruhi taharimi ne barin fasiƙi ya yi limanci." An rubuta a cikin **Marak-il-falah** cewa: "Makaruhi ne a bar fasiƙi ya zamo Limami (ya riƙa jan sallar jam'i) ko da yana da ilimi (na addinin Musulunci). Domin ya nuna gazawa wajen riƙo da Musulunci. Wajibi ne a dauke shi matsayin mai saɓo. Barin shi ya yi limanci ya nuna za a girmama shi. Idan ba za ka iya hana limancin sallar jam'i ba, sai mutum ya riƙa halartar Juma'a da sallolin farilla na yini a wani Masallaci na daban." Sa'ilin da 'Allama Tahtawi 'rahmatullahi 'alaih' yake bayanin wannan jawabin, ya ce: "Makaruhi taharimi ne (ga Musulmi) a bar fasiƙi ya zama Liman (ya riƙa jan sallar jam'i)."

Bai kamata a sanya Liman ya yi hudùba da Harshen da ba Larabci ba. Saɓo ne yin hakan. Ibni 'Abidin 'rahmatullahi 'alaih' ya fadà a **Radd-ul-muhtar** cewa: "Ba za a yi sallah (cikin jam'i) a bayan Limami fasiƙi ba. Ya kamata a nemi Limamin da ba fasiƙi ba. Sallar Juma'a batu ne na daban. Amma, ita ma makaruhi ne yin sallar Juma'a a bayan Limami fasiƙi, idan akwai wasu Masallatan da ake yin ta a gari. Idan haka ne sai mutum ya yi sallar a bayan wani Limamin. A cikin littafin **Fat-h-ul-ƙadir**[1] ya bayar da irin wannan hukuncn." Don haka, kar a yi ta a bayan Limamin da yake yin hudùba da fassara, maimakon yin ta da harshen Larabci kadai, sai mutum ya nemi Limamin da yake yin hudùbar da Larabci kadai ya yi sallar Juma'ar a bayansa, (wato, mutum ya bi sallar jam'in da wannan Limamin yake jagoranta). Domin ƙarin bayani, a karanta littafin **At-tahƙikat-us-saniyya fi-karahat-il-khutba-t-i-bi-ghayri-l-'arabiyya wa ƙiraatiha bi-l-'arabiyyat-i-**

[1] Wanda ya rubutashi shine Ibni Humâm 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' (730 [1388 A.D.] – 861 [1456]) a matsayin sharhi ga littafin Hidâya, wanda shi kuma Burhânaddîn Merghinânî 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' (593 [1197 A.D.] – martyred by the hordes of Jenghiz Khân.) ya rubuta shi.

ma'a tarjamaha bi-ghayr-il-'arabiyyati. Nan muka kawo ƙarshen bayani daga 'Allama Muhammad Tamimi Madrasi.

Wannan rubutun na sama wanda aka yi da Larabci a Indiya a shekarar 1349H. [1931 M.], ya samu amincewa daga manyan Malaman Indiya guda goma sha uku. Tare da wannan fatawar mai tarihi, akwai fatawar ta Larabci ta Malaman Indiya daga **Diobend** da **Bakiyat-us-salihat** da **Madras** da **Haydarabad** wanda aka buga a Istanbul, Turkiyya a shekarar 1396H. [1976 M.]. Dubban manyan Malaman Ottoman na Musulunci da Sheikh-ul-islam 'rahmatullahi alaih' sun binciki hanyoyin da za su taimaki mutane su fahimci hudubar da suke saurare. Gazawar da suka yi wajen lalubo wata hanya da ta halatta samar da hudubar a harshen Turkanci, ya sanya ba su halatta yin hakan ba. An samar da hanyar wayar da kan (Musulmin da suka halarci) jam'i ta hanyar yin wa'azi a dukkan Masallatai bayan sallar Juma'a, ana sanar da mutane abin da ke ƙunshe a cikin fatawowi tsawon shekaru ɗari shida, ta haka aka kiyaye iyakokin ayyukan ibada na Musulunci daga keta iyaka.]

Sallar Idi, (wato, sallar da ake yi da safiyar ranakun Idi biyu) suna da (kabbarori guda tara da ake kira) **Kabbarorin Zawaid**: Ɗaya daga cikinsu farilla ce. Ɗaya kuma sunnah ce. Sai guda bakwai kuma wajibai ne. Kabbarar harama farilla ce. Kabbarar yin ruku'u na farko sunnah ce. Kabbarorin zawaid wajibai ne. Kabbarar ruku'u na biyu wajiba ce saboda kasancewarta lokaci ɗaya da kabbarar da take wajibi; (wato, lokaci ɗaya ake yin ta da kabbarar zawaid ta ƙarshe, waɗanda suke wajibai ne.)

GABATAR DA SALLAH

An rubuta a cikin **Ni'mat-i-islam** cewa: Farilla ne ga kowane Musulmi mai hankali kuma baligi ya yi salloli biyar a yini. Babu wani mutum da zai iya yin sallah a madadin wani. Mutum na iya bayar da kyautar ladar sallah ko wani aiki na ibada da ya yi ga wani mutum daban [mai rai ko mamaci. Kowane daga cikinsu, (wato, mutanen da ake bai wa kyautar ladar aikin ibadar,) za a ba su daidai adadin ladar da wanda ya yi kyautar ya samu; sannan ba za a rage ladar wanda ya yi kyautar ba.] Bai halatta mutum ya yi sallah ya bayar da ladar da ya samu kyauta ga wanda suke jayayya ko yake bin sa bashi domin sun yafe masa haƙƙinsu. Mutumin da ya yi imani salloli (na yini guda biyar) farilla ne, amma bai aikata su ba, kuma ba tare da uzuri ba, ba zai zama kafiri ba. Zai zama fasiƙin (Musulmi). [An faɗa a cikin sahihin isnadi) cewa hukuncin barin sallah guda ɗaya shi ne zaman shekaru dubu saba'in cikin wutar Jahannama.] (Mutumin da ya bar sallolin farilla) za a kai shi gidan yari, a tsare shi a can har sai ya cigaba da sallah tukunna. Idan

yaro ya kai shekaru bakwai, (iyayensa) su riƙa horar da shi yin sallah. Idan ya kai shekaru goma ba ya sallah, za a riƙa dukansa da hannu. Ba za a duke shi fiye da sau uku ba. Kuma ba za a doke shi da bulala ba. Duka da bulala hukunci ne da ake yi wa baligai da suka aikata manyan laifuka, don haka yana buƙatar umarni daga kotu. Mutum ba zai doki matarsa da bulala ba, [bai halatta a doki kowane abin halitta a kai ko a fuska ko a ƙirji ko ciki ba.] Farilla ne ga marar lafiya ya yi sallah gwargwadon ƙarfinsa. (Mafi yawan mujalladi na hudu na littafin **Endless Bliss** ya yi Magana ne a kan abin da shafi sallah).

SHIGA CIKIN UZURI (‘UDHR)

Idan wani abu yana fita da jikin mutum ba ƙaƙƙautawa, ana kiransa **‘udhur** (uzuri), (mutumin da yake fuskantar wannan matsalar yana cikin mutane masu uzuri). Mutumin da yake fama da yoyon fitsari ko zawo, ko yawan fitar da rihi ta dubura, ko haɓo ko rauni da yake zubar da jini da sauransu, haka nan da ruwa (da ke fita daga rauni), da hawaye da suke zuba sakamakon ciwon ido, da mace da take jinin rashin lafiya, dukkan su ana kiransu **mutane masu uzuri**. Ya kamata su kawar da matsalar da ta haddasa uzurin ta hanyar amfani da dabarar toshewa ko shan magani, da yin sallah daga zaune ko ta hanyar yin ishara. [Mutumin da ke fama da lalurar yoyon fitsari, ya tura auduga gwargwadon girman ƙwayar alkama a cikin ƙofar da fitsari ke fita. Idan aka yi amfani da auduga marar inganci, gashin jikinta zai iya kutsawa cikin ƙoda ya haifar da cuta. Idan mutum zai yi fitsari sai ya zare audugar. In ya kasance fitsari mai yawa ya fito daga mafitsara, har ya fito ta cikin audugar, ya warware alwalar mutum. Fitsarin da ya fito kada ya taɓa tufafin mutum, wanda za a iya tarewa ta hanyar naɗa wani ƙyalle a kan azzakari a ɗaure shi da zare a haɗa a maƙale shi a jikin wando. Idan ya zamana fitsarin ya cigaba da fita da yawa, sai a sanya auduga a cikin ƙyallen. Idan ƙarshen zaren da aka matse ya zamo akwai tsanani wajen cire shi, ana iya amfani da wani abu mai danƙo a matse shi. Ya fi sauƙi a raba su, ta yadda za a iya wanke ƙyallen sau uku a waje wanke hannu. Ya kamata mutumin da yake fama da lalurar yoyon fitsarin ya riƙa ɗaukar ƙyallaye uku zuwa biyar a aljihunsa. Ya haɗa kowane ƙyalle da zare a kusurwarshi mai faɗin (12×15) cm. sai a murɗe ta, sannan a ɗaura zare mai tsawon 50cm a kusurwar da aka murɗe. Wasu daga cikin tsofaffi da marasa lafiya azzakarinsu yana ƙanƙancewa, saboda haka sai ƙyallen ya riƙa cirewa. Irin waɗannan sai su riƙa sanya ƙyalle mai faɗi kamar adiƙo a cikin leda, su sanya kan azzakarin a cikin ledar, sannan su ɗaure bakinta. Idan faɗin fitsarin da ya ɗiga a kan ƙyallen ya zarce na dirhami ɗaya (4.80 gr.) sai a sauya wani ƙyallen. Idan

lokacin sallah ya wuce, alwalar mutumin da yake da uzurin ta warware. Idan kuma wani sabon uzuri ya ɓulla kafin lokacin sallar ya fita, alwala ta warware bisa samuwar sabon uzurin kafin fitar lokacin sallah. Misali, idan mutum ya yi alwala yayin da jini ke fita (wato haɓo) daga ɗaya daga ƙofofin hancinsa; idan jini ya fito daga ɗaya ƙofar hancin, to alwalar ta warware. A Mazhabobin Hanafiyya da Shafi'iyya, zamowa mutum mai uzuri, yana buƙatar wannan lalurar da ke warware alwala ta cigaba da faruwa har lokacin sallar ya fita. Idan misali, haɓo ya ɗauke wa mutum na wucin gadi (wato na ɗan wani lokaci), bai sake dawowa ba sai bayan da mutumin ya yi alwala ya yi sallar farilla ta wannan lokacin, to wannan mutumin ba shi daga cikin masu uzuri, Da zarar mutum ya kasance mai uzuri to zai cigaba da zama a haka a dukkan lokuttan sallah, muddin idan ya zama lalurar tana dawo mashi a wadannan lokuttan, idan ya kasance haɓon ya zo ne sau ɗaiɗaya a tsakanin lokuttan sallar, ko da ɗigo ɗaya ne na jinin ya ɗiga. Idan jinin bai zo ba ko kaɗan, wannan mutumin ba shi daga cikin masu uzuri. Idan najasar[1] da ta haifar da uzuri ta zuba a kan situra gwargwadon faɗin dirhami ɗaya, wajibi ne a wanke inda najasar ta taɓa, idan zai yiwu kuma kada a sake bari najasar ta taɓa siturar. An faɗa a cikin littafin **al-Fiƙh-u-'ala-l-Madhahib-il-arba'a** cewa: "Akwai zantuka biyu game da kasancewar marar lafiya a cikin masu uzuri a bisa hukuncin Mazhabar Malikiyya: zance na farko ya nuna cewa, abin da yake warware alwala sai ya yi ta afkuwa adadin rabin lokacin sallah, kuma sai an san lokacin da ya fara da lokacin da ya ƙare. Zance na biyu ya nuna cewa, marar lafiya yana zamowa mutum mai uzuri yayin da (lalurar) abin da ke fitowa ya fara ko da babu ƙa'idojin can biyu na zancen farko. Alwalar marar lafiyar ba ta warware ba. Idan an san lokacin da lalurar ta tsaya, mustahabbi ne ga marar lafiya ya sake alwala kafin ya yi sallah. Marar lafiya ko tsoho wadanda suke bin Mazhabar Hanafiyya ko Shafi'iyya wadanda ba sa cikin mutane masu uzuri (bisa hukuncin wadannan Mazhabobin biyu) sai ya yi koyi da zance na biyu na Mazhabar Malikiyya."]

Idan mutum ya yi fargabar kamuwa da rashin lafiya, ko rashin lafiyarsa za ta tsananta ko kuma za ta daɗe ba ta warke ba idan ya yi alwala, to sai ya yi taimama. Wannan fargabar za ta yi tasiri ne idan mutum ya taɓa shiga irin wannan yanayin ko kuma bisa shawarar adalin likita Musulmi. Za a iya karɓar shawarar likita idan ya zamo ba mutum ba ne mai yawan aikata saɓo. Wasu dalilai da ke haddasa rashin lafiya sun ƙunshi: Yanayin sanyi sannan ba wurin fakewa; rashin samun wani abu da mutum zai ɗumama ruwan da

[1] Wani abu kamar jini, fitsari, giya da saurans su wanda ya kamata a wanke daga inda zakayi sallah ko kuma daga tufafin mutum. A duba babi na shida a cikin mujalladi na hudu na littafin Endless Bliss domin ƙarin bayani.

shi, ko rashin kudin da mutum zai biya ya yi amfani da makewayi na kasuwa. A Mazhabar Hanafiyya, za a iya yin sallolin farilla da yawa da taimama ɗaya da mutum ya yi. A Mazhabar Shafi'iyya da Malikiyya wajibi ne a yi taimama ga kowace sallar farilla.

Idan mutum yana da rauni a ɗaya daga cikin gaɓoɓinsa na alwala, (wato a gaɓar da wajibi ne a wanke ta a wajen alwala) zai yi taimama (a madadin alwala). Idan ya zamana raunin ya shafi ƙasa da rabin gaɓar ne (gaɓar alwalar) sai ya wanke inda babu raunin, ya yi shafa a kan raunin. Saboda dukkan jiki yana matsayin gaɓa ɗaya ne a wajen wanka, mutum zai yi taimama idan ya zamana yana da rauni a rabin jikinsa. Idan raunin bai kai rabin (dukkan jiki ba), sai mutum ya wanke inda babu raunin, ya yi shafa a kan raunin. Idan shafar za ta iya fama raunin, sai a yi shafar a kan bandeji. Idan yin hakan zai iya cutarwa, to an ɗauke wa mutum shafar baki ɗaya. Idan shafa saman kai zai iya cutarwa a yayin wanka ko alwala, sai a bar shafar a saman kan. Mutumin da ba zai iya amfani da hannunsa wajen ɗibar ruwa ba saboda wani abu da ya same shi [kamar ƙurajen ƙazuwa ko rauni] a kan hannun, sai ya yi taimama. (Wajen yin ta, sai ya shafa fuska da hannunsa a hankali saman ƙasa [ko a bangon laka ko dutse ko ƙasa]. Idan mutum ba shi da hannuwa da ƙafafu, kuma yana da rauni a fuskarsa, to zai yi sallarsa ba tare da alwala ba. Mutumin da bai samu wani da zai taimake shi ya yi alwala ba, sai ya yi taimama. 'Ya'yansa ko bayinsa ko kuma mutanen da ɗauka aiki, za su taimake shi (ya yi alwala). Haka nan yana iya neman wasu su taimaka mashi. Bai kamata miji ko mata su taimaki junansu a wajen alwala ba. Idan mutum ya yi amfani da bandeji [ko filasta da aka sanya a kan bandeji, ko mai] saboda zubar jini, ko sanya wani abu a kan raunin da yake zubar da ruwa, ko ƙuna, ko rauni a ƙashi; idan ya gaza wanke wannan wurin da ruwan sanyi ko na zafi ko ya gaza shafa a kai yayin alwala ko wanka, sai ya yi shafa sau ɗaya a kan fiye da rabin wajen. Idan ya zamana Akwai cutarwa wajen warware bandejin, ba sai an wake wajen da babu rauni da yake ƙarƙashin bandejin ba. Shafar da aka yi a kan inda yake da lafiya ta isar wa ƙarƙashin bandejin. Ba lallai ba ne ya zamo mutum ya yi alwala kafin ya saka bandejin. Idan aka sauya bandejin bayan an yi shafar, ba lallai ba ne sai an sake shafa a sabon bandejin, ko an sake sanya wani a bayansa.

SALLAH YAYIN RASHIN LAFIYA

Idan marar lafiya ba ya iya tsayuwa ko ya tabbatar cewa tsayuwar za ta ƙara tsananta rashin lafiyarsa, sai ya yi sallarsa daga zaune; sai ya riƙa dukar da jikinsa kaɗan yayin ruku'u, bayan ya dawo ya zauna, sai ya yi sujada a ƙasa, (wato da goshi da hancinsa a kan ƙasa). Sai ya taso ya zauna yadda ya fi yi masa sauƙi. Ya halatta ya durƙusa a kan guiwarsa, ko ya hardɛ ƙafafunsa

ko ya zauna a kan ɗuwainiyarsa, hannuwansa da guyawunsa kusa da gangar jikinsu. Ciwon kai da na haƙori da na ido dukkansu rashin lafiya ne. Wani uzurin (a kan wannan) fargabar cewa abokan gaba za su iya ganin mutum. Haka nan mutumin da alwalarsa za ta iya warwarewa idan ya miƙe tsaye, sai ya yi sallarsa daga zaune. Mutumin da ya ke iya tsayuwa idan ya jingina da wani abu sai ya yi sallarsa a jingine. Mutumin da ba ya iya daɗewa a tsaye, zai yi kabbarar harama (wato, ya fara sallah da faɗar "Allahu akbar") daga tsaye, ya cigaba da sallar daga zaune idan ya (ko ta) matsu.

Mutumin da ba ya iya sujada a kan ƙasa, ya yi karatu (na surori) daga tsaye, sai ya zauna ya yi ruku'u da sujada ta hanyar ishara. (Yayin hakan) zai ɗan risina da jikinsa kaɗan yayin ruku'u, sai kuma ya risina sosai yayin sujada. Mutanen da ba sa iya tanƙwara jikinsu, sai su duƙar da kansu. Ba lallai ba ne (ga waɗannan mutanen) su yi sujada a kan wani abu. Idan suka yi sujadar a kan wani abu, sallarsu ta inganta idan duƙawar da suka yi ta zarta wadda ya yi a ruku'u ƙwarai, sun aikata makaruhi, (saboda makaruhi ne yin sujada a kan wani abu da zai sanya wurin sujadar ya yi sama sosai.) Bai halatta a kwanta sosai a yi sallah da ishara ba, idan da hali a zauna a jingina (a kan wani abu). Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya ga wani marar lafiya yana sujada a kan matashi da yake gabansa; sai ya ɗauke matashin ya yi jifa da shi. Bayan nan sai mutumin ya sanya wani katako a gabansa. Sai fiyayyen halitta ya sake jifa da shi, sannan ya ce: "**Ka yi ta a ƙasa,** [wato, ya sanya goshinsa a ƙasa,]! **Idan ba za ka iya ba, ka yi ishara, ta hanyar tanƙwara (jikinka) domin yin sujada ya ɗara na ruku'u kaɗan!**" Kamar yadda aka faɗa a cikin littafin **Bahr-ur-raiƙ** (wanda Zaynal'abidin bin Ibrahim ibni Nujaym-i-Misri 'Allah ya yi masa rahama' ya rubuta, 926 – 970H. [1562 M.], Egypt, wanda sharhi ne na littafin **Kanz-ud-daƙaiƙ**, wanda Abul-barakat Hafidh-ud-din 'Abdullah bin Ahmad Nasafi 'rahmatullahi 'alaih' ya rubuta, d. 710H. [1310 M.], Baghdad), aya ta ɗari da cas'in da ɗaya ta suratul Al-i-Imran ta ce: "Duk wanda yake iya yin sallah daga tsaye. Wanda ba ya iya yi ya yi ta daga zaune. Da wanda ba ya iya yin duka, ya yi ta daga kwance." Yayin da Imran bin Husayn 'radiyallahu 'anh' ba shi da lafiya, Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya ce masa: "**Ka yi** (sallah) **daga tsaye! Idan ba za ka iya ba, ka yi ta a kwance kan gefe ko bayanka**." [Kamar yadda aka gani, marar lafiya wanda ba ya iya tsayuwa, ya yi sallarsa daga zaune. Wanda ba ya iya zama ko ta halin ƙaƙa, ya yi sallah daga kwance. Bai halatta ba ga mutum marar lafiya da yake iya zama a ƙasa, ko ga matafiyi da yake cikin babbar motar safa ko a jirgin sama ya yi sallah daga zaune a kan hannun kujera ko a kan kujerar yayin da ƙafafunsa suna reto a kan iska. Idan mutum ba ya iya yin sallah daga tsaye a cikin jam'i a Masallaci, sai ya yi ta a tsaye a gidansa. Akwai uzuri guda ishirin da idan

(daya daga ciki) ya auku, ya ɗauke wa mutum fita (zuwa masallaci) domin sallar jam'i, (wato, ya kange shi daga halartar sallar jam'i.) Waɗannan su ne dalilan da za su zamo uzuri ga mutum kar ya bar gidansa ya halarci sallar Juma'a: Ruwan sama; tsananin zafi ko sanyi; tsoron gamuwa da maƙiyi da zai iya kai maka hari ya raba ka da rayuwa ko dukiyarka; fargabar kar ayarinku na matafiya su tafi su bar ka; gari ya yi tsananin duhu; talaka da ake bi bashi idan ya yi fargabar za a iya kama shi a kulle; makanta; mutuwar jiki da ba a iya tafiya; mutum mai ƙafa ɗaya wanda aka yanke (masa ɗayar ƙafar); gurgu; taɓo; mutumin da ba ya iya tafiya; tsufa da ya hana tafiya; fargabar rasa darasi na Fiƙihu; fargabar rasa abincin da mutum yake so; Shirin fara doguwar tafiya; zamowa ƙwararren ma'aikacin kiwon lafiya wanda ya rasa wanda zai karɓe shi a wajen aiki; dare da ke ɗauke da guguwa mai ƙarfi; matsuwa ga yin fitsari; marar lafiya da yake fargabar tsanantar rashin lafiya ko tsawaita lokacin warkewarta ko ma'aikacin kiwon lafiya da yake fargabar babu wanda zai kula da marasa lafiya idan ya tafi; shiga tsanani yayin rashin lafiya saboda tsufa. Tafiya da ƙafa zuwa masallacin Juma'a ya fi falala fiye da zuwa a kan abin hawa. Bai halatta a yi sallah ta amfani da ishara zaune a kan kujera ko a hannun kujera a masallaci ba. **Bidi'a** ne yin aikin ibada ta hanyar da Musulunci bai koyar ba. Haka nan a rubuta a cikin litattafan Fiƙihu cewa aikata bidi'a babban zunubi ne.]

Mutumin da yake cikin tsananin rashin lafiya (wadda ba zai iya yin sallah ba) yana kallon Alƙibla, ya kalli duk inda ya samu ya yi sallar. Idan marar lafiyar yana kwance ne a kan gadon bayansa, sai a sanya masa wani abu (mai laushi) a ƙasan kansa ta yadda fuskarsa za ta kalli Alƙibla. Ya fi dacewa ya ɗago guyawunsa sama. Idan mutum (na cikin tsananin rashin lafiya) ta yadda ba zai iya yin ishara da kansa ba, ya halatta ya bar sallar ta zama ƙara'i (wato, ya dakatar da ita har lokacinta ya fita). Mutumin da ya kamu da rashin lafiya yayin da yake cikin sallah, ya cigaba idan zai iya. Idan marar lafiya mai sallah daga zaune ya samu sauƙi yayin da yake cikin sallah, sai ya cigaba da sallar daga tsaye. Mutumin da ya rasa hankalinsa ba zai yi sallah ba. Idan ya samu sauƙi kafin fitar lokacin salloli biyar, sai ya rama sallolin biyar. Idan lokacin sallah ta shida ya fita, ba zai rama sallah ko ɗaya ba.

Farilla ne a gaggauta yin ramuwar sallolin da suka kuɓuce masa daga lokacinsu, aƙalla ya rama sallar koda ta yin ishara ne. Idan mutum ya tsinci kansa mutuwa ta kusa riskar shi kafin ya samu damar rama sallolin, ba wajibi ba ne ya faɗa a cikin wasiyyarsa cewa a yi masa sadaka daga cikin dukiyarsa da ya bari ta isƙat ɗin sallolin da ake bin sa. Amma, ya zama wajibi idan har ya samu sauƙi gwargwadon lokacin da zai iya rama waɗannan sallolin. Idan

bai faɗa ba a wasiyyarsa, wasu Malamai sun ce, waliyyinsa ko wani mutum na daban yana iya amfani da dukiyarsa ya yi masa isƙat. Nan muka kawo ƙarshen bayanin da muka cirato daga littafin Ni'mat-i-islam.

An faɗa a ciki Hadisi cewa: **Akwai ayyuka ishirin da huɗu da suke kawo talauci ga mutum**:

1- Yin fitsarin tsaye ba tare da lalura ba. (Lalura na nufin wani yanayi da babu yadda mutum zai yi, da ya tilasta wa mutum aikata wani abu ko ƙin aikata wani abu).

2- Cin abinci yayin (da mutum ke cikin) **janaba**, (wato, lokacin da ya kamata a yi wanka).

3- Yin watsi da guntattakin biredi da tattaka su.

4- Kona albasa da tafarnuwa.

5- Tafiya a gaban manya (magabata)

6- Mutum ya kira iyaye da sunansu.

7- Mutum ya yi sakacen haƙora da tsinken icce ko na tsintsiya.

8- Mutum ya wanke hannuwansa da taɓo.

9- Zama a kan dokin ƙofa.

10- Yin alwala a inda mutum ya yi fitsari.

11- Zuba abinci a cikin tukunya ko kaskon da ba a wanke ba.

12- Ɗinke siturar da mutum yake sanye a jikinsa.

13- Cin albasa yayin da mutum yake jin yunwa.

14- Mace ta tsane fuska da bujenta.

15- Barin gizo-gizo a cikin gida.

16- Gaggauta ficewa daga Masallaci bayan kammala sallar Asuba (cikin jam'i).

17- Fita kasuwa da wuri da baro ta da dare.

18- Sayen biredi a hannun talaka.

19- Mutum ya zagi iyayensa.

20- Yin bacci tsirara.

21- Barin tukane da kasko a buɗe ba tare da an rufe su ba.

22- Hure wuta da ke ba da haske, kamar kyandir.

23- Yin dukkan al'amurra ba tare da yin "Bisimilla" ba.

24- Sanya situra daga tsaye.

Idan mutum ya karanta suratul Kauthar “**Inna a’ɗayna…,**” kafin ya kwanta bacci, sannan ya ce “Ya Rabbi (Ya Ubangiji)! Ka tashe ni a lokacin sallar Asuba ta gobe,” Bi-iznillahi ta’ala wannan mutumin zai farka a lokacin Sallar Asuba.

MUHIMMANCIN SALLAH

Littafin **Ashi’at-ul-lama’at** (wanda **‘Abd-ul-Haƙƙ bin Seyf-ud-din Dahlawi** ‘rahmatullahi alaih’ ya rubuta, 958H. [1551 M.] – 1052 [1642], Delhi) ya ƙunshi Hadisai daban-daban da suke bayani game da muhimmancin sallah. Littafin, sharhi ne da aka rubuta da harshen Farisanci na littafin Hadisi mai suna **Mishkat-ul-Masabih** (wanda Waliyy-ud-din Khatib-i-Tebrizi Muhammad bin ‘Abdullah ‘rahmatullahi ‘alaih’ ya rubuta, ya rasu 749H. [1348 M.] a matsayin sharhi da yabo ga littafin **Masabih** (wanda Imam Beghawi Huseyn bin Mes’ud Muhy-is-sunna ‘rahmatullahi ‘alaih’ ya rubuta, ya rasu 516H. [1122 M.]). Ashi’at-ul-lama’at littafin ne mai mujalladi huɗu. Bugu na tara na littafin ya fito ne a shekarar 1384H. [1964 M.] a Lucknow, Indiya.

Ana Kiran sallah ‘**salât**’ da harshen Larabci. Ma’anar **salât**’ na asali ita ce addu’a, rahmat (tausayi) da istighfar (neman gafarar Allâhu ta’âlâ). Saboda sallah ta haɗa waɗannan ma’anonin guda uku ya sa ake kiranta ‘**salât**’.

1- Abu Hurayra ‘radiyallahu ‘anh’ ya ruwaito Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Sallolin farilla biyar na yini da sallar Juma’a suna kankare zubnuban mutum wanda zai aikata har zuwa wata Juma’ar; azumin** (kwanaki talatin) **na watan Ramadan yana wanke zunuban da za a aikata har zuwa wani watan na Ramadan. Suna sanyawa a gafarta ƙananan zunubai idan mutum ya guji aikata manyan zunubai**.” Suna kankare ƙananan zunubai da aka aikata a tsakanin waɗannan lokuttan waɗanda ba su ƙunshi haƙƙin mutane ba. Musulmin da aka yafewa dukkan ƙananan zunubansu har ya zamo babu saura, za su (sallar Juma’a da azumin Ramadan) rage masu raɗaɗin azabar manyan zunuban da suka aikata. Manyan zunubai suna buƙatar yin tuba kafin a yafe wa mutum, (yana nufin mutum ya tuba daga zunuban da ya aikata, ya roƙi Allâhu ta’âlâ, tare da niyyar cewa ba zai koma ga aikata zunubin ba, sannan ya yi wa Allâhu ta’âlâ alƙawarin ba zai sake aikata saɓon ba.) Idan Musulmi bai aikata kowaɗanne irin manyan zunubai ba, to za ɗaga darajarsa. Wannan Hadisin yana cikin littafin **Sahih-i-Muslim**. Sallar Juma’a tana sanyawa a gafarta wa Musulmi wanda sallolinsa biyar na yini suke da tangarɗa. Idan sallolinsa na Juma’a suna da tangarɗa, to azuminsa na Ramadan zai jawo masu gafarar.

2- Abu Hurayra ‘radiyallahu ‘anh ya kuma ruwaito: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Misali a ce Akwai ƙorama da take gudana a ƙofar gidan mutum, yana wanka a cikin ƙoramar sau biyar a rana. Za a samu wani datti a jikinsa**?” Sahabbai suka amsa cewa “A’a ba za a samu datti a jikinsa ba ya Manzon Allah” sai Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ce: “**Haka lamarin yake ga salloli biyar na yini. Allah yana gafarta ƙananan zunubai ga Musulmin da suke yin salloli biyar na yini**.” Wannan Hadisin yana cikin **Sahihi-Bukhari** da kuma **Sahih-i-Muslim**.

3- Abdullahi ibni Mas’ud ‘radiyallahu ‘anh’ ya ce: Wani mutum ya sumbaci wata mata wadda ba muharramarsa ba. Abin da ya faru, wani daga cikin mutanen Madina yana sayar da dabino. Wata mata ta zo gare shi domin ta sayi dabino. Sai shaukin ƙaunar matar ya ɗebe shi. Ya ce mata “Ina da waɗanda suka fi waɗannan kyau a gida. Ki biyo ni in ba ki dabinon mai kyau.” Yayin da suka isa gidan nasa sai ya rungume matar kuma ya sumbace ta. Matar ta ce masa “Me kake yi haka? Ka ji tsoron Allah.” Sai ya tuba. Ya zo wajen Manon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya shaida masa abin da ya yi. Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ bai amsa masa ba, ya jira wahayi daga Allâhu ta’âlâ. Nan take mutumin ya yi sallah. Sai Allâhu ta’âlâ ya saukar da aya ta ɗari da goma sha huɗu ta suratul Hud (ga Annabi ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’). Ayar tana cewa: “**Ku yi sallah kodayaushe a ɓangarori biyu na yini da lokacin da dare ya shigo! Domin kyawawan ayyuka suna goge munanan ayyuka;…**” Ɓangarori biyu na yini su ne Safiya da maraice. Sallolin da ake nufi su ne sallolin Asuba da Azahar da La’asar. Sallolin shigowar dare su ne Magriba da Isha’i. Wannan ayar tana nuna cewa salloli biyar na yini suna sa a samu gafarar zunubai. Sai mutumin ya tambaya: “Ya Rasulallah (Manzon Allah)! Wannan labarin mai daɗi ya shafi ni kaɗai ne?” Annabi ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ce: “**Ya shafi dukkan al’ummata** (Musulmi).” Wannan Hadisin yana cikin litattafan ‘Sahih’ (wato, Sahih-i-Bukhari da Sahih-i-Muslim.)

4- Anas bin Malik ‘radiyallahu ‘anh’ ya ce: Wani mutum ya zo wajen Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ce: “Na aikata laifi da na cancanci a yi mani hukuncin haddi. Ka sa ayi mani bulalar haddi.” Manzon Allah bai tambaye shi laifin da ya aikata ba. Da lokacin sallah ya shiga, sai muka yi sallah tare. Bayan Manzon Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya kammala sallar, sai wannan mutumin ya miƙe ya ce: “Ya Rasulallah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’! Na aikata saɓo da na cancanci hukuncin haddi. Ka yi mani hukuncin da littafin Allâhu ta’âlâ ya shardanta!” Sai Annabi ya tambaye shi, “**Ka yi sallah tare da mu**” mutumin ya ce: “Eh na yi.” Sai babban masoyin Allah ya yi masa albishir: “**Kar ka yi baƙin ciki. Allâhu ta’âlâ ya yafe maka zunubin**.” Wannan Hadisin yana cikin mashahuran

litattafan Hadisai biyu. Cewa wani cikin Sahabbai ya aikata zunubin da ya cancanci haddi. Amma yafe masa da aka yi sakamakon sallar da ya yi, ya nuna cewa ƙaramin zunubi ne. Ko faɗar "haddi" da ya yi, yana nufin '**ta'zir**', wanda ake yi ga wanda ya aikata ƙaramin zunubi. Haka hukuncin yake tun da bai ce a yi masa haddi ba a karo na biyu.

5- Abdullah ibni Mas'ud 'radiyallahu 'anh' ya ce: na tambayi Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' wane aiki ne Allâhu ta'âlâ ya fi so. Sai fiyayyen halitta ya amsa mani da cewa: "**Sallah a kan lokacinta**." An faɗa a wasu Hadisai cewa, Allâhu ta'âlâ "**Ya fi son sallar da aka yi a farkon lokacinta**." Na tambaya wane aiki ne na biyu da Allâhu ta'âlâ ya fi so. "**Biyayya ga iyaye**" ya ce, na tambaya wane aiki ne na uku da Allâhu ta'âlâ ya fi so, sai masoyin Allâhu ta'âlâ ya amsa: "**Yin jihadi saboda Allah**." Shi ma wannan Hadisin yana cikin sahihan litattafai. An faɗa a cikin wani Hadisin: "**Aiki mafi soyuwa shi ne bayar da abincin dare**." A wani Hadisin kuma: "**Aikin da ya fi, shi ne yaɗa gaisuwa a tsakanin Musulmi**." (A duba babi na sittin da biyu na mujalladi na uku a littafin **Endless Bliss**.) A wani Hadisin kuma: "**Yin sallah cikin dare, lokacin da mutane ke bacci**." Har ila yau wani Hadisin ya ce: "**Aikin ibada mai tsada shi ne (ka kasance) babu wanda ya cutu daga hannunka**, (wato ɗabi'arka) **da Harshe**, (wato kalamanka)." A wani Hadisin: "**Jihadi shi mafi soyuwar ibada**." Wani Hadisin kuma ya ce: "**Mafi soyuwar ibada ita ce Hajj-i-mabrur**." Hajj-i-mabrur na nufin aikin hajjin da aka yi ba tare da an aikata wani zunubi ba. Wani Hadisin yana cewa, mafi tsadar aikin ibada shi ne "**Zikirin Allâhu ta'âlâ**." Wani Hadisin shi kuma ya ce shi ne "**Ibadar da aka dawwama ana yi**." An samu bambancin amsoshin nan ne saboda bambancin da aka samu na masu tambayoyin, da kuma yanayin da ake ciki. Ko bambancin lokacin yake kawo bambancin amsoshin. Misali, jihadi shi ya fi falala a farko-farkon yaɗuwar Musulunci. [A lokacinmu aikin da ya fi falala shi ne martani ga kafirai, da mutanen da suke kore Mazhaba, ta hanyar rubuce-rubuce da kafafen yaɗa labarai, da yaɗa koyarwar (Malaman) Ahl as-sunnat. Mutanen da suka goyi bayan wannan jihadin, da dukiya ko da ƙarfinsu, za su samu rabo a ladar da suka samu. Ayoyin Alƙur'ani da Hadisai sun nuna cewa sallah ta fi falala fiye da zakka ko kuma kowace irin sadaka. Abin da ya fi falala fiye da sallah shi ne, bayar da wani abu ga mutumin da ke gargarar mutuwa domin ceto rayuwarsa.]

6- Jabir bin Abdullah 'radiyallâhu 'anh' ya ce: Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' yana cewa: "**Abin da ya raba mutum da kufr** (kafirci) **shi ne barin sallah**." Domin sallah ita ce hijabin da ya kare mutum daga kafirci. Idan wannan hijabin ya kauce a tsakaninsu, bawa (mutum) zai afka cikin kafirci. Wannan Hadisin yana cikin **Sahih-i-Muslim**. Hadisin ya nuna

irin haɗarin da ke tattare da barin sallah. Mafi yawa daga cikin Sahabbai sun ce mutumin da ya bar sallah ba tare da uzuri ba, ya zama kafiri (kafir). Sai dai a Mazhabobin Shafi'iyya da Malikiyya, wannan mutumin bai zama kafiri ba, amma wajibi ne a kashe shi. A Mazhabar Hanafiyya, za a kulle shi a gidan fursuna a yi masa bulala, a cigaba da tsare shi a gidan fursuna har sai ya cigaba da sallah.

7- Ubada bin Thabit 'radiyallâhu 'anh' ya ruwaito: Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' yana cewa: "**Allâhu ta'âlâ ya yi umarni (gare mu) mu yi salloli biyar (a kowace rana). Idan mutum ya kyautata alwala ya yi su a kan lokacin tare da cikakkar nutsuwa a ruku'u da tsoron Allah, Allâhu ta'âlâ ya yi alƙawarin gafarta wa wannan mutumin. Bai yi alƙawarin haka ga waɗanda ba su aikata hakan ba. Zai iya gafarta masu ko ya azabtar da su, bisa ganin damarsa**." Wannan Hadisin Imam Ahmad, da Abu Dawud da Nisa'i suka ruwaito shi. Kamar yadda aka gani, wajibi ne a sanya nutsuwa a cikin sallah, a wajen ruku'u da sujada. Allâhu ta'âlâ ba ya saɓa alƙawarinsa. Tabbas zai gafarta wa Musulmin da suka yi sallah yadda ya dace.

8- Abu Emama-i-Bahili 'radiyallâhu 'anh' ya ce: Manzon Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' ya ɗaɗa cewa "**Ku yi sallah sau biyar (kowace rana)! Ku yi azumi a wata ɗaya (na Ramadan)! Ku fitar da zakka daga dukiyarku! Ku yi biyayya ga shugabanninku. Za ku shiga dausayin Ubangijinku**." Kamar yadda aka gani, Musulmin da ya yi salloli biyar na yini, ya yi azumin watan Ramadan, ya kuma fitar da zakka daga dukiyarsa, ya yi ɗa'a ga umarni da shugabannin waɗan suke halifofin Allah a doron ƙasa, za su shiga Aljanna. Wannan Hadisin Imam Ahmad da Tirmuzi suka ruwaito shi.

9- Burayda-i-Aslami 'radiyallâhu 'anh' ɗaya daga cikin manyan sahabbai, ya ruwaito: Manzon Allah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yana cewa: "**Sallah ita ce alƙawarin da ke tsaninmu da ku. Duk wanda ya bar sallah ya kafirta**." Kamar yadda aka gani, mutumin da yake sallah ya riƙe alƙawarin zama Musulmi. Idan mutum bai bayar da muhimmanci a kan sallah ba, kuma ya zamo ba ya yin sallah saboda bai yarda cewa ita ce ginshiƙin ibada ba, to ya zama kafir (kafiri). Wannan Hadisin Imam Ahmad da Tirmizi da Nisai da Ibni Majah (huɗu daga cikin manyan Malaman Hadisi) suka ruwaito shi.

10- Abu Zar-i-Ghifari 'radiyAllâhu ta'âlâ 'anh' ya ce: A wani lokacin kaka, na fita tare da Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam'. Ganyayyaki suna faɗowa daga kan itatuwa. Sai ya ɗauke biyu daga cikin gayyakin na wani icce waɗanda suka faɗo tare. Sai ya ce "**Ya Aba Zar! Idan Musulmi ya**

yi sallah domin neman yardar Allah, dukkan zunubansa za su kakkaɓe kamar yadda ganyayyakin nan suke zuba daga rassan nan.” Wannan Hadisin Imam Ahmad ne ya ruwaito shi.

11- Zayd bin Khalid Juhemi ya ce: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Idan Musulmi ya yi sallah raka’a biyu yadda ya dace tare da khushu’ za a gafarta masa zunuban da ya aikata a baya**.” Wato, za a gafarta masa ƙananan zunubansa. Wannan Hadisin Imam Ahmad ‘rahima-hullahu ta’ala’ ya ruwaito shi.

12- Abdullahi bin ‘Amr ibni ‘As ‘radiyallâhu ta’âlâ ‘anhuma’ ya ce: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Idan mutum ya yi sallah, wannan sallar za ta zama nur** (haske) **da burhan** (hujja) **ta sanya ya samu rahama. Idan bai tsaida sallah ba, ba za ta zamo nur da burhan ba, kuma ba zai samu rahama ba. Za a sanya shi tare da Karun da Fir’aun, haka nan da Haman da Ubayy bin Khalef**.” Kamar yadda aka gani, idan Musulmi ya yi sallah tare da kulawa a kan fards da wajib da sunnat da adabs, wannan sallar za ta sanya masu haske a ranar tashin Kiyama. Idan ba su yi sallah a kan wannan tsarin ba, za su tashi tare da kafirai a ranar tashin Kiyama. Za su fuskanci azabar wuta. Ubayy bin Khalef yana daga cikin manyan kafiran Makka. A yaƙin Uhud, Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya aika shi wutar jahannama da hannunsa. Wannan Hadisin, Imam Ahmad da Imam Bayhaƙi da Darimi (‘Abdullah bin ‘Abd-ur-Rahman Hafid Abu Muhammad) suka ruwaito shi.

13- ‘Abdullahi bin Shaƙiƙ ‘rahima-hullahu ta’ala’ ɗaya daga cikin manyan Tabi’in, ya ce: “Sahabbai ‘radiyallahu ‘anhum’ sun ce, a dukkan ayyukan ibada, sallah kaɗai ce ke sa wanda ba ya yin ta ya zama kafiri (maƙiyin Allah),” (Muhammad bin Isa) Tirmuzi ‘rahmatullahi ‘alaih’ ya inganta wannan bayanin, ‘Abdullah bin Shaƙiƙ ya ruwaito Hadisin daga (Sahabbai da suka ƙunshi) ‘Umar da ‘Ali da Uthman da kuma Aisha ‘radiyllahu ‘anhum’. Ya rasu a shekara ta ɗari da takwas bayan Hijira.

14- An karɓo daga Abu-d-darda ‘radiyallahu ‘anh’ ya ce: Masoyin da na fi ƙauna ya ce mani: “**Ko da za a datsa ka gunduwa-gunduwa ko a ƙona ka a wuta, kar ka taɓa haɗa Allâhu ta’âlâ da wani wajen bauta! Kada ka bar sallar farilla! Duk mutumin da ya bar sallar farilla ya fita daga addininsa. Kar ka sha giya, giya ita ce mabuɗin dukkan sharri**.” Kamar yadda aka gani, mutumin da ya bar sallah da gangan ya zama kafiri. Mutumin da ya bar ta saboda ragganci bai zama kafiri ba, sai dai ya aikata mummunan saɓo. Ba laifi ba ne idan mutum ya gaza yin ta saboda dalili na ɗaya daga cikin uzuri biyar da Musulunci ya yarda da su. Giya da makamantanta suna fitar da

mutum daga hankalinsa. Mutumin da hankalinsa ya gushe zai iya aikata kowane irin mugun aiki.

15- ‘Ali ‘radiyallahu ‘anh’ ya ce: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Ya ‘Ali! Akwai abubuwa uku, kada ka kuskura ka jinkirta yin su: Idan lokacin sallah ya yi, ka gaggauta yin wannan sallar! Idan an shirya janaza** (Musulmin da ya rasu wanda za a binne) **ka gaggauta yi masa sallar janaza! Idan ka samar wa diyarka miji, ka gaggauta yi mata aure!**” Ana yin sallar janaza ko da lokutta uku ne da aka karhanta yin sallah. (lokuttan uku ana kiransu ‘Kharahat’ wadanda aka yi bayaninsu a kashi na ƙarshe na babi na goma a mujalladi na hudu na littafin **Endless Bliss**).

[Kamar yadda aka gani, wajibi ne a aurar da mace ko yarinya ga kufw, wato mijin da ya dace da ita. Zama kufw ba yana nufin zama mawadaci ba, ko mai karɓar albashi mai ƙarfi ba. Zama kufw na nufin namiji ya zamo Musulmin ƙwarai, ya zamo yana koyi da Ahl as-sunnat, yana salloli biyar na yini, wanda ba ya shan giya, wato mai yin ɗa’a ga koyarwar Musulunci, ya zamo yana samun abin da zai isa nafaƙa; (wato, ya kasance yana iya riƙe iyali). Iyayen da ke auna mazan aure da dukiyar da suke da ita da gidan zama, za su jefa ‘ya’yansu mata cikin halaka da fadà wa cikin wuta. Haka nan wajibi ne yarinyar ta zamo tana salloli (biyar na yini), kar ta fita waje kanta da cinyar hannunta a buɗe, kuma kada ta keɓe tare da wanda ba muharraminta ba, ko da ɗan uwantane na jini.]

16- an karɓo daga ‘Abdullahi ibni ‘Umar ‘radiyallahu ‘anhuma’ cewa: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ce: “**Allâhu ta’âlâ yana farin ciki da mutanen da suke yin sallah da zarar lokacinta ya shiga. Kuma Yana yafe wa wadanda suka yi ta a farkon lokacinta**.” Tirmuzi ‘rahimah-hullahu ta’ala’ ya ruwato wannan Hadisin.

A Mazhabobin Shafi’iyya da Hambaliyya, ya fi falala a yi kowace sallah a farkon lokacinta. Mazhabar Malikiyya ta yarda da haka. Amma a lokacin tsananin zafi, ya fi dacewa ga mai yin sallah shi kadai ya jinkirta sallar Azahar. A Mazhabar Hanafiyya, ya fi falala a jinkirta sallolin Asuba da Isha’i, a yi sallar Azahar idan rana ta yi sanyi a watannin yanayin zafi. [Yana da kyau da taka tsantsan a yi sallar Azahar kafin lokacin sallar La’asar ya shiga, inji Tarafeyn, da yin sallar La’asar da sallar Magriba da Isha’i da zarar lokuttansu sun shiga inji Imam A’zam Abu Hanifa. (Domin ƙarin bayani game da lokuttan sallah, a duba babi na goma a mujalladi na hudu na littafin **Endless Bliss**). Mutane masu taƙwa (tsoron Allah) suna taka tsantsan a kan dukkan abin da suke aikatawa.]

17- Umm-i-Farwa ‘radiyallahu ‘anha’ ta ce: an tambayi Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ wane aiki ne ya fi falala? Sai ya ce: “**Aikin da**

ya fi falala shi ne sallah a farkon lokacinta.' Imam Ahmad da Tirmuzi da Abu Dawud 'rahima-humullahu ta'ala suka ruwaito shi. Falalar ta fi kauri idan aka yi ta da zarar lokacinta ya shiga.

18- Aisha 'radiyallahu 'anha' ta ce "Ban ga Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya yi sallah a ƙarshen lokacinta sau biyu ba."

19- Umm-i-Habiba 'radiyallahu 'anha' ta ce: Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yana cewa: "**Idan bawan** (Allah) **Musulmi ya yi raka'o'i goma sha biyu na sallolin taɗawwu'i baya ga sallolin farilla na yini, Allâhu ta'âlâ zai gina mashi katafaren gida a Aljanna**." Wannan Hadisin yana cikin **Sahi-i-Muslim**. Kamar yadda aka gani, Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya kira sallolin da ake yi tare da sallolin farilla na yini da **taɗawwu'i**, wanda ke nufin sallolin nafila.

20- 'Abdullah bn Shaƙiƙ 'rahima-hullahu ta'ala' ɗaya daga cikin manyan Tabi'in: na tambayi Aisha 'radiyallahu 'anha' game da sallolin **taɗawwu'i** wato sallolin nafila na Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam'. Sai uwar Muminai ta ce: "Yana yi raka'o'i huɗu kafin sallar Azahar, da raka'a biyu bayanta (wato bayan sallar farillar) da raka'a biyu bayan sallar Magriba, da raka'a biyu bayan sallar Isha'i, da raka'a biyu kafin sallar Asuba. An cirato wannan bayanin ne daga Muslim da Abu Dawud 'rahima-hullahu ta'ala'.

21- Aisha 'radiyallahu 'anha' ta ce: "A cikin ayyukan nafila, sallar nafila kafin sallar Asuba ita ce wadda Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' ya fi aikatawa kodayaushe." Wannan riwayar tana cikin (Sahih-i-) **Bukhari** da (Sahih-i-) **Muslim**. A nan Aisha radiyallahu 'anha' ta kira sallolin sunnah da ake yi tare da sallolin farilla biyar da 'salloli nafila'.

[Imam Rabbani mujaddid-i-alf-i-thani Ahmad bin 'Abd-ul-Ahad Faruƙi Serhendi 'ramatullahii 'alaih', babban malamin Musulunci, kuma gwarzon Ahl as-sunnat wajen yaƙi da mummunar aƙida da marasa Mazhaba, babban Mujaddadi wanda ya yaɗa Addinin Allâhu ta'âlâ da yaƙi da bidi'a, ya faɗa cewa a cikin babi na 29 na mujalladi na farko na littafinsa mai suna **Muktubat**, irin abin da ba a rubuta ba a Addinin Musulunci:

Ayyukan ibada da Allâhu ta'âlâ yake so, su ne ayyukan da suke farilla da waɗanda suke nafila. Nafilolin ba a bakin komai suke ba idan aka kwatanta su da farillai. Yin sallar farilla guda ɗaya a kan lokacinta ya fi yin sallar nafila ta tsawon shekaru dubu ɗaya. Wannan hukuncin ya shafi dukkan ayyukan ibada na nafila, misali zakka da azumi da umara da Hajji da zikiri da fikr (lazimi). Batun gaskiya, idan mutum yana sallah ta farillah, ya aikata sunnoninta da adab ɗinta, ya fi falala akan aikata sauran nafiloli. Wata rana Amir-ul-mu'uminin 'Umar-ul-Faruƙ radiyallahu ya jagoranci sallar Asuba a

cikin jam'i, sai ya lura cewa bai ga ɗaya daga cikin mutanen da ya sani ba, sai ya tambaya (Musulmin da suke nan) ko me ya sa wannan mutumin bai zo ba. Sai suka ce "Yana sallolin nafila kowane dare. Kila bacci ya ɗauke shi ya gaza zuwa nan domin sallah a cikin jam'i." sai Khalifa ya ce: "Ya fi masa a ce ya yi bacci baki ɗayan dare, amma ya halarci sallar Asuba a cikin jam'i." Kamar yadda aka gani, idan mutum ya yi ibada ta farilla, (misali, farillan salloli biyar na yini) aikata adab (mandubanta) ko guje wa makaruhanta ya kai falalar aikata cikakkar ibada (ta nafila) kamar zikiri da lazimi da murakaba. Gaskiya ne cewa ayyukan ibada na nafila da ake magana, suna da amfani matuka idan aka yi su bayan an aikata mandubai da guje wa aikata makaruhai. Amma ba su da kyau idan aka yi su ba tare da karin ba. Haka nan bayar da kudin (Turkiyya) lira ɗaya a matsayin zakka (wadda farilla ce ga Musulmi, kamar yadda aka yi cikakken bayani a babi na farko a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss**,) ya fi bayar da dubban kudin lira a matsayin sadaka, wadda take nafila ce. Babu shakka aikata ɗaya daga cikin manduban (zakka) kamar yadda aka bayar da wancan kudin na lira, wato bayar da ita ga ɗan uwa[1] makusancinka, ya fi aikata ayyukan nafila. [Don haka mutanen da suke son aikata sallolin dare (waɗanda ake kira tahajjud su tabbata sun rama sallolin farilla da ake binsu. Umarnin Allâhu ta'âlâ su ake kira **fard**, haninsa kuma su ake kira **haram**. Horon Annabinmu su ake kira **sunnoni**, gargaɗinsa kuma ana kiran su **makruh**. Dukkan waɗannan a dunkule su ake kira **Ahkam-i-islamiyya**. Farilla ne riko da kyawawan ɗabi'u da kyautata wa jama'a. Mutumin da ya musanta ko ya kore ɗaya daga cikin ginshikan Ahkam-i-islamiyya ya zama **kafiri (kafir)**, kuma ya yi **ridda (murtadd)**. Mutumin da ya yarda da dukkan Ahkam-i-islamiyya a dunkule, shi ake kira **Musulmi**. Musulmin da ya bijire wa Ahkam-i-islamiyya saboda kasala ya zama **fasiki**. Fasikin Musulmi da bijire wa ɗaya daga cikin umarni ko ya aikata abin da aka yi hani zai shiga Wuta. Ba za a karɓi dukkan kyawawan da sunnonin da fasikin Musulmi ya aikata ba, kuma ba za a ba shi lada ba. Idan mutum bai fitar da zakka ba, ko da kudin lita ɗaya (na Turkiyya) ne, ba za a karɓi ayyukansa na bayar da tallafi ko sadaka ba. Ba za a ba shi lada ba ga ayyukansa na gina masallatai da makarantu da asibitoci da ya yi ba, ko wani tallafi ga kungiyoyin jin kai ba. Ba za a karɓi sallar Tarawih ta mutumin da bai yi sallar Isha'i ba. Ayyukan ibada waɗanda ba na farilla ko wajibi ba, ana kiran su **nafila**. Sunnoni ayyukan ibada ne na nafila. Karin haske a kan wannan ma'anar, mutumin da ya rama sallar da ake binsa, zai iya yin sallar nafila ita ma. Ladar (da za a samu) ta aikata farilla, ko guje wa haram, ta fi

[1] Anan ɗan uwa makusanci ba shi kaɗai ne zaka taimakawa ba, kamar mata, 'ya'ya da kuma iyaye.

ladar da za a samu ta aikata ayyukan nafila. Mutumin da ya bar farilla, ko ya aikata haram, zai shiga wutar Jahannama. Ayyukansu na nafila ba za su iya kare su daga shiga wuta ba. Sauyin da aka kawo ga ayyukan ibada su ake kira **bid'at**. Harramun ne yin bidi'a yayin aikata ibada, kuma zai ɓata wannan aikin na ibada. [A duba babin da ya yi magana a kan kiran sallah!] An faɗa a cikin wani Hadisi cewa: "**Ba za a karɓi dukkan ibadar mutumin da ya aikata bidi'a ba**. Idan mutum ya zamo fasiƙi; misali, idan matarsa da ɗiyarsa suka fita ba tare da rufe jikinsu yadda ya kamata ba, ko ya aikata bidi'a, misali, idan ya yi amfani da lasifika wajen aikin ibada, kada a bi shi sallah; (wato, kada mutum ya bi sallar jam'in da wannan mutumin yake jagoranta;) ba za a saurari jawabansa ba ko a karanta litattafansa ba. Sai dai wajibi ne ka yi mu'amala da kowa da murmushi, aboki ko maƙiyi, da tausasa harshe wajen yi masu magana; kar ka yi jayayya da kowa. An faɗa a cikin wani Hadisi cewa: "**Ba a mayar da martani ga wawaye**." Ibada tana ƙara tsarkake zuciya. Saɓo yana sanya duhu a zuciya, ta yadda ba za ta riƙa samun haske ba. Farilla ne ga kowane Musulmi ya san rukunan imani da farillai da haram. Rashin saninsu ba uzuri ba ne. hakan daidai yake da cewa mutum ba ya aikata wa bayan ya riga ya san su.] Littafin **Maktubat** a harshen Larabci. A nan fassarar littafin ta ƙare. Hadrat Imam Rabbani ya rasu a birnin Serhend na ƙasar Indiya a shekarar 1034H. [1624 M.].Bisa abin da aka fahimta daga abin da aka rubuta a baya, sunnonin da ake yi na sallolin farilla biyar na yini suna daga cikin sallolin nafila. Saboda ana yin su tare da sallolin farillar, domin cike giɓin da aka bari a sallolin farillar, sun fi sauran nafilfili falala. Musulmin da bai yi sallah a kan lokacinta ba, ba tare da (wani dalili mai ƙarfi ba) uzuri ba, amma ya ɗauki sallar da muhimmanci, kuma babbar ibada a gare shi, ya aikata babban saɓo. Zai kasance tare da Fir'auna da Hamana a cikin wuta. Sallolin nafila, wato, sunnonin (da ake yi tare da sallolin farilla) ba za su ceto mutum daga wannan mummunan saɓon da kuma azabar da za a yi masa ba. Don haka farilla ne ya rama wannan sallar ta farilla. Saɓo ne mai girma jinkirta ramuwar sallar. Abin zai cigaba da ƙaruwa, don haka duk wani zunubi mai ƙaruwa ya wajibi ne a dakatar da shi. Tun da ya kasance farilla ne ramuwar salloli, yin ta ya ruɓanya sallolin nafila da dubban lada. Don haka, tun da ya halatta a bar sallar nafila saboda wani uzuri, dukkan Musulmi wajibi ne a gare shi ya rama sallolin farlla waɗanda bai yi ba, ba tare da wani uzuri ba, maimakon yin nafila a lokacin sauran sallolin yini guda huɗu. Saboda akwai Malaman Musulunci da suka ce sallar nafila ta lokacin sallar Asuba wajibi ce, ba za a yi ramuwar sallah ba maimakonta. Don haka sai su kawar da manyan zunubai cikin gaugawa ta hanyar rama sallolinsu a kodayaushe. Idan aka kammala ramuwar dukkan sallolin, sai a cigaba da sallolin nafila na lokacin sallolin farilla biyar. Domin ƙaramin zunubi ne

mutum ya ƙi aikata sallolin sunnah ba tare da uzuri ba (mutum ya ƙi aikata su bisa ƙashin kansa). Haka nan mutumin da ya wulaƙanta sunnah, ya zama kafiri.

Duk da cewa farilla ne a gaggauta rama sallah (farilla) da ta kuɓuce, wato wadanda mutum ya rasa sakamakon wani uzuri, amma Malaman Mazhabar Hanafiyya sun ce, ya halatta a jinkirta ramuwar har sai mutum ya yi nafila (ta lokuttan salloli biyar na yini), tun da ba laifi ba ne mutum ya gaza yin sallah a kan lokacinta saboda uzuri. Amma wannan hukuncin nasu ba ya nufin ya halatta a jinkirta ramuwar sallar da ta kuɓuce ba tare da uzuri ba. Domin cewa 'ya hallata' ba ya nufin 'wajibi' ko 'yana da kyau'. Akwai ayyuka da dama wadanda suka 'halatta' a lokaci guda kuma 'makaruhi' ne. Misali, ya halatta a bayar da **sadaƙa-i-fitr** ga dhimmi kafiri, amma makaruhi ne yin hakan. (A duba babi na uku a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss** game da sadaƙa-i-fitr. *Dhimmi na nufin mutumin da ba Musulmi ba wanda yake zama a kasar Musulmi).*

Ka yi sallah, kuma kar ka bar hannuwanka su taɓa haram;
Kar ka tsammaci rayuwa mai tsawo, ko kuma duniya marar iyaka!
Ka yi riƙo ƙwarai da sallolin nan guda biyar, tun kana da ƙuruciya,
Abin da ka shuka a nan, za ka tsince shi a gobe lahira.

Mutane biyu ba sa taɓa tuna mutuwa ba:
Mai aikata haram, ɗa kuma mai barin sallah!
Wata rana hannuwan nan ba za su iya yin komai ba;
Da harshen da ba ya faɗar "Allah" zai gaza furtawa!

FITAR DA ZAKKA

Hujjoji a cikin nassi da ke tabbatar da (fitar da) zakka farilla ce su ne, aya ta arba'in da uku da aya ta ɗari da goma na suratul Baƙara.

Akwai mutane goma sha biyu da ba su halatta a ba su zakka ba:

Mutum mahaukaci; akan sayen likkafani ga mamaci; kafiri (wanda ba Musulmi ba); attajiri; usul na mutum (iyaye da kakanni) da furu' ('ya'ya da jikoki); matar mutum; bayin mutum; mukataba na mutum [bawan da aka bayar da fansarsa a kan wani farashi]; mudabbera na mutum [wato bawan da ke jiran 'yanci idan mamallakinsa ya mutu]. Game da mata ta bai wa mijinta zakka; batu ne da (Malaman Musulunci) suka tattauna, amma bai kamata ba.

Idan mutum ya yi zaton wani mutum ba ɗan uwansa ba ne, amma sai ya kasance ma ɗa ne a gare shi, ko kuma ya zamo ba Musulmi ba, amma kai ka

yi zaton Musulmi ne; wadannan mutane ba su cancanci a ba su zakka ba; amma idan ka bai wa daya daga cikinsu zakka bisa rashin sani, zance mafi dacewa, ba dole ba ne ka sake bayar da wata zakkar ba a madadinta.

Ga adadin mutane takwas da suka cancanci a ba su zakka:

1- Mutum wanda yake 'miskin' a Musulunci. (Musulmin da yake iya ciyar da kansa yini daya kadai shi ake kira 'miskin';)

2- Musulmi talaka, wanda dukiyarsa ba ta kai nisab (nisabin) Kurban ba. (nisab na nufin iyakar da ke tsakanin arziki da talauci a Musulunci. Nisabin Kurban da na sadaka ta musamman da ake kira fitra ya sha bamban da na zakka. A duba babi na 1, 3 da na 4 na mujalladi na biyar na littafin Endless Bliss domin karin bayani;)

3- Musulmin da ake binsa bashi.

4- Musulmin da aka dora wa alhakin karbo dukiyar zakka da 'udhr (kudaden albashi);

5- Musulmin da ya zamo talaka a wani wuri, amma yake da dukiya a gida;

6- Musulmin da ya zama talaka a kan hanyar zuwa jihadi ko aikin hajji;

7- Bawan da zai biya mamallakinsa adadin wasu kudade domin ya 'yanta shi.

8- Mutumin da ba Musulmi ba wanda ake kira muallafa-i-kulub, wadanda babu su a yanzu.

Mutumin da ya mallaki dukiyar da za ta ishe shi fiye da kwana daya, amma ba ta kai nisabi ba, shi ake kira 'talaka' (a Musulunci). Dukkan ma'aikacin gwamnati da yake shan wahala wajen kula da iyalansa, komi yawan albashinsa, ya cancanci a ba shi zakka, kuma ba sai ya yi Kurban ba ko ya biya Fitra. Musulmin da yake koyarwa ko yake neman ilimin addini ya cancanci a ba shi zakka, ko da yana da dukiyar da za ta ishe shi rayuwa tsawon shekaru arba'in. Ba a amfani da kudaden zakka wajen gina masallaci ko jihadi ko kuma sayen likafani ga Musulmin da ya rasu. Bai kamata a bayar da zakka ga karamin yaro dan attajiri, ko ga iyayen mutum ko 'ya'yansa ko kuma matarsa. Ta fi lada a bai wa 'yan uwanka, matan 'ya'yanka da mazajen 'ya'yanka da mahaifiyar matarka da mahaifin matarka, da 'yan uwan mahaifi maza da mata, da 'yan uwan mahaifiya maza da mata. Za a ba wa talaka Musulmi dukiya kasa da nisabi. Amma, idan yana da mata da 'ya'ya, za a iya ba shi dukiyar fiye (da nisabi) idan ya zamanto babu wani daga cikin 'yan uwa da aka bai wa fiye da nisabin. Bai kamata a bayar da zakka ga mutumin da ya wulakanta dukiyarsa ko ya kashe ta bisa hanyar haram. Za a iya bai wa shugabanni zakka tun da ba za su iya samun kasonsu daga ganima ba. (A

duba ‘Bayt-ul-mal’ a ƙarshen babi na ɗaya na mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss**).

Akwai sharuɗɗa guda shida da suka kamata mutum ya cika domin zama farilla a gare shi ya bayar da zakka:

1- Ya zama Musulmi.

2- Ya zama ya kai shekarun balaga.

3- Ya zama ya kai shekarun hankali da zai iya yanke wa kansa hukuncin.

4- Ya zamo mai ‘yanci.

5- Ya zamo dukiyarsa da zai fitar da zakka ta halal ce, ta kuma kai nisabin zakka.

6- Dukiyar da yake da ita ta zamo ta wuce buƙatunsa da basussukan da ake bin sa.

Idan mutum bai fitar da zakka ba ya bai wa mabuƙata ba, bayan cewa zakkar ta zamo farilla a kansa, daidai yake da wanda ake bi bashi, don haka ayyukansa na taimako da suka ƙunshi bayar da gudunmuwa da sadaka, baya ga cewa ba su da lada, suna jawo masa zunubi. Farilla ne gare shi ya fitar da zakka, ko ya biya bashi, idan akwai. Kamar yadda aka rubuta a shafi na ɗari shida da talatin da biyar (635) a mujalladi na biyu na littafin **Hadiƙa** da shafi na dubu ɗaya da ɗari uku da sittin da tara (1369) a littafin **Bariƙa**, bai halatta ba a [bayar da zakka a kuma] bayar da sadaka ga mutanen da suke kashe kuɗaɗensu a wuraren da suke haram, ko waɗanda suke wulaƙanta kuɗaɗensu. Saboda haramun ne ka goyi bayan wani abu da yake haram.]

Bai kamata ba a ce wanda ya bayar da zakka kuma ya amfana da ita. Idan miji ko mata suka bayar da zakka ga daya daga cikinsu, wanda ya bayar ba zai iya hana ya amfana da ita baki ɗaya ba. Kamar kowane aiki na ibada, yin niyyat (niyya) wajibi ne a wajen fitar da zakka. Dukiyar zakka dole ne ta zamo ta ɗara bashin da ake binsa, da kuma **hajat-i-asliyya** (Buƙatu) na mutum, sannan ya zamo abin da ya ɗara na dukiyar, ya zamo ya kai **adadin nisabi**. (Adadin) nisabi na zinare shi ne mithƙal 20, [wanda yake daidai da nauyin giram 96 ko kwabban zinare 13.3.] Nisabin azurfa shi ne dirhami 200 [nauyin giram 672]. Kafin zakka ta zamo farilla ga mutum ya fitar, sai dukiyar zakkar ta zamo a hannunsa tsawon shekarar hijri (hijira) ɗaya. Imam Muhammad ya ce, makaruhi ne yin (dabara ta shari’a da ake kira) hila-i-shar’iyya kafin ƙarewar shekarar (hijri) don guje wa zakkar ta zamo farilla. Ba makaruhi ba ne in ji Imam Abu Yusuf. A misali: Idan ta zamo farilla, to saɓo ƙin fitar da ita. Kuma **ɗa’at** ne guje wa aikata saɓo. Fatwa ta yarda da ƙaulin Imam Muhammad. (Fatwa kakkyawan bayani ne, inda Malamin da aka amince da shi zai riƙa amsa tambayoyin Musulmi. Ana bayar da hujjojin

fatwa tare da ita. An yi bayanin sharuɗɗan da za a cika domin zama amintaccen Malami a cikin litattafanmu **Belief and Islam, The Sunni Path** da **Endless Bliss** [babi na 33 a mujalladi na biyu da babi na goma a mujalladi na uku]).

Dukiyar zakka na nufin dukiyar da ta ƙaru, ta ruɓanya. Dukiyar zakka iri huɗu ce: Dabbobi masu ƙafa huɗu waɗanda suke kiwo a fili tsawon fiye da rabin shekara a tattare wuri ɗaya, na matan dabbobi, kuma waɗanda ake kira **saima**; dukiyar da ake saye da sayarwa na kasuwanci; zinare da azurfa; kayan abinci da aka noma. Masu dabbobi maza kaɗai, ko jakai, ko alfadarai da suke kiwo a fili, ba sa buƙatar fitar da zakka; wato zakka ba ta zama farilla a kansu ba. Idan ƙananan dabbobi irin su raƙuma da shanu da tumaki, suna tare da manyansu, ana sanya su cikin lissafin zakka. A madadin dukiyar da za a bayar a matsayin zakka da ‘ushr da kaffara (wanda aka yi cikakken bayani a babi na shida na mujalladi na biyar, da kuma babi na goma sha uku a mujalladi na shida na littafin **Endless Bliss**) da sadakar fitr, za a iya bayar da wani abu da suke da daraja ɗaya. A Mazhabar Shafi’iyya, bai halatta ba a yi hakan. Idan dukiyar mutum ta ƙare bayan fitar da zakka ya zamo farilla a kansa, ta tashi daga zama farilla; (wato, ta zamo ba farilla a kansa ba. Ba ta faɗi a kansa ba idan ya bayar da dukiyar tasa; (wato dole ne ya fitar da zakkar dukiyar).

Shekara ɗaya (ta Miladiyya) bayan dukiyar Musulmi nagari ta zakka ta kai adadin nisabi, idan ita ce cikakkiyar dukiyarsa kuma ya same ta hanyar da take halal, ya zama farilla gare shi ya fitar da wani adadi daga cikin dukiyar ya bayar ga ɗaya daga cikin mutanen nan takwas; wannan bayarwar (ta dole) shi ake kira zakka. Mutumin da za a bai wa zakkar wajibi ne ya zama Musulmi. Cikakkiyar dukiyar mutum ita aka yarda kuma ya halatta ya yi amfani da ita. Dukiyar da mutum ya saya ta zama dukiyarsa da zarar an ƙulla yarjejeniya; amma ba ta zama cikakkiyar dukiyarsa ba kafin ta shiga hannunsa, domin ba zai iya amfani da ita ba a lokacin. Dukiyar da aka samu ta hanyar ƙeta ko zalunci ko aka ƙwata da ƙarfi ko sata, ko ta riba ko cin hanci, ko ta hanyar caca ko aka same ta a hanyar kaɗe-kaɗe da waƙe-waƙe, ko sayar da kayan maye, ana kiran ta **dukiyar khabith**. Ba a fitar da zakka a dukiyar khabith. Domin wannan dukiyar ba ikonka ba ce); (wato, ba dukiyarka ba ce). Wajibi ne a mayar ga masu ita, ko ga magadan masu ita idan sun mutu, idan babu magada, sai a bai wa mabuƙata a cikin Musulmi. Idan dukiyar (da aka samu a ɗaya daga cikin hanyoyin haram da aka lissafa) aka cakuɗa ta da wata dukiya ta haram, ko da dukiyar mutum ta halal, sun zamo ƙarƙashin ikonsa, (wato, sun zamo nashi) amma wannan karon ta zama **mulk-i-habith** (dukiyar khabith), wadda haramun ce ya bai wa wani ya yi kowane irin amfani da ita, kuma ba za a fitar da zakka ba a cikinta domin ba

ka da cikakken iko a kanta. Idan ka biya diyya ga masu dukiyar da dukiyar zakkarka ta halal da mithl (makamanci) na dukiyar ta khabith, ko da gwargwadon darajarta idan babu mithl, ya halatta gare ka a kan ka yi amfani da mulk-i-khabith sai ka ƙara lissafinka na nisabi. Idan ba ka da wadatar dukiyar halal da za ka biya wannan bashin, sai ka ranto ka biya su (daga wani makusancinka). Amma haramun ne yin amfani da mulk-i-khabith ko bayar da ita ga wani; idan ka sayar ko ka bayar kyauta, ba za ta zamo haramun ba ga wanda ya saya da wanda aka bai wa kyautar. Idan ba a san mai ita ba ko magadansa ba, ko an cakuɗa dukiyar da aka karɓa daga hannun mutane daban-daban, don haka suka zamo mulk-i-khabith, sai a rabar da ita matsayin sadaka ga mabuƙatan Musulmi.

Idan mabuƙata a cikin Musulmi suka mayar da sadakar dukiyar da aka ba su a matsayin kyauta, to ya halatta wannan mutumin da ya bayar da ita ya sake karɓa.

Ba a yin amfani da ɗanyen zinare da azurfa. Idan ya zamana fiye da rabinsu ɗanye ne, wajibi ne a fitar masu da zakka, kuma za a yi amfani da nauyinsu wajen lissafinsu. Idan ya zamo akwai iri biyu a kasuwa kuma ana amfani da su a matsayin ababen kuɗi, wanda ya fi kyau shi ne **jayyid**, ƙaramin kuma shi ne zuyuf. Idan kyaun su bai kai kashi hamsin cikin ɗari ba kuma ana amfani da su wajen cinikayya, wajibi ne a fitar masu da zakka idan sun kai nisabi, wato zinare ko azurfa.

Idan ya zamo amfanin da ake samu daga gona wanda a kan samu ruwa ne daga ruwan sama ko ƙorama ɗan kaɗan ne da kayan marmari, waɗanda suke ruɓewa da lalacewa da sauri, za a bai wa jami'in da aka ɗora wa alhakin karɓar 'ushr kashi ɗaya bisa goma. Shi wannan jami'in zai sayar da 'ushr ɗin da ya karɓa, a kai kuɗin a ajiye su a wurin da ake kira **Bayt-ul-mal**. (A duba babi na ɗaya da na ishirin da tara da na talatin da tara a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss**). Akwai bayanai na Malamai da ke nuna cewa farilla ne a bayar da 'ushr na kayan marmari a lokacin da suka fito, ko lokacin da suka ƙosa ko bayan sun nuna. Ana bayar da kashi ɗaya bisa ishirin na kayan noma idan an yi amfani da dabba ko famfo ko injin da sauran na'urori wajen yin ban ruwa. Za a bayar da ita kafin a cire sauran abubuwa. Bai halatta ga gwamnati ba ta bayar da kyautar 'ushr ga mai dukiyar ba ko ta yafe masa fitar da ita ko ta hana bayarwa. Ana bayar da 'ushr ga zumar da aka ɗebo ta daga saman duwatsu ko a ƙasa.

Ba a bayar da zakka ga dhimmi. Ana iya ba su sadaƙa-i-fitr da sauran taimako. *(dhimmi su ne kafiran da suke zaune a ƙasashen Musulmi).* Kafiran da ba dhimmi ba, ba za a ba shi tallafin da yake farilla ko wajibi ko nafila ba, ko da ya kasance musta'min ne *(wato, kafirin da yake zaman wucin gadi a*

ƙasashen Musulmi) ko harbi *(wato, wanda yake zaune a ƙasar da ba ta Musulmi ba).* (A duba babi na arba'in da shida a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss**)." Idan Musulmi mabuƙaci ba ya da bashi a kansa, makaruhi ne a ba shi zakka fiye da adadin nisabi. Idan mabuƙaci yana da iyali da yake kula da su, wato, mata da yara, to ya halatta a bashi adadin da idan aka raba shi ga adadin iyalin nasa ba zai kai nisabi ba.

Ya halatta a sayar da kadara a bayar da kudî da ake amfani da su a kasuwanni. Fulû s na nufin kudîn da aka yi da ƙarfen da ba zinare da azurfa ba, ba kuma takardun kudî ba; saboda a al'ada ana amfani da su a wajen yin themen (farashi), ba dole ba ne sai an yi ta'ayin; wato, ba dole ba ne sai an fito da su, sai an nuna su. Idan ya zamo kasid, cewa, idan ba a amfani da su a kasuwa, cinikin (da aka yi) ya zama badîl (ɓatacce) inji Imam A'zam Abu Hanifa 'rahima-hullahu ta'ala'. (A wani ɓangaren) Imamayn wato Imam Abu Yusuf da Imam Muhammad 'rahima-humullahu ta'ala' sun ce, cinikin bai zama badîl ba. Za a bayar da kudî daidai da darajarsu. Idan Fulûs (kudîn ƙarfe ko na takarda) suka zama kasid, (suka zamo ba a amfani da su a kasuwa), bayan an karɓa bashi, za a mayar da mithl, wato fulûs na adadain da aka ranto, inji Imam A'zam. Imamayn su kuma sun ce za a mayar da kudî (wato zinare da azurfa) wanda adadinsu ya yi daidai kudîn da aka ranto. Saye da sayarwa ta amfani da fulûs da aka yi bayaninsu, yana buƙatar yin ta'yin na fulûs dîn, wato, a nuna su. Dukiyar da ake yi wa ta'yin, sai tana da (ikon a yi mata) ta'ayyun. (a duba babi na ishirin da tara a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss** domin ƙarin haske a kan kalmomin fannu da aka yi amfani da su). Wannan ya nuna idan aka yi wa wata dukiya ta'yin (an nuna shi) dole ne a bayar da wannan dukiyar a cinikin da ake yi. Ba za a bayar da makamancinta ba. Misali, mutum ya bayar da azurfa da ta kai nauyin dirhami dâya ga mai canza kudî, ya buƙaci ya ba shi fulûs na rabin dirhami, da azurfa da ta kai nauyin habba ƙasa da nauyin rabin dirhami da sauran rabin da ya rage, bay' (cinikin) zai zama fasid. Domin aiki ne na faiz (ko faidh) a sayar da rabin dirhami na azurfa a karɓi wata azurfar da ba ta kai nauyin rabin dirhami ba. (Habba wani yanki ne na nauyi daidai da ƙwayar hatsin sha'ir). Idan ya ce "Ba ni fulûs na nauyin rabin dirhami, da azurfa da ta kai nauyin habba, wadda ba ta kai rabin dirhami ba, a madadin wannan dirhamin dâya na azurfa," duka cikin biyu sun inganta. Domin azurfa mai nauyin habba za a iya sayar da ita da azurfar da suke da nauyi dâya, sannan rabin dirhami na fulûs za a iya sayar da shi a kan azurfa da ta kai nauyin habba wadda ta dâra rabin dirhami na azurfa. Duk da cewa fulûs da azurfar da aka bayar sun bambanta wajen nauyi, amma cinikin ya halatta tun da asalinsu ma ya bambanta.

An faɗa a cikin littafin **Badayi'us-sanayi' fi tartib-ish-sharayi'**[1]cewa: "Dukiyar da za a bayar zakka dole ne ta zama asalinta ɗaya, ko dukiyar zakka mai asali daban-daban. [Bai halatta ba a bayar da situra ko takalmi ko alkama ko kitse da makamantansu ga mabuƙata a madadin zinare ba]. Dukiyar zakka ko ɗai ta zamo 'ayn ko dayn. Ingantacciyar zakkar da take 'ayn ana auna ta da nauyi ko adadi, ko abin da ba a auna shi. Idan ya zamo abin da ba a aunawa ne, ko dai ya kasance dabba sâima ce ko ta kasuwancin 'uruz, (wato, dukiyar ƙiyami da ba dabbobi ba). (A duba sakin layi na goma sha bakwai a babi na ishirin da tara a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss** domin ƙarin bayani a kan ƙiyami'.) Idan dabba sâima ce; ya zamo dabbar da kanta wadda aka bayyana a nassi (na ayoyi da Hadissai da kyakkyawan bayani) za a bayar, to ana bayar da matsakaiciya ne. Idan aka bayar da ƙarama, za a cike giɓin bambancinta da matsakaiciyar da zinare ko azurfa. Idan za a bayar da gwargwadon darajar dabbobin, ana bayar da darajar matsakaiciyar ne. Idan aka bayar da darajar ƙarama, sai a cike giɓin da zinare ko azurfa. Maimakon tumaki guda biyu, ya halatta a bayar da tunkiya mai ƙiba da ta kai darajarsu. Domin ana la'akari da daraja a kan dukiyar da ake iya samun faiz (riba). A kan kasuwanci na 'uruz, kashi ɗaya bisa arba'in na dukiya da aka bayyana a nassi za a bayar, bayar da wani abu matsakaici ko wanda ba shi da inganci yana janyo cike giɓin da aka samu (na inganci ko daraja). Game da 'uruz, yana nufin dukiyar da ba a auna nauyinta ba, ko ƙimarta ba. A kan 'uruz, bambancin da ake samu ba ya kawo faiz. Misali, saitin situra guda biyu marasa inganci, za a iya bayar da su a madadin situra ɗaya mai inganci. Idan aka bayar da wata dukiya da asalinta ya bambanta, bayar da wani abu da bai kai adadin darajarta ba zai wajabta cike giɓin bambancin da aka samu. Idan dukiyar zakka ta zamo abu ne da ake aunawa da nauyinsa ko ƙarfinsa, za a fitar da ɗaya bisa arba'in na dukiyar. Idan mutum zai fitar da dukiyar zakka wadda asalinta ya bambanta, wajibi ne ya fitar da adadin daidai da farashinta. Idan kuma zai fitar da dukiyar da take da asali iri ɗaya, mutum zai fitar da daidai adadin ne, ba farashinta ba, inji Shaikhayn, (wato, Imam A'zam Abu Hanifa da ɗalibinsa Imam Abu Yusuf,) 'rahima-humallâhu ta'âlâ'. Misali, idan ya kasance farashin kilogiram ɗari biyu na alkama shi ne dirhami ɗari biyu na azurfa, ya halatta a fitar da kilogiram biyar na alkama marar inganci a matsayin zakkarta. Haka nan a maimakon dirhami biyar na azurfa jayyid (mai inganci) a matsayin zakkar dirhamin azurfa jayyid, za a iya fitar da

[1] Wanda ya rubutashi shine Abû Bakr bin Mes'ûd Alâuddîn Shâshî Kâshânî 'rahmatullâhi ta'âlâ 'alaih' (d. 587 [1191 A.D.], Aleppo) a matsayin sharhi ga littafin **Tuhfa-t-ul-fuƙahâ**, wanda malaminsa ya rubutashi mai suna Alâuddin Muhammad bin Ahmad Samarkandî 'rahmatullâhi 'alaih' (d. 540 [1145 A.D.])

dirhami biyar na zuyuf (marar inganci). Wannan hukuncin ya ƙunshi har da mas'alolin da suka shafi nazr. (A duba babi na biyar a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss** domin ƙarin bayani a kan 'nazr').

"Zinare da azurfa suna da daraja ta **themen** (farashi). An halicce su ne a themen. Ba ana amfani da su ba ne domin biyan buƙatu na mutane. Ana amfani da su ne wajen saye da sayarwa. Sauran abubuwa kuma a ɗaya ɓangaren an halicce su ne a matsayin themen da kuma amfani da su a kankin kansu," nan muka kawo ƙarshen fasarra daga **Bedâyi'**.

Abubuwan da mutum yake buƙatar ya yi rayuwa cikin wadata a kan tsarin da Musulunci ya yarda da shi su ake kira **muhimman buƙatu**. A duba babi na goma na littafin '**Ethics of Islam**!' Muhimman buƙatu suna sauyawa, bisa la'akari da hali, da yanayi da lokacin da mutane suka rayu. Tarin kadarori da ba a buƙata domin samun wadatar rayuwa waɗanda ake amfani da su domin nishaɗi da ƙawa, ko jan hankali, ana kiran su kayan ado (zinat). Zinari da azurfa ba sa cikin muhimman buƙatu; suna cikin kayan ado. Ya halatta maza su yi amfani da kayan ado da suke mubah (halal) a cikin gida ko a waje; amma ga mata za su yi amfani ne da su a cikin gida kaɗai.

Kamar yadda aka gani, fulûs da ake amfani da su, dukiya ce ta kasuwanci kodayaushe. Idan adadinsu ya kai nisabin ƙaramin kwabon zinare da ake amfani da shi a kasuwa, ya zamo farilla gare shi ya fitar da zakka a kansu. Ana lissafin nisabin farashin dukiyar kasuwanci da zinare da azurfa, ya fi dacewa a yi amfani da wanda aka fi cinikayya da shi a kasuwa, inji Imamayn (wato Imam Abu Yusuf da Imam Muhammad 'rahima-humallâhu ta'âlâ' manyan ɗaliban Imam A'zam Abu Hanifa 'rahima-hullahu ta'ala), za a fitar da zakka ga wannan dukiyar da kuɗi (wato zinare ko azurfa), bisa tsarin lissafin farashin da aka yi ko ɗaya bisa arba'in na dukiyar. Mabuƙata za su yi amfani da dukiyar a wajen biyan muhimman buƙatunsu. Fulûs na nufin kuɗin da ba zinare da azurfa ba. Sun ƙunshi kuɗin ƙarfe da aka yi daga jan ƙarfe da tagulla da makamantansu, ko kuɗi na takarda. Wannan na nufin takardun kuɗi fulûs ne. Wajibi ne a fitar masu da zakka. Amma **darajarsu** ba ta **haƙiƙa** ba ce kamar zinare da azurfa. Daraja ce ta **darajar suna** ce kawai. Gwamnati ce ke sanya masu daraja. Suna iya janye su kuma. Idan darajar ta suna (ta fulûs) ta gushe, ba za su cigaba da zama **themen** (farashi) ba. Sun rasa darajarsu a matsayin dukiyar zakka. Ibni 'Abidin ya ce: "Ana lissafa darajar dukiyar kasuwanci da kwabban zinare da azurfa, waɗanda aka buga a matsayin kuɗi, waɗanda ake amfani da su domin kasuwanci. Idan ya zamo darajar wata dukiya ta yi daidai da dirhamin azurfa ɗari biyu da arba'in, idan aka lissafa ta azurfa, da kuma mithƙal na zinare ishirin, idan aka lissafa ta da zinare, adadinta ya kai nisabi a dukkan lissafin biyu; amma za a yi amfani da

azurfa ne wajen lissafinta. Domin mai dukiyar zai bayar zai fitar da dirhami shida ko rabin mirhƙal na zinare, wanda yake daidai da darajar dirhami biyar na azurfa, inda hakan zai rage alfanun da mabuƙata za su samu (wadanda za a bai wa zakkar). [Tun da ya kasance mithƙal ishirn na zinare da dirhamin azurfa dari biyu (farashinsu) daya ne na nisabi, to darajarsu iri daya ce]. Kwabon zinare mai nauyin mithƙal daya ana kiransa **dinar**. [dukkan lira na zinare na Turkiyya yana da nauyin mithƙal daya da rabi, wato giram 7.2 kowannensu]. Wajibi ne a fitar da zakka a kan kudin da ake kira fulûs [da zinare ko azurfa] wadanda ake amfani da su wajen lissafa nisabinsu." Wannan na nufin cewa dole ne a lissafa nisabin takardun kudi da mafi ƙarancin darajar lira na zinare da ake amfani da wajen hada-hadar kasuwanci, za a fitar da zakkar ne da zinare. Domin ba a amfani da azurfa a matsayin kudi a yanzu. Ana fitar da zakkar takardun kudi da ƙarfe, wato zinare wanda ake amfani da shi wajen lissafin (farashin) nisabinsu. Ba za a bayar da kashi daya bisa arba'in na farashinsu a takardun kudin ba. Ba a amfani da takardun kudi a kankin kansu wajen biyan muhimman buƙatu. Almubazzaranci ne yin amfani da takardun kudi a madadin lalatattun takardu da ake da su. Saboda almubazzaranci haramun ne. Haka nan bai halatta a bayar da takardun kudin a matsayin zakka na takardun kudi ba, don gudun yin amfani da su a matsayin kudi. Domin akwai zinare, wanda yake da tsayayyar daraja kuma kudi na haƙiƙa, wanda ya fi dacewa a bayar da zakka da shi.

Ana iya bayar da zinaren ba a tsarin kwabbai kadai ba, har da kowane irin tsari. Akwai shi wadace a kowane lokacin kuma a ko'ina. Idan misali Musulmi bai samu zinare a cikin garin da yake zama ba; sai ya aika da takardun kudin zuwa ga wani abokinsa da yake zaune a garin da ake sayar da ƙarafan zinaren, ya rubuta masa wasiƙa cewa ya sayo mashi zinaren da takardun kudin, sannan ya fitar da zakkar a madadinsa. Ya halatta ya biya bashi da takardun kudin bayan nan. Da wannan hukuncin na fitar da zakka a kan takardun kudi, ba abu da ya dace ba a ƙi fitar da zakka da zinare da nufin fitar da ita da takardun kudi da darajarsu ta ta'allaƙa ga suna da sharadi, an saɓa wa ƙa'ida idan aka bayar da muhimmanci wajen bijire wa hukunce-hukuncen da litattafan Fiƙihu suka bayar. Mutanen da suka nuna halin ko'in kula wajen yin da'a ga koyarwar Musulunci da aka rubuta a litattafan Fiƙihu[1], da wadanda suke ƙoƙarin yin ayyukan ibada bisa fahimtarsu daga ayoyin Ƙur'ani, wadanda ake kira **la-Mazhabi**, (wato mutanen da ba su da ko kuma ba subin wata Mazhaba) da masu bambancin **aƙida**. Martaninmu a kan

[1] Ayi ƙokari a duba babi na talatin da uku na mujalladi na biyu na littafin Endless Bliss domin ƙarin bayani akan wannan reshen ilimi na musulunci mai suna 'Fiƙhu'.

wadanan mutanen shi ne: “Ina aikin ibada ne ba bisa fahimtarku a kan Kur’an al-karim da Hadisi ba, sai a kan amincewa da fahimta da bayanin Imamai na Mazhabobi (hudu) ‘rahima-hullahu ta’ala’ da suke a **litattafan Fikihu**.

Kitab-ul-fikh ‘alal-madhahib-il-arba’a, wanda ayarin wasu mudarrisin (farfesoshi) na madrasa (jami’ar) na **Jamu’ul adhhar** karkashin jagorancin Prof. Abd-ur-Rahman Jeziri suka shirya, sun samar da dukkan koyarwa ta Fikihu a bisa tsari hudu, kowane daya daga cikin koyarwar yana kan daya daga cikin Mazhabobin nan hudu: Dukkan littafin mai bangarori biyar an buga shi ne a Cairo a shekarar 1392 hijiriyya [1972 M.]. An fada a cikin babin ‘Zakka a kan awrak-i-maliyya (takardun kudi) cewa: “Malaman Fikihu sun ce wajibi ne a fitar da zakka a kan awrak-i-maliyya, wato, takardun kudi. Domin ana amfani da su a madadin zinare da azurfa a wajen kasuwanci. Za a iya canza su da zinare da azurfa cikin sauki. Ga mutumin da yake da takardun kudi da yawa, ba abu ba ne karbabbe ga zukatan mutane ya ki sanya su cikin zinare da azurfa a lissafin nisabin zakka, don haka ya ki fitar masu da zakka. A kan haka, Malaman Fikihu na Mazhabobi uku sun hadu a kan cewa wajibi ne ya fitar da zakka ga takardun kudin. Mazhabar kadai da ta kauce wa wannan hukuncin ita ce Mazhabar Hambaliyya. Malaman Mazhabar Hanafiyya sun ce takardun kudin **dayn-i-kawi** ne, za a iya canza su da zinare da azurfa a lokacin da aka ga dama kuma nan take. (A duba babi na daya a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss** domin karin bayani a kan ‘dayn-i-kawi’). Sun kara da cewa, a kan wannan mas’alar, wajibi ne a fitar masu da zakka ba tare da bata lokacin ba. Fitar da zakka a kan bashin da lokacin biyansa ya yi, ya zamo farilla idan an karbi zinare ko azurfa. Duk da cewa zakkar ta zamo farilla kafin a karbe su, ba ta zamo farilla ba a bayar da ita.” A nan mutum yana da zabi biyu: Ko dai ya jira har sai ya karbe su, sannan ya bayar da zakkar ta shekarun baya gaba daya, ko ya bayar da zakkarsu duk shekara ta hanyar amfani da ‘ayn na zinare da azurfa da ke hannunka. Ba za ka bayar da takardar yarjejeniya da ke hannunka a matsayin zakkar kwabban zinare da kake bi bashi ba; idan ka karbi kwabban zinare da azurfar da aka rubuta a kan takardar yarjejeniyar daga wanda kake bi bashi, ya zamo farilla ka raba kashi daya cikin arba’in nasu na dukkan shekarun da suka shude ka raba wa mabukata. A kan kudi iri daya, ba za a iya biyan zakka da takardun kudi ba. Abin da ya zamo wajibi shi ne a sayi zinare da karancin farashi daga mai canjin kudi, ta hanyar bayar da kashi daya cikin arba’in a raba kwabban da aka saya, ko zobban zinare ko awarwaro da nauyin su ya kai na kwabban ga mabukata.

Bai halatta ba ka yafe wa wanda kake bi bashi ba a matsayin zakkar da za ka ba shi, ta yadda zakkar ba ta kai adadin bashin ba, sai ya kasance bai kammala biyanka bashi ba, kuma kai ba ka ba shi zakkar ba. Dole ne ka bayar da zakkar ga mabuƙacin, daga bisani shi kuma ya zama dole ne ya biya bashi ta hanyar mayar da kuɗin da aka ba shi. Ga mutumin da yake bin bashi wanda ba shi da yaƙinin cewa wanda yake bi bashi zai biya shi, akwai wata hikima da aka bayar a ƙarshen mujalladi na shida na littafin **Fatawa-yi-Hindiyya** cewa: "Mai bin bashi zai nuna mutumin da ya amince da shi ga wanda yake bi bashi, ya ce, 'Ka naɗa wannan mutumin a matsayin wakili ya karɓi zakkar da zan ba ka, ya kuma biya ni bashin da nike binka.' Mabuƙacin da ake bi bashi, sai ya naɗa wannan mutumin a matsayin wakili. Idan mutumin ya karɓi zakkar, dukiyar (zakkar) da ya karɓa ta zama mallakin mabuƙacin. Daga nan sai ya mayar da dukiyar ga mawadacin, shi kuma mabuƙacin an biya masa bashi ke nan. Misali, idan wani mabuƙaci ya zamo mutane biyu na bin sa bashi, ɗaya daga cikinsu yana son ya fitar da shi daga bashin, ta hanyar ba shi zakka daidai da bashin da yake binsa; sai ya bayar da dukiyar a matsayin sadaka ga mabuƙacin. Ke nan ya tsame mabuƙacin daga bashi ta hanyar da take halal. Daga nan sai mabuƙacin ya mayar da (zinaren da aka ba shi) zakkar ga mawadacin a matsayin kyauta. Ko mabuƙacin ya aro zinare daidai da bashin da ake binsa daga wani mutum, sai ya bayar a matsayin kyauta ga mawadacin, wanda shi kuma zai mayar da zinaren ga mabuƙacin a matsayin zakka, sai ya tsame shi daga bashin, wato ya yafe masa bashin. Shi kuma mabuƙacin sai ya mayar da zinaren da aka ba shi zakka (daga mawadacin) ga wanda ya aro zinaren a hannunsa. (dukiyar da za a bayar a matsayin) zakka [ko dukiyar alƙawari] ba a amfani da ita wajen aikin Allah ko tallafi (a madadin zakka) [ko dukiyar alƙawari]). Domin yin hakan, sai ka bayar da ita (a matsayin zakka [ko alƙawari]) ga wani mabuƙaci da ka sani, shi kuma wannan mutumin sai ya yi aikin tallafin da ita." Bayan waɗannan misalan, idan za ka fitar da zakka da takardun kuɗi, sai ka aro kayan ado na zinare daga wajen matarka, gwargwadon nauyin kwabban zinaren da ka yi niyyar bayarwa a matsayin zakka a madadin takardun kuɗin ko daga wani makusancinka. Sai ka bayar da wannan zinaren da niyyar zakka ga wani makusanci ko ɗan uwanka mabuƙaci. Yanzu ka fitar da zakkar takardun kuɗinka (ta hanayar bayar da zinare mai nauyi daidai da kwabban zinaren da aka lissafa darajarsa daidai da takardun kuɗin da za a fitar a matsayin zakka). Daga nan sai mabuƙacin ya bayar da kyautar zinaren ga mawadacin, shi kuma ya mayar ga wanda ya aro a hannunsa. Tun da ka bayar da zakka, sai ka bayar da wasu daga cikin takardun kuɗin da ke hannunka waɗanda ka ware domin fitar da zakkar ga mabuƙacin. Kana iya kashe sauran kuɗin wajen bayar da tallafin da kake buƙata. Idan mabuƙacin

yana son ya samu wani kaso na ladar sadakar, sai ya sayar maka da zzinaren da ya karɓa a matsayin zakkar. Daga bisani ya mayar maka da takardun kuɗin, ya naɗa ka wakili da zai raba tallafin a madadinsa.

Sayyid Abd-ul-Hakim Arwasi ‘rahmatullahi ‘alaih’ (1281H. [1865 M.], Baskale, Ɓan, Turkiyya – 1362H. [1943], Ankara), ƙwararren malami a kan koyarwar dukkan Mazhabobi huɗu, ya ce: “Darajar kuɗin takarda suna ne kawai. Idan aka janye su daga matsayin kuɗi, darajarsu za ta gushe. Don haka bai halatta a bayar da fitra ko zakka da takardun kuɗi ba. Mutum zai sake zakkar da ya yi da takardun kuɗi a baya ta hanyar dawr da zinare. Dukkan ayyukan ibada da ake yi da kuɗi, baya ga aikin hajji, za a iya sake su (ramawa) ta hanyar dawr.” (A duba babi na ishirin da ɗaya a mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss** domin ƙarin bayani a kan dawr’).

An faɗa a cikin Darr-ul-mukhtar cewa: Idan Baghis, Musulmin da suka yi wa gwamnati bore, suka ƙwace mulki, sai Musulmin shugaba azzalumi ya karɓi zakkar dabbobi da zakkar (da ake kira ‘ushr) ta kayan abinci ya raba su (ta hanyar da) inda Allâhu ta’âlâ ya bayar da umarni, dukiyar da aka karɓa (a hannun Musulmi) ta zama zakka (da ‘ushr) (ga waɗannan Musulmin). Amma idan aka raba dukiyar (ta hanyar da ba ta dace ba) a inda bai dace ba, wannan dukiyar da aka karɓa ba za ta tsaya matsayin zakka ba (da ‘ushr). Dole ne ga masu dukiyar su sake fitar da wata zakkar (da ‘ushr) ta hanyar raba wa ga mabuƙata Musulmi. Idan shugaban ya karɓi dukiyar kasuwanci a matsayin zakkar kuɗi, ba za ta tsaya a matsayin zakka ba, bisa zantukan mafi yawa daga cikin malaman Musulunci. Fatawar da aka bayar ta yi dadai da ijtihadinsu. Wasu Malaman sun ce, tun da azzaluman shugabannin da suka karɓa Musulmi ne (a daidai wannan lokacin) kuma dukiyar da aka karɓa mallakin mutane ce, za a riƙe su a matsayin mabuƙata, don haka dukiya da aka ba su da niyyar zakka, za ta tsaya matsayin zakka.”

Ibni **‘Abidin** ya faɗa a kan wannan batun cewa: “Hukuncin ya shafi har da kadara da kuɗin da aka karɓa a matsayin haraji da na fito da sauransu. Zancen Malamai da ya fi shahara na cewa dukiyar da aka karɓa ba za ta tsaya matsayin zakka ba duk da niyyar da aka yi, shi ya fi inganci. Wato, azzaluman shugabanni Musulmi ba su da ikon karɓar zakka daga dukiyar al’umma.” Batun cewa fatwa ta amince da wannan ijtihadin yana cikin sharhin **Tahtawi** (na littafin da aka faɗa a baya). Kamar yadda aka gani, zakkar dabbobi da ‘ushr (ta kayan noma) tana zama ingantacciya ne idan gwamnatin da ta karɓa, ta Musulunci ce, ta kuma raba wa mutanen da suke karɓar albashi daga ma’ajiyar gwamnati da ake kira **Bayt-ul-mal**. Babu wani haraji da gwamnati ke karɓa da ke tsayawa a matsayin zakkar kadara ko kuɗi inji mafi yawa daga manyan Malamai. Akwai wata magana ta Malamai da

ke cewa tana iya halatta bisa sharaɗin cewa gwamnatin da za ta karɓa ta zamo ta Musulunci, kuma a bayar da kadarar ko kuɗin da niyyar fitar da zakka. Amma isnadin wannan batun da'if (mai rauni) ne. (A duba babi na shida a mujalladi na biyu na littafin **Endless Bliss** domin samun cikakken bayani a kan da'îf).

Haba! Ya kai ɗan uwana, ka yi tunani ka rabu da wannan kafiyar!
Rayuwarka tana da tsada, kar ka shashantar da ita wajen almubazzaranci!

Ka kare zuciyarka daga buƙatu na son rai!
Ka tsarkake cikinka kamar yadda wajenka yakei!

Idan aka cakuɗa zinare da jan ƙarfe,
Mai canjin kuɗi zai karɓe su cikin farin ciki kuwa?

Kar ka yi tinƙaho da difulomarka ta babbar makaranta!
Ka yi tunani kafin ka yi magana, don guje wa shiga matsala!

Ka nemi mutum mai ma'arif(kyawawan aiki), ka kusance shi matuƙa!
Don ka samu jin ƙan Ubangiji mai yawa!

Ka je tekun Haƙikat ka yi iyo a cikinta,
Sannan ka fito da wani abu mai girman daraja!

Kar ka bar jahilin ɗalibi ya ɓatar da kai!
Malaman farko sun nuna maka hanyar tsira tuni!

BABI A KAN AZUMI

Akwai farillai guda uku na azumi:

1- Ɗaura nniyya.

2- Ɗaura niyya tsakanin farkon azumin zuwa ƙarshensa.

3- Guje wa abubuwan da ke karya azumi a lokacin nahar-i-shar'i (yini a bisa tsarin Musulunci), da ke ƙarewa idan rana ta faɗi. Lokacin imsak shi ne yayin da idan fajr-i-sadiƙ ya bayyana kaɗan sama da layin ufƙ-i-zahiri (mahudar rana). Mutumin da yake guje wa abubuwan da ke karya azumi har zuwa faɗuwar rana, ba tare da ya yi niyyat (niyyar) azumi ba (a lokacin da Musulunci ya tsara) bai yi azumi a wannan ranar ba. Zai rama azumin wannan ranar kaɗai.

Akwai sharuɗɗa bakwai da za a cika, da suka zamo farilla ga mutumin da zai yi azumi:

1- Ya zamo Musulmi.
2- Ya kai shekarun balaga.

3- Azumin ƙaramin yaro ya halatta. Ya kai shekarun hankali da sanin ya kamata
4- Ga Musulmin da yake zama a dar-ul-harb ya san cewa farilla ne yin azumi (na Ramadan).
5- Ya zamo muƙim (mazaunin gida. Wato, ba ya cikin doguwar tafiya. A duba babi na goma sha biyar a mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**).
6- (Ga mace ko budurwa) ya zamo ba sa cikin haid (jinin al'ada) 7-ko cikin nifas (jinin haihuwa).

Akwai abubuwa shida da ke karya azumi: Cin abinci; shan abin sha; haid; nifas; yin amai gwargwadon cikin baki. ƙarya da gulma da haɗa husuma, wato haɗa faɗa a tsakanin Musulmi da damfara ba sa karya azumi. Amma suna ɓata ladar da za a samu idan an yi azumi.

Mutane bakwai suna da damar ajiye azumi:

1- Marar lafiya; 2- Musafir [Musafir shi ne mutumin da yake kan doguwar tafiya da ake kira safar. Ana kuma kiransa mutum mai safari, saɓanin mutum muƙim da aka yi bayaninsa a baya). 3- (Macen da take cikin jinin al'ada na wata-wata da ake kira) haid 4- Macen da take (jinin haihuwa da ake kira) nifas. 5- Mace mai ciki, wadda ta galabaita ba za ta iya azumi ba; 6- Macen da take shayarwa wadda ke fargabar jinjirinta zai cutu; 7- (Mutumin da ake kira) pîr-i-fânî (wanda ya tsufa kuma yake da rauni wajen yin azumi).

Dole ne a yi niyyat (niyya) kowace rana ta azumi. An rubuta a cikin **Fatawa-i-Hindiyya** cewa: "Ana yin niyyat ne a cikin zuciya. Tashi (cikin dare domin cin abinci da ake kira) Sahûr yana nufin an yi niyyat ne." Akwai niyyat iri biyu ga azumi: Niyyat ta farko ita wadda ake yi kowace rana a watan Ramadan, ko ga azumin nafila ko azumin bakance, wadda ake yi tsakanin lokacin faɗuwar rana na jiya zuwa yau a lokacin da ake kira **dahwa-i-kubra**. Dahwa-i-kubra shi ne rabin lokacin yini na shar'i, wato rabin lokacin da ake azumi, wanda aka lissafa kamar haka bisa tsarin lokacin kiran sallah:

$$\text{Fajr} + \frac{24-Fajr}{2}, \quad \text{ko Fajr} + 12 - \frac{Fajr}{2} = 12 + \frac{Fajr}{2}.$$

Wannan na nufin cewa lokacin dahwa-i-kubra shi ne rabin adadin da ke nuna lokacin fajr a tsarin lokacin kiran sallah. Yana zuwa ne kafin zawal (tsakar rana) kamar bambancin da yake tsakanin lokacin yini na shari'a da na hasken rana bisa la'akari da daidaitaccen lokacin; wannan bambancin shi ne ya zo daidai da rabin hissa-i-fajr, wadda yake nuna adadin lokacin tsakanin fitowar rana da alfijir, ko lokacin imsak. Ana ɗaura niyyar azumi

aƙalla zuwa lokacin Dahwa-i-kubra – idan ba ka ci abinci ko abin sha ba (bayan lokacin imsak). Bai halatta a ɗaura niyya a lokacin Dahwa ba. Niyyar da ake yi kafin fitar alfijir dole ne ta zamo kamar haka: "Na yi niyyar yin azumi gobe," yayin da ita kuma niyyar da ake yi bayan fitar alfijir za ta zamo kamar haka: "Na yi niyyar yin azumi yau."

Nau'in niyya na biyu ana yin sa ne domin ramuwa ko kaffara ko kuma nazr-i-mutlaƙ. Waɗannan nau'ukan azumin uku, niyyarsu iri ɗaya ce, wato nau'in niyya na biyu. Farkon lokacinta shi ne daga faɗuwar ranar jiya, ƙurarren lokacinta kuma shi ne gab da lokacin fajr-i-sâdiƙ, wato kafin haske ya bayyana a gabas. Bai halatta a yi niyya ga waɗannan nau'ukan azumi uku ba bayan wayewar gari. An rubuta a cikin Ibni 'Abidin, a ƙarshen babin da ke bayani a kan ramuwar sallah ya ambato, idan kana ramuwar azumin Ramadan na wasu 'yan kwanaki, ba sai ka ambaci sunayen ranakun ko tsarin kwanakin ba ɗaya bayan ɗaya. Azumi mataki uku ne bisa la'akari da mutanen da suke yin azumin: azumin mutanen da ba su da ilimi; azumin mutane masu ilimi; da azumin Annabawa da Waliyyai (mutane masu albarka da suka samu soyayyar Allâhu ta'âlâ). Idan marasa ilimi suka yi azumi, ba sa cin abinci da shan abin sha, kuma ba sa yin jima'i. Amma suna aikata wasu ayyuka marasa kyau. Masu ilimi ba sa aikata abubuwa mara kyau. Su kuma Annabawa da Waliyyai suna ƙaurace wa duk wasu ayyuka da ake kokwanto a kansu idan suna azumi.

Akwai nau'in Idi iri uku, bisa la'akari da waɗanda suke yin hawan idi bayan kammala azumi: Idin marasa ilimi; da Idin masu ilimi; da Idin Annabawa da Waliyyai. Marasa ilimi (suna buɗa baki) ta hanyar (cin abincin da ake kira) iftar bayan faɗuwar rana, suna cin abinci da shan abin sha son ransu, sannan su ce "Yau ranar Idinmu ce." Masu ilimi suma suna yin buɗa baki bayan faɗuwar rana, amma sai su ce "Wannan Idinmu ce, idan Allâhu 'adhîm-ush-shân ya karɓi azuminmu." Sai kuma su tsunduma cikin tunanin "Me zai faru da mu idan Allâhu ta'âlâ bai karɓi aikin ibadarmu ba!" Idin Annabawa da Waliyyai ru'yatullah ne. Sun cancanci albarkar Allâhu 'adhîm-ush-shân.

Akwai nau'in Idi biyar ga dukkan Musulmi:

Na farkonsu shine idan mala'ikan da yake hannun hagun Musulmi bai samu wani mummunan aiki tattare da shi ba.

Na biyu shine a lokacin ɗaukar ran mutum (sakarat-ul-maut), mala'iku masu bushara za su bayyana gare shi, su gaishe shi, su ba shi kyakkyawan albishir cewa shi mumini ne kuma ɗan aljanna.

Na uku ita ce lokacin da aka sanya mutum cikin ƙabari, ya samu ƙabarin a matsayin dausayi, daga dausayin aljanna.

Na hudu shine idan mumini ya samu kansa tare da Annabawa da Waliyyai da manyan Malamai da Salihan bayi a ƙarƙashin inuwar al'arshi a ranar lahira.

Na biyar shine lokacin da mumini ya amsa dukkan tambayoyin da za a yi masa a wurare bakwai a yayin da yake tafiya domin tsallake siradi, wanda ya fi gashi sirantaka, ya fi takobi kaifi, ya kuma fi duhun dare tsananin duhu, wanda zurfin ƙasansa ya kai tafiyar shekaru dubu ɗaya, samansa ma tsawon shekaru dubu, tsayinsa tsawon shekaru dubu. Idan ya gaza amsa tambayoyin, za a yi masa azabar shekaru dubu a kowace tambaya da ya gaza amsawa. A cikin tambayoyin bakwai, ta farkon za a tambaye shi ne a kan imani, ta biyu kuma za a tambaye shi a kan sallah, ta uku za a tambaye shi a kan azumi, ta hudu za a tambaye shi a kan aikin Hajji, ta biyar kuma za a tambaye shi ne a kan zakka, ta shida za a tambaye shi a kan haƙƙin hallitu, ta bakwai kuma za a tambaye shi ne a kan wanka da istinja, da alwala. (istinja na nufin tsarkin gaba da baya, bayan mutum ya yi fitsari ko bayan gida, wanda aka yi cikakken bayani a kai a babi na shida na mujalladi na hudu na littafin **Endless Bliss**).

Idan mutun ya karya azuminsa (kafin faɗuwar rana) da gangan wanda ya ɗaura niyyarsa kafin lokacin imsak, to wajibi ya yi kaffara da ramuwa. Karya azumin nafila ko azumin ramuwa, ba ya wajabta kaffara.

Ana 'yanta bawa wajen yin kaffara. Mutumin da ba ya iya azumin kwanaki sittin, ban da kwanakin watan Ramadan da kwanaki biyar da aka haramta azumi yin azumi a cikinsu. Sai ya yi ramuwar azumin na gwargwadon waɗanda ya karya (a baya). [Haramun ne yin azumin a ranar sallar Idi ƙarama ko ɗaya daga cikin wasu kwanaki hudu na babbar sallar Idi.] Mutumin da ba shi da ikon yi, ko dai ya ciyar da mabuƙata sittin sau biyu a rana ɗaya, ko kuma ya ciyar da mabuƙaci ɗaya sau biyu a rana har tsawon kwanaki sittin. Ko ya ba kowannensu wata kadara da farashinta ya kai na wanda ake bayarwa a matsayin fitra.

Ana yin ramuwar azumi ɗaya ne ta hanyar yin azumin rana ɗaya.

Mutane biyar ba su da buƙatar yin kaffara. Na farko shi ne marar lafiya. Na biyu shi ne musafir (wato wanda yake kan doguwar tafiya da ake kira safar). Na uku macen da ke shayarwa, wadda ke fargabar azuminta zai iya cutar da jaririnta. Na hudu shi ne pîr-i-fânî. Na biyar shi ne mutumin da ya ji tsoron mutuwa saboda yunwa ko ƙishin ruwa.

Idan wannan uzurin nasu ya kau, dole ne su rama azumin da ya kuɓuce, kwana na ɗaya a madadin azumin kwana ɗaya.

Batun niyya a yaumu-shakk[1] (ranar kokwanto), akwai ‘yan maganganu kamar haka: A yaumu-shakk ya halatta a yi niyya amma akwai karhanci a ciki, a yi niyyar azumin watan Ramadan ko wani azumi da yake wajibi ko yin niyyar azumin kwana ɗaya na Ramadan, idan a watan Ramadan ne, ko azumin nafila, ko wanda ba wajibi ba, idan ba a cikin watan Ramadan ba ne. Wani nau’i na niyya kuma shi ne wanda babu karhanci a ciki, wanda ake yi a azumi masu falala, ko (azumin watan) Sha’aban, wanda ke nufin yin niyyar azumin nafila. (Karahat na nufin wani abu kamar yanayi ko lokaci wanda Manzonmu ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam ba ya son a yi wani aiki na ibada. Idan ibadar ta nafila ce, ba za a yi ta a wannan lokacin na karahat ba. Idan ibadar farilla ce wadda mutum bai yi ba, kuma dole ne a yi ta kafin lokacinta ya wuce, wajibi ne ya aikata ta ko da kuwa zai aikata karhanci. Ana iya samun bayani kan lokuttan karhanci a ƙarshe-ƙarshen babi na goma a mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**).

Nau’in azumin da bai halatta ba shi ne wanda aka yi wa niyya kamar haka: “Na yi niyyar yin azumi idan wannan watan (da muke ciki) Ramadan ne, idan ba shi ba ne, ban yi niyya ba.”

Idan misali mutum bai yi niyyar azumi ba har sai bayan fitar alfijir, wato har sai lokacin da haske ya bayyana a gabas, a cikin watan Ramadan, sai ya ci abinci kafin rana ta yi; wannan mutumin ba zai yi kaffara ba, (wadda ke nufin azumin kwanaki sittin jere bayan Ramadan) inji Imam A’zam Abu Hanifa. Su kuma Imamayn, sun ce zai yi kaffara. Saboda ya ci abinci yayin da yake iya yin niyya ya cigaba da azuminsa. Idan ya ci abinci da rana ba zai yi kaffara ba – bisa ijtihadi na gama-gari.

Idan misali ya karya azumi a watanni biyu ko uku na Ramadan daban-daban, wato ya karya azumi ɗaya a kowane wata na Ramadan da gangan, zai yi kaffarar ga kowane azumin ne daban-daban ko zai yi kaffara ɗaya ga dukkan azumi biyu ko ukun da ya karya? Wannan mas’alar tana da sarƙaƙiya (a tsakanin malamai). Ya fi dacewa mutum ya yi kaffara ga kowane azumi daban-daban. Idan ana bin mutum bashin azumin Ramadan; idan bai rama azumin ba har shekara ta zagayo, wasu malamai sun ce ya aikata saɓo.

Idan ranar ɗaya daga cikin Idi biyu ta zo, wato idin ƙaramar sallah ko idin babbar sallah a lokacin da mutum yake azumin kaffara, na kwanaki sittin a jere, kuma kamar yadda aka sani haramun ne yin kowane irin azumi a waɗannan ranakun na Idi, dole ne ya sake azumin na kaffara daga farko. Ba

[1] Ana nufin ranar da ake kokwanto a yaren larabci. A kalmar musulunci tana nufin ranar da a da tabbacin kasance warta ranar farko na Ramadan ko kuma ranar ƙarshe na watan Sha’aban.

za a yi amfani da azumin da ya yi a baya ba (a cikin kwanaki sittin na azuminsa).

Idan mutum ya karya azuminsa ba tare da ya yi niyyar doguwar tafiya ba, daga baya sai ya yi niyyar tafiya, kuma ya yi tafiyar, zai rama azumin kuma zai yi kaffara,(wato zai yi azumi ɗaya na wannan ranar da ya karya, sannan ya yi na kwanaki sittin a jere na hukuncin da ake kira kaffara). Ba mustahabbi ba ne ajiye azumi saboda doguwar tafiya. Idan mutum ya kama hanyar doguwar tafiya, wajibi ne a gare shi kada ya karya azumin wannan ranar. Idan matafiya ya yi niyya (ta azumi) a cikin dare, ko kuma duk wani lokaci kafin Dahwa-i-kubra, bai halatta gare shi ya karya wannan azumin ba a wannan ranar. Idan kuma ya karya azumin, to zai yi ramuwa ne kaɗai (wato zai yi azumin rana ɗaya bayan Ramadan). Abin da yake mustahabbi ga mai doguwar tafiya shi ne kada ya ɗauke azumin (wannan ranar baki ɗaya).

Idan mutum ya samu taɓin hankali a cikin watan Ramadan, ya zamo ba zai iya azumi ba, daga baya sai hankalinsa ya dawo, to zai zama azumin kwanakin da bai yi ba. Idan bai warke ba har watan Ramadan ya fita, kuma lalurar taɓin hankalin tasa ta tsawaita, to an ɗauke masa azumin wannan watan na Ramadan.

Idan mutum ya manta cewa yana azumi, har ya kai ga karya azumin, azuminsa bai ɓaci ba. Idan ya tuna cewa yana azumi, amma ya cigaba da cin abinci bisa zatonsa cewa azumin nasa ya kare, to zai rama wannan azumin (bayan Ramadan), sai dai ba zai yi kaffara ba. Amma idan ya cigaba da cin abinci tare da sanin cewa azumin nasa bai kare ba, to dole ne ya yi ramuwa tare da kaffara.

Idan mai azumi ya haɗiye zufarsa ko ya tauna zaren da aka rina ya tsotse shi ya haɗiye yawun, ko ya haɗiye yawun wani, ko ya haɗiye yawunsa bayan ya fitar da shi daga bakinsa, ko kuma ya haɗiye kingin abinci da ya maƙale a tsakanin haƙoransa wanda ya kai girman kwayar dawa, ko ya yi ma kansa allurar magani, to azuminsa ya kare, amma zai yi ramuwa ne kaɗai.

Idan mutum ya ci fallen takarda ko ya sha gishiri cikin tafin hannu, ko ya haɗiye hatsi ko alkama ko shinkafa, azuminsa ya kare, sai dai zai yi ramuwa ne kaɗai. Saboda a al'adance ba shan gishiri haka kai tsaye, ko a matsayin abinci ko a matsayin magani. Kamar cin ƙasa ne. Haka nan idan gishirin da mutum ya sha kaɗan ne, to kaffara ta hau kansa. Wannan bayanin yana rubuce a cikin littafin **Ashbah**. Domin ana amfani da gishiri kaɗan a matsayin abinci ko magani.

Idan ma'aikaci ya san cewa idan ya yi aikin da yake samun abinci da shi zai kamu da rashin lafiya, duk da haka bai halatta ya karya azuminsa ba kafin ya kamu da rashin lafiyar. Idan ya karya azumin (kafin lokacin shan

ruwa) kaffara ta wajaba a gare shi. Domin guje wa yin kaffara, yana iya fara hadîye takarda da farko (kafin ya ci abinci). Idan mace mai ciki ko wadda ke shayarwa, ta ji ta galabaita (saboda yunwa ko ƙishin ruwa da makamantansu yayin da take azumi) ta ci abinci ko ta sha abin sha, za ta rama azumin ne kadai. Mutumin da ya ci abinci ko ya sha abin sha da izgili ba tare da uzuri ba a cikin azumin watan Ramadan, ya yi ridda. (Fatawa-i-Fayziyya).

Idan mutum ya tauna ƙwayar ridî azuminsa bai karye ba, amma idan ya hadîye ƙwayar ridîn ko da bai tauna ba, azuminsa ya karye, dole ne a rama shi.

Azumi yana da nau'uka guda goma sha biyar: guda uku daga ciki na farilla ne, guda uku kuma na wajibi, guda biyar daga ciki haramun ne, hudu daga ciki kuma sunnah ne. Azumin da suke farilla su ne: Azumin watan Ramadan, da azumin ramuwa da azumin kaffara.

Azumin da suke wajibi su ne: azumin nazr-i-mu'ayyen, da azumin nazr-i-mutlaƙ, da cigaba da azumin nafila har zuwa fadûwar rana idan aka riga aka ɗauke shi.

Azumin da suke haram su ne: azumin ranar idin sallah ƙarama da, azumin a kwanaki hudu na Idin babbar sallah, haramun ne yin azumi a dukkan wadannan kwanaki biyar.

Azumin da suke sunnah su ne: Azumin ayyam-i-baydhi a kowane wata na Musulunci, da azumin da ake kira sawm-i-Dawud, da azumin Litinin da Alhamis, da azumin Ashura, da azumin ranar arfa da sauran ranaku masu muhimmanci irinta. Ranakun goma sha hudu da goma sha biyar da goma sha shida na watannin Musulunci su ake kira **ayyam-i-baydhi**. Yin azumi yau a huta gobe tsawon shekara guda shi ake kira **sawm-i-Dawud**. (**ranar Ashura** ita ce ranar goma ga watan Muharram, watan farko na kalandar Musulunci. **Ranar Arfa** ita ce ranar tara ga watan Musulunci na Du'l-hijja, wato ranar daren babbar sallah).

Azumi yana da falala guda goma sha ɗaya:

1- Yana kare mutum daga shiga wuta.

2- Yana sanyawa (Allâhu ta'âlâ) ya karɓi Ibadu (wadanda mutum ya yi).

3- Zikiri ne da jikin mutum yake yi.

4- Yana kawar da kibr (girman kai da nuna isa).

5- Yana kawar da 'ujb (ji-ji da kai da tinƙaho da ibadar da mutum ya yi).

6- Yana inganta khushu' (tsoron Allâhu ta'âlâ).

7- Ladar da ake bayarwa ga mai azumi za ta cika mizaninsa (za ta ƙara nauyi ga kyawawan ayyukan mutum a ranar lahira).

8- Allah yana farin ciki da bawansa (mai azumi).

9- Idan mutum ya mutu da imani, (azumin) zai yi sanadin shigar da mutum aljanna cikin gaugawa.

10- Zuciyar mutum na cika da haske.

11- Za a haskaka ran mutum.

Idan rana ta faɗi a ran ishirin da tara ga watan Sha'aban, wajibi ne a fara duban jinjirin watan Ramadan a shiyar yamma mafaɗar rana. Idan Musulmi adali, wato wanda ba ya aikata manyan zunubai, wanda kuma yakebin Mazhabar Ahl as-sunnat, ya ga jinjirin watan a sararin sama, sai ya sanar da alƙali ko wani shugaba. Ramadan na farawa ne da zarar Musulmi sun ga watan. Ba a karɓar maganar mutumin da ke aikata bidi'a ko fasiƙi a wannan batun. A wasasshen yanayi, ana buƙatar masu sanarwa kaɗan (a matsayin shaidu wajen zartar da farawar watan Ramadan). Idan ba a ga jinjirin watan ba, za a ɗauki watan na Sha'aban ya cika kwanaki talatin ke nan, yayin da washe gari zai zamo ɗaya ga watan Ramadan kai tsaye. Ba a tantance shigowar watan Ramadan da kalanda, ko ta hanyar lissafin kimiyyar sararin samaniya. An rubuta a littafin **Bahr-ur-raiƙ** da **Fatawa-i-Hindiyya** da **Kadikhan** cewa: "Idan bawan da ke zaune a **Dar-ul-harb** bai san shigowar watan Ramadan ba, sai ya yi amfani da kalanda ya azumci watan, yana iya fara azumin kwana ɗaya kafin shigowar watan, ko a rana ta biyu ko kuma a rana ta farko ta watan na Ramadan. A ƙauli na farko, ya fara azumi kwana ɗaya ke nan kafin Ramadan, ya kuma yi sallar Idi a rana ta ƙarshe ta Ramadan. A ƙauli na biyu, bai fara azumi a ranar farko ta Ramadan ba, ya kuma yi azumi a ranar Idi da niyyar azumtar ranar ƙarshe ta Ramadan. A dukkan ƙaulin biyu, ya azumci kwanaki ishirin da takwas na Ramadan, don haka zai yi azumi biyu bayan sallah da niyyar ramuwa. A ƙauli na uku, akwai kokwanto a kan ko rana ta farko da ta ƙarshe sun yi daidai da na Ramadan. Tun da azumin da ya yi a waɗannan ranakun akwai kokwanto a kansu, to azumin biyu ba su inganta ba, a nan ma zai rama azumi biyu bayan sallah." Don haka, mutanen da suka fara azumin Ramadan ba tare da ganin wata ba, suka yi amfani da kalanda za su yi azumi biyu bayan sallah da niyyar ramuwa. An yi cikakken bayanin yadda ake gano ranar farko ta Ramadan a babi na goma na mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**.

[Ibn 'Abidin 'rahima-hullahu ta'ala' ya ce: "Idan gizagizai suka lulluɓe sama, ba za a sha ruwa ba, (wato ba za a yi buɗa baki ba) har sai mutum ya tabbatar da cewa rana ta faɗi, ko da kuwa an yi kiran sallah (domin sanar da

shigar lokacin Magriba [da iftar]). Idan dai har mutum ya sha ruwa a kafin lokacin (da ake kira) ishtibak-un-nujum, wato lokacin da taurari suka bayyana a sararin samaniya, to ya aikata mustahabbin da ake kira 'ta'jil' (wanda ke nufin gaggauta buɗa baki). Idan rana ta faɗi aka sha ruwa a wani wuri, wanda yake kan tudu, kamar hasumiya, ba zai sha ruwa ba har sai ya tabbatar da rana ta faɗi. Wannan hukuncin ya shafi har da sallar Asuba da yin sahur." A tsarin jadawalin **Tamkin** a cikin litattafan ilimin kimiyyar sararin samaniya (Astronomy) tudu yana daga cikin abubuwan da ake auna tsawon lokaci da ake kira tamkin (wanda aka yi cikakken bayaninsa a babi na goma na mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**). Yayin da aka yi jadawalin lokuttan sallah, ana amfani da ƙayyadajjen lokacin na tamkin a kaɗaitattun wurare, wato lokacin tamkin yana dacewa da wurin da yake kan tudu. (A duba rataye na biyar (B) a mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss** domin ƙarin bayani kan jadawalin tamkin). Kalandar da aka tsara ba tare da la'akari da lokacin tamkin ba, tana nuna lokacin faɗuwar rana mintuna kaɗan kafin lokaci, (na jadawalin faɗuwar rana idan aka kwatanta da wadda aka yi la'akari da lokacin tamkin). Rana ba ta faɗuwa a lokacin da faɗuwar ranar (wanda ke cikin kalandar). Waɗanda suka sha ruwa ta amfani da lokacin kalanda da babu tamkin a ciki, azuminsu ya ɓaci.]

AKWAI SHARUƊƊA GUDA UKU (DA ZA A CIKA) GAME DA (AIKIN) ƘURBAN (LAYYA)

1. Zama nagartacce kuma balagaggen Musulmi.
2. Mutum ya zama muƙim (mazauni, wato wanda ba matafiyi ba).
3. Mallakar dukiya wadatacciya da takai nisabi.

Rukn (rukunnai) na (dabbar da za a yanka) Kurban (Layya) na tumaki da awaki da raƙuma ko sa da saniya), raƙumi ko shanu (mace ko namiji) yana isa ƙurban bakwai, wanda ke nufin mutane bakwai za su iya yanka sa ko saniya a matsayin ƙurban na dukkan su bakwai. Idan wani mutum ya ce "bari in shiga cikinku" to ƙurban ta mutane takwas ɓatatta ce. Nisabin ƙurbani daidai yake da nisabin fitra, (wanda aka yi cikakken bayani a kai a babi na uku na mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss**).

[Kamar yadda Ibni 'Abidin 'rahima-hullahu ta'ala' ya faɗa cewa, idan kason kowanne daga cikinsu bai kai kashi ɗaya cikin bakwai ba, Ƙurban ɗin su duka bakwan ba ta halatta ba. Don haka, ya halatta mutanen da ba su kai bakwai ba su haɗu a kan Kurban ɗaya. Ya inganta mutun ya shiga a lokacin da ake cinikin. Haka nan ya inganta mutum ya shiga bayan an yi cinikin, amma ya fi dacewa a shiga kafin cinikin. Mutum na iya yin Ƙurban tare da

hadin guiwa da wani mutum, ta hanyar sayen kashi ɗaya cikin bakwai ko kashi shida cikin bakwai na sa (ko saniya) mallakin waccan mutumin. Za su raba naman daidai kason abokin hadin guiwar nasa. Idan ɗaya daga cikinsu ya rasu, ya inganta ga magadansa su ce wa abokin hadin guiwar cewa "Ka yi Kurban din a madadinsa da kai kanka." Domin (aikin ibada ne na) ita Kurban ana yin ta ga Musulmin da ya rasu. Idan magadan ba su fadi haka ba, Kurban din ba ta karɓu ba, kuma shi ma abokin hadin guiwar tasa ba ta inganta ba. Idan ɗaya daga cikin abokan hadin guiwar kafiri ne ko kuma ya shiga hadin guiwar ne da nufin ya samu nama kawai, to Kurban ta sauran abokan hadin guiwarsa ba ta halatta ba. Domin dukkansu wajibi ne su yi niyyar Layyar. Niyyar kafiri badil (ɓatatta) ce, mutum ya yi niyyar cin nama, ba (aikin ibadar Layya) Kurban ba ne. haka nan, idan ɗaya daga cikin abokan hadin guiwar ya yi niyyar Kurban ta bana, sauran kuma suka yi niyyar Kurban ta badi, to niyyarsu ta zama badil (ta ɓaci) kuma kasonsu na nama ya zama tatawwu' (sadaka) doh haka dole ne su rabar da shi ga mabukata a matsayin sadaka. Niyyar na farkon ta inganta, amma ba zai iya cin naman ba. Saboda hukuncin cewa dole ne a raba naman a matsayin sadaka ya rinjaye shi. Kurbat da ake yi wa niyya ba dole ba ne ta zamo sai ta wajibi. Tana iya zama Kurbat ta sunnah ko ta nafila. Ta iya zamowa Kurbat da ta shafi ayyukan ibada na wajibi daban-daban. Kazalika ya halatta ta zama 'Akika ga yaro ko babba. (A duba sakin layi nakarshe a babi na hudu na mujalladi na biyar a littafin **Endless Bliss** domin karin bayani a kan Akika). Ita Akika Kurbat ce da ake yi domin nuna godiya da samun haihuwa. Haka nan, walima taro ne na cin abinci, inda ake shirya shagali ga Musulmi domin murnar nikah (ɗaurin aure bisa koyarar Musulunci, wanda aka yi cikakken bayani a kai a babi na goma sha biyu na mujalladi na biyar na littafin **Endless Bliss**), nuna godiya ne da Kurbat da take sunnah. Abin da ya fi falala shi ne, dukkan waɗanda suka yi hadin guiwar su yi niyyar Layya ta ranar Idi. Yanka dabba saboda Akika ba sunnah ba ne a Mazhabar Hanafiyya. Mustahabbi ne ko mubahi. Aikin ibada na mustahabbi Kurbat ne. Shi ma aikin ibada na mubah shi ma Kurbat ne idan an yi ta da niyyar nuna godiya. Akwai ayyukan na al'ada da dama da suka zamo ibada bisa niyyar da aka yi masu. Mubahi yana zama aikin ibada na ɗa'at idan mutum ya yi niyyar hakan. Litattafan Larabci na **'Ukud-ud-durriyya** da **Durr-ul-mukhtar** sun yi cikakken bayani game da yanka dabba domin Akika.]

HAJJI TANA DA RUKUNNAI UKU:

1- Ɗaura niyyar aikin hajji a lokacin da mutum ya shiga ihirami.

2- Yin (tsayuwa da ake kira) wakfa a kan (dutsen) 'Arafat.

3- Yin Ɗawaf-i-ziyarat (a ɗakin Kaba).

Lokacin farko na yin waƙfa (tsayuwa) a ranar ‘Arfa shi ne daga lokacin da rana ta karkata (tsakar rana) a ranar tara ga watan Dhu’llhijja zuwa wayewar gari. [Idan mutum ya yi tsayuwar Arfa a kafin ranar ko ya yi ta kwana ɗaya bayan ranar, hajjinsa ta ɓaci. Wahabiyawa suna yin bikin Idi (ta Ƙurban) kwana ɗaya kafin ranar, ba tare da sun ga jinjirin wata ba (a yammacin jiya). Hajjin mutanen da ba su yi tsayuwar Arfa ba a lokacin da aka shardanta ba ta inganta ba.]

Akwai nau’in ɗawafi guda bakwai (zagayen ɗakin Ka’ba-i-mu’azzama a cikin masallacin Makka) kamar haka:

Na farko shine ɗawaf-i-ziyarat.

Na biyu ɗawafin umara. (waɗannan nau’ukan ɗawafin biyu farilla ne).

Na uku shi ne ɗawaf-i-ƙudum, wanda sunnah ne.

Na huɗu shi ne ɗawafi na wada’i (bankwana).

Na biyar shi ne ɗawafin nazr, wanda yake wajibi.

Na shida shi ne ɗawaf-i-nafila.

Na bakwai kuma ɗawafin taɗawwu’i (tatawwu’ ko tatawwu’), wanda yake mustahabbi ne.

Farilla ne yin niyya yayin shiga ihiramin aikin hajji. Sunnah ne ɗaura fallen tufafi biyu da ake kira ihirami. Wajibi ne a guji sanya ɗinkakken tufafi.

Akwai sharuɗɗa guda takwas da za a cika kafin ya zama farilla ga mutum ya je aikin hajji kamar haka:

1- Mutum ya zama Musulmi.

2- Mutum ya kai shekarun balaga.

3- Mutum ya kai shekarun bambance mai kyau da marar kyau.

4- Mutum ya zamo lafiyayye.

5- Mutum ya zamo ba bawa ba ne.

6- Mutum ya zamo yana da wadatar dukiya bayan ya biya dukkan buƙatunsa na wajibi.

7- Ya zamo lokacin aikin hajji ne. Lokacin aikin shi ne ranar Arfa, da kwanaki huɗu na Idi (ta Layya). Lokacin da aka yi a kan hanya yana daga cikin lissafin.

8- Ga macen da take nesa (da Makka) wadda za ta yi (doguwar tafiya da ake kira) safar, wato tafiya mai tsawon kwanaki uku a ƙafa, ko tsawon kilomita kusan ɗari da huɗu a Mazhabar Hanafiyya, dole ne ta samu rakiyar

ko dai mijinta ko wani namiji muharraminta, wanda ya haramta ta (yi aure na Musulunci tare da shi wanda ake kira) nikah. [Farilla ne ga dukkan mutanen da suka cika wadannan sharuddan su je aikin hajji sau daya a tsawon rayuwarsu. Idan suka je hajji fiye da sau daya, to hajjin da suka yi daga baya ta nafila ce. Aikin **ibada wanda yake nafila** shi ne wanda mutum ya yi da ganin damarsa, wanda ba farilla ba, ba kuma sunnah ba (ya aikata shi). Adadin ladar da ke tsakanin aikin farilla da na nafila bai wuce digon ruwa daya ba a cikin teku. Malaman Musulunci ba su bayar da dama ba ga mutumin da yake zaune a wurin da yake nesa kwarai da Makka ya je aikin hajji sau biyu. 'Abdullah-i-Dahlawi 'kuddisa sirruh' ya fada a cikin kasida ta sittin da uku (ta littafinsa mai suna **Makatib-i-sharifa**) cewa: "Idan mutum ya fara irin wannan tafiyar zuwa aikin hajji, yana da wahala kwarai ya iya ayyukan ibada yadda suka dace. Don haka, Imam Rabbani 'rahmatullahi 'alaih' ya fada a cikin harafi na dari da talatin da uku da na dari da ishirin da hudu (a mujalladi na farko na littafinsa Maktubat) cewa bai amince da a yi tafiyar domin aikin Umara ko hajji ta nafila[1] ba." Aikin hajji na nafila ya haramta idan ya hana mutum aikata ibada, ko ya sa mace ta gaza rufe jikinta da kyau. Tafiya zuwa irin wannan aikin hajjin yana sa mutum ya samu zunubi, maimakon samun lada. Haka hukuncin yake ga irin wannan tafiyar zuwa Umara.

FARILLAI GUDA HAMSIN DA HUDU

Yaro yana zama Musulmi ne a lokacin da ya balaga, haka nan wanda ba Musulmi ba yayin da ya furta **Kalima-i-tawhid**, wato ya ce "**La ilaha il-l-Allah Muhammadun Rasulullah**," kuma ya yi imani da abin da ya furta. Dukkan zunuban da wanda ba Musulmi ba ya aikata, da zarar ya Musulunta, (Allâhu ta'âlâ) ya gafarta masa nan take. Kazalika wadannan mutanen biyu kamar kowane Musulmi, dole ne ya hardace rukunnan imani guda shida, wadanda ake kira Amantu, duk lokacin da suka samu dama, su san ma'anarsu su kuma yarda da su, su ce "Na yarda (da gaskiya) cewa dukkan Musulunci, wato umarni da hani (baki daya) Allâhu ta'âlâ ya bayyana su." Daga bisani, duk lokacin da suka samu lokacin da iko, farilla ne a gare su cewa su koyi abubuwan da suke farilla a kansu, wato wadanda aka bayar da umarni da wadanda aka haramta ko kuma abubuwan da aka hana a koyarwar Musulunci, wadanda suka shafi dabi'u da halaye da sababbin abubuwa da suke fuskanta. Idan suka musanta ko suka ki yarda da cewa farilla ne su san wannan koyarwar ta Musulunci, da kuma cewa farilla ne su aikata wadannan

[1] Wasikokin guda biyu an rubatasu ne ga Molla Tahir Beddakhshi. Akwai wasikun da takaitaccen tarihinsa a harshen Turanci acikin wannan littafin.

farillan, da guje wa aikata wadanda suke haram, to sun yi ridda. Ana iya cewa wanda yayi isgilanci ga daya daga cikin wannan koyarwar, misali, mace ta rufe jikinta (kamar yadda Musulunci ya koyar) to yayi ridda. Sai dai idan wanda ya yi riddar ya tuba bisa laifin da ya aikata, amma ba zai koma Musulmi ba ko da sun furta "La ilaha il-l-Allah" ko su aikata wani aiki da Musulunci ya bayar na umarni, kamar sallah ko azumi ko zuwa aikin hajji, ko aikata kyawawan ayyuka, ko bayar da sadaka. Kuma ba za su samu wani alfanu ba daga wadannan kyawawan ayyukan ba a ranar lahira. Sai sun tuba bisa musantawar da suka yi, wato bisa kin yin imani da daya daga cikin rukunnan Musulunci.

Manyan malaman Musulunci sun zayyana wasu farillai guda hamsin da hudu wadanda dole ne kowane Musulmi ya yarda da su kuma ya aikata su, kamar haka:

1- Ya san cewa Allâhu ta'âlâ shi kadai ne kuma kar ya manta da shi.

2- Ya ci ya sha daga abin da yake halal.

3- Yin alwala.

4-Yin salloli biyar na yini, kowace a kan lokacinta.

5- Idan za a yi sallah a tabbatar an yi wanka na tsarkin jinin al'ada (ga mace budurwa ko babba) da kuma na janaba.

6- Sani da yarda da cewa Allâhu ta'âlâ ke azurtawa.

7- Sanya tufafi na halal mai tsafta.

8- Yin aiki da tawakkul (dogaro) ga Allâhu ta'âlâ.

9- Wadatar zuci.

10- Nuna godiya ga Allâhu ta'âlâ bisa ni'imarsa. Wato yin hakan ta yadda Allah ya umaurta.

11- Rungumar kaddara da ta zo daga Jenab-i-bari tare da sallamawa.

12- Yin hakuri a kan al'amurra. Wato kada a yi bore ko tawaye.

13- Tuba a kan aikata sabo. [Fadar (addu'ar) istigifari kowace rana].

14- Yin ayyukan ibada da ikhlas (wato, bauta wa Allâhu ta'âlâ shi kadai, da neman yardarsa).

15- Ka rika kallon shedanun mutane da aljannu a matsayin abokan gabarka.

16- Yin Riko da Kur'an-i-'adhim-ush-shan a matsayin littafi kuma hujja. Da aiki da hukunce-hukuncensa.

17- Sanin cewa mutuwa gaskiya ce (bisa ikon Allâhu ta'âlâ) da shirya ma zuwanta.

18- Son dukkan abin da Allâhu ta'âlâ yake so, da nisantar dukkan abin da yake ƙi. [Wannan shi ake kira hubb-i-fillah da bughd-i-fillah].

19- Mutum ya girmama iyayensa.

20- Yin umarni da kyakkyawa da hani daga aikata mummuna.

21- Mutum ya ziyarci 'yan uwansa muharramai.

22- Kar mutum ya ci amana.

23- Jin tsoron Allâhu ta'âlâ a kowane lokacin, da guje wa aikata haram.

24- Yin ɗa'a ga Allah 'adhim-ush-shan' da Manzonsa. Wato aikata farillai da nisantar haram.

25- nisantar aikata zunubai da ribantar lokacin wajen aikata ibada.

26- Kar a bijire wa ulu-l-amr (shugabanni) kuma kar a karya doka.

27- Nuna ƙauna ga dukkan halittu da suke zagaye da kai.

28- Yin zikirin wanzuwar Allâhu ta'âlâ, wato ta fuskar girma da ɗaukakarsa da halittunsa.

29- Mutum ya tsare harshensa maganganu na haramun da na rashin ɗa'a.

30- Mutum ya tsarkake zuciyarsa daga ma-siwa [son duniya].

31- Kar mutum ya yiwa wani ba'a.

32- Kar mutun ya kalli (abin da aka haramta kallonsa).

33- Cika alƙawari kamai wahalarsa.

34- Kiyaye kunnuwa daga sauraren duk abin da yake saɓo, kamar maganganun banza da kaɗe-kaɗe.

35- Mutum ya koyi farillai da abubuwan da aka haramta.

36- Yin gaskiya wajen cika ma'auni.

37- Kar mutum ya sakankance game da azabar Allah 'adhim-ush-shan, ya zamo cikin tsoro kodayaushe.

38- Bayar da zakka ga mabuƙata a cikin Musulmi da taimakonsu.

39- Kar mutum ya yanke tsammani ga rahamar Allahu 'adhim-ush-shan.

40- Kar Mutum ya biye wa son ransa.

41- Ciyar da mai jin yunwa domin Allah.

42- Yin aiki tuƙuru domin samun wadatar arziki, [wato abinci da situra da muhalli].

43- Fitar da zakka daga dukiyarka da ushiri a cikin kayan noma.

44- Kar mutum ya sadu da matarsa a lokacin da take jinin al'ada ko na haihuwa.

45- Tsarkake zuciya daga aikata saɓo.

46- Mutum ya guji girman kai.

47- Kula da dukiyar marayan da bai kai shekarun balaga ba.

48- Bai dace nisanta kai daga ma'amala da yara.

49- Yin salloli biyar na yini a kan lokacin, kar a bari su zama ƙara'i (wato kar a jinkirta su har lokacinsu ya fita).

50- Kar ka ci dukiyar kowa.

[Haƙƙi ne ga mutum ya biya kuɗin da ake kira mahr ga matarsa idan zai sake ta. ƙin biyan waɗannan kuɗaɗen yana iya janyo wa mutum hukuncin mai tsananin duniya da azabar lahira. A cikin haƙƙoƙi mutane, amr-bil-ma'ruf ga 'yan uwanka da waɗanda suke ƙarƙashin kulawarka, (wato koyar da su Musulunci), wanda gaza yin hakan zai iya haddasa azaba mai tsanani (a ranar lahira). Duk mutumin da ya kange su da sauran Musulmi daga koyon addininsu da ayyukan ibadarsu, ta hanyar tilastawa da musgunawa, kafiri ne, kuma maƙiyin Musulunci. Misalin wannan su ne 'yan bidi'a da marasa Mazhaba da su kore aƙidar Ahl as-sunnat da ɓatar da Musulmi suna fita Musulunci suna warware imaninsu ta hanyar suka da rubuce-rubuce].

51- Kar mutun ya yi wa Allah 'adhim-ush-shan kishiya (abokin tarayya).

52- Guje wa fasiƙanci.

53- Kar mutum ya sha giya da sauran kayan maye.

54- Kar mutum ya yi ƙarya.

[Giya da sauran kayan maye ƙaba najâsat ne, (ɗaya daga cikin nau'uka biyu na najasar da aka yi cikakken bayani a kai a babi na shida na mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss**). An samo a cikin littafin **Bahr-ur-raiƙ** da **Ibni 'Abidin** cewa idan aka cakuɗa ƙasa da ruwa, taɓon da suka samar ya zama mai tsarki idan ɗaya daga cikin abubuwan biyu yana da tsarki, wannan ƙaulin ingantacce ne, kuma fatawar da aka bayar ta amince da wannan ijtihadin. Sai dai akwai wasu malaman da su nuna cewa fatawar tana da rauni. An rubuta a **'Ibni 'Abidin** da **Hadiƙa** cewa ana iya yin amfani da ƙauli wanda yake mai rauni idan akwai haraj (tsananin). Idan aka gauraya wasu abubuwa da sinadarin giya domin samar da wani abu mai kyau, da ya ƙunshi turare da mai, da magani da lalle na ƙunshi dukkansu masu tsarki ne, gaurayar ma mai tsarki ce. An rubuta a cikin sharhin (da Suleymhan bin 'Abdullah Shi'ridi 'rahmatullahi ta'ala 'alaih' ya yi na littafin **al-Ma'fuwat**

na Molla Halil Shi'ridi 'rahmatullahi ta'ala 'alaih' cewa wannan hukuncin ana amfani da shi har a Mazhaba Shafi'iyya. Ba za su hana sallah ta inganta ba, idan akwai tsananin wajen tsarkakesu. A bisa ra'ayin magabata, duk da tsarkin da wadannan abubuwa suka samu saboda haraj (tsananin wajen tsarkake su), bai halatta a sha su ba sai dai idan akwai lalurar da ta tilasta yin hakan. Kayan maye dangin giya ba masu tsarki ba ne. Saboda ita giyar da ke ciki da wasu sinadarai ba don biyan wata bukata ba, sai don sharholiya. Duk abin da aka gwama su tare ya zama najasa. Haramun ne a sha su ba tare da lalura ba a kowane lokacin].

BAYANI A KAN GHUNAH-I-KABA'IR (MANYAN ZUNUBAI)

Akwai manyan zunubai nau'i daban-daban wadanda ake kira ghunah-i-kaba'ir. Ga jerin guda saba'in da biyu daga cikinsu.

1- Kisan kai ba da hakki ba.

2- Aikata fasikanci.

3- Luwadi da madigo haramun ne a kowane addini.

4- Shan giya da sauran kayan maye na danginta.

5- Sata.

6- Ci ko shan muggan kwayoyi.

7- Karbe dukiyar mutum ta amfani da karfi. Wato kwace.

8- Yin shaidar zur.

9- Cin abinci a gaban mutane ba tare da uzuri ba a cikin azumin watan Ramadan mai albarka.

10- Cin Riba, wato karba ko bayar da rance tare da dora kudin ruwa.

11- Yawan yin ranstuwa a-kai a-kai.

12- Saba wa iyaye.

13- Yanke sila-i-rahm ga dan uwa muharrami wanda yake Musulmi salihi. (Sila-i-rahm na nufin sada zumunta tsakanin 'yan uwa makusanta).

14- Tserewa daga fagen yaki, da guduwa daga cikin sojoji.

15- Yin amfani da dukiyar maraya ba tare da amincewarsa ba. An fada a karshe-karshen shafi na dari biyu da sittin da shida (na bugu na goma) na mujalladi na biyar a littafin **Endless Bliss** cewa: "Mai kula da dukiyar marayu ba zai iya biyan bashin mamaci da dukiyar marayu ba. Kuma ba zai iya biyan fitra na marayun ba, ko ya yi masu layya (a cikin dukiyar marayun).

Amma mahaifin marayun zai iya yi. Idan mai kula da dukiyar ya kasance cikin tsananin buƙata, zai iya yin amfani da dukiyar marayun, amma ba zai iya bayar da ita ga wani ba.”

16- Tauye ma’auni.

17- Yin sallolin farilla biyar kafin shigar lokaci ko bayan fitar lokacinsu.

18- Muzguna wa ɗan uwanka Musulmi.

19- Kirƙiro zance da danganta shi da Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ bayan zancen ba daga Manzon Allah yake ba.

20- Cin hanci da rashawa.

21- Gujewa bayar da shaidar gaskiya.

22- Kin fitar da zakka da ushiri daga dukiyar mutum.

23- Kawar da kai daga hana wani mutum aikata saɓo duk da cewa kana iya hanawa.

24- Kona dabba da ranta.

25- Mutum ya manta yadda ake karatun Kur’an Karim, bayan ya koya.

26- Yanke ƙauna ga rahamar Allah ‘adim-ush-shan.

27- Cin amanar mutane; babu bambanci Musulmi ne ko kafirai.

28- Cin naman alade, wanda haramun ne.

29- Nuna ƙiyayya da zagin ɗaya daga cikin sahabban Rasulullah, ‘ridwanullahi ta’ala ‘alaihim ajma’in’.

30- Cigaba da cin abinci bayan mutum ya ƙoshi; haramun ne yin hakan.

31- Mace ta bijire wa saduwa da mijinta (ba tare da wani dalili ba).

32- Mace ta fita zuwa ziyarar ‘yan uwanta ba tare da yardar mijinta ba.

33- Zargin mace ta gari da aikata fasiƙanci.

34- Annamimanci, wato haɗa husuma a tsakanin Musulmi.

35- Bayyana al’aura ga wasu mutane. [Al’aurar namiji tana farawa ne daga cibiya zuwa guiwarsa. Gashi da hannuwa da ƙafafu suna cikin al’aurarta]. Da kallon al’aurar mutane.

36- Cin naman dabbobin dawa da suka yi mushe. Da kuma dabbobin dawa da aka kashe ba tahanyar da Musulunci ya amince ba, Don hake bai yiyuwa aci.

37- Aikata cin amana.

38- Cin naman ko gulma (ko yi da) Musulmi.

39- Hassada.

40- Yin kishiya ko hadɗa Allah ‘adhim-ush-shan’ da wani wajen bauta. (Ana kiran wannan mummunan aikin da suna ‘shirk’).

41- Kirƙirar ƙarya.

42- Girman kai, mutum ya riƙa tunanin cewa ya fi wani.

43- Mutumin da yake kan gargarar mutuwa ya ce ɗaya daga cikin magadansa ba zai gaje shi ba.

44- Hadɗama wajen tara dukiya da maƙo.

45- Shagala da duniya [ta hanyar haram]

46- Rashin tsoron azabar Allâhu ta’âlâ.

47- Kin yarda da haramcin abin da aka haramta.

48- Kin yarda da halaccin abin da aka halatta.

49- Yarda da maganganun mai duba, game da rayuwar mutane game da ghayb (gaibu, abin da zai faru nan gaba).

50- Fita daga addini, mutum ya yi ridda.

51- Kallon mata ko ɗiyar wani ba tare da uzuri ba.

52- Mace ta sanya situra irin ta Maza.

53- Namiji ya sanya situra irin ta mata.

54- Aikata saɓo a farfajiyar haram-i-sharif (masallatan Makka da Madina).

55- Kiran sallah da yin sallar kafin shigar lokacinta.

56- Bijire wa shugabanni da karya dokokin ƙasa.

57- Kamanta sashen jikin matar mutum da na mahaifiyarsa.

58- Mutum ya yi rantsuwa da mahaifiyar matarsa.

59- Nuna wa juna bindiga.

60- Cin abinci ko shan abin sha wanda kare ya rage.

61- Yin gori ga wani a kan taimakon da ka yi masa.

62- Maza su sanya situra da aka yi da yadin siliki.

63- Nacewa a kan zama cikin jahilci. [Kin yarda da aƙidar Ahl as-sunnat a kan farillai da haramun da sauran wajibai].

64- Yin rantsuwa da wani wanda ba Allâhu ta’âlâ ba, ta hanyar fadɗar sunayen da Musulunci bai amince da su ba.

65- Guje wa neman ilimi.

66- Kin fahimtar cewa jahilci fitina ne.

67- Yawaita aikata manyan zunubai.

68- Kyaƙyatawa wajen yin dariya ba tare da uzuri ba.

69- Zama da janaba tsawon lokacin da zai iya sa mutum ya rasa sallar farilla.

70- Saduwa da mata a lokacin da take jinin al'ada ko na haihuwa.

71- Tsara sautin ƙidã, da waƙoƙi marasa kan gado, da yin kaɗe-kaɗe.

Mirza Maz-har-i-Jan-i-Janan 'rahima-hullahu ta'ala' ɗaya daga cikin manyan malaman ƙasar India, ya faɗa a cikin littafinsa **Kalimat-i-tayyibat** da harshen Farisa cewa: "Manyan Malaman Muslunci sun haɗu a kan cewa, haramun ne yin amfani da kowane irin kayan kiɗa ko saurarensu. Akwai wani zance na malaman da ke cewa mabusa ita kaɗai ce abin da aka karhanta, da kuma cewa mubah, wato ya halatta a kaɗa ganga idan ana bikin aure. [Yin waƙe wajen karatun Kur'an al-karim da kiran sallah haramun ne, idan har ya sauya ma'ana ko aka ƙara wani sauti (da zai kai ga sauya ma'ana). An Faɗa a cikin littafin **al-Fiƙh-u-'alal-Madhahib-ul-arba'a** cewa: "Haramun ne a yi kiran sallah da waƙe. Kuma bai halatta a saurare shi ba." Yin sa cikin furuci mai tsari da murya mai daɗi, ana kiransa **teghanni** ko **sima**.

Teghanni na nufin furuci (karantawa) murya mai rausaya mai daɗin saurare. Karatu iri biyu ne, karatun Kur'an al-karim ko kiran sallah ko maulidi ko ilahis (yabo) da teghanni:

1- Teghanni da yake sunnah wanda ke sa a samu lada, (wato lada a ranar lahira). Shi ne karanta su ta hanyar amfani da tsarin ƙa'idoji da ake kira 'tajwid' (wanda ke koyar da yadda ake kkaranta Kur'an al-karim daidai). Irin wannan teghanni yana ratsa rai da zuciya.

2- Teghanni da aka hana, wanda yake haram, shi ne karanta su cikin muryar waƙa. Wannan teghanni yana haddasa faɗar abu ba daidai ba; ya ɓata sautukansu da sauya masu ma'ana. Irin sautukan da waɗannan suke yi, suna da daɗi ga nafs al-ammara. Suna sa rayukan mutane su sosu su zubar da hawaye, su yi kuka da rausaya, wanda zai haddasa shagalta a kan ma'anarsu, ta yadda ba zai yiwu zukatansu su gaza fita daga shaukin da suka shiga.

An faɗa a shafi na ɗari da sittin da biyu a littafin **Targhib-us-salat** (na Muhammad bin Ahmad Zahid 'rahmatullahi ta'ala 'alaih' wanda ya rasu a 632 H [1234 M.] a India), haka nan a shafi na dubu ɗaya da ɗari uku da arba'in da biyu na mujalladi na biyu na littafin **Bariƙa** (na Muhammad bin Mustafa Hadimi, Konya, Turkiyya), da shafi na ɗari biyar da tamanin da tara na mujalladi na biyu na littafin **Hadiƙa** (na Abd-ul-Ghani bin Isma'il Nablusi, 1050 [1640 M. Damascus – 1143 [1731], a ƙasa ɗaya:) "Kar mutum ya hau dabbar da aka ɗaura wa ƙaraurawa da nufin nishaɗi, domin makaruhi

ne yin hakan. Ita ƙaraurawa kayan kiɗan sheɗan ce. Mala'ikun rahama ba sauka ga ayarin da ke tafiya da dabbobin da aka yi wa ƙawa da ƙaraurawa." Amma ya halatta yin hakan bisa dalili na kasuwanci.

Akwai haɗuwar malamai a kan batun cewa haramun ne mutum ya rera waƙar da ta saɓa wa addini ko ta rashin ɗa'a, ko a rera ta inda ake fasiƙanci, wurin da ake amfani da kayan kiɗa ake kuma shan giya, ko inda ake samun cakuɗuwar maza da mata ko da kuwa waƙar ta dace da Musulunci da ɗa'a, ko sauraren haɗuwarsu suna rera waƙar a wasu wurare waɗanda ake sanyawa a radiyo ko nunawa a talabijin a cikin kaset, ko 'yan mata da samari su riƙa rerawa a tare]. Ya halatta a rera waƙar da ta dace a inda ya dace. Tana kawo natsuwa a cikin rai, wanda zai samu rahama Allâhu ta'âlâ. Wasu malamai akwai abin burgewa ko a cikin mubahi na sima (waƙa). Nuna halin ko'in kula da suke yi ga waƙa, ya samo asali ne daga ɗabi'arsu ta tsantseni wadda ke kange su daga nuna sha'awa a kanta. Wannan keɓaɓɓiyar ɗabi'ar tasu ba ta hana wasu daga manyan malaman musanta ra'ayin takwarorin nasu ba game da waƙa'." Haramun ne karatun Kur'an al-karim da mawlid da ilahis (yabo) ko salati ga Annabi a wuraren da ake fasiƙanci. Ko da akwai girmamawa a ciki. (Wuraren da ake fasiƙanci su ne inda ake aikata zunubai) kafirci ne idan an yi da nufin nishaɗi. An rubuta a cikin littafin **Durr-ul-ma'arif**: cewa: "Kayan kiɗa da muryoyin mata da yara maza Ghina (waƙoƙin saɓo) ne kuma haramun ne. waƙoƙi masu amfani su ne sima' kuma mubahi ne, sai dai idan an yi su da (wani yanayi) da waɗannan muryoyin."

72- Kashe kai, wato mutum ya kashe kansa da kansa, ya fi mutum ya kashe wani munin zunubi. Kashe kai yana gadar da azabar wuta a cikin ƙabari. Idan bai mutu ba a lokacin, ya tuba daga baya, za a yafe masa zunubansa. Ba za a yi masa azabar ƙabari ba. [Ingantacciya (sahihiyar) tuba da aka yi ga sallar da ta kuɓuce ta dogara ne ga ramuwarsu. Mutumin da ya fara ramuwar sallolin da suka kuɓuce kamar ya yi niyyar yin ramuwar ne har ƙarshen rayuwarsa. Saboda wannan niyyar, za a yafe masa dukkan zunubansa. Haka nan idan kafiri ya musulunta, ya tuba a kan zamansa kafiri a baya ko bidi'o'in da ya aikata, kamar sun yi niyyar ba za su sake komawa kafirci da aikata bidi'a ne, kuma ba za su sake aikata saɓon da suka aikata ba a wancan lokacin. Saboda wannan niyyar tasu ta gaskiya, an yafe masu dukkan zunuban nasu].

SASSAN AL-AURA (TSIRAICI) DA SITURTA JIKI GA MATA

An faɗa a babin da yake bayani a kan 'nikah' (aure bisa koyarwar Musulunci) a cikin littafin **Ashi'at-ul-lama'at** (na Abd-ul-Haƙƙ Dahlawi

‘rahmatullahi ta’ala ‘alaih’ ya rayu daga 958H. [1551 M.] – 1052 [1642]) cewa:

1- Abu Hurayra ‘radiyallahu ‘anh’ ya ce: Wani mutum ya zo wajen Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ce “Ina son auren wata mace daga cikin al’ummar Ansar.” Annabin tsira ya ce masa: “**Ka gana da matar** (sau ɗaya). **Akwai wani abu a cikin idanun** (mutanen da suka fito daga) **ƙabilar Ansar**.” An ruwato wannan Hadisin a cikin littafin **Sahih-i-Bukhari**. Sunnah ne mutum ya kalli matar da zai aura sau ɗaya kafin ɗaura auren.

2- Abdullah ibni Mas’ud ‘radiyallahu ‘anh’ ya ce: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Kar mata su riƙa faɗa wa mazajensu kyaun matan da suke gani. Yin haka kamar mazajen nasu sun kalli matan ne**.” An ruwaito wannan Hadisin ne a cikin litattafan **Sahih-i-Bukhari** da **Sahih-i-Muslim**.

3- An karɓo daga Abu Sa’id-i-Hudri ‘radiyallahu ‘anh’ (ya rasu a shekara ta 64H. [683 M.]) cewa: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Kar namiji ya kalli tsiraicin wani namiji, haka nan kar mace ta kalli tsiraicin wata mace**!” Kamar yadda aka gani, haramun ne ga maza su kalli sassan tsiraici na mata, haka nan haramun ne mata su kalli sassan tsiraici na maza, kazalika haramun ne namiji ya kalli tsiraicin wani namiji, ko mace ta kalli tsiraicin wata mace. Tsiraicin namiji wanda yake haramun ga wani naimiji (ya kalla) shi ne tsakani cibiyarsa zuwa guiwa. Haka hukuncin yake ga mata. Tsiraicin mata da ya haramta namiji ya kalla; shi ne dukkan jikinta ban da tafukan hannuwanta da fuskarta. Don haka ake kiran mata da al’aura. Ba tare da la’akari cewa mace Musulma ce ko kafira, haramun ne mutum ya kalli fuskar wadda ba muharramarsa ba da sunan sha’awa, kuma haramun ne ya kalli tsiraicinta ko da ba tare da sha’awa ba.

4- An karɓo daga Jabir bin ‘Abdullah ‘radiyallahu ‘anh’ (ya yi shahada a shekara ta 74 H. [693 M.]) cewa: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Kar mutum ya kwana a gidan macen da ba muharramarsa ba**!”

5- ‘Aƙaba bin Amir ‘radiyallahu ‘anh’ ya ce: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Kar ku keɓe da matar da ba muharramarku ba a cikin ɗaki! Idan mace ta keɓe da ɗan uwan mijinta ko ɗansa, za ta jawo musiba**.” Wato za ta haddasa fitina (wadda za ta yi mummunar illa). Dole ne a yi dukkan mai yiyuwa wajen guje wa aikata hakan. Wannan Hadisin yana cikin litattafan **Sahih-i-Bukhari** da **Sahih-i-Muslim**.

6- Abdullah bin Mas’ud ‘radiyallahu ‘anh’ ya ce: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Jikin mace tsiraici ne**.” Wato dole ne a rufe shi. “**Idan mace ta fita, sheɗan yana bin ta da kallo a kowane lokaci**.” (Wato yana amfani da ita wajen jan hankalin maza su aikata saɓo).

7- An karɓo daga Burayda ‘radiyallahu ‘anh’ cewa: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ce wa sayyidina ‘Ali: “**Ya ‘Ali! Idan ka ga mace ka kauda fuskarka daga kallonta. Kar ka ƙara kallonta! Ba laifi ba idan ka kalle ta ba da gangan ba. Amma saɓo ne ka sake kallonta**.” Abu Dawud da Darimi suka ruwaito shi.

8- ‘Ali ‘radiyallahu ‘anh’ ya ce: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Ya ’Ali! Kar ka bayyana cinyoyinka, kuma kar ka kalli cinyar wani, matacce ko mai rai**!” Wannan Hadisin Abu Dawud da Ibni Maja suka ruwaito shi. Wannan ya nuna kallon tsiraicin mamaci daidai yake da kallon tsiraicin mai rai. [Mu yi bakin ƙoƙarinmu wajen kauce wa kallon tsiraicin masu wasannin motsa jiki da masu ninƙaya a cikin ruwa].

9- Abdullah ibni Umar ‘radiyallahu ‘anh’ (ya rasu a shekara ta 73 H. [692 M.] a Makka) ya ce: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Kar ku bayyana tsiraicinku**! [Kar ku bayyana su ko da kuna keɓe ku kaɗai ne]. **Domin akwai halittun da ba sa rabuwa da kai ko da ka keɓe kai kaɗai. Ka zama mai jin kunyar su tare da girmama su**!” Su ne Mala’ikun da ake kira Hafadha, waɗanda ke kare ka daga aljannu, waɗanda suke rabuwa da mutum a duk lokacin da ya shiga makewayi da lokacin da yake saduwar ma’aurata.

10- An Umm-i-salama ‘radiyallahu ‘anha’ cewa: Maymuna ‘radiyallahu ‘anha’ da ni muna tare da Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yayin da Ibni Umm-i-Maktum ‘radiyallahu ‘anh’ ya nemi izinin shigowa, sannan ya shigo. Yayin da Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya gan shi, sai ya ce mana: “**Ku shige bayan shamaki**!” Sai ne ce, “Ba makaho ba ne? Ai ba zai iya ganinmu ba,” sai fiyayyen halitta ya ce “**Kuma makafi ne? Ba za ku iya ganinsa ba**.” A wani ƙaulin kuma ya ce: “Zamansa makaho ai bai mayar da ku makafi ba kuma.” Imam Ahmad da Tirmizi da Abu Dawud ‘rahimahullahu ta’ala’ suka ruwaito Hadisin. Wannan Hadisin ya nuna cewa, haramun ne namiji ya kalli macen da ba muharramarsa ba, haka nan bai halatta ga mace ta kalli namijin da ba muharraminta ba. Manyan Imamai (malamai) na Mazhabobinnan guda huɗu ‘rahima-humullahu ta’ala’ bisa la’akari da wasu hadisan, sun ce: “Yana da matuƙar wahala ga mace kar ta kalli kai da gashin namijin da ba muharraminta ba. Hukunce-hukuncen da suke da wahalar yi su ne **‘azimat**. Tsiraicin namiji a wurin mace shi ne daga cibiyarsa zuwa guiwarsa. Waɗannan sashen na jiki ba’a yawan ganinsu a waje. Hukunce-hukuncen da suke da sauƙi su ne **rukhsat**.

[Kamar yadda aka gani, Azwaj-i-tahirat (matan Manzon Allah masu albarka, wato uwayen muminai) ‘radiyallâhu ta’âlâ ‘anhuma’ da Sahabbai ‘radiyallahu ‘anhum’ sun fi yin riƙo da hukunce-hukuncen ‘azimat, suna

guje wa rukhsat. Wani zance da bashi da tushe da ke nuna cewa "mata ba sa rufe jikinsu a zamanin Manzon Allah. Yau ga shi muna ganin mata suna rufe jikinsu wanda babu shi a wancan zamanin. Sayyida Aisha ta taɓa fita da kanta a buɗe. Wannan al'adar ta mata su rufe jikinsu malamai masu tsanantawa a Fiƙihu ne suka ɓullo da shi daga baya." Zancen mayaudara ne 'yan Ingila masu yunƙurin yaƙi da Musulunci da zindiƙai. Gaskiya ne cewa rufe jiki ga mata ba ya cikin koyarwar Musulunci a farko-farkon shi. Sai a wani lokaci tsakanin shekara ta uku zuwa ta biyar bayan Hijira (Hijrat) sannan aka umarci mata su riƙa rufe jikinsu. Babanzada Ahmad Na'im Begh (1290 [1872 M.] – August 14th 1352 [1934], Edirnekapi, Istanbul) ya rubuta a (Turkanci) littafinsa mai suna **Tecrid-i-sarih Tercemesi** cewa ayoyin hijab (mata su rufe jikinsu) an saukar da su ne daki-daki a lokutta daban-daban har guda uku].

11- Behz bn Hakim ɗaya daga cikin manyan mutane a cikin Tabi'ai ya karɓo daga babansa da kakansa cewa: Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yana cewa: "**Ku rufe tsiraicinku! Kar ku bari kowa ya gani, baya ga matanku da Jariya (ƙwarƙwarorinku)! Haka nan ku kasance masu jin kunyar Allâhu ta'âlâ**!" Wannan Hadisin Tirmizi da Abu Dawud da Ibni Maja 'rahima-humullahu ta'ala' suka ruwaito shi. Ana kiran Jariya da **mulk-i-yamin**, wanda ke nufin mulk (dukiya) ta hannun dama. Domin ana duba Jariya da hannun dama a lokacin da za a saye ta, kuma ana biyan kuɗin da aka saye ta da hannun dama.

12- 'Umar-ul-Faruƙ 'radiyallahu 'anh' ya ce: Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yana cewa: "**Idan mutum ya keɓe da wata mata da ba muharramarsa ba**, (wato shi da matar su zauna tare a ɗaki ba tare da kowa ba), **sheɗan ne na ukunsu**." Tirmizi ne ya ruwaito wannan Hadisin. [Haramun ne mutum ya keɓe da macen da ba muharramarsa ba, wato mace da namiji su shiga wani keɓantaccen wuri su kaɗai. Ibni 'Abidin ya faɗa a tattaunawarsa ta zama Imam cewa: "Idan akwai wani daga cikin'yan uwan mutumin, namiji ko mace waɗanda ake kira zi-rahm-i-mahram, to abin bai zamo na keɓewa ba."]

13- An karɓo daga Jabir bin 'Abdullah 'radiyallahu 'anh' cewa: Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yana cewa: "**Kar ku ziyarci matan da mazansu ba sa nan! Domin** (idan kuka yi haka) **sheɗan zai riƙa zagayawa a jikinku kamar yadda jini ke zagayawa a cikin jijiyoyinku**." Sai suka ce, "Zai zagaya har a cikin jikinka" sai masoyin Allâhu ta'âlâ ya ce: "**Kwarai. Zai zagaya har a jikina. Sai dai Allâhu ta'âlâ ya taimake ni a kansa. Ya musuluntar da shi, sai ya miƙa wuya gare ni**." Tirmizi 'rahima-hullahu ta'ala' ya ruwaito Hadisin.

14- Umm-i-salama ‘radiyallahu ‘anha’ ta ce: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana tare da ni wata rana (a ɗakina). Bawan ɗan uwana Abdullah bin Abi Umayya yana cikin ɗakin shi ma. Wannan bawan muhanneth (Ɗandaudu) ne. Yayin Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya gan shi, kuma yaji muryarsa, sai ya ce: “**Kar ki ƙara barin irin wannan mutumin ya shigo gidanki**!” Wannan Hadisin yana cikin litattafan **Sahih-i-Bukhari** da **Sahih-i-Muslim**. Muhanneth shi ne mutum (ko yaro) wanda yake ɗabi’a da magana da shiga irin ta mata. An la’anci mutanen da suke yin wannan ɗabi’ar. Wani Hadisi yana cewa: “**Allah ya la’anci maza masu kamanceceniya da mata da matan da suke kamanceceniya da maza**!” matan da suke sanya kaya irin na maza suke aske gashin kansu kamar maza, suke yin wasu ɗabi’u irin na maza, da mazan da suke barin gashin kansu ya yi tsawo kamar na mata, suke yin ɗabi’u irin na mata, ba tare da wani uzuri da ya tilasta masu yin hakan ba, sun shiga cikin la’antar wannan Hadisin.

15- Misɓer bin Mahrama ‘radiyallahu ‘anh’ an haife shi a shekara ta biyu bayan Hijira. Ɗa ne ga ‘yar uwar Abd-ur-Rahman bin ‘Awf ‘radiyallahu ‘anhuma’. Ya ce: Wata rana ina ɗauke da wani dutse mai girma, sai siturar da ke jikina ta saɓule. Na kasa duƙawa in ɗaga ta, da Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya gan ni a wannan halin, sai ya ce: “**Ja siturarka sama! Kar ka fita ba tare da ka rufe jikinka ba.**” Wannan Hadisin yana cikin littafin **Sahih-i-Muslim**. Wannan Hadisin ya shafi maza da mata da suke kasancewa ba tare cikakkar situra ba a kan hanya ko gaɓar teku ko a filayen wasannin motsa jiki.

16- Abu Umama ‘radiyallahu ‘anha’ ta ce: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Idan mutum ya kalli yarinya kyakkawa, sai ya kawar da idonsa, Allâhu ta’âlâ zai ba shi ladar wani sabon aiki na ibada, kuma zai fara ɗandanar daɗinta nan take**.” Imam Ahmad bin Hambal ‘rahima-hullahu ta’ala’ ne ya ruwaito wannan Hadisin.

17- Hasan Basri ‘rahmatullahi ‘alaih’ ya karɓo wannan Hadisin da ke cewa: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ce: “**Allah ya la’anci mutumin da yake bayyana al’aurarsa, da wanda ke kallon al’aurar wani**!” Imam Bayhaki ya ruwaito Hadisin a cikin littafinsa **Shu’ab-ul-imam**.

18- Abdullah ibni ‘Ummar ‘radiyallahuma’ ya ce: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Idan mutum ya yi kamanceceniya da wata ƙabila** (taron al’umma) **to yana cikinsu**!” Imam Ahmad da Abu Dawud ‘rahima-humullahu ta’ala’ suka ruwaito wannan Hadisin. Wannan na nuna cewa idan mutum ya ɗabi’antu ko ya yi wani aiki ko ya sanya situra irin na maƙiyan Musulunci, zai kasance a cikinsu. [Wannan Hadisin zai zamo gargaɗi ga mutanen da suke yin shiga irin ta kafirai, da zane-zane da aka

haramta, da kuma masu kiran waɗanda ke aikata irin wannan haramun ‘masu fasahar zane’ (Artist)].

19- ‘Amr Shu’ayb ya karɓo daga babansa da kakansa cewa: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Allâhu ta’âlâ yana son ganin bawa na amfani da kyautar da ya yi masa**.” Wannan Hadisin Tirmuzi ‘rahima-hullahu ta’ala ya ruwaito shi. Kamar yadda aka gani, Allâhu ta’âlâ yana son ya ga siturar (mutum) cikka kuma mai tsafta. Yana son mutumin da yake yin su (da wanda yake sanya su) su nuna wannan ni’imar. Ba ya son wanda yake yin su (da wanda yake sanya su) suna tinƙaho da alfahari. Bai halatta ba a ɓoye kyautar da Allâhu ta’âlâ ya yi ba. Ilimi shi ma kyauta ne daga Allâhu ta’âlâ.

20- An karɓo daga Jabir bin ‘Abdullah ‘radiyallahu ‘anh’ cewa: Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya zo wani wuri, sai ya ga wani mutum da gashi cikuikuye a gidan. Sai Manzon Allah ya ce: “**Wannan bai samu abin da zai gyara gashinsa da shi ba ne**?” Yayin da ya ga wani da situra mai datti, sai ya ce: “**Wannan ba shi da abin da zai wanke tufafinsa da shi ne**?”

21- Abu-l-ahɓas, ɗaya daga cikin tabi’ai, ya karɓo daga babansa cewa: Na je wajen Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ siturata ta tsufa kuma ta kekkece. Sai ya tambaya “**Ba ka da dukiya ne**?” sai na ce ina da dukiya. Ya ƙara tambaya: “**Wace irin dukiya kake da ita**?” na amsa “Ina da kowace irin dukiya,” daga nan sai fiyayyen halitta ya ce: “**Idan Allâhu ta’âlâ ya ba ka dukiya, ya kamata ya ganta a jikinka**!” wannan Hadisin Imam Ahmad da Nisa’i ‘rahima-humullahu ta’ala suka ruwaito shi. Nan muka kawo ƙarshen bayani daga mujalladi na uku na littafin **Ashi’at-ul-lama’at**.

22- An faɗa a cikin littafin **al-Halal-u-wa-l-haram-u-fi-l-islam** na Yusuf Ƙardawi cewa: Addinin Musulunci ya haramta wa mace ta sanya situra mai shara-shara da za a iya gani ta cikinta. A wani Hadisi da ke cikin litattafan **Sahih-i-Muslim** da **Muwatta** ya ce: “**Matan da suke sanya situra amma tsirara suke da (mata) waɗanda suka yi ƙari a kansu sama kamar tozon rafkumi ba za su shiga aljanna ba. A wani ƙaulin ba za su ji ƙanshin aljanna ba**.” Wannan Hadisin ya hana mata sanya situra mai shara-shara da ake iya gani ta ciki, da matsattsun kaya da yin zanzaro da sanya hula da nannaɗe gashinsu ta saman kai kamar ƙwallo. Yin irin wannan shigar (daidai yake) da fita a tsirara. Bai dace mata da ‘yan mata Musulmai su sanya situra shara-shara da matsattsa ba, kuma kar su nannaɗe gashi ko ƙarin gashi da kamar tozon rafkumi a kansu. Ya kamata su san cewa waɗannan zunuban suna da munin da za su iya kai mutum wuta.

[Wancan Ƙardawin malami ne wanda ba shi da takamaiman Mazhaba, an faɗe shi a farkon littafin. Addinin Musulunci ya shaɗanta cewa farilla ne ga mata su rufe jikinsu da kyau, ya kuma bayyana irin abin da ya kamata a yi amfani da shi wajen rufe jikin. Wannan bayanin bai zurfafa ba a kan irin nau'in yadi da za a yi amfani da shi ba wajen ɗinka sitiru da ake sanyawa ba. An faɗa a cikin litattafan Fiƙihu cewa farilla ne ga mace ta rufe jikinta (a kan yadda aka yi bayani), amma irin nau'in abin da za a rufe da shi, da siturar da za a sanya mas'ala ce ta **sunnat-i-zewaid**, wadda ta ƙunshi sunnonin da suka shafi al'adun mutane, maimakon ibada. Don haka, zai fi dacewa nau'in abin rufe jikin ya zamo wanda al'adar mutane da yadda da shi. Makaruhi ne a yi watsi da al'ada idan abu bai shafi ibada ba. Hasali ma yana iya zama haramun idan dai zai kai ga tayar da fitina. An faɗa a cikin **Hindiyya** cewa: Ya halatta a kalli macen da ta sanya situra mai kauri kuma cikakka. Bai halatta a kalli macen da ta sanya situra da ta matse jikinta ba. Haramun ne mutum ya yi kallon sha'awa ga macen da ta rufe jikinta yadda ya kamata. Makaruhi ne yin hakan ba tare da nufin sha'awa ba. Haka hukuncin yake a kan kallon macen da ba Musulma ba. Wani ƙaulin na malamai ya nuna cewa ya hallata a kalli gashin kanta kaɗai."

Sanya wadatattar situra mai kauri mai duhun kala daga sama har ƙasa zuwa dugadugi ta kuma rufe hannuwa da har zuwa wuyan hannu, ta fi (sanya doguwar riga da ake kira) charshaf wadda aka yi wa sassa biyu. An faɗa a cikin **Halabi-yi-kabir** cewa: "Gashin mace Musulma wanda ya bayyana ya sauko da wurin kunnenta yana cikin tsiraicinta bisa zance da malamai suka haɗu a kai. Haka nan ma wanda ya bi ta ƙƙarƙashin kunnuwan bisa zancen mafi yawan malamai. Wasu malaman sun ce, gashin da ya fiton ba tsiraici ba ne a wajen sallah. Amma bai hallata namijin da ba muharraminta ba ya ga wannan gashin." Dole ne ta rufe dukkan gashinta da kallabi mai kauri, ta dora gabansa a kan goshinta har ya zuwa girarta, ta biyo da gefen biyu ta gefen girarta ta yi ƙasa da shi zuwa haɓarta, sannan ta ɗaure shi a anan, ta saki jelarsa biyu zuwa kirjinta; ta tabbatar wanda ya sauka zuwa bayan kanta ya rufe har saman bayanta. Idan akwai yiwuwar afkuwar wata fitina, sai ta rufe haɓarta. Haka nan dole ne ta yi amfani da zani mai kauri wanda keda duhu. Idan kashi ɗaya bisa huɗu na gashin mace ya zamo a buɗe, har tsawon rukuni ɗaya na sallah, to sallar ba ta inganta ba. Idan kuma wani ƙanƙane ne ya bayyana (tsawon wannan lokacin) hakan ya zama makaruhi. Babu wani littafin na Musulunci da ya rarrabe 'yan mata da tsofaffin mata bisa abin da ya shafi shekaru. Akwai malaman da suka ce ya halatta a amsa gaisuwar tsohuwa ko gaisa (musafaha) hannu da hannu[1] da ita ko keɓewa da ita, (wato kaɗaicewa da ita a cikin ɗaki) amma babu wani malami da ya ce tsohuwa tana iya bayyana gashin kanta (ga mazan da ba muharramanta ba)

su gani. Wasu malaman sun ce ana iya kallon gashin macen da ba Musulma ba. Amma babu ɗaya daga cikinsu da ya ce ya halatta a kalli gashin tsohuwa Musulma. Malaman da suka ce ya halatta ga tsohuwa ta je masallaci da ziyartar maƙabarta, sun nuna cewa dole ne ta rufe gashin kanta da kyau.

Ba daidai ba ne a ce, "An faɗa a cikin aya ta hamsin da tara ta suratul Ahzab, cewa wajibi ne mata Musulmai su rufe jikinsu da **jilbab**. Wannan ayar ta umarce su a kan su rufe jikinsu da abaya, wadda take da ɓangarori biyu." Idan wannan ayar ta umarci mata su sanya gyale, matan Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' da na Sahabbai 'raḍiyallâhu ta'âlâ 'anhum ajma'in da sun sanya gyale. Amma babu wani littafi da ya ruwaito cewa suna sanya gyale. Littafin tafsiri na Turkiyya mai suna **Tibyan** ya yi bayanin wannan ayar da cewa tana umarni ne ga mata "su rufe gashin kansu" An faɗa a cikin littafin littafin tafsir na **Jelaleyn** cewa ita (jilbab) kallabi ne da mata suke ɗaurawa a kai ya rufe har saman fuskarsa. Sawi ya yi bayanin wannan, ya ce: "Ya ƙunshi kallabi da dhir' wato, wani ƙyalle da ake ɗorawa saman situra." An rubuta a cikin litattafan tafsir masu suna **Ruh-ul-bayan** da **Abu-s-su'ud** cewa: "Jilbab kallabi ne da ake ɗaurawa a kan tufafi a kewaye kai da shi domin hana shi ya ɗauki datti; jilbab ya fi ƙyalle marar kauri da ke yafawa fuɗi; yana saukowa har zuwa ƙirji ya kuma rufe jeyb, [wato ya rufe wuyanta baki ɗaya) na mayafi. A wannan ayar, an umarci mata ne su rufe kansu da jikinsu baki ɗaya." litattafan **Zewajir** da **al-Fiƙh-u-'ala-l-madhahib-ul-arba'a** sun ruwaito wani Hadisi da ke nuna jilbab da cewa (situra ce da) maza su ma suna sanyata, ya yi bayanin cewa jilbab na maza doguwar riga ce da ake kira ƙamis. Tsarin siturar mata ta fita waje da suka ƙunshi doguwar riga da kallabi mai kauri da wani nau'in tufafi da ake kira Hijabi wanda aka yi da ɓangare biyu yana daidai da tsarin umarnin da ya shafi mata na rufe jikinsu kamar yadda aka bayyana a sama. Dole ne mata su rufe jikinsu yadda ya kamata da sitirarsu ta al'ada domin gudun kada su jawo fitina. An rubuta a cikin shafi na ishirin da shida a babi na shida na littafin **Sahih-i-Bukhari** cewa an saukar da ɓangaren ayar da ta umarci mata su rufe jikinsu a ranar da aka ɗaura auren Zainab 'radiyallahu 'anha'. An ɗaura auren ne a shekara ta uku bayan Hijira].

Mutumin da yake jin shi cikakken Musulmi ne dole ne ya san ko abin da yake aikatawa ya dace da Musulunci. Idan bai sani ba, wajibi ne ya koya ta hanyar tambayar malaman Ahl as-sunnat ko ta hanyar karanta litattafan da waɗannan malaman suka koyar. Idan abin da zai aikata bai dace da Musulunci ba, to ba zai kuɓuta daga aikata zunubi ko fita daga addini ba. Tuba ta gaskiya ana yin ta ne a kowace rana. Allâhu ta'âlâ yana yafe dukkan zunubai da abubuwan da ke fitar da mutum daga Musulunci idan har mutum ya tuba. Idan mutum bai tuba ba, zai fuskanci azabar duniya da ta wutar

jahannama. Wato za a yi masa azaba. An rubuta ire-iren hukunce-hukuncen azaba da za a yi masa a wurare daban-daban na wannan littafin.

Sassan jikin namiji da na mace da wajibi ne a rufe su a wajen sallah da sauran wurare ana kiransu **sassan tsiraici**. "**Haramun ne bayyana tsiraicin mutum ko kallon tsiraicin wani**." Sunnah ne ga maza su rufe ƙafarsa (misali ta hanyar sanya safa) yayin da yake sallah. Mutumin da ya ce babu sassan jiki na tsiraici a Musulunci ya zama kafiri. Addininmu ya umarce mu a kan mu rufe tsiraicinmu. Duk wurin da ke akwai namiji ko mace da suka bayyana al'aurarsu da wurin da ake kaɗe-kaɗe, ko wurin da ake caca, ko ake shan giya ko wurin da mata suke waƙa, ana kiransu **wuraren fasiƙanci**. Haramun ne halartar wuraren da ake fasiƙanci. Haka nan wajibi ne a tsarkake zuciya. Zuciya mai tsarki ita ce wadda aka ƙawata da kyawawan ɗabi'u. Ana tsarkake zuciya ne ta hanyar ɗa'a ga Musulunci. Mutanen da ke saɓa wa Musulunci ba za su samu tsarkin zuciya ba. Idan mutum ya ce "halal ne" game da bayyana sassan jiki na tsiraici bisa ijma' (haɗuwar malamai) a dukkan Mazhabobi, ko kallon tsiraicin wasu, kuma ba ya fargabar fuskantar azaba saboda wannan saɓon, ya zama kafiri. Haka hukuncin yake ga macen da take bayyana tsiraicinta ko take waƙa ko take maulidi a gaban maza. Sashen jiki da ke tsakanin guiwa zuwa hantsa ba al'aura ba ne a Mazhabar Hambaliyya kaɗai.

Mutumin da ya ce "Ni Musulmi ne" dole ne ya san rukunnan imani da na Musulunci da farilla da haramun waɗanda Mazhabobin nan huɗu suka haɗu a kai, wato wanda ijma' (haɗuwar malamai) suka koyar, ya kuma yi kyakkyawan riƙo da su. Ba uzuri ba ne rashin saninsu. Wannan na nufin kamar mutum ya san su ne kuma ya musanta su. "**Dukkan jikin mace tsiraici ne ban da fuskarta da tafukan hannuwanta**, (wato dole ne ta rufe su) **a dukkan Mazhabobin nan huɗu**." Idan Musulmi ya bayyana sashen jikinsa ko jikinta wanda babu ijma', wato wanda ba tsiraici ba ne a ɗaya daga cikin Mazhabobin kaɗai, ban da sauran ukun, ya aikata babban saɓo bisa koyarwar Mazhabarsu, amma ba su kafirta ba. Misalin wannan shi ne namiji ya bayyana tsakanin guiwa zuwa hantsarsa. Farilla ne ga Musulmi ya nemi ilimi akan abin da bai sani ba. Da zarar sun san hukuncin wannan abun, dole ne su gaggauta tuba su kuma rufe wannan gaɓar tasu.

CIKAKKEN MUSULMI

Akwai haƙƙoƙi guda bakwai da Musulmi ya kamata ya cika game da ɗan uwansa Musulmi:

Amsa gayyatarsa.

Iyâdat [wato ziyartarsa idan ba shi da lafiya].

Halartar jana'izarsa.

Ba shi shawara.

Gaishe shi (kamar yadda aka koyar a babi na sittin da biyu na mujalladi na uku na littafin **Endless Bliss**).

Ceto shi daga hannun azzalumai.

Ce masa **"Ya-r-hamukallah"** idan ya yi atishawa, ya ce **"Al-hamd-u-lillah."**

Musulmi nagari shi ne wanda yake aikata waɗannan ayyukan guda shida:

Yana aikata ibada. Yana koyon ilimi. Baya aikata sharri. Yana gudun haramun. Ba ya sha'awar dukiyar wani. Baya mantawa da mutuwa.

Karin bayani: an faɗa a cikin wani Hadisi cewa: "**Kowane mutum zai so mutanen da suke yi masa alfarma. Wannan halayya ce ta ɗan adam tun asali**." Mutumin da yake biye wa son ransa yana son mutanen da suke taimakonsa ya cim ma burinsa na son rai. Mutum wayayye kuma mai ilimi, a ɗaya ɓangaren yana son mutanen da suke taimakonsa ya zama mutum nagari. A taƙaice mutanen kirki za su so mutanen kirki. Mutanen banza za su so mutanen banza. Za a iya gene yadda mutum yake bisa la'akari da mutanen da yake ƙauna ya zaɓe su a matsayin abokai. Mu riƙa yin fara'a ga kowa da magana mai daɗi, abokai da maƙiya duka, Musulmi da waɗanda ba Musulmi ba, ban da 'yan bidi'a. Alfarma mafi amfani da za a iya yi wa mutane, kyauta mafi tsada da za ka iya bai wa mutane su ne yi masu magana mai daɗi da yi masu murmushi. Idan muka ga mutane suna bauta wa wata dabba, mu ciyar da dabbar abinci a baki, ta dalilin hakan zai iya rage ƙiyayyar da ke tsakaninmu. Kar mu yi jayayya da kowa. Yin jayayya na raba abokanta da kuma ƙara ƙiyayya. Kar muyi fushi da kowa, fushi yana kawo ciwon kai da cututtukan zuciya. Wani Hadisi yana cewa: "**Kar ka zamo mai yawan fushi**!" (A wannan Hadisin Manzon Allah ya shawarce mu a kan mu guji yin fushi).

Mutum yana zama nagari (mai amfani) idan ya ɓoye abubuwa huɗu:

1- Talaucinsa.

2- Sadakarsa

3- Raɗaɗinsa

4- Matsalolinsa.

Aljanna na marmarin mutane huɗu:

1- Mutumin da harshensa yake yawan zikiri.

2- Mutumin da yake hafidh-i-kalamullah.

3- Mutumin da yake ciyar da jama'a.

4- Mutumin da yake yin azumin watan Ramadan.

Kowane mutum kar ya bar ɗaya daga cikin waɗannan abubuwa guda bakwai da za a lissafa a ƙasa:

Su yi Bisimillah a duk lokacin da za su yi wani abu (mai kyau ko mai amfani ko wanda ya halatta). (Yin Bisimillah shi ne faɗar "**Bismillah-ir-Rahman ir-Rahim**).

Su ce "**Al-hamd-u-lillah**," duk lokacin da suka kammala wani abu (mai kyau ko mai amfani ko wanda ya halatta).

Su riƙa faɗar "**Insha-Allah**," duk lokacin da suka ce: misali "Zan je (wani wuri)."

Su ce "**Inna lillah wa inna ilaihi raji'un**," duk lokacin da suka samu mummunan labari.

Su yi tawba da istighfar a duk lokacin da suka faɗi ko aikata wani abu marar kyau. (yin tawba na nufin tuba daga wani zunubi, tare da yaƙini da alƙawari ga Allâhu ta'âlâ cewa ba za ka sake aikata wannan zunubin ba. Yin istighfar na nufin faɗar "Astaghfirullah" wato roƙon gafara daga wajen Allâhu ta'âlâ.).

Su riƙa faɗar Kalima-i-tayyiba a-kai a-kai, wato cewa: "**La ilaha il-l-Allahu wahdahu la Sharika lah, lahul-mulku wa lahul-hamdu wa huwa 'ala kulli shay'in ƙadir**."

Su riƙa furta Kalima-i-sharifa a-kai a-kai, wato, faɗar "**Ash-hadu an la ilaha il-l-Allah wa ash-hadu anna Muhammadan 'abduhu wa Rasuluh**."

Su riƙa faɗar wannan dare da rana:

1- "**Astaghfirullah**."

2- "**Subhanallah wa-l-hamd-u-lillahi wa la-ilaha il-l-Allahu wallahu akbar wa-la-hawla wa-la ƙuwwata illa billah-il'aliy-yil 'adhim**."

ABIN DA YA SHAFI AKHL Â K-I-HAMIDA

(Kyawawan Ɗabi'u)

Akwai kyawawan ɗabi'u guda saba'in da biyu da za su sanya mutum ya zamo mai nagarta:

Iman; yarda da Ahl as-sunnat; ikhlas; ihsan; tawadu'; dhikr-i-minnat; nasihat; tasfiya; ghayrat ghibta; sekha; isar; muruwwat; futuwwat; hikmat, shukr; rida; sabr; khawf; raja; bughd-i-fillah; hubb-i-fillah; hamul; istiwa-i-dham wa med-h; mujahada; sa'y; ƙasd; 'amal; dhikr-i-mawt; tefwidh; teslim;

talab-ul-‘ilm; sela-‘ahd; inzaj-i-wa’d; husn-i-khulƙ; zuhd; ƙanaat; rushd; sa’y-i-fi-l-khayrat; riƙƙat; sewƙ; haya; thebat-i-fi emrillah; unsu billah; shawƙu ila liƙaillah; waƙar; dhekawat; istiƙamat; adab; firasat; tawakkul; sidƙ; murabata; muraƙaba; muhasaba; muataba; khadm-i-ghaydh; hubb-i-tul-i-hayati li ‘ibadatihi; tawba; khushu’; yaƙin; ‘ubudiyyat; mukafat; ri’ayat-i-huƙuƙ-i-‘ibad.

Tawadu’ na nufin nagarta; dhikr-i-minnat na nufin sanin cewa duk wani ɗa’at (aikin ɗa’a ga Allâhu ta’âlâ) yana kai wa ga shiriya, da taimako da jin ƙai daga Allahu adhim-ush-shan, da nuna godiya ga (Allâhu ta’âlâ) a kan wannan; nasihat na nufin yin gargaɗi ga ɗan uwanka Musulmi; tasfiya na nufin kore akhlaƙ-i-dhamima (miyagun ɗabi’u) daga zuciya, tare da ƙawata ta da akhlaƙ-i-hamida; ghayrat na nufin yin riko da imani; ghibta na nufin neman albarka daga wajen masu ita; sekha da futuwwat (su biyun) suna nufin yawan kyauta; isar na nufin taimakawa wajen maganin matsalar ɗan uwanka Musulmi; muruwwat na nufin yi wa al’umma hidima; hikmat na nufin mutum ya san ilm-i-hal (koyarwar Musulunci a abin da ya shafi ibada da Musulmi zai aikata) da kuma aiki da ilimi; shukr na nufin yin amfani da ni’imomin da aka ba mutum a wurin da ya dace (ta halin da ya dace) bisa koyarwar Musulunci; rida na nufin mutum ya yi farin ciki da tsarin rayuwa da Allâhu ta’âlâ ya yi masa; sabr kuma na nufin haƙuri a jarabawar da ta sami mutum.

[Ri’ayat-i-huƙuƙ-i-‘ibad na nufin mutum ya kula da haƙƙoƙin bayin Allah, (wato mutane). Haƙƙi mafi muhimmanci a ciki shi ne ƙƙhaƙƙin iyaye. Da kalamai masu dadi da sakin fuska, dole ne mu yi gaugawar taimaka masu, mu dukkan abin da ya kamata domin mu faranta masu rai. Daga wannan sai haƙƙin maƙabta, sai ƙƙhaƙƙin malamai da ƙƙhaƙƙin ma’aurata, sannan ƙƙhaƙƙin abokai da haƙƙin Gwamnati. Kar mu yi ƙarya ga kowa kuma kar mu zalunci kowa, haka nan mu cika ma’auninmu da biyan ma’aikata haƙƙinsu kafin gumin jikinsu ya bushe. Cin amana ne mutum ya ƙi biyan bashi, ko ƙin biyan kuɗin mota na tafiya da ya yi da makamantansu. Kin biyan haraji ga gwamnati, domin yin hakan yunƙuri ne na rashin adalci ga dubban mutane. Idan misali gwamnati tana zaluntar jama’a, har ta kai ga jama’ar sun yi bore ga gwamnatin, to bai halatta ka taimaka wa masu boren ba, kamar yadda aka rubuta a babin da ke magana a kan fitina a cikin littafin **Bariƙa**, haka nan a cikin litattafan **Fatawa-i-Hindiyya** da **Durr-ul-mukhtar**. An faɗa a cikin wani Hadisi cewa: “**Idan mutum ya yi tawaye ga gwamnati, Allah zai hukunta shi**.” Wato zai lalata boren ya kuma kunyata shi [Nibras]. *A kan haka, kar mu yarda da rubuce-rubucen da ake yaɗawa da suke tunzura Musulmi su yi tawaye waɗanda mutanen nan marasa Mazhaba ke yi, irin su*

Sayyid Kutb da Mawdudi. Tawaye ba abu ba ne mai kyau, ko da an yi shi ne ga azzalumar gwamnati, kuma a shawarce kar mutum ya goyi bayan masu tawaye. Sa'ilin da Ibni 'Abidin 'rahima-hullahu ta'ala' yake bayani a kan cewa haramun ne maza su sanya tufafi na siliki, ya ce: "Ya halatta a shimfiɗa yadin siliki ko a baje kolin zinare da azurfa ba tare da an yi amfani da su a wajen bukukuwan sallar Idi da ɗaurin aure da nufin bin umarnin gwamnati, ba don alfahari ba. Yana daga cikin ɓannar dukiyar a kunna wuta ko kunna kendir, ko kuma kunna wutar sainbod din tallace-tallace domin jan hankalin jama'a da rana tsaka . Ya halatta mutum ya sanya 'ya'yansa a makarantar da ke haɗe da yara maza da mata, idan gwamnati ce ta bayar da umarnin hakan. Wurin da bai kamata Musulmi ya halarta ba shi ne inda aka cakuɗe maza da mata kuma sannan kuma mutanen ke bayyana tsiraicinsu." An rubuta a cikin **Ibni 'Abidin** a babin da ke bayani a kan 'sallar Juma'a' da 'zama Alƙali', cewa bai halatta mutum ya bijire wa dokokin (gwamnatin) kafirai. Wasu malaman Musulunci sun ce, ba za a karɓi aikin ibadar da aka aikata ta hanyar tauye haƙƙin bayin Allah (jama'a) ba, kuma ba zai taimaki masu ibadar su shiga aljanna ba. Haka nan an faɗa cewa, bayar da haƙƙin wanda ba Musulmi ba ya fi tsanani a kan bayar da haƙƙin Musulmi. Dole ne mu kyatata mu'amala da kowa, kuma kar mu biye wa masu aikata saɓo. Musulmi na ƙwarai shi ne wanda yake bin umarni da hanin Allâhu ta'âlâ da dokokin gwamnatinsa.]

Samun suhubar waliyyi mai albarka tana da wuyar gaske,
Mutanen da suka kai matsayinta ta, ba za su bari ta kuɓuce masu ba.

Mutum ya duba gida da waje domin ya samu irin wannan mutumin,
Mai canjin kuɗi shi ya san darajarsu ba ɗan caca ba.

Idan ka sanya rufaffen gora a cikin kogi na ruwa,
Ko da tsawon shekaru arba'in ne, za ka same shi a bushe.

Kusanci yana wanke zuciya, har aljanna ta ƙaunace shi;
Ai ba situra da jikin namiji ce kan saka shi nagarta ba.

Abu na farko, ka yi imani, ka guji aikin haramun;
Kasani, abincin da rai kebuƙataya wuce biskit da gyaɗa!

BAYANI A KAN DARAJOJIN SAHABBAI

A cikin dukkan Sahabban Manzon Allah, Halifofinsa guda huɗu ‘radiyallâhu ta’âlâ ‘anhum ajma’in su ne suka fi daraja. Halifancin su duka huɗun ya wanzu ne tsawon shekaru talatin. [Gaskiyar magana ita ce, dukkan Sahabbai ‘radiyallâhu ta’âlâ ‘anhum ajma’in’ za su shiga Aljanna. Bai halatta a soki ko ɗaya daga cikinsu ba].

Karamomin Waliyyai gaskiya ne (haƙƙ)[1]

Hadrat Abu Bakr as-Siddiƙ ‘radiyallâhu ta’âlâ ‘anh’ shi ne ya fi kowa daraja, kuma mafi ɗaukaka a cikin Waliyyai (Awliya). Halifancinsa gaskiya ne. Kasancewarsa Halifa na farko wannan tabbataccen abu ne bisa ijma’ (haduwar malamai a kan Sahabbai). Shi surukin Rasulullah sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ne. Ya aurar da ɗiyarsa Aisha ‘radiyallahu ‘anha’ ga Rasulullah sallallahu ‘alaihi wa sallam’. Yana da ilimi mai zurfi a kan Haƙiƙat. Ya kashe baki ɗayan dukiyrsa bisa hanyar gaskiya, (hanyar Musulunci), har ya kai ga ba shi da komai. Ya riƙa ɗaura ganyen dabino a ƙugunsa yana rufe jikinsa. Mala’ika Jibril ‘alaihis-salâm’ ya yi shiga ta irin wannan ya ziyarci Manzon Allah. Yayin da Manzon tsira ya ga Mala’ikan a wata irin shiga da bai saba gani ba, sai ya tambaya “**Ya ɗan uwana Jibril! Ban taɓa ganin ka a irin wannan shigar ba, ina mamakin abin da yake faruwa**.” Sai Jibril ‘alaihis-salâm ya yi masa bayani: “Ya Rasulullah (ya Manzon Allah)! Yadda ka ganni a irin wannan shigar, dukkan mala’iku ma a haka suke. Dalili shi ne: Allahu Adhim-ush-shan ya ce: ‘**Bawana Abu Bakr ya salwantar da dukkan dukiyarsa saboda girmana kuma ta hanyata. Yanzu ya yi tufafi da ganyen dabino. Ya ku mala’ikuna, ku yi koyi da shi**!’ Sai dukkan mala’iku suka yi wannan shigar.” Daga lokacin aka riƙa kiran Hadrat Abu Bakr da ‘Siddiƙ’.

Waliyyi na biyu mafi daraja bayansa, shi ne ‘Umar ‘radiyallahu ‘anh’. Halifancinsa ya samu jagoranci ne da ijma-i-ummat (Amincewar Sahabbai). Yana da zurfin ilimin a kan sassan ilimin Musulunci. Wata rana wani Bayahude da wani munafiki[2] suka zo wurin Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ suna neman ya warware jayayya da ke tsakaninsu. Hadrat Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya saurari jawabansu, ya gane Bayahuden ke da gaskiya (sai Manzon Allah ya bai wa Bayahuden

---

[1] Wannan al’adar Allâhu ta’âlâ’s ’âdat-i-ilâhiyya ya halicci abubuwa ta hanyar sabab. Misali abin da ya fi ruwa nauyi yakan nutse acikin ruwa. Wani lokaci Allah ya kan baiwa wasu daga cikin zaɓaɓɓun bayinsa mu’jiza da karama kamar Annabawa da Waliyai. Idan abin mamaki ya faru daga annabi ana kiranta Mu’jiza, sannan idan ta faru ta wajen Waliyyi ne ana kiran wannan abun mamakin Karama.

[2] Munafiki shine wanda bai yi imani ba sannan ya ikirarin zama musulmi, yana zama tare da musulmai harma yana yin wasu daga cikin nau’uka na bauta a tare cikin jam’i.

gaskiyarsa). Yayin da munafikin ya ƙi karɓar wannan hukuncin, Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ce: “**Ya ku waɗannan mutane! Ku je wajen ‘Umar ya yi maku shari’a**!” sai suka tafi wajen Hadrat ‘Umar ‘radiyallâhu ta’âlâ ‘anh’. Sai Sahabin mai albarka ya tambaye su abin da ke tafe da su, sai munafikin ya ce: “Muna jayayya ne ni da wannan Bayahuden.” Hadrat ‘Umar ‘radiyallahu ‘anh’ ya ce: “Ta yaya zan yi hukunci a tsakaninku tare da sanin cewa wanda yake da addinin Musulunci (Manzon Allah) yana tare da mu?” Sai munafikin ya ce: “Mun je wajen Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya bai wa Bayahuden nan gaskiya. Ni kuma ban yarda da hukuncin ba.” Daga nan sai ‘Umar radiyallâhu ta’âlâ ‘anh’ ya ce: “Ku jira ni a nan zan zo maku da mafita,” sai ya shiga daga ciki.

Bayan wani ɗan lokaci sai ya dawo ɗauke da wuƙa boye a cikin tufafinsa, yana zaro ta sai ya fille kan munafikin. Sannan ya ce: “Wannan shi ne hukuncin da ya dace da wanda bai amince da hukuncin Rasulullah ba.” Bisa wannan dalilin ne ake kiransa da suna ‘’Umar-ul-Faruƙ ‘radiyallâhu ta’âlâ ‘anh’ har ya zuwa yanzu.

Hadrat Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Umar ne yake bambance gaskiya da ƙarya**.”

Waliyyi na uku mafi daraja bayansa shi ne ‘Uthman-i-Zinnurayn ‘radiyallahu ‘anh’. Ya yi Halifanci bisa gaskiya da adalci. Wannan gaskiya ce da ijma’-i-Ummat (bisa haduwar Sahabbai) suka tabbatar. Rasulullah ‘sallallâhu ta’âlâ ‘alaihi wa sallam’ ya aura masa ‘ya’yansa guda biyu ɗaya bayan ɗaya. Bayan da ɗiyarsa ta biyun ta rasu, sai ya ce: “**Idan da a ce ina da wata ɗiyar, da na ƙara ba shi ita**.”

Yayin da Manzon Allah ya aura wa ‘Uthman radiyallahu ‘anh’ ɗiyarsa ta biyun, sai ya girmama shi ƙwarai. Bayan tajwij (hidimar aure) sai ɗiyar ‘yar albarka ta ce: “Ya mahaifina! Kana girmama Hadrat Uthman sosai. Bai cancanci yabo haka daga gare ka ba!” Sai Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ce wa ɗiyar tasa: “**Ya ke ‘yata! Mala’iku da ke sama suna jin haya** (kunyar) **Hadrat ‘Uthman**!”

Saboda Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ba shi auren ‘ya’ya har biyu (ɗaya bayan rasuwar ɗaya) ya sa ake kiransa ‘Uthman Zinnurayn. Zinnurayn na nufin ma’abocin haske biyu. Yana da ilimi mai zurfi a kan Ma’rifat (Ilimin sanin Allâhu ta’âlâ).

Waliyyi na huɗu mafi daraja bayansa shi ne ‘Ali ‘karramallahu wajhah wa ‘radiyallahu ‘anh’. Ijma’-i-ummat sun tabbatar da gaskiya da adalcin Halifancinsa. Surukin Rasulullah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ne. Manzon Allâhu ta’âlâ yaba shi auren ‘yarsa Fatima ‘radiyallahu ’anha’. Yana da zurfin ilim a kan Tariƙat. Yana da wani Ghulam (bawa). Wata rana wannan

bawan ya yi niyyar gwada ubangidan nasa. Yayin da ya shigo ya sanya bawan ya yi masa wani aiki, sai bawan ya yi shiru. Bayan nan Hadtar ‘Ali karramallahu wajhah ya tambaya: “Ya kai Ghulam! Me na yi maka na ba daidai ba, me na yi maka na cutarwa?” Sai bawan ya ce: “Babu wani abu na ba daidai ba da ka yi mani. Ni bawanka ne. Na yi haka ne kawai domin in gwada ka. Kai waliyyi ne na gaskiya.”

[Musulmai da ke son Ashab-i-kiram (Sahabbai) suke bin sawunsu, ana kiransu **Ahlus Sunnah** (ko **Musulmi Sunni**). Waɗanda ke cewa suna son wasu daga cikinsu, suke kuma nuna ƙiyayya ga mafi yawa a cikinsu ana kiransu **Shi’i** (‘yan Shi’a). Waɗanda kuma suke cutar da Sahabbai ana kiransu **Rafidawa**. Mutumin da ke iƙirarin yana son dukkan Sahabbai, amma ba ya bin kowane daga cikinsu ana kiransa **Wahhabi**. **Wahabiyanci** gamin gambiza ne da ra’ayoyin bidi’a na wani malami da ake kira Ahmad ibni Taymiyya, da ƙarairayin wani ɗan leƙen asiri na ƙasar Ingila mai suna Hempher. Suna kiran Ahl as-sunnat da ‘kafirai’ saboda sun ƙi amincewa da koyarwar Wahabiyanci. [Wannan iƙirarin nasu ya koma a kansu, ya mayar da su kafirai da kansu].

Wani Baturen Ingila da ke yankin ƙasashen Larabawa ya ƙirƙiro wahabiyanci a shekarar 1150H. [1737 M.]. Sun zubar da jinin Musulmi da dama a ƙoƙarinsu na yaɗa wannan manufar ta Ingila. Yanzu suna kafa cibiyoyin Wahabiyanci waɗanda suke kira **Rabita-t-ul ‘alam-il-islami** a kowace ƙasa, suna farautar marasa ilimin addini, ta hanyar ba su kuɗi. Ta wannan hanyar ne suke ɓatar da al’ummar Musulmi. Suna ɓata sunan malaman Ahl as-sunnat, waɗanda suka bai wa Musulunci kariya tsawon shekaru fiye da dubu ɗaya da ɗari huɗu da Ottomans ke ba su kariya. Suna kore koyarwar Musulunci ta gaskiya wadda waɗannan malaman suka cirato daga nassoshi (ayoyi da Hadisai).

Wasu Wahabiyyawan suna cewa, “Mu ma muna bin Mazhabin Sunnah ne. Muna bin Mazhabar Hanbaliyya.” Wannan iƙirarin nasu daidai yake da iƙirarin da ‘yan bidi’ar da ake kira Mu’tazilawa, waɗanda ke cewa “Mu ma mabiyan Sunnah ne a cikin Musulmi. Muna binMazhabar Hanafiyya ne.” Suna faɗar haka ne saboda sun san cewa mutanen da ba sa cikin Ahlus Sunnah za su shiga wuta. Gaskiyar magana ita ce, ko da wasu ayarin mutane suna ayyukan ibada na addini da suka yi daidai da na Mazhabobin nan huɗu, ba shi yake tabbatar da waɗannan mutanen suna bin wata Mazahaba ba. Zamowa ɗaya daga cikin mai bin wata Mazhaba yana buƙatar yin riƙo da koyarwa da yarda da kuma ayyukan ibada na wannan Mazhabar. Dukkan Mazhabobin nan huɗu suna kama da juna ta fuskar koyarwa da imani. Kasancewar mutum mabiyin Hanafiyya ko Hanbaliyya yana buƙatar yin riƙo

da abubuwan da wannan Mazhabar ta Ahlis Sunnah ta yarda da su. Wahabiyawa ba su yi riƙo da koyarwar Sunni ba.]

BAYANI A KAN ABINCI DA YADDA AKE CINSA

Akwai alfanu guda goma game da wanke hannuwa kafin cin abinci ganin cewa Sunnah ne (wanke hannun a lokacin):

Idan mutum ya wanke hannunsa kafin ya ci abinci ya sanya jiƙaƙƙen yatsansa manuniya a kusurwar marfin idonsa ya ja shi baya a kan fatar idonsa da ke rufe har ya kai ƙarshe, da yardar Allâhu ta'âlâ wannan mutumin ba zai yi ciwon ido ba. Alfanun guda goma su ne:

1- Mala'ikan da ke ƙarƙashin 'Arsh-i-Rahman zai ce: Yadda ka wanke hannuwanka, haka aka yafe maka (ƙananan) zunubanka.

2- Zai samu lada kamar ya yi sallar nafila.

3- Za a tsare shi daga talauci.

4- Zai samu lada daidai da wadda ake bai wa Siddiƙai.

5- Mala'iku za su roƙa masa gafara (istighfar).

6- A kan kowace lomar abinci da ya yi, zai samu lada gwargwadon kamar ya bayar da abinci baki ɗaya sadaka.

7- Za a kankare masa zunuban sa, idan dai har ya fara ci da Basmala.

8- Duk addu'ar da ya yi bayan ya kammala cin abincin za a karɓa masa.

9- Idan ya mutu a wannan daren, zai samu lada daidai da ta shahidi.

10- Idan ya mutu da rana, za a sanya sunanshi a cikin shahidai.

Akwai falala guda shida a kan wanke hannu da niyyar aikata wani aiki na sunnah:

1- Mala'ikan da yake ƙarƙashin Al'arshi zai ce: "Ya kai wannan Mumini! Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yana farin ciki da kai."

2- Za ka samu lada ta musamman da aka ajiye wa wannan aikin mai albarka.

3- Ladar da mutum zai samu za ta kai yawan gashin jikinsa.

4- Mutum zai samu kaso a cikin kogin Rahama (tausayin Allâhu ta'âlâ).

5- Mutum zai samu ladar gwargwadon ruwan da ya zuba daga hannunsa.

6- Mutum zai mutu a matsayin shahidi.

[Dokokin Allâhu ta'âlâ sun kasu zuwa gida biyu muhimmai, Amr-i-takwini da Amr-i-taklifi ko Amr-i-tashri'i.

Amr-i-takwini: shi ne faɗarsa "**Zamo**" ga abubuwan da yake nufin halitta. Wannan abin zai samu da zarar ya ce, "Zamo!" babu wanda zai hana wannan abin ya kasance. Ya halicci wasu abubuwan saboda sauran halittu masu rai. Haka nan ya halicci wasu sinadarai domin halittar wasu abubuwan, Kazalika ƙarfin jiki da kuma ruhin mutum da sauran karsashi, sun zamo sanadin halittar wasu abubuwan da dama. Idan ya ga damar bayar da wata baiwa mai kyau ga bawansa, sai ya sanya bawan ya samu sila ta samun wannan baiwar. Idan silar ta samu, idan kuma ya ce wa wannan abin "Zamo!" Wannan abin (baiwar, da sauransu) sai su kasance. Babu wani abu da yake samuwa har sai ya so. Ya lulluɓe Hikimarsa da Halittarsa da sila. Mutane da yawa suna kallon silar ne, amma ba sa ganin Hikima da Hallitar a bayan silar. Wannan rashin fahimtar yana kai wa ga halaka.

Amr-i-taklifi: Ya ƙunshi dokokin Allâhu ta'âlâ waɗanda ya sanya wa mutane game da abubuwan da suka kamata a yi da waɗanda za a guji aikatawa. Waɗannan dokokin nasa sun dogara ne ga 'yancin mutum na yin zaɓi. Ya bai wa mutum 'yanci na yi wa kansa zaɓi. Sai dai shi ne ya halicci abubuwan da mutum zai yi da waɗanda ba zai yi ba. Idan mutum ya so aikatawa ko ƙin aikata wani abu, Zai iya halicce shi idan ya ga dama. Kuma idan ya ga dama ba zai halicce shi ba. Shi kaɗai ne ya halicci dukkan komi, sannan ya samar da abubuwan masu amfani daban-daban. Babu wani mahalicci bayan shi. Yarda da cewa waninsa yana da martaba ta uluhiyyat (abin bauta) yana nufin yi wa Allâhu ta'âlâ kishiya. Ya shaɗanta cewa ba zai yafe wa duk wanda ya haɗa shi da wani wajen bauta ba a ranar lahira, zai yi azaba mai tsanani ga duk wanda ya aikata haka. Idan mutane suka bi dokokin Sa suka yi ayyuka masu kyau, zai ɗora su a kan tafarki nagari bisa jin ƙansa da ganin damarsa. Idan mutanen da suka kafirce suke saɓa masa suka so yin mummunan aiki, Shi da ganin damarsa zai halicci mummunan aikin. Idan mutanen da suka yi imani da Shi suke roƙonsa suka so yin wani mumman aiki, Shi kasancewarsa mai Rahama ba zai ga dama ya halicci wannan mummunan aikin ba. Don haka, saboda maƙiyansa suna samun nasara wajen biyan munanan buƙatunsu, sai su ƙara tsunduma cikin aikata ɓarna.

An tsara Amr-i-taklifi na Allâhu ta'âlâ bisa muhimmancin su kamar haka:

1- Ya bayar da umarnin dukkan mutane su yi imani su zamo Musulmai.

2- Ya umarci waɗanda suka yi imani kar su aikata haramun da munanan ayyuka.

3- Ya bayar da umarni ga waɗanda suka yi imani su aikata farillai.

4- Ya umarci Musulmi da suka guje wa haram, suke aikata farillai, su guji aikata makaruhi, sannan su aikata sunnoni da sauran ibada ta nafila.

Bisa wannan tsari na sama, ba a yarda ka tsallake wanda ya fi muhimmanci ka aikata na ƙasa da shi ba wajen tsarin muhimmanci; ba a son haka. Ba ya da amfani. Idan mutum ya guji aikata munanan ayyuka ba tare da ya yi imani ba, ko ya aikata farillai ba tare da ya guje wa aikata munanan ayyuka da haramun ba, ko ya aikata sunnoni da nafila ba tare da aikata farillai ba, Allâhu ta'âlâ ba zai so shi ba, kuma ba zai karɓi ayyukansa ba. A kan haka, idan Musulmi ya ƙi yin sallah ko ya ƙi fitar da zakka, ko ya ƙi bayar da haƙƙin iyayensa ko matarsa ko 'ya'yansa, Allâhu ta'âlâ ba zai karɓi ayyukansa masu kyau ba, waɗanda suka ƙunshi sadaka ko tallafi ko gudunmuwa ko gina masallatai ko tallafin kuɗi ko wanke hannuwa kafin da bayan cin abinci ko aikin 'Umra. Kamar yadda aka gani, dole ne kowa ya aikata awamir-i-taklifiyya bisa tsarin da aka yi a sama. A wani ɓangaren kuma, idan mutum ya aikata wani abu wanda bai kai muhimmancin na ajin da ke samanshi ba, idan har hakan ya kai ga farilla ta kuɓuce masa ko ya aikata haramun; ba zai samu wata lada ba, amma bai kamata ya bar wannan aikin kyakkyawa ba. An rubuta a cikin littafin Tafsiri mai suna **Ruh-ul-bayan**, a ƙarshen babi na shida cewa, saboda albarkar wannan kyakkyawan aikin da yake yi yau da gobe, ana fatan cewa, Allâhu ta'âlâ cikin rahamarsa zai taimake shi da aikata waɗannan dokokin maɗaukaka].

Akwai farillai guda huɗu na cin abinci:

1- A yayin cin abinci da shan abin sha, a san cewa ana ƙoshi ne da izinin Allah 'adhim-ush-shan.

2- Cin abincin da yake halal.

3- Yin amfani da ƙarfin da mutum ya samu sakamakon cin abincin, wajen gudanar da ayyukan ibada a matsayinka na bawan Allâhu ta'âlâ.

4- Samun wadatar zuci daga abin da mutum ya ci.

Kafin mutum ya fara cin abinci, zai yi niyyar neman ƙarfin jiki domin bauta wa Allâhu ta'âlâ, da yin abubuwa masu amfani ga bayin Allâhu ta'âlâ, da samar da zaman lafiya da kwanciyar hankali ga addinin Allâhu ta'âlâ zuwa ga dukkan al'umma. Ya halatta mutum ya ci abinci da kansa a buɗe.

Mustahabban cin abinci: Ajiye kwanon cin abinci a ƙasa (maimakon teburin cin abinci); sanya tufafi masu tsafta yayin zaman cin abinci; zama a kan guiwa; wanke hannuwa da baki kafin cin abinci; yin Basmala, (wato faɗar "Bismillah-ir-Rahman-ir-Rahim,") yayin fara cin abinci, ɗandana gishiri kaɗan kafin fara cin abincin; cin burodi da aka yi da garin filawa; gutsirar burodin da hannu; kar a zubar da ɓantalen burodin; mutum ya ci

abincin daga gabansa; shan ruwan tsami (ɓinegar) kaɗan; cin burodin kaɗan; tauna abincin da kyau; cin abincin da yatsu uku; suɗe kwanon abinci da yatsa; lashe yatsun sau uku; yin Hamdala bayan kammala cin abincin; yin sakace.

Makaruhan cin abinci: cin abinci da hannun hagu; sunsuna abincin da kake ci; ƙin yin Basmala; [za a iya yin Basmala a duk lokacin da aka tuna ta, ko da an yi nisa wajen cin abincin].

Haramun na cin abinci: Cigaba da cin abinci bayan mutum ya ƙoshi; [idan kana ci tare da baƙonka, mutum zai yi kamar yana cin abincin domin gudun kar ya hana baƙon ya cigaba da ci; kar a ɓata abinci; wasu malaman sun ce, yin Basmala yayin cin abincin da aka karɓa daga wani (bisa zalunci); zuwa taron cin abinci da ba a gayyace ka ba; cin abincin wani ba tare da izininsa ba; cin abincin da zai cutar da lafiyarka; cin abincin da aka samar da nufin aikata riya (yin abu ba don Allah ba); cin abincin da aka yi rantsuwa a kai.

Cin abinci mai zafi yana cutarwa kamar haka: yana haddasa kurumta; yana koɗar da hasken fuska; yana sanya duhun idanu, yana sanya idanu su zamo ɗorowa; yana kashe ɗanɗanon baki; yana haddasa rashin ƙoshi; yana dakushe fahimta; yana gurɓata rai; yana cutar da jiki.

Cin abinci kaɗan yana da amfani kamar haka: Yana sa ƙarfin jiki; yana haskaka zuciya; yana ƙara kaifin basira; mutum zai yi rayuwa mai sauƙi; mutum zai ji daɗin gudanar da aikinsa; za ka yi zikirin Allahu ‘adhim-ush-shan sosai; zai riƙa tunatar da kai lahira; zai sa mutum ya ji daɗin ibada; mutum zai riƙa tunani mai zurfi da hangen nesa a dukkan al’amurransa; za a yi masa hisabi mai sauƙi (a ranar lahira).

Duk mutumin da ya ce “Ni Musulmi ne;”
Salloli biyar na yini sun wajaba a kansa.
A ranar tashin ƙiyama da ke tafe ba daɗewa,
Ga tufafi da rawanin sarauta, da doki da zai ɗauke shi.

HUKUNCE-HUKUNCEN AURE

Akwai alfanu masu yawa da ke tattare da aure.

Da farko, zai zamo garkuwa ga imaninka. Zai samar maka da kyawawan ɗabi’u. Za a sanya albarka ga abin da kake samu. Ka aikata aiki wanda yake Sunnah. Batu na gaskiya, Manzon Allah yana cewa: “**Ku yi aure**, (wato, yin aure ta hanyar Musulunci da ake kira ‘nikah’) **ku hayayyafa. Domin in yi alfahari da yawan al’ummata** (Musulmi)**ranar tashin ƙiyama, fiye da sauran al’umma**.”

Dole ne miji da mata su kula da haƙƙin junansu.

Mutumin da yake shirin yin aure, wajibi ne ya yi bincike sosai har ya samu yarinya (ko mace) da take saliha, (wato mai riƙo da addini wadda ba muharramarsa (‘yar uwarsa ta kusa wadda musulunci ya hana aure tsakani) ba ya aure ta. Ya halatta a auri macen da ta yi ciki ta hanyar fasiƙanci. Idan wanda ya yi fasiƙancin wani mutum ne daban, bai halatta a yi waty (saduwar aure) kafin haihuwa ba (Fatawa-i-Fayziyya)[1].

Kar mutum ya auri mace saboda kyaunta ko dukiyarta. Domin zai iya haddasa ƙiyayya. Manzon Allah ‘sallallâhu ta’âlâ ‘alaihi wa sallam’ yana cewa: “**Idan mutum ya auri mata saboda dukiyarta ko kyaunta, za a hana masa amfana da dukiya da kyaun nata**.”

Idan mutum ya auri mace saboda tsoron Allanta da kyawawan ɗabi’unta, Allâhu ta’âlâ zai ƙara mata yawan dukiya da kyau.

Mata tana ƙasan mijinta ta wurare huɗu: Shekarunta da matsayinta da asalinta da nasabarta. Ita kuma mata ana so ta ɗara mijinta da abubuwa huɗu: Ta zamo kyakkyawa, ta zamo mai ladabi ta zamo mai kyawawan ɗabi’u, ta kuma guji aikata haram da abubuwan zargi, kuma kar ta bayyana gashin kanta da hannuwanta da ƙafafunta ga waɗanda ba muharramanta ba.

Kar yarinya ta auri tsoho. Hakan zai iya haddasa ɓarna (wanda ke nufin mummunan aiki).

Kafin a fara shirye-shiryen aure, iyayen ma’auratan za su gudanar da bincike game da su, wanda sunnah ne wanda zai taimaka wajen cigaba da shirye-shiryen auren. Malamai sun ce, wannan yana samar da alfanu guda uku: Na farko za a samu soyayya mai ƙarfi a tsakanin ma’auratan; na biyu za a samu albarka (tari, da bunƙasa) a arzikinsu (rayuwa da wadatar abinci); na uku sun yi abin da yake sunnah.

Daga nan za a gudanar da ƙa’idoji da sharuɗɗa bisa tsarin doka. Babban saɓo ne yin (aure) nikah da bai dace da ƙa’idar sunnah ba. Kuma laifi ne ƙin kammala matakan ɗaurin auren.

Ya halatta ga mata ta janyo hankalin mijinta da kwalliya; yana sa a samu lada (a ranar lahira).

Sunnah ne yin walimar cin abinci a ranar aure. [Ana cin abincin dare ne bayan sallar isha’i. daga nan za a kai ango wurin amaryar sa, bayan sun yi masa addu’o’i da sanya albarka sai kowa ya yi tafiyarsa.

---

[1] Fayzullah Efendi of Erzurum, na ƙasar Turkiyya ‘rahmatullâhi ta’âlâ ’alaih’ (wanda yayi shahada a garin Edirne a shekarar 1115 [1703 A.D.]), babban Shaikh-ul-islâm na araba’in da shida a daular Ottoman.

Sunnar da ya kamata ango ya yi a darensa na farko shi ne ya wanke ƙafar amaryar sa sannan ya kuma yayyafa ruwan a ko'ina a cikin gidan. Zai yi sallah raka'a biyu ya yi addu'o'i. Duk addu'ar da ya yi a wannan daren karɓaɓɓa ce (a wurin Allâhu ta'âlâ). Mutane idan sun ga angon sai riƙa ambaton wannan. Su ce "**Barakallahu laka wa barakallahu 'alaiha wa jama'a baynakuma bi-l-khayri**," wadda ke nufin "Allah ya sanya maka albarka a ciki, ya sanya albarka ga matarka a ciki, kuma ya sanya Alkhairi a tsakanin ku!" Wasu mutane suna taya sababbin ma'aurata murna ta hanyar cewa "Ina maku fatan alheri, ina maku fatan samun ɗa da bayi!" Wannan zancen jahilci ne marar amfani. Sunnah ne yin addu'o'in da aka koyar na wannan lokacin.

Dole ne ka san abubuwan da suka wajaba a addini ka koyar da matarka. Domin za a tambaye ka game da su a ranar lahira. Rashin sani ba zai zamo uzuri a gare ka ba. [farilla ne a koyi farillai da haramun da koyarwar Alhalus Sunnah da aƙidarsu, sannan ka koyar da su ga matarka da 'ya'yanka. Haka nan sunnah ne koyon sunnoni, sannan ka koyar da su].

Kar ka sake ka tura matarka zuwa wurin da Musulunci bai yarda ba! Kar ka fita da ita ko ka bar ta ta fita waje ba tare da ta rufe jikinta yadda ya kamata ba. Domin Manzon Allah 'alaihis-salâm' ya ce: "**Idan mace ta zo masallacinmu tana ƙamshi da nufin yin sallah,** (Allâhu ta'âlâ) **ba zai karɓi sallar wannan matar ba, har sai ta koma gida ta yi wanka kamar wankan janaba**." Tun da bai halatta su je masallaci suna ƙamshi ba, to sai mu duba girman zunubin da za ta samu idan ta je wani wurin tana nuna kanta ga jama'a. Mu kwatanta, sannan mu auna irin azabar da za su iya fuskanta!

Manzon Allah ya faɗa a cikin wani Hadisi cewa: "**Mafi yawan 'yan aljanna talakawa ne** (a rayuwarsu ta duniya) **sannan mafi yawan 'yan wuta mata ne**!" Sai Hadrat 'Aisha 'radiyallahu 'anha' ta tambaya: "Meye dalilin da ya sa mafi yawan 'yan wuta suka zamo mata?" sai Rasul 'sallallahu 'alaihi wa sallam ya amsa mata: "**Ba sa nuna juriya idan musiba ta faɗa masu. Idan wani da yake taimakonsu a kullum, misali ya taimake su sau goma, ya yi masu ba daidai ba sau ɗaya, za su yi ta mitar wannan abin na ba daidai ba, su manta da waɗancan taimakon goma da ya yi masu. Sun ruɗu da ƙyale-ƙyalen duniya ba su tanadi komi ba a lahira kuma suna da yawan gulma**."

Dukkan mutanen da suke da irin wannan munanan ɗabi'un 'yan wuta ne, ko da maza ne ko mata duka.

Hadrat 'Ali 'karramallahu wajhah' ya ce: Wata rana wata mata ta zo wajen Rasulullah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' ta ce: "Ya Rasulullah (ya Manzon Allah)! Ina son auren wani mutum. Meye shawararka mai albarka? Sai fiyayyen halitta ya ce: "**Namiji yana da tarin haƙƙoƙi a kan matarsa, za ki iya sauke su**?" Sai matar ta ce: "Ya Rasulullah! Waɗanne

haƙƙoƙi ne na miji?" sai ya amsa mata: "**Idan kika ɓata masa rai, kin yi tawaye ga Allah, kuma ba za a karɓi sallarki ba**," Matar ta sake cewa: "Akwai wasu haƙƙoƙin? Rasulullah sallallahu 'alaihi wa sallam ya amsa: "**Idan mace ta fita daga gidanta ba tare da izinin mijinta ba, za a rubuta mata zunubi a dukkan sawu ɗaya da ta taka** (a cikin littafinta na ayyuka). Matar ta ƙara tambaya: "Akwai wasu haƙƙoƙin?" sai Rasul-i-kiram ya ba ta amsa mai kyau cewa: "**Idan mace ta munana magana ga mijinta, za a fito da harshenta ta cikin wuyanta a ranar lahira**." Matar ta sake cewa: "Akwai wasu haƙƙoƙin?" Rasul-lulAllah (Manzon Allah) ya amsa: "**Macen da take da dukiya, amma ba ta biyan buƙatun mijinta za ta tashi ranar lahira da baƙar fuska**." Wannan matar ta cigaba da tambaya: "Akwai wasu haƙƙoƙin?" Rasul- ya amsa: "**Idan mace ta saci wani abu daga dukiyar mijinta, ta bai wa wani, Allahu adhim-ush-shan ba zai karɓi zakka da sadakarta ba, har sai ta nemi gafarar mijinta, kuma ya yafe mata**." Matar ta sake tambaya: "Akwai wasu haƙƙoƙin?" A nan sai Manzon Allah ya ce: "**Idan mace ta yi wa mijinta rantsuwa ko ta ƙi yi masa ɗa'a, za a ratayeta ta harshenta a cikin ramin wuta, haka nan idan mace ta fita ta je wajen da ake rawa da kaɗe-kaɗe ta saurare su, har ta ba da kuɗi, za a shafe ladar dukkan ayyukan ta na alkhairi waɗanda ta yi tun daga ƙuruciyarta sannan tufafin da ta riƙa sanyawa za su yi ƙararta, su ce, 'Ba ta sanya mu a ranakun bukukuwan addini ba, da lokacin da take tare da halal ɗin ta (mijinta) ba; ta sanya mu a wurare na haramun da ta je.' Daga nan sai Haƙƙ ta'ala ya ce: 'Zan ƙona wannan matar tsawon dubban shekaru**.'" [Daga yanzu ya kamata mu lura da irin ɓarnar da shirye-shiryen gidajen sinema da radiyo da talabijin suke yi]. Yayin da wannan matar ta ji waɗannan amsoshin sai ta ce: "Ya Rasulallah! Ban kai ga yin aure ba yanzu, kuma nan gaba ma ba zan yi ba."

A wannan lokacin sai Rasul-ull-Allah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' ya yi ƙarin bayani, ya ce: "**Ya Khatun** (Ya ke wannan mata)! **Bari kuma in faɗa maki albarkar da ke cikin auren namiji; ki saurara! Idan miji ya ce da matarsa 'Allah ya yi maki albarka da girmanSa,' ya fi ki yi ibada ta shekaru sittin. Idan ta bai wa mijinta ruwan sha, ya fi azumin shekara ɗaya lada. Idan ta yi wankan tsarki bayan saduwar aure da mijinta, za ta samu ladar kamar ta yi Kurban** (layya). **Idan ba ta yaudari mijinta ba, mala'iku daga sama za su riƙa yin tasbihi**[1] **a madadinta. Idan ta yi wasa na faranta rai da mijinta za ta samu albarka fiye da ta 'yanta bayi sittin. Idan ta kare dukiyar mijinta ta tausaya wa 'yan uwansa, ta yi sallah biyar na farilla, ta yi azumi**

[1] Yin tasbihi na nufin cewa, "Subhânallah," wanda ke nufin "tsarki ya tabbata ga Allah" ko kuma "na san Allah ya nisanta daga dukkan wata tawaya ko naƙasu" Yin tasbihi yana samar da lada mai tarin yawa a ranar lahira.

(na Ramadan) **ya fi ta ziyarci ɗakin Kaba sau dubu lada**." Fatima-i-Zahra ‘radiyallahu ‘anha’ (‘yar Manzon Allah) ta tambaya: “Me zai faru da mace idan ta saɓa wa mijinta?” sai fiyayyen halitta ya ce: “**Idan mace ta ƙi yin ɗa’a ga mijita za ta dawwama cikin tsinuwar Allah har sai mijin nata ya yafe mata; idan ta ƙi zuwa shimfiɗarsa domin saduwa, za ta yi asarar dukkan ladarta; idan ta yi masa girman kai, za ta shiga cikin fushin Allâhu ta’âlâ; idan ta ce masa ‘shin kai mutum ne mai shisshigi?’ ko ta ce ‘Amfanin me ka taɓa yi mani?’ Allâhu ta’âlâ zai haramta mata samun albarkarsa. Ko da za ta riƙa lashe jinin da yake zuba a jikin mijinta da harshenta, bai ishe ta biyan haƙƙinsa ba. Idan mijinta ya bar ta ta fita ba tare da ta rufe jikinta yadda ya kamata ba, za a rubuta zunubi dubu a littafin mijinta na ayyuka bisa barinta da ya yi**.” Wannan zai taimaka wajen fahimtar tsananin zunubin mace idan ta fita ba da izinin mijinta ba!

Rasul-i-akram ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya ce: “**Ya Fatima! Idan da Allâhu ta’âlâ ya umarci wani mutum ya yi sujada ga wani, da na umarci mata su yi sujada ga mazajensu**.”

Hadrat Aisha ‘radiyallahu ‘anha’ ta ce: na tambayi Rasulullah ya yi mani wasiyya. Sai Manzon tsira ya ce: “**Ya ‘Aisha! Zan yi maki wasiyya, ke kuma ki isar da wannan wasiyyar ga sauran matan al’ummata! Yayin da aka tashi mutane domin yin hisabi a ranar lahira: da farko za a yi tambaya a kan imani. Na biyu za a yi tambaya a kan alwala da sallah. Ga mata tambaya ta uku za a yi masu ita ne a kan** (haƙƙoƙin) **Mazajensu. Idan mutum ya yi haƙuri da wautar matarsa, Haƙƙ ta’ala zai ba shi lada gwargwadon wadda aka bai wa Annabi Ayyub (Job). Idan mace ta yi haƙuri da mugun hali na mijinta, Allâhu ta’âlâ zai ɗaukaka darajarta zuwa ta ‘Aisha-i-Siddiƙa.**

“Idan miji ya doki matarsa zan yi shari’a da shi a ranar lahira,” shi ma wannan Hadisi ne na Rasul-i-akram ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’.

Akwai dalilai uku da suka halatta miji ya doki matarsa tafin hannu ko ƙyalle: Idan ta ƙi yin sallah ko wankan tsarki ko ta ƙi zuwa shimfiɗarsa ko ta fita ba tare da izininsa ba. Ba a yarda ko ta halin ƙaƙa ya doke ta da sanda ko da damtsen hannu ko ya harbe ta ko ya yi amfani da ƙullallen ƙyalle, ko ya doke ta a kai ko gangar jiki. Kuma ba koyaushe ake dukanta ba, sai an yi mata gargaɗi sau biyu, idan ba ta gyara ba, sai ka ƙyale ta kar ta azabtar da kai.

[An faɗa a cikin **Shir’at-ul-islam** cewa: “Idan matar mutum tana aikata ɗabi’u na wauta, to ka tuhumi kanka. Ka ce wa kanka “Ba za ta aikata haka ba idan ni na kirki ne. Idan matarka ta zamo nagartacciya, kar ka auri mata ta biyu. Bai halatta ba ga mutumin da ba zai iya adalci a tsakanin iyalansa ba ya auri mata ta biyu. Idan ya san cewa zai iya adalci, to ya halatta a gare shi

(ya auri mata ta biyu). Amma ya fi dacewa a gare shi kar ya yi hakan. Idan matarka ta fita zuwa wuraren da suka halatta, dole ne ta sanya kallabi, sannan ta rufe jikinta baki ɗaya. Haramun ne ga mace ta fita tana ƙamshin turare tare da bayyana kayan adonta. Mace ta gari ita ce mafi jin daɗin rayuwar duniya. Tausayawa da karimci ga Musulmi ya fi ibadar nafila lada." An rubuta a cikin **Riyad-un-nasikhin** cewa: aya ta goma sha takwas ta Suratun Nisa'i tana cewa: "**Ku kyautata hali da karamci ga matanku**!" Wannan Hadisin yana cewa: "**Ya Aba Bakr! Idan mutum ya yi magana cikin murmushi da karimci ga matarsa, za a ba shi lada gwargwadon kamar ya 'yanta bawa**." Haka nan "**Allah ba zai tausaya wa macen da ta auri fasiƙi ba**." Haka nan "**Duk wanda yake son cetona, kar ya bayar da ɗiyarsa a matsayin mata ga fasiƙi**." Wani kuma "**Mafi alherin mutane shi ne wanda yake kyautata wa mutane. Mafi sharrin mutane shi ne wanda yake cutar da mutane**." Da kuma "**Cutar da Musulmi ba bisa haƙƙi ba, ya fi rushe ɗakin Kaba muni sau saba'in**."

An daɗa a cikin **Durr-ul-Mukhtar** cewa: daga lokacin da mutum ya yi aure na Sunnah da mace (ta zama matarsa) ya zama farilla a gare shi ya samar mata (abubuwan buƙatun rayuwa da ake kira) nafaƙa. **Nafaƙa** sun ƙunshi abinci da tufafi da wurin zama. Dole ne ya zaunar da matarsa a gida ko dai mallakinsa ko kuma wanda ya karɓa haya. Mata tana da damar cewa ba ta buƙatar wani ɗan uwan mijinta ya shigo gidan. Shima mijin yana da damar cewa ba ya buƙatar wani ɗan uwan matarsa ya shigo gidan. Dukkansu biyun suna da wannan ikon. Ya kamata gidan ya zamo a unguwar Musulmi ne. [Ya kamata a jiwo muryar Ladan daga gidan (ba tare da an yi amfani da lasifika ba, domin bidi'a ce amfani da ita wajen ayyukan addini).] Miji ba shi da ikon hana mata ta fita domin ziyarar iyayenta sau ɗaya a mako. Su ma suna da damar ziyartar ɗiyarsu sau ɗaya a mako. Idan ɗaya daga cikinsu ba shi da lafiya, ya zamana babu wani wanda zai kula da shi, matar ta je ta kula da iyayenta ko da mijinta bai yarda ba. Miji ba shi da ikon hana 'yan uwanta muharramai su ziyarce ta, ko ya hana ta ita ma ta ziyarce su sau ɗaya a shekara. Idan kuma ya bari ta ziyarci wasu daban ko ta je wurin da ake aikata saɓo, dukkansu sun haɗu wajen aikata saɓo. Haka nan ya hana ta yin aiki na albashi ko kyauta a gida ko a wani wuri, da fita zuwa makaranta ko wa'azi. Mace ta riƙa sadaukar da lokacinta wajen aikin gida; kar ta zauna haka nan. Kar ya bari ta je wuraren da mutane ke bayyana tsiraici, da suka ƙunshi wurin wanka [da gaɓar teku, ko inda ake kallon wasannin motsa jiki. Kar ya sanya talabijin a gidansa inda za a iya kallon waɗannan abubuwan.] Kar ya bari ta fita waje da kayan ado ko sababbin tufafi." Yana iya fita da ita zuwa wuraren da Musulmin da ke guje wa haramun suke zama, ko da ba muharramanta ba ne, wato 'yan uwanta na kusa waɗanda suka haranta ta aura; amma duk da

haka za a raba wurin zama na maza da mata. **Muharraman mace** su ne maza guda goma sha takwas kamar haka: Mahaifinta, da kakanta, ɗanta da jikanta; ‘yan uwanta, har da waɗanda take uwa ɗaya ko uba ɗaya kaɗai da su; ‘ya’yan ‘yan uwanta mata ko maza; ‘yan uwan mahaifinta ko na mahaifiyarta. Waɗannan mazajen guda bakwai muharramanta ne idan suka samu dangantaka ta hanyar shayarwa ko fasiƙanci. Wasu mazan huɗu kuma suna zama muharramanta ta hanyar aure (wanda aka yi bisa tsarin Musulunci). Su ne: Surukinta (da ya haifi mijinta) da kakan mijinta; surukinta (wanda ya auri ɗiyarta), wanda ya auri mahaifiyarta da wanda ta auri mahaifinsa. Haka nan surukan ‘ya’yansa mata haka nan ga mace surukan ‘ya’yanta maza suma muharramai ne. Muharramai na nufin waɗanda ba za a iya aure ba. Misali ‘yar uwar mutum (yaya ko ƙanwa) muharramarsa ce. ‘Ya’yan ‘yan uwa duka muharramai ne. Matar ɗan uwan mutum da matan ‘yan uwan mahaifiya da na mahaifi da ‘ya’yan ‘yan uwan mahaifiya da na mahaifi ba muharramansa ba ne. ‘ya’yan ‘yan uwan iyaye da mazansu na aure ba muharramai ba ne, ‘yan uwan miji da ‘yan uwan mata ba muharramai ba ne. haka nan mijin ‘yar uwa ko na ‘yar uwar iyaye da ‘yan uwan mijinta ba muharramai ba ne ga mace. An rubuta a cikin littafin **Ni’imat-i-islam**, a babin da yake bayani a kan aikin Hajji cewa: Haramun ne ga mace ta bayyana kanta ga waɗannan mutanen ba tare da ta rufe jikinta baki ɗaya ba kamar yadda Musulunci ya tanada, ko ta keɓe da su a ɗakin da ke rufe ko da ta rufe jikinta ko ta yi (doguwar tafiya da ake kira) safar da su. Haka nan kakanninta mata na kowane ɓangare muharramai ne ga mijinta. Mace ba za ta iya auren muharraminta ba. Ya halatta ta zauna a cikinsu ba tare da ta rufe jikinta baki ɗaya ba kamar yadda za ta rufe idan tana tare da waɗanda ba muharramanta ba. Tana iya kaɓewa da muharraminta a cikin ɗaki wanda yake rufe ko yin doguwar tafiya tare da shi. Idan ɗaya daga cikin ‘yan uwanta wanda ba muharraminta ba ya ziyarce ta, za ta ce masa “maraba” a gaban mijinta ko wata mace wadda take ‘yar uwarta tare da rufe jikinta baki ɗaya ban da fuskarta. Za ta ba shi abin sha. Amma ba za ta zauna a wurin ba. Ya kamata Musulmi su yi riƙo da koyarwar litattafan Musulunci, maimakon al’adu. Dole ne ga kowane Musulmi ya koyar da matarsa shika-shikai da rukunnan Musulunci, idan ba shi da ilimi sosai, sai ya tura ta wajen wata mata mai ilimi wadda take saliha abin yarda ta koyar da ita. Idan bai samu macen da take ɗa’a ga Musulunci take kuma gudun haram ba, sai ya zauna tare da matar su riƙa karanta litattafan da suke koyar da Musulunci daidai waɗanda malaman Alhalus Sunnah suka rubuta; ta haka zai sa ta san Musulunci da imani da haram da farillai duka. Kar ya kawo litattafan tafsir na ‘yan bidi’a gidansa waɗanda wasu malamai da ba su da Mazhaba suka rubuta; bai kamata a riƙa karanta irin waɗannan litattafan ba. Kar ya kawo rediyo da

talabijin da ake yaɗa shirye-shiryen da suka saɓa wa Musulunci da tarbiyya. Waɗanda sharrin su ya fi na zama da sheɗanin mutum. Suna ɓata imani da kyawawan halayen na mata da ‘ya’ya. Ya kamata matan aure da ‘ya’ya su duƙufa wajen aikin gida; bai kamata su yi aiki a waje ko masana’antu ko bankuna ko kamfanoni ko aikin gwamnati ba. Bai kamata mata da ‘ya’ya mata su riƙa taimaka wa mazaje da iyaye maza wajen sana’a ko kasuwanci ba. Aikin namiji ne yin dukkan waɗannan, da kuma kawo masu abubuwan buƙatu na cikin gida a shaguna da kasuwanni su kawo masu gida. Idan aka tilasta wa mace yin hakan, za a cutar da imani da ɗabi’a da kuma lafiyarta. Za a lalata duniyar su da lahirar su duka. Za su yi nadama mai tsanani, baya ga cewa ba za ta yi masu amfani ba. Domin ba za ta kare su daga zunubi da halaka ba. Mutumin da ya yi ɗa’a ga Musulunci zai samu wadata a nan duniya da kuma lahira. Mu yi riƙo da koyarwar litattafan Musulunci, kar mu yarda mu bi yaudarar murmushi da kalamai na yaudara na miyagun abokai da munafukai. Mu kare ‘ya’yan mu mata da maza daga aikata haramun. Mu tura ‘ya’yan mu makarantar da ke da malamai da suke Musulmi. Mace ba ta buƙatar yin aiki cikin maza a shaguna da kamfanoni ko aikin gwamnati. Idan ba ta da miji, ko mijin nata ba shi da lafiya, sai muharramin ta ya riƙa kawo mata dukkan kayayyakin buƙata. Idan ya kasance ‘yan uwan nata ba su da hali, sai gwamnati ta riƙa biyan ta wasu kuɗaɗe na alawus. Allâhu ta’âlâ ya sanya dukkan buƙatun mace a gabanta. Ya wajabta wa maza ɗaukar nauyin al’amurran rayuwa. Don haka mace ba ta buƙatar yin aiki domin ɗaukar ɗawainiyar kanta, ya bai wa mace rabi a tsarin rabon gado. Aikin mace ya tsaya ne a harkokin cikin gida. Kuma aiki na farko mafi muhimmanci shi ne tarbiyyar ‘ya’ya. Malamar farko (murshid) ta yaro ita ce mahaifiya. Idan yaro ya koyi addini da kyawawan ɗabi’u daga mahaifiyarsa, malamin da ba shi da addini ba zai taɓa iya ɓatar da shi ba ko wani mugun aboki, ko kuma daga ƙarairayin zindiƙai maƙiyan Musulunci. Zai zamo Musulmi na ƙwarai kamar iyayensa. A duba babi na goma sha biyu a mujalladi na biyar da kuma babi na goma sha biyar a mujalladi na shida na littafin **Endless Bliss**! Munafikan da suka riƙa cutar da Musulunci su ake kira **zindiƙ**].

BAYANI a kan TEJHIZ da TEKFIN da TEDFIN na JANAZA (Yadda ake WANKA da SANYA LIKAFANI da BINNE MAMACI MUSULMI)

Yin sallar janaza da yin wanka da sanya likafani da binne Musulmi dukkansu ayyukan ibada ne na farilla.

Ana yi wa mamaci wanka ne ta hanyar kwantar da gawarsa a kan bayansa a kan siminti ko wani katako a keɓaɓɓen wuri. Za a cire masa tufafi. Za a yi masa alwala. Za a wanke maɗaukakin jikinsa daga kai zuwa cibiyarsa da ruwa mai ɗumi. Sannan za a wanke daga cibiyarsa zuwa guiwa wanda yake a rufe. Mutumin da yake masa wankan zai sanya safar hannu a hannunsa na dama. Za su sanya hannun (mai safa) ƙarƙashin kyallen da aka rufe wurin, ya zuba ruwa yana wankewa. Kar su kalli wajen da aka rufen. Sannan a juya gawar zuwa hagunta a wanke sashen dama; daga nan sai a juya ta zuwa damanta a wanke sashen hagun da hannun mai safa. Za a shimfiɗa ɗaya daga cikin fallen likafani uku a naɗe gawar a ciki. Daga nan sai a sanya gawar da ke cikin likafanin a cikin makara.

Likafani ya kasu kashi uku (kefen): Kefen-i-fard, [wanda kuma ake kira kefen-i-darurat;] kefen-i-sunnat; da kefen-i-kifaya.

Kefen-i-sunnat ga maza falle uku ne, ga mata kuma falle biyar ne.

Kefen-i-kifaya ga maza falle biyu ne, kefen-i-kifaya ga mata kuma falle uku ne.

An faɗa a cikin **Bahr-ur-raiƙ** cewa: “Kafen-i-kifaya ga mata shi ne izar, da lifafa da himar, wato kallabi. Mata suna rufe jikinsu da waɗannan tufafin uku (ƙaranci) a lokacin da suke raye.” Izar a da can tufafi ne da ke rufe dukkan jiki tun daga kafaɗa ko tun daga sama har ƙasa. Wannan lifafar ita ce ‘ƙamis’ (riga) an yi bayaninta a Ibni ‘Abidin. Kamar yadda aka gani, bisa ƙa’ida mata suna saka riga babba da kallabi idan sun fita waje. An rubuta a Bahr-ur-raiƙ da **Durr-ul-muntaƙa** cewa: “‘Nafaƙa’ wadda wajibi ne ga miji ya kawo wa matarsa ta ƙunshi abinci da tufafi da muhalli. Tufafi ya ƙunshi himar (kallabi) da milhafa, wadda ke nufin mayafi. [Ana kiransa ‘feraja’ ko ‘manto’ ko ‘saya’ a yanzu. Kamar yadda bayani ya gabata, tufafin mace kashi uku ne, kuma charshaf (wani samfarin hijabine, na al-adar mutanen Turkiyya) baya ɗaya daga cikinsu. Charshaf ya zo ne daga baya. Ya halatta ga mace ta sanya charshaf a wurin al’ada ta yadda a sanya shi, sannan ta sake ɗora riga babba a sama (manto) da kallabi mai kauri a inda al’ada ta yadda a sanya. Mutum ya sha bamban ko ya fita daban daga sauran mutane wajen ayyukan al’ada yana haddasa fitina, wanda hakan haramun ne].

Kafen[1]-i-fard ya ƙunshi falle ɗaya ga maza da mata.

A wurin da babu wani nau’in tufafi sai na siliki, sai a yi amfani da guda ɗaya ga maza guda biyu ga mata.

[1] Ma’anar kalmar kefen a nahawu itace ‘likkafani’.

Bayar da fifiko wajen limancin sallar jana'iza zai kasance: Shugaba, idan Musulmi ne; babban Alƙali na gari; Limamin sallar Juma'a; da imam-i-hay. (A duba babi na ishirin a mujalladi na huɗu na littafin **Endless Bliss** domin ƙarin bayani).

Mutumin da ake kira imam-i-hay shi ne Musulmi mai ilimi wanda mamacin (da za a yi wa sallar jana'iza) ya yarda da shi sa'ilin da yake da rai. Daga nan sai waliyyin mamacin. Idan waliyyin baya nan, sai wani daga cikin Musulmi da ba ya cikin waɗanda aka lissafa a sama ya yi masa sallah, a nan waliyyin yana da zaɓi biyu. Yana iya bari ko kuma ya sanya a sake sallah. [Za a samu cikakken bayani a cikin mujalladi na huɗu da na biyar a littafin **Endless Bliss**.

Misali a ce an datsa mutum gida biyu, sai aka samu rabin gangar jikin gawarsa, sai a yi sallar jana'iza ga wannan rabin gawar da aka samu.

Misali kuma a ce an daddatsa gawar gunduwa-gunduwa, kuma an warwatsa su nan da can; to za a yi sallar jana'iza ga wannan mamacin idan aka tattaro sassan jikin aka haɗa su wuri ɗaya.

Idan aka yi wa mamaci wanka, sai aka ga wata gaɓa ta jikinsa a bushe; sai a wanke wannan gaɓar idan ya zamo ba a kai sanya shi a likafani ba. A wani ɓangaren kuma idan aka ce ba a wanke wata gaɓa ta alwala ta mamacin ba har aka kusa kai shi kabari, sai a wanke ta nan take a kuma yi masa sallar jana'iza. Idan kuma aka ga haka bayan an saka shi cikin kabari; a nan ba za a fito da gawar ba. Idan (bayan an saka gawar kabari) aka gano cewa ba a yi masa wanka ba; sai a fito shi a yi masa wankan, idan ba a kai ga binne shi ba.

Idan ya kasance an yi wa gawar taimama ne, daga baya sai aka samu ruwa bayan an ɗauki gawar (a cikin makara) kuna da zaɓi.

Misali mutane ne da yawa suka mutu a lokaci ɗaya a wani gari; ya halatta a yi masu sallar jana'iza guda ɗaya dukkansu. Za a yi haka ne ba tare da cewa ya yi daidai da dokar Musulunci ba. Ya fi dacewa a yi masu sallar daban-daban ga kowane mamaci ɗaya.

Ana yin niyyar sallar jana'iza kamar haka: "(Na yi niyyar) **yin sallah da izinin Allâhu ta'âlâ, ta yin addu'a ga maniji** (ko mace) **Musulmi, zan yi koyi da limamin da yake nan wanda zai jagoranci sallar**."

Idan aka kama mutum yana yi wa matafiya fashi da makami, sai aka kashe shi bisa hukuncin Alƙali ko na waliyyinsa, ko kuma aka kashe ɗan tawaye lokacin da yake yaƙi da gwamnati ko aka kashe mutum namiji ko mace saboda sun kashe iyayensu; ba za a yi masu sallar jana'iza ba baki ɗayan su ukun nan.

Ana yin sallar jana'iza ga wanda ya kashe kansa (Durr-ul-mukhtar).

Musulmi Ahl as-sunnat yana da wasu martabobi guda goma:

1- Musulmi Ahl as-sunnat ba ya fashin zuwa masallaci sallar jam'i (sallolin farilla biyar na yini)

2- Yana halartar Jam'i ya yi sallah a bayan Liman [wanda imanin sa da fasiƙancin sa (saɓo) ba su yi munin da za su iya fitar da shi daga Musulunci ba].

3- Ya yarda da halaccin yin shafa a inda yake da rauni, (wanda aka yi cikakken bayani a kai a babi na uku na mujalladi na huɗu na littafin Endless Bliss).

4- Ba ya zagin Sahabbai 'radiyallâhu ta'âlâ 'anhuma ajma'in'.

5- Ba ya yi tawaye ga Gwamnati.

6- Ba ya fafutika ko gardama bisa rashin adalci a kan wani al'amari na Musulunci.

7- Ba ya mayar da hankali a kan kokwanto a cikin addini.

8- Ya san cewa duk wani abu, mai kyau da marar kyau daga Allâhu ta'âlâ ne.

9- Ba ya zargin wani Musulmi daga cikin mutanen Kibla da kafirci [sai waɗanda ilhad ɗin su ya bayyana].

10- Yana bayar da fifiko ga Khalifofin farko (wato Hadrat Abu Bakr da Hadrat 'Umar da Hadrat 'Uthman da Hadrat 'Ali) a kan sauran Sahabbai.

BAYANI a kan HALIN MUTUWA

Ya ku masu rauni, kuna ta guje wa mutuwa! Ka ce "Wane da wane sun mutu. Idan ina kusa da shi, mutuwa za ta iya yaɗuwa zuwa gare ni," idan annoba ko wata cuta mai yaɗuwa ta watsu a wani wuri, sai ka gudu zuwa wani wurin. Irin wannan halin haramun ne. Cuta za ta iya riskarka ko'ina idan Allâhu ta'âlâ ya so.

Ya ku mabuƙata masu rauni, idan kun gudu ina za ku je! Alƙawari ne cewa mutuwa ita ce ƙarshen ka. Ba za a ƙara maka ko daƙiƙa ba idan lokacin mutuwa ya yi! Idan lokacin mutuwarka ya yi Khallaƙ-i-'alam (Mahaliccin kowa da komi) ba zai ƙara maka lokaci ko da na kyaftawar ido ne ba. Ba za ta ɗauke ka kafin lokaci ko ta ƙara maka lokaci ba.

Duk wurin da Haƙƙ ta'ala ya ƙaddara za a ɗauki ran wani, wannan mutumin zai je wannan wurin, ya bar dukiya da iyalan sa da 'ya'yan sa. Kuma ba za a ɗauki ransa ba sai ya je wannan wurin inda mutuwa take jiransa.

Kowa zai mutu idan lokacin mutuwarsa ya yi. A aya ta talatin da uku tana cewa: "**… idan wa'adinsu ya cika, babu wani ƙanƙanen abu da zai kawo jinkiri (ƙanƙanen lokaci) kuma ba za su iya ƙara komi ba**."

Kafin a haifi mutum, za a ɗibar masa tsawon lokacin da zai rayu. Kuma an rubuta shi a Lawh-il-mahfuz: inda wannan mutumin zai mutu, ko ya tuba ko bai tuba ba, zai mutu, da irin rashin lafiyar da za ta kashe shi (idan akwai), ko zai mutu da imani ko babu imani. Wannan bayanin yana cikin aya ta ƙarshe ta suratul Luƙman.

Khallaƙ-i-'alam ya halicci mutuwa. Sannan ya halicci rayuwa. Sannan ya halicci arzikin mu ya rubuta su a Lawh-il-mahfuz.

Haƙƙ ta'ala ya san adadin numfashin da za ka yi. Ya kuma rubuta a Lawh-il-mahfuz. Mala'iku ne suke kula da shi, idan lokacin ya yi sai su sanar da Malak-ul-mawt (Mala'ikan mutuwa).

Idan ka yi rayuwa tare da yarda da gaskiyar da ke cikin Kur'an al-karim tare da yin aiki da hukunce-hukuncen da ke cikinsa, za ka je (rayuwa ta gaba) cike da farin ciki! A karɓi duk abin da ya zo daga Allâhu ta'âlâ! Kar ka yi kuka ga mamaci! Aikata hakan yana sa mutum ya mutu babu imani. Mu nemi tsarin Allâhu ta'âlâ. Idan mun aikata saɓo ko kuskure, sai mu yi tuba ta gaskiya.

Haƙƙ subhanallahu wa ta'ala ya bayar da umarci Mala'ika Azrail ''alaihis-salâm' (mala'ikan mutuwa) cewa: "**Ka zare ran masoyana cikin sauƙi, su kuma mafiyana ka zare ransu cikin tsanani**!" Al-ayaz-u-billah, idan mutum ya kasance marar ɗa'a!

Rana ɗaya ta lahira daidai take da shekaru dubu ɗaya ko dubu hamsin na duniya. Akai bayanai daban-daban game da wannan batun. An fahimci haka ne a cikin aya ta biyar ta suratul Sajda da aya ta huɗu ta suratul Ma'arij.

Don haka mala'iku suna zare ran wanda ya bijire cikin tsanani. Harshe ba zai iya bayyana tsananin ba. Mu miƙa wuya ga Allah, wanda ya halicce mu daga babu. Wasu mutanen a lokacin da za su mutu, su kan yi ta mirgina da juye-juye daga nan zuwa can. Allâhu ta'âlâ ya bayyana su a cikin suratul Nazi'at. Mala'iku za su azabtar da su, sannan su yi magana da juna. Jebrail ''alaihis-salâm' zai ce masu: "Kar ku tausaya masu!" Ran munafiki zai zo har bakin hancinsa. Sai kuma mala'ikun su sake shi. Za su matse gaɓoɓinsa har idonsa ya fita. Mala'ikun za su ce masa: "Kai ba ɗan Aljanna ba ne! ka manta irin ayyukan assha da ka aikata lokacin da kake raye? Ya kai wannan mutum marar amfani! An tanadar maka da azaba irin wadda za a yi wa munafukai da kafirai. Domin ba ka damu da sallah da zakka da sadaka ko tausayin talakawa ba. Ba ka guje wa haram, kana aikata munanan ayyuka

(fasad). Kana aikata cin amana sanna ka ce ‘Allah shi ne mai girma’. Yanzu kuma za ka ɗanɗani azaba.” Sai Hadrat Haƙƙ subhanahu wa ta’ala ya yi jawabi: “**Waɗannan munafukan ba su yi tunanin mutuwarsu ba ko da rana ɗaya. Sun yi girman kai. Ba sa aikata farillai da sunnoni da wajibai. Don haka za su ɗanɗani azabata yanzu**!” haka nan mala’iku Zabaniyawa (mala’ikun azaba) za su kama ƙasan akaifunsa su fizge ransa ta jijiyoyin da ke ƙirjinsa, su bi da shi ta maƙoshinsa sannan su sake shi ya ƙoma ciki kuma. Kazalika wani jawabin na Allâhu ta’âlâ zai ce: “**Malamai ba su faɗa maka ba? Baka karanta littafinmu ba? Ba ka jiya ce: Kar ka bari a mamaye ka, kuma kar ka bi shedan ba? Ba ka ji ya ce: Ka sani komi daga Allah yake ba**?” Kar ka biye wa ruɗin duniyar nan, wurin da ake mutuwa! Ka wadatu da abin da Allâhu ta’âlâ ya ba ka, ka tausaya wa bayinsa, ka ciyar da miskinai! Allâhu ta’âlâ da ƙarfin ikon sa ya halicce ka, ya kuma ɗauki nauyin ciyar da kai, idan wata musiba ta same ka daga wurinsa, ka roƙe shi, ka ƙara roƙon sa ya yaye maka. Kar ka ce “Na biya likitoci sun warkar da ni! Ka sani cewa Allâhu ta’âlâ ne ya yaye maka! Dukiyar da kake iƙirarin taka ce, abu ne da ya ba ka domin ka kula da shi. Ba za ta yi maka maganin matsalolinka ba. Idan ka same ta a kan hanya ta halal, za a neme ka a kan ka bayar da bayani a kanta. Duk abin da Haƙƙ subhanahu wa ta’ala ya hukunta a kanka, ka karɓe shi; babu wani taimako da za ka samu daga dukiyar ka da ‘ya’yanka ko daga abokan ka, kuma ba za ka iya kauce wa ƙarshenka ba duk yadda ka yi kuka da ƙorafi kuma ko a wurin wa ka je. A ƙarshe za a binne ka ƙarƙashin ƙasar kabarinka. Idan kuma lokacin mutuwarka bai yi ba, babu wanda ya isa ya cutar da kai. Kai kaɗai aka bai wa umarnin kare kanka daga haɗari, da kuma tsayuwa a kan abubuwan da za su zamo maganin matsalolin ka.

Idan Haƙƙ ta’ala ya ba ka ni’ima da ta ƙunshi lafiya da dukiya da ‘ya’ya, ka nuna godiya a kansu, ka ce, “Ubangijin mu ya taimake mu.” Idan kuma Allâhu ta’âlâ ya jarabce ka da wata musiba, wato idan ya aiko maka da wani ibtila’i sai mutum ya yi baƙin ciki maimakon yin haƙuri, sai ya mance da nuna godiya.

Wani zance na Haƙƙ ta’ala yana cewa: “**Ya ku mala’ikuna ku riƙe shi**!” mala’ikun za su riƙe ran ta ƙarƙashin dukkan gashin jikinsa, sannan su sake shi. Babu wani mahaluki da ya isa ya ceto mutum daga azabar Allâhu ta’âlâ.

Idan mutumin da yake kwance a kan gadon mutuwarsa ya hango irin wannan azabar, sai ya ce: wayyo, wayyo, ina ma a ce na aikata dukkan abin da Musulunci ya umarce ni lokacin da nike duniya, da ban fuskanci wannan azabar da nike fuskanta yanzu ba! Haka nan wani zancen na Allâhu ta’âlâ yana cewa ga mutanen da suke ƙoƙarin kulawa da marar lafiya: “**Ya ku kangararrun bayina! Ku cigaba da ƙoƙarin ceto masoyin ku ta hanyar ɓatar**

da dukiya! A duniya ba ku nuna juriya ba a kan azabata da za ta zo, ku ka yi ta ƙorafi a kaina. Yanzu wannan bawan yana cikin azaba, ransa ya zo gargara. Ya ƙarfin Ikona!" Idan mala'iku suka ji wannan zancen, sai su yi sujada, su ce: "Ya Ubangijin mu! Azabar ka gaskiya ce! Haƙƙ ta'ala ya faɗa mana wannan al'amarin ne a cikin Kur'an al-karim. Daga nan kuma sai zancen ya zo, yana umartar mala'iku cewa "Ku riƙe shi" zai ji wani raɗaɗi mai tsanani a kan wannan riƙon, ya zamo babu wata mahudar gashin jikin sa da ba zai ɗandani wannan azabar ba. Mala'iku za su yi tsawa mai ƙarfi: "Ya ke ran bijirarren bawan Allah! Zo ki fito daga gangar jikin ki. Yau rana ce ta azaba gare ki, saboda kin so wani abin halitta wanda ba Allâhu ta'âlâ ba, kuma girman kai ya hana ka gaishe da talakawa, ka aikata abubuwan da suke haramun, kuma ka zaɓi ɓata a kan daidai." Waɗannan bayanan suna cikin Kur'an al-karim.

Daga nan wannan mutumin zai ce da mala'iku: "Ku ba ni ɗan lokaci in huta." A wannan lokacin yana ganin Mala'ikan mutuwa tsaye a kansa. Da zarar ya ga Mala'ikan mutuwa zai fara kyarma, zai manta da azabar da yake ciki. Sai ya ce: Waye kai, duk da irin azabar da waɗannan mala'ikun suke yi masa, ya ce me kake yi a nan? Sai mutuwa ta zo masa cikin ban tsoro ta ce: Ni ce mutuwa da za ta ɗauke ka daga doron ƙasa, zan mayar da 'ya'yan ka marayu, in sa maƙiyanka na duniya su gaje dukiyarka.

Idan ya ji waɗannan kalaman daga mutuwa, zai gigice yana waiwayawa dama da hagu. Wannan su ne alamun da Rasul-i-akram 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam ya bayyana a cikin wannan Hadisin da ke cikin littafin Sahih-i-Bukhari: "**Idan ya ji motsin mala'iku, zai juya fuskarsa ya kalli bango, sai ya ga mutuwa tana tsaye a gabansa**."

Idan ya juya ɗaya gefen sai ya ga mutuwa a nan ma, sai ya juya baya kuma.

Mala'ikan mutuwa zai ƙwatsa tsawa ya ce: Ni ne mala'ikan nan mai girma da ya ɗauki ran iyayen ka; kana nan a lokacin; wane taimako ka iya ba su? Yanzu makusantan ka na kallo. Wane taimako za su iya ba ka? Ni ne mala'ikan nan mai girma, na ɗauki rayukan mutane da suka fi ka ƙarfi kafin kai.

Yayin da wannan mutumin yake kwance a kan gado yana magana da mala'ikan, su kuma mala'ikun azaba za su bar shi su tafi. Idan ya ga Azara'il ''alaihis-salâm' cikin kwarjini, zai ruɗe a wannan lokacin.

Azra'il ''alaihis-salâm zai tambaya: Yaya ka samu duniya? Sai ya amsa masa: Na biye wa ruɗin duniya. Wannan shi ne sakamakon abin da na aikata.

Sai Khallaƙ-i-jihan (Mahaliccin dukkan halittu) ya sauya duniyar zuwa mace. Da jajayen idanu, haƙoranta kamar ƙahon saniya, tana wari marar daɗi, sai ta zauna a kan ƙirjinsa.

Sai kuma a kawo dukiyar mutumin a gabansa. Duk da ƙorafin sa, za a bayar da dukiyar da ya samu ta hanyar halal ko ta hanyar haram ga magadansa.

Daga nan sai dukiyar ta ce da mai ita: "**Ya kai wannan bijirarren bawan! Ka same ni kuma ka yi amfani da ni ta hanyar da ba ta dace ba, ba tare da bayar da sadaka da zakka ba. Yanzu kuma na fita daga hannunka, na zama dukiyar mutanen da ba ka so. Sun ɗauke ni ba tare da nuna godiya a gare ka ba**."

Yana cikin wannan halin, zai duba kusa da shi yana jin wata irin ƙishin ruwa wadda za ta sa zuciyarsa ta riƙa ƙuna.

Wannan yanayin da ya shiga zai bai wa shedan damar da yake murna da samunta: zai zo kusa da shi ɗauke da kofin ruwa da nufin raba shi da imaninsa. Zai girgiza kofin ɗauke da ruwa mai sanyi a ciki a gefen gadon marar lafiyar. Marar lafiyar zai kalle shi ya kumaji motsin ruwan da ake girgizawa. A nan ne wuri da lokacin da talaka da mai arziki za su sani daga junansu.

Idan mutum ba shi da rabo, sai ya ce: "Ba ni ruwan nan in ɗan kurɓa." Wannan shi ne abin da la'ananne yake buƙata! Sai ya ce: Ka ce – hâshâ – duniya ba ta da mahalicci! Idan marar lafiyar ya zamo ba shi da rabo, sai ya faɗi abin da aka nemi ya faɗa, toh –al– ayazu billah– zai rabu da imaninsa. Sai dai, kamar yadda hikima take tare da mai shiriyarwa (Allâhu ta'âlâ), mutanen da suke da marar lafiya, su ajiye ruwa a kusa da shi. A riƙa buɗa bakin marar lafiyar a-kai a-kai ana ɗura masa ruwa. Idan shiriya ta cece shi, zai la'anci shedan, sannan ya ƙi karɓar ruwan da ya zo masa da shi.

Idan wa'adinsa ya cika, kuma ya zamo Mumini ne, za a umarci Azra'il ''alaihis-salâm' ya zare ransa, shi ma mala'ikan sai ya cika wannan umarnin. Mala'iku ɗari uku da sittin ne za su karɓi wannan ran (mai albarka) daga hannun Azra'il ''alaihis-salâm' cikin sifa irin 'yan uwa da abokan arziki na mamacin, za su rufe ran da wani ƙyalle na Aljanna, su tafi da shi zuwa Aljannar su nuna masa wurin zamansa, sannan su gaggauta mayar da shi zuwa ga gawar mamacin.

Haka nan idan ya mutu babu imani, mala'iku ɗari uku da sittin daga sijjin za su zo da ganyen (wata itaciya wuta) Zaƙƙum, mai tsananin baƙi, su rufe ran da shi, wanda ya bar jikin sa babu imani, za su gaggauta kai shi wuta, su nuna masa mazaunin sa, sannan su mayar da shi a jikin gawar.

Idan mutum ya balaga, ya yi rayuwa mai tsawo a duniya, ya ƙi yin ɗa'a ga umarni da hani na Musulunci, kuma ya bar duniya ba tare da ya tuba ba – na'uzu billah (Allah ya yi mana tsari daga irin wannan ƙarshen)– zai fuskanci waɗannan azabobin da abubuwa na kunyatarwa, ya kuma shiga wuta daga ƙarshe, sai dai idan Hidayat (shiriya) ta zo masa daga Allâhu ta'âlâ, ko ya samu shafa'at-i-Muhammadi 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam'. (A duba babi na talatin da biyar na mujalladi na biyu na littafin **Endless Bliss** domin samun cikakken bayani a kan shafa'at [ceto]).

BAYANI a kan MUTUWAR KANANAN YARA

Idan ƙaramin yaro Musulmi ba shi da lafiya har ya kai gargarar mutuwa, idan ya mutu, Maƙam-i-illiyin, wato Aljanna ita ce makomar sa. Mala'iku ɗari uku da sittin za su zo daga can, su jera sahu a gaban yaron, su ce masa: "Ya Ma'sum (Ya kai tsarkakken yaro)! Albishir a gare ka! Yau ne za ka roƙi afuwa Haƙƙ ta'ala game da abin da ka aikata a baya, da kuma iyayen ka da kakannin ka da maƙwabta." Daga nan sai mala'iku ɗari su sanya masa hular ceto a kansa, wasu mala'ikun ɗari su sanya masa hular ƙauna, wasu mala'ikun ɗari kuma za su sanya masa rigar karsashi da kuzari, wasu mala'ikun sittin kuma za su janye masa shamaki da labulan da ke gaban idanun sa. Duk lokacin da aka janye shamakin zai ga iyaye da kakannin sa na Muminai da suka shuɗe, tun daga lokacin Annabi Adamu, da kuma azabar da aka tanadar wa wasu daga cikinsu. Idan ya ga wannan hali da waɗannan mutanen suke ciki, sai ya yi kuka ya yi takaici, ya gigice, har mutanen da ba su san ainahin dalili ba su ɗauka zafin fitar rai ne.

Idan mala'ikun da za su ɗauki ransa suka zo, suka gan shi da huluna da rigar ceto sanan kuma an janye shamaki a fuskarsa, sai su kasa ɗaukar ran nasa, su ce masa: "Ya Ma'sum! Khallaƙ-i-'alam (Mahaliccin dukkan abin halitta) ya aiko da sallama gare ka (yana gaishe ka tare da fatan alheri), ya ce: Ni na halicce shi, kuma zai dawo gare ni. Domin na ba shi ajiyar rai ne, yanzu kuma zai dawo gare ni. Kuma zan ba shi Aljanna da didar (ganina) a maimakon shi. Idan ba ka gasgata mu ba, ka kalli sama domin ka gani da idonka." Sai yaron ya duba ya ga mala'iku da kuma cikar Kyau (Jamal) na Allâhu ta'âlâ. Sai ya yi murna da farin ciki matuƙa. Tsananin murnar za ta sa ya ji kamar ya yi tsalle ya hanzarta zuwa ya miƙa ran nasa, sai kuma ya ga azabar da kakannin sa suke ciki sai ya fasa. Sai mala'ikun su ce "Ya Ma'sum! Me ya sa ba za ka sadaukar da ranka ba?" Sai yaron ya ce: "Ya ku waɗannan mala'iku! Ku roƙi Allâhu ta'âlâ ya yafe wa 'yan uwa da kakanni na a madadi na." Sai mala'ikun su ce: "Ya Ubangiji! Ka san abin da yake faruwa tsakanin mu da wannan yaron." Daga nan Hadrat Allah 'jalla shanuhu' zai ce masu: "Da Izzata (ƙarfin iko) na yafe masu." Sai mala'ikun

su juya ga yaron su ce: “Ya Ma’sum! Albishir a gare ka! Allâhu ta’âlâ ya yafe wa waɗanda suke da imani, ya kuma karɓi dukkan roƙon ka.” A yayin da yaron yake murna, Allâhu ta’âlâ zai tura matan Hurul-Ain daga Aljanna, a cikin siffar iyayen sa, su zo gaban sa su buɗe hannuwansu su ce: “Ya kai ɗa ko ɗiyar mu! Zo ka tafi tare da mu! Ba za mu iya rayuwa a Aljanna ba tare da kai ba.” Sun zo wa yaron da tuffa (apple) daga Aljanna, sai su ce, “karɓi wannan.” Idan yaron ya sunsuna tuffa ɗin, Hadrat Azra’il ‘’alaihis-salâm (Mala’ikan mutuwa) zai zo da sifar ƙaramin yaro mai kyau, sai ya ɗauki ransa nan take.

Wata ruwayar ta ce, idan yaron ya sunsuna tuffa ɗin, sai ransa ya koma kan tuffa ɗin, shi kuma Mala’ikan mutuwa ya ɗauki ran a jikin fuffa ɗin, dukkan riwayoyin biyu za su iya kasancewa.

Daga nan sai Mala’ikan mutuwa ya ɗauki ransa zuwa Aljanna, yana ganin sammai a kan hanya. Za su ga wani wuri da aka yi da shuɗin lu’u-lu’u. idan suka zo wurin sai yaron ya tambaya: “Me ya sa ka kawo ni nan?” Sai mala’ikan ya ce: “Ya ma’sum! Nan ne wajen da za a yi tashin ƙiyama. Waje ne mai tsananin zafi. Wannan wurin yana ɗauke da ƙofofin rahama dubu saba’in. Ga kuma tabki mai albarka na Hadrat Rasul-i-akram ‘’alaihis-salâm’, sannan ga wani kofi na gilas mai haske! Idan iyayenka suka zo wannan wurin a ranar lahira, sai ka cika kofin da ruwa ka ba su, ka riƙe su a wurin kar ka bari su wuce, kar su faɗa wuta su shiga cikin azaba mai raɗaɗî. Domin addu’ar da ka yi karɓaɓɓa ce a wurin Haƙƙ ta’ala. A dararen juma’a, (daren da ke tsakanin ranakun Alhamis da Juma’a) ka koma duniya. Idan ka je, ka kai amincin Allâhu ta’âlâ ga al’ummar Annabi Muhammad ‘sallallâhu ta’âlâ ‘alaihi wa sallam’. Ka kai haske a gare su, ka kuma karɓo godiyar su ka kai ga Allâhu ta’âlâ”

Bayan sanya ran wannan yaro ya zagaya a wurin, sai a gaggauta dawowa da shi, a sanya shi a bisa kan gawar yaron. A yayin shirye-shiryen jana’izarsa da suka ƙunshi sallar jana’iza, da binne gawa, da kuma tambayoyin kabari, ran zai tsaya a kan kabarin. Idan iyayen sa sun mutu babu imani za a sanya wani shamaki tsakanin iyayen da ɗan. Yaron ba zai neme su ba, kuma ba zai haɗu da su ba a ko’ina. Wannan shi ne gaskiyar abin da zai faru ga ‘ya’yan Musulmi ƙananan waɗanda suka mutu kafin su balaga.

BAYANI A KAN MUTUWAR MACE MUSULMA

Idan mace ta mutu wajen haihuwa ko saboda ciki, ko annoba ko wata damuwa, ko ba tare da ko ɗaya daga waɗannan ba, ta mutu salin-alin, kuma lokacin da ta rayu ba ta taɓa mu’amala da wani wanda ba muharraminta ba sai tare da cewa ta rufe jikinta yadda ya kamata, (wato, shiga irin yadda

addinin Musulunci ya koyar) kuma mijinta yana farin ciki da ita, a lokacin da aka ɗauki ranta, mala'ikun Aljanna za su bayyana a gabanta, su yi mata sallama cikin girmamawa, su ce mata: "Ya ke masoyiya kuma shahidiya baiwar Allâhu ta'âlâ! Ki fito, me kike yi ne cikin wannan duniyar? Allâhu ta'âlâ yana farin ciki da ke kuma ya yafe maki zunuban ki sakamakon rashin lafiyar da kika yi, ya kuma ba ki Aljannarsa. Ki gaggauta bayar da abin da aka ba ki ajiya!" Idan matar ta ga irin matsayin da za ta samu, sai ta nemi bayar da ran nata. Amma sai ta duba ta ce: "Sai Allâhu ta'âlâ ya tausaya wa abokan arzikina, sannan in bayar da raina." Sai mala'iku su gabatar da buƙatarta ga Jenab-i-Haƙƙ. Daga nan za a ji zancen Allâhu ta'âlâ ya bayyana, yana cewa: "Da ƙarfin ikona, zan karɓi dukkan addu'ar wannan baiwar tawa." Sai mala'ikun su yi mata wannan albishir. Daga nan sai Mala'ikan mutuwa da mala'ikun rahama guda ɗari da ishirin su zo wurin. Hasken fuskarsu ya kai ga Al'arshi, suna sanye da huluna na alfarma a kawunansu, suna sanye da wani tufafi na haske da ado na zinare, suna da koren fikafiki. Suna ɗauke da kayan marmari na Aljanna a hannunsu, suna ƙamshin turaren almiski, za su zo kusa su yi mata sallama da girmamawa, sannan su ce: "Khallaƙ-i-'alam (mahaliccin kowa) yana gaishe ki, ya ba ki Aljanna, ya sanya ki maƙabtaka da Annabin sa mai albarka Muhammad 'sallallahu 'alaihi wa sallam' kuma kina cikin sahabban Hadrat Aisha."

Idan wannan matar mai imani ta ji wannan batun da ake faɗa mata, shamakin da aka sanya a idon ta zai yaye, za ta ga mata masu imani, da waɗanda ake yi wa azaba saboda saɓon da suka aikata. Sai ta yi roƙo, ta ce: "Ya Rabbi! Ka yafe masu zunubansu." Daga nan sai zancen Jenab-i-izzat ya ce: "Ya ke baiwata! Na karɓi dukkan buƙatunki. Yanzu ki bayar da ajiyar da aka ba ki (rai) yayin da mata da ɗiya suke jira." Da zarar ta ji wannan zancen, sai ta yi yunƙurin bayar da rayuwarta, ranta yana ƙagara, ƙafafun ta suna gaugawa, tana fitar da gumi. Yayin da za ta bayar da ran nata sai wasu mala'iku biyu su bayyana a wurin, kowannen su yana riƙe da sanda ta wuta a hannun sa, ɗaya zai tsaya a gefenta na dama ɗaya kuma a gefen hagun ta. A nan kuma sheɗan la'ananne zai garzayo zuwa gare ta, ya ce: "Ba ni tsammanin samun wani abu daga wannan, amma bari in gwada!" Zai matso kusa, ya nuna mata ƙoƙo da aka yi da zinare, da ruwa mai sanyi a ciki. Da zarar waɗannan mala'ikun sun ga wannan muguwar halittar, sai su fasa ƙoƙon da yake riƙe da shi da wannan sandar, su tsoratar da shi har ya tsere. Wannan matar Musulma za ta yi dariya yayin da take kallon su. Daga nan kuma matan (Aljanna) da ake kira Hurul'aini za su ba ta ruwan (Aljanna) na tabkin alkausara a cikin wani ƙoƙo na zinare, sai ta sha. Ruwan na Aljanna suna da matuƙar daɗin da har ranta zai yi fice ya liƙe a jikin ƙoƙon, shi kuma Mala'ikan mutuwa ya ɗauke shi a nan. Mala'ikun za su sanar da mutuwarta

ga junansu, suna cewa: "**Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un** (Daga Allah muke, kuma gare shi za mu koma)!" Sai su ɗauki ran zuwa sama, kamar tana yawon buɗe ido, za a nuna mata masaukinta a Aljanna, a dawo da ran cikin ƙanƙanen lokaci, a ajiye ran a kusa da kan gawarta.

Idan aka cire mata kaya, aka warware gashin kanta, ran zai matso kusa da kan gawar ya ce: "Ya ku waɗanda za ku yi mata wanka! Ku tausasa wajen riƙe ta! Domin ta samu mummunan rauni daga zare ran da Azrail ya yi. Kuma jikin ya yi tsami saboda wahalar da ya sha." Idan aka ɗora gawar inda za a yi mata wanka, ran zai zo ya ce: "Kar ku sanya ruwan ya yi zafi ƙwarai! Jikin ya yi rauni. Ku bar ni in tsira daga hannunku cikin gaugawa, domin in samu nutsuwa!" Yayin da aka wanke gawar aka sanya ta a likafani, ran zai ɗan jira kaɗan sannan ya ce: "Wannan ce rana ta ƙarshe da zan ga duniya. Ku bar ni in ga 'yan uwana suma su gan ni, domin in zama gargaɗi a gare su. Domin su ma nan ba da jimawa ba za su mutu kamar ni, kuma kar su yi mani kuka da kururuwa. Kar ku bari su manta da ni, su riƙa tunawa da ni a kodayaushe, su karanta Ƙur'an al-karim (Su sadaukar da ladar wannan kyakkyawan aikin gare ni). Kar su yi jayayya a kan dukiyata da na bari, domin gudun kar a yi mani azabar kabari saboda jayayyar su. Su riƙa tunani a duk ranakun Juma'a da sallar Idi."

Bayan an ajiye makarar da gawar take ciki a wurin da ake kira musalla (domin yi mata sallar jana'iza) ran zai ce: "Ka tausaya wa 'ya'yana maza da mata da iyayena! Babu wata ranar rabuwa da ta kai wannan ranar. Za mu yi kewar juna har zuwa lokacin da za mu sake haɗuwa, a ranar tashin ƙiyama. Ina maku bankwana, ya ku mutanen da kuke kukan rabuwa da ni!"

Idan aka ɗaga makarar zuwa kafaɗu, ran zai sake cewa: "Ku ɗauke ni a hankalli! Idan niyyarku ta samun lada ce, kar ku haifar mani da matsala! Ku kar ni in samu jin daɗi tare da ku ga Allâhu ta'âlâ!"

Yayin da aka ajiye makarar a gaban kabari, ran zai ƙara cewa: "Ku dubi halin da nike ciki domin ya zamo gargaɗi a gare ku! Yanzu za ku saka ni a cikin wuri mai duhu ku tafi ku bar ni. Zan kasance ni kaɗai a ciki sai ayyukana (wato, kyawawan ayyuka na duniya). Ku yi duba a kan wannan lokacin mai matuƙar muhimmanci, domin gudun kar ku ruɗu da wannan mayaudariyar duniyar!"

Idan aka saka gawar a cikin kabari, ran zai tsaya a gefen kanta. Kada wani dalili yasa a bar mamaci shi kaɗai ba tare da telƙin (addu'a) ba. [Sunnah ne ga nagartaccen Musulmi ya aikata (addu'ar da ake kira) **Telƙin** bayan an binne shi. Wahabiyyawa sun yi musun cewa sunnah ne yin telƙin. Sun ce bidi'a ne yin hakan. Sun ce mamacin baya jin ka. Malaman Ahl as-sunnat 'rahima-humullahu ta'ala' sun rubuta litattafai da dama da ke nuna

hujjar cewa sunnah ne yi wa mamaci addu'a. Ɗaya daga cikin waɗannan litattafan shi ne **Nur-ul-yaƙin fi mebhas-it-telƙin**, wanda Mustafa bin Ibrahim Siyami 'rahima-hullahu ta'ala' ya rubuta. Wani Hadisi da Tabarani da Ibni Manda suka ruwaito wanda aka kawo a cikin littafin ya yi umarni a kan yin telƙin. Littafin, wato **Nur-ul-yaƙin…**, an buga shi ne a garin Bangkok, a ƙasar Thailand a shekarar 1345, yayin da bugu na biyu aka yi shi a garin Istanbul na ƙasar Turkiyya, a shekarar 1396 H. [1976 M.]. Da izinin Allâhu ta'âlâ, gawar da ke cikin kabari za ta tashi, kamar ta tashi daga bacci, za ta samu kanta cikin duhu. Za ta kira ɗaya daga cikin bayinta ko mai yi mata hidima a nan duniya ta ce: "Kawo mani fitila!" Sai ta ji shiru, babu motsin komi ko murya. Kabarin zai rabu gida biyu, yayin da mala'iku matambaya za su ɓullo [masu suna Munkar da Nakir]. Wata wuta tana fita daga bakinsu, hancinsu yana fitar da hayaƙi. Sai su matsa kusa da ita su tambaye ta: "**Man Rabbuka, wa ma dinuka, wa man nabiyyika**, (wato waye Ubangijinki, mene ne addininki, kuma waye Annabinki)?" Idan ta amsa tambayoyin daidai, sai mala'ikun su yi mata albishir na samun rahamar Haƙƙ ta'ala, su tafi. Daga nan sai wata taga ta buɗe daga ɓangaren dama na kabarinta, wani zai ɓullo da hasken fuska kamar wata ɗan daren goma sha huɗu, ya shigo ta wannan tagar. Da wannan matar mumina ta ga wannan kyakkyawan mutumin ya zo gare ta, sai ta yi murna bisa wannan abokin, ta tambaya: "Waye kai?" Sai ya amsa mata "An halicce ni ne daga haƙurinki da godiyarki a duniya." Zan kasance abokin zaman ki har zuwa lokacin da za a yi tashin ƙiyama."

In har rai ta shagaltu da haramun ta gauraya da shi,

Zuciya ba za ta taɓa samun haske da ya zuwa daga Mamallaki ba!

BAYANI A KAN MUTUWAR WANDA aka ZALUNTA, da MAI HAKURI da SHAHIDAI-GHARIB

Mutuwar dukkan waɗannan tana kamaceceniya da juna. Za mu yi bayani a kan ɗaya, sai a yi amfani da bayanin a kan sauran. Akwai Gharib iri uku, mutanen da ke cikin (kaɗaici, wanda aka yi watsi da shi da wanda aka bari shi kaɗai): Ɗaya daga cikinsu shi ne mutumin da aka bari shi kaɗai a wani wuri mai nisa, wanda ba shi da 'yan uwa ko makusanta tare da shi. Ɗaya kuma mabuƙaci ne amma yana zaune a garinsu. Babu wanda ya damu ya je inda yake ya duba shi. Dukkan waɗannan muminan biyu mutane ne Gharib waɗanda idan suka mutu, sun yi mutuwar shahada (a wannan yanayin). Wani muminin kuma wanda zai yi mutuwar shahada shi ne wanda ya wuce shekaru sittin a duniya amma bai taɓa barin sallah ta kubce masa ba. [Mutumin da ya mutu yana aikata haram ba zai taɓa zama shahidi ba;

misalin wannan shi ne kamar mutumin da ya sha giya, ta zame masa guba. (Wannan mutumin ba zai zama shahidi ba idan ya mutu sakamakon wannan gubar). Sai dai idan mutum ya mutu yayin da yake shan giya, amma saboda wata sila ta daban ba giyar ba, misali, ginin wurin da suke shan giyar ya faɗo mashi, to ya yi shahada. Dukkan jikin mace tsiraici ne ban da fuskarta da tafukan hannuwanta. Farilla ne ta rufe dukkan jikinta, ban da fuska da hannu, (a duk lokacin da ta bayyana a gaban mazan da ba muharramanta ba). Duk macen da ba ta ɗauki hakan da muhimmanci ba ta kafirta. Wata shahadar kuma ita ce, yarinya ko mace wadda ba ta taɓa fita waje ba tare da ta rufe kanta da gashinta da cinyar hannunta da ƙafafunta ba. Umarni da hanin Allâhu ta'âlâ, a dunƙule su ake kira **Ahkam-i-islamiyya**. Iyayen da suka koyi Ahkam-i-islamiyya suka koyar da su ga 'ya'yansu suna cikin shahidai]. Babu ko ɗaya daga cikin waɗannan da za su samu shahada har sai idan suna da imani (kamar yadda malaman Ahl as-sunnat suka koyar) suna aikata salloli biyar na yini. Haka nan Musulmin da ya mutu a hannun maƙiyan Musulunci, shi ma ya yi shahada. Kafirin da ya mutu sakamakon tsananta horo wajen tuhuma bai yi shahada ba. Mutumin da ya mutu a matsayin kafiri ba zai shiga Aljanna ba.

Da zarar waɗannan shahidai da aka lissafa a sama sun kai gargara, za a buɗe ƙofofin sama, mala'iku da yawa za su sauko zuwa ƙasa, Allâhu ta'âlâ ne kaɗai ya san iyakarsu. Suna ɗauke da hular alfarma da riga ta haske a hannunsu. Cikin karramawa za su nemi ran wannan mutumin. Haƙƙ ta'ala ya yi wannan bayanin a ƙarshen suratul Fajr.

Wani shahidin kuma shi ne Muminin da ya fuskanci Derghah-i-izzat ya yi wannan addu'a ya ce: "Ya Ma'bud (Ya wanda nike bauta masa)! A duk rayuwata babu wanda nike tsammanin wani abu daga gare shi sai zatinka! Kuma ba ni sadda kaina a gaban kowa (face Kai). Kuma ban taɓa biye wa ruɗin duniyar ko abokin gaba ba. Ya Rabbi! A halin yanzu ina fatan za ka yafe wa Ummat-i-Muhammadi 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' Ka kuma yi masu gafara." Wannan mutumin shi ma shahidi ne.

Mala'kun masu albarka za su nannade ran a cikin wannan rigar (da suka zo da ita). Daga nan Haƙƙ ta'ala zai yi magana: "Ku tafi da wannan ran zuwa Aljanna! Domin ya (ko ta) yi sallah fiye da saura, kuma yana (ko tana) son baƙi, da yafe wa mutane bisa kuskuren su da gangancin su, da yin 'Istighfar' a-kai a-kai. Yana (ko tana) yawan ambato na. Kuma bai (ko ba ta) taɓa fita ba tare da rufe jikin su yadda ya kamata ba, haka nan yana (ko tana) guje wa haram. Sannan ya (ko ta) yi ɗa'a ga Annabawa da Musulunci a duniya."

Mala'ikun da suke gefen kafaɗunsa na dama da hagu, waɗanda suke rubuta ayyukan wannan bawan masu kyau da marasa kyau, za su yi addu'a:

“Ya Rabbi! Ka ɗora alhakin kula da wannan mutumin a duniya. Ka ba mu dama mu ɗauko ran wannan mutumin zuwa sama. Sai muryar Mai Girma da Ɗaukaka ta ce: “Ku tsaya kusa da kabarin wannan mutumin, ku yi tasbihi da kabbara, ku yi sujada sannan ku bayar da ladar (waɗannan ayyukan) sadaka ga wannan bawan nawa.” Daga nan za su cigaba da yin zikiri da tasbihi, suna rubuta ladar a littafin wannan mutumin, za su cigaba da yin haka har ranar tashin ƙiyama.

[A LURA DA **BAYANI MAI MUHIMMANCI ANAN**: Munafukai da suke ƙasar Masar (Egypt) sun yi bore ga (shiryayyen) Khaifa ‘Uthman ‘radiyallahu ‘anh’ suka zo Madina da niyyar kashe shi. Wasu abokan hulɗarsu a Madina suka goya masu baya da ƙarairayi da kalamai na ɓatanci. Suka riƙa zagin Sahabbai suna yaɗa jita-jita cewa: “Musulmai a Madina ba su taimaki Khalifa ba.” Gaskiyar kuma ita ce niyyar Khalifa ita ce samun babban matsayin na shahidai a Aljanna, kuma yana ta roƙon Allâhu ta’âlâ a kan haka. Sauran Musulmi sun zo domin taimakon sa, ya ce masu kar su yi komi a kan lamarin. Ya umarce su a kan su yi tafiyarsu. Masu boren suka yi amfani da wannan damar suka kashe Khalifa ya yi shahada cikin sauƙi. Shi kuma ya samu biyan buƙatarsa. Allâhu ta’âlâ ya karɓi addu’arsa. Shahiɗai ba sa jin raɗaɗin komi yayin da za su mutu. Za a nuna masu tanadin da aka yi masu a Aljanna, ta yadda za su miƙa ransu cikin sauƙi ga mala’iku, suna murnar matsayin da yake jiransu].

BAYANI a kan MUTUWAR KAFIRI

Idan kafiri ko wanda ya yi murtad (wanda ya yi ridda) ko wawa wanda ya nuna ƙiyayya ga Musulunci yake kiran Kur’an al-karim ‘shari’ar sahara’, wanda kuma ya zamo Jahili marar kunya yake kiran Muhammad ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ mafificin halitta shugaban Annabawa da suna ‘makiyayin raƙuma’, muna roƙon Allâhu ta’âlâ ya kare mu daga wannan mummunan aikin, haka nan wanda yake cewa addini ba shi da muhimmanci da nufin cin mutunci ga Musulunci, wanda shi ne zaman lafiyar al’umma da farin cikinsu, kuma maɓuɓɓugar ilimi da kyawawan ɗabi’u da tsafta da lafiyar jiki da adalci, wanda ya daidaita al’adu da makamantan su, idan ya zo mutuwa, za a yaye shamakin da ke kan idanunsa. Za a nuna masa Aljanna. Wani kyakkyawan mala’ika zai ce masa: “Ya kai wannan kafirin! Ya kai wannan jahilin da kake kiran Musulmi da sunaye na ƙasƙanci, kake kiran mutanen da ke biye wa sha’awarsu, suke nuna rashin ɗa’a a matsayin ‘wayayyun mutane’! Kana kan ɓatattar hanya. Kana ta wulaƙanta Musulunci addinin gaskiya. Mutanen da suka yarda suke girmama koyarwar da Muhammad ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’ ya zo da ita daga Allâhu ta’âlâ za su shiga Aljannarsa.” Zai ga ni’imar da ke cikin Aljanna. Sai matan Hurul-Aini na

Aljanna su ce: “Mutanen da suke da imani, za a kare su daga azabar Allâhu ta’âlâ.” Daga nan shedan zai bayyana a sifar malami, ya ce: “Ya kai wane dan wane! Wadannan da suka zo maka dazu, makaryata ne. Za ka samu wannan ni’imar.” Sai kuma a nuna masa wutar jahannama. Ta kunshi manyan tsaunuka na wuta, da kunamu da manyan macizai masu girma kamar alfadari. Zai ga azabar da aka fada a cikin Hadisai. Mala’ikun azaba da ake kira Zabaniyawa suna duka da wata sanda ta wuta. Wuta na fesowa daga bakunansu. Sun kai hasumiya tsawo, hakoransu kamar kahon saniya, muryarsu kamar tsawa lokacin ruwan sama. Kafirin zai firgita da jin muryarsu, ya juya wajen Shedan. Zai gan shi abin tsoro har ya kawar da idonsa. Sai mala’iku su kama shedan su dankwafar da shi. Sai su juya a kan kafirin su ce: “Ya kai makiyin Musulunci! A duniya kana saba wa Ma’aikin Allah ‘sallallahu ‘alaihi wa sallam’. Yanzu kuma kana musanta Mala’iku, haka nan shedan la’ananne ya sake yaudarar ka.” Za su daura masa sarkar wuta a wuyan sa, a lankwasa kafafunsa zuwa kansa, ta yadda za su kai har bayan keyarsa, a tura hannunsa na dama zuwa hagu a kan kirjinsa, yayin da hannunsa na hagu a tura shi zuwa dama, su zagayo ta bayansa. Akwai ayar da take ba mu bayani game da wannan labarin. Zai yi kururuwa ya nemi taimakon abokansa. Sai zabaniyawan su amsa masa: “Ya kai wannan kafirin; ya kai wawa da kake kaskantar da Musulmi! Yanzu ba lokacin roko ba ne. ba za a karbi imani ko addu’arka ba. Yanzu lokaci ne na azaba a kan kafircin da ka yi.” Za su fizgo harshensa ta bayan wuyansa. Za su kwakwale idanunsa. Da sauran wasu hanyoyi na dandanon azaba mai tsanani, sannan su zare ransa su ja shi zuwa wuta. Muna rokon Allâhu ta’âlâ ya albarkace mu da sadaukar da rayukan mu wajen bin addinin Muhammad ‘’alaihis-salâm’ tare da bin koyarwar litattafan Ahl as-sunnat, wadanda suka kawo mana addini kamar yadda yake daga Annabin tsira! Amin.

Duk yadda mutum ya yi tsawon rai, wata rana zai mutu. Annabin mu ‘’alaihis-salâm yana cewa: “**Yayin da ran mutum ya bar jikinsa, wata murya za ta ce: Ya ku mutane, kun bar duniya, ko kuwa duniya ta bar ku? Kun samu duniya, ko kuwa duniya ce ta same ku? Kun kashe duniya, ko kuwa duniya ce ta kashe ku? Idan aka fara wanke gawar wata murya za ta yi tambayoyi guda uku:**

1- Ina jikinka yake mai karfi? Me ya sanya maka rauni?

2- Ina jawabanka masu dadi? Me ya sanya ka shiru?

3- Ina abokanka masoyan ka suke? Me ya sa suka tafi, suka bar ka kai kadai?

Idan aka saka gawar a likafani, wata murya za ta ce: Kar ka tafi ba tare da guzuri ba! Wannan tafiyar ba a dawowa, har abada. Inda za ka je akwai

mala'iku masu azabtarwa. Idan aka sanya gawar a makara, wata muryar za ta ce: Idan ka yi aiki domin neman yardar Jenab-i-haƙƙ, muna maka albishir, na samun ɗaukaka da farin ciki da suke jiranka! Idan ka saɓa wa Jenab-i-Haƙƙ, to kaicon ka! Idan aka kawo gawar kusa da kabari, wata muryar za ta ce: Ya ku mutane! Me kuka shirya a rayuwarku ta duniya (mai amfani) da za ku je da shi cikin kabari? Wane haske kuka kawo na shiga wuri mai tsananin duhu? Me kuka zo da shi na dukiyar da matsayi da kuke da shi? Me kuka zo da shi da za ku ƙawata wannan kufan kabarin da shi? Idan aka sanya gawar a kabari, sai kabarin ya fara magana ya ce: Ka yi zance a bayana, amma ka yi shiru a cikina. Sannan idan aka kammala binnewar, mutane suka watse, sai Hadrat Haƙƙ ta'ala ya ce: Ya kai bawana, kai kaɗai ne a halin yanzu; sun tafi, sun bar ka kai kaɗai a cikin kabari mai duhu. Abokanka ne da 'yan uwanka da 'ya'yanka da masoyanka. Amma babu wani wanda zai amfane ka a cikinsu. Ya kai bawana, ka saɓa mani; ba ƙi bin umarni da hanina, amma ba ka taɓa tunanin wannan yanayin ba. Idan kuma wanda ya mutu da imani ne, ana fatan cewa Jenab-i-Haƙƙ zai yi masa gafara, ya ce masa: Ya kai bawana, wanda ya yi imani! Ba ka cancanci girman ikona ya bar ka gharib (kai kaɗai) ba a cikin kabari. Saboda 'Izzat-u-jalal ɗina, zan tausaya maka ta yadda abokanka za su yi mamaki, sannan in yi maka jin ƙai fiye da yadda iyaye ke tausayin ɗansu. Saboda karimcinsa da alfarmarsa, zai gafarta dukkan zunuban wannan bawan, sai kabarinsa ya zamo dausayin Aljanna, tare da 'yan matan Hurul-aini da ni'ima ta Aljanna. Allâhu ta'âlâ mai tausayi ne, yana yafe zunuban bayinsa. Ya wadatu da jin ƙai don haka yana kallon zunuban bayinsa sai ya rufe su maimakon ya kama su da su. Mu yi riƙo da umarni mu guji aikata hani na Mahalicci, domin mu kare kanmu daga azaba mai raɗaɗi ta hanyar aikata 'amal-i-salih."

Dukkan Musulmai masu saɓo da waɗanda ba sa saɓo, za su fuskanci tambayoyin kabari. Za a yi azaba ga waɗanda ba a yi wa gafara ba, tare da kafirai. Waɗanda suke yaɗa jita-jita a tsakanin Musulmi da waɗanda suke bari fitsari yana fallatsa a tufafinsu a makewayi za su fuskanci azabar kabari. [Azabar kabari ba rai kaɗai take shafa ba, tana shafar ran tare da gangar jiki. Wannan batun ya wuce awo na hankali. Don haka mu guji neman bin diddigin su ta hanyar aunawa da hankali].

Idan mutum ya mutu babu imani (wato ya mutu kafiri) zai (ko za ta) fuskanci azaba mai raɗaɗi har zuwa mahsher, (wato ranar lahira) [daga ƙarshe ma ya shiga wuta].

Wannan shi ne fassarar waƙen Turkanci na Ottoman wadda **'Abd-ur-Rahman Sami Pasha** ya rubuta, wanda tsohon babban hafsan soji ne na

Ottoman, wanda ya rasu a shekarar 1295 H. [1878 M.] a lokacin da yake wakili a Majalisar Dattawa:

Ya kai rayayyen maziyarci! Kar ka saki zuciyarka ga kowa in ba Allâhu ta'âlâ ba!

Babu wanda za a bari a duniya. Babu mai iya yin komi sai Allah ta'ala. Babu wanda zai ci da rayuwa sai Allâhu ta'âlâ.
Kowa ya damu da ranakun farin ciki da na bakin ciki. Wannan duniyar. Babu wani abin gasa da wani a cikinta.

Ni kaina, wani ne a lokacin da nake tashe, kamar wani dutse mai daraja ne a kan zoben shugaba, kamar hatimi na mulki. Amma yanzu kaddara duk ta sauya al'amurra.

Sai zuciyata ta kamu da cuta, karfina ya kare. Daga karshe tsuntsun rayuwata [raina] ya tashi ya bar ni. Shi kuwa kejin [na raina] ya tagayyara ya lalace.
Lafiyata, kamar fitila, ta dauke. Sai duhu ya mamaye ni.
Rana ta bullo ta tashin kiyama. Komi ya haskaka da hasken Allah.

A wannan lokacin zan gana da Ubangijina. Zunubaina suka bayyana. yayin da na roki gafara, sai na dace da jin kansa marar iyaka.
Ya Ubanagiji! Na aikata dubban zunubai. Duk da haka na yarda da kaina, da wannan bakar fuskar tawa, na gurfana gabanka madaukaki. Ina roko ka yafe mani!

Na sanya sunanka Ghafur a kwanan watan wannan rubutun nawa [1286]. Ma'anarta za ta fito fili. Ban da Allah babu mai iya yin komi. Baya ga Allah babu wanda zai cigaba da wanzuwa!

Wannan rayuwar mafarki ce da ke cike da wahalhalu;
Shin ba an haife mu ba ne domin mu mutu a daga bisani?
Bayan mun shafe 'yan sa'o'i a cikin nishadi,
Damuwa tana kawar da duk wani jin dadi a yanzu.

Muna kara yin nutso cikin jahilci a koyaushe,
A cikin zurfin mutuwa cikin hanzari.
A cikin matsaloli da wahalhalu masu yawa,
Duniya tana kara ingiza mu cikin tsananin bashi.

Sannan gamu cikin talauci, kuma mun shagaltu da son manyan benaye,
Muna tambayar inda mazaunan su suka fito.
Daga mahalicci, abin halitta, abin sirri ne,
Dalilansa na boye, suna da ban al'ajabi.

Amma sirrin Haƙƙi(Allah) da kansa ya ɓoye,
Sun zarce hankalin bayinsa, tabbas.
Mutum mai jahilci, fanko, gajiyayye,
Zai riƙa kuskure a cikin raunin fahimtarsa.

ZIYARAR KABARI da KARANTA, KUR'AN AL-KARIM

Ziyarar maƙabarta aiki ne na sunnah. Ya kamata a riƙa ziyartar maƙabarta mako-mako, ko aƙalla a ranakun Idi. Ziyarar da ta fi lada ita ce wadda aka yi a ranakun Alhamis ko Juma'a ko Asabar. An rubuta a cikin shafi na ƙarshe na littafin **Shir'at-ul-islam**, (wanda Muhammad bin Abi Bakr 'rahmatullahi ta'ala 'alaihi' ya rubuta, d. 573 [1178 M.] Bukhara) cewa sunnah ne ziyartar maƙabarta. Mai ziyarar zai yi tunani ganin yadda gawarwakin da ke kwance a wurin suka ruɓe, wanda hakan zai zame masa gargaɗi. Duk lokacin da 'Uthman 'radiyallahu 'anh' yake wucewa a maƙabarta, sai ya zubar da hawaye har gemunsa ya jiƙe da hawaye. Haka nan (baya ga zamowa gargaɗi ga mai ziyarar) mamatan da ke cikin kabarin za su amfana da addu'o'in da ya yi masu. Rasulullah sallallahu 'alaihi wa sallam' yana ziyartar kaburburan 'yan uwansa da na sahabbansa radiyAllâhu ta'âlâ 'anhum'. Bayan yin sallama da yin addu'o'i, mai ziyarar zai zauna ya fuskanci kabarin, ya bai wa Alƙibla baya. Al'adar kiristoci ce shafa kabarin da hannuwa da goga fuska a hankali a kan kabarin ko sumbatar kasar da ke kan kabarin. An faɗa a cikin wani Hadisi cewa: "**Idan mutum ya ziyarci kabarin dan uwansa ya yi masa sallama, dan uwan nasa da ke cikin kabari zai gane shi, ya kuma karɓa masa sallamar**." Ahmad bin Hanbal 'rahima-hullahu ta'ala ya ce: "Idan kana wucewa ta maƙabarta, ka karanta suratul Ikhlas (Kulhuwal Lahu) da surorin Kula'uzzai (Kul-a'udhu…) da Fatiha, ka bayar da ladar ga mamatan da suke kwance a wurin. Ladar za ta je masu." Wani Hadisi da aka karɓo daga Anas bin Malik 'rahmatullahi ta'ala 'anh' yana cewa: "**Idan aka karanta Ayat-al-kursi, aka sadaukar da ladar ga mamatan da suke kwance a maƙabarta, Allâhu ta'âlâ zai sa ta je ga duk wanda yake kwance a wurin**."

An faɗa a cikin littafin **Khazanat-ur-riwayat** (wanda Kadi Hindi 'rahmatullahi ta'ala 'alaih' ya rubuta) cewa: "Idan aka ziyarci wasu malamai a lokacin da suke raye, ya halatta a yi tafiya mai tsawo domin a ziyarce su idan sun rasu. Ta fuskar falala babu bambanci tsakanin ziyartar Annabawa ''alaihim-us-salawat-u-wa-t-taslimat' da ziyartar waliyyai ko manyan malamai (na Musulunci) 'rahima-humullahu ta'ala'. Bambancin shi ne muƙami da matsayinsu."

[Idan Musulmi ya sanya wata alama ɗauke da sunan wani masoyin sa a bangon ɗakin zaman sa, ko ya ajiye wani dutse ɗauke da sunan mutumin a kan kabarin mutumin, a duk lokacin da wani Musulmi ya shiga ɗakin, ko ya ziyarci maƙabarta, ya yi wa wannan mutumin addu'a, Allâhu ta'âlâ zai albarkaci mamacin da jin ƙai da gafara. Ba ana sanya sunan mutum a bango ko dutsen da ake alama da shi a kabari ba ne domin a riƙa tunawa da shi, illa saboda al'ummar Musulmi su karanta Fatiha su yi addu'a ga mai sunan. A kan haka, ya zama al'ada a ƙasashen Musulmi arubuta sunaye a bangayen ɗakuna da duwatsu da ake ajiyewa a kabari. Idan aka rubuta sunan Waliyyi, wani ya karanta sunan ya nemi shifa'at (ceto) wajen mai sunan da addu'a da neman tubaraki, Waliyyi zai ji ka, ya kuma roƙa maka biyan buƙatun ka na duniya da lahira, kuma Allâhu ta'âlâ zai karɓi addu'arsa].

Duk da cewa halal ne mata su ziyarci maƙabarta, amma ya fi dacewa a gare su kar su ziyarci wani kabari sai na Rasulullah. Ya halatta a ziyarci maƙabarta a cikin halin jinin al'ada ko janaba, haka nan sunnah ne yin alwala yayin ziyarar. An faɗa a cikin wani Hadisi cewa: "**Idan mutum ya ziyarci kabarin Mumini ka yi masa wannan addu'ar: 'Allahumma inni as-alu-ka bi-haƙƙi Muhammadin wa ali Muhammadin an la-tu'adh-dhiba hadhal mayyit,' za a tsare wannan Muminin daga azaba**." Wani Hadisin kuma yana cewa: "**Idan mutum ya ziyarci kabarin iyayen sa ko na ɗaya daga cikin su a ranar juma'a, zai samu gafara**." Ya halatta ka sumbaci ƙasar kabarin idan ya kasance na ɗaya daga cikin iyayenka ne. Kamar yadda ya zo a cikin littafin **Kifaya**, wani ya tambayi Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam': "Na yi alƙawarin sumbatar ƙofar Aljanna. Ya za a yi in cika wannan alƙawarin? Sai shugaban Annabawa ya ce: "**Ka sumbaci ƙafafun mahaifiyarka**." Yayin da wannan mutumin ya ce iyayensa ba sa raye, sai Rasulullah ya ce: "**Ka sumbaci kabarin iyayen ka! Idan ba ka san inda kabarin su yake ba, to ka ja layuka biyu a ƙasa da niyyar cewa kabarin su ne, ka sumbaci waɗannan layukan! Ka cika alƙawarinka**!"

Ya fi dacewa mu ziyarci kaburburan muhimman mutane da suke nesa da mu, yayin da wani dalili ya kai mu wurin maimakon yin doguwar tafiya musamman domin ziyartar kabarin su mai albarka. Amma akwai lada mai yawan gaske mutum ya yi doguwar tafiya domin ziyartar shugaban mu Annabi Muhammad 'sallallahu 'alaihi wa sallam'. Mutumin da ya ziyarci (kabarin) Manzon Allah 'sallallahu alaihi wa sallam' da na Waliyyai ''alaihih-ir-rahma' waɗanda aka amfana da rayuwar su. Zai tsarkake zuciyar sa gwargwadon so da ƙauna da yake yi masu. Idan aka aikata saɓo a gaban kabarin Waliyyan, misali: idan mata da ba su rufe jikin su da kyau ba suka ziyarce su, wannan ba zai zamo dalili na daina ziyartar waɗannan wuraren ba; idan ba za a iya hanawa ba, sai mu ƙi su a zukatan mu. Haka nan, dole

ne mu halarci jana'izar Musulmi ko da kuwa akwai mata ko waƙa ko waƙe na yabo da ake yi a wurin.

Idan mace ta ziyarci kabari da niyyar makoki, ko kuka ko ƙorafi ko yin fasadi (saɓo) ta hanyar cuɗanya da maza, ziyarar ta zama haram. An la'anci matan da suke yin haka. Duk da cewa ya halatta ga tsohuwa ta ziyarci kabarin 'yan uwanta ko Waliyyai ba tare da cuɗanya da maza ba, amma wannan sharaɗin na ziyarar kabarin makaruhi ne ga 'yan mata. Haka hukuncin yake ga mata su halarci jana'iza.

An faɗa a cikin littafin **Jila-ul-ƙulub** (wanda Zayn-ud-din Muhammad bin 'Ali Birghiɓi ya rubuta, 928 H. [1521 M.], Balikesir, Turkiyya–981 H. [1573 M.] na plague, Birgi) cewa: Duk mutumin da ya shiga maƙabarta ya ce: "**As-salamu 'alaikum, ya Ahla dar-il-ƙawm-il-mu'minin! Inna insha-Allahu 'an ƙaribin bikum lahiƙun**," a nan inda yake tsaye. Sai ya yi Basmala ya karanta suratul Ikhlas sau goma sha ɗaya (kowace da Basmala) ya karanta fatiha sau ɗaya (ita tare da Basmala). Daga nan sai ya yi wannan addu'ar: "**Allahumma Rabb-al-ajsad-il-baliyah, wa-l-izamin nahira-t-illati harajat min-ad-dunya wa hiya bika mu'minatun, adhil-'alaiha reɓhan min 'indika wa salaman minni**." Sai ya tunkari kabarin ta gefen daman [ta wajen Alƙibla] mayyit (mamacin da ke cikin kabarin) an so kusa da kafafun mamacin. Sai ya yi sallama, (wato ya ce "Salamun 'alaikum.) daga tsaye ko a tsugune ko a zaune, sai ya karanta ayoyin farko da na ƙarshen suratul Baƙara, sai ya karanta suratul Yasin, sai kuma surorin Tabaraka da Takathur da Ikhlas-i-sharif da Fatiha, ya sadaukar da ladar ga Mayyit (mamacin).

Abin lura **mai muhimmanci**: Malaman mu sun yi bayani game da tattaunawar su a kan yi wa wani aikin hajji cewa, ya halatta a bayar da ladar aikin ibada na farilla da aka yi ko na nafila da sauran kyawawan ayyuka da suka ƙunshi salloli da azumi da sadaka da karatun Kur'an al-karim da zikiri da ɗawafi da aikin hajji da umara, da ziyarar kabarin Annabi ko na Waliyyai, da yi wa Musulmi likafani, dukkan waɗannan a matsayin kyauta ga mamaci. Wanda ya yi aikin ibadar ya bayar da ladar kyauta da mamacin da aka bai wa ladar kyauta za su samu ladar (a wajen Allâhu ta'âlâ). A kan wannan, za a karanta Kur'an al-karim a yayin ziyarar kabarin da wani wurin na daban a bayar da ladar kyauta ga mamacin Musulmi, kuma nan take za a sanya masa albarka a yi masa addu'a. Domin Rahama da albarka suna sauka a wurin da ake karanta Kur'an al-karim. Duk addu'ar da aka yi a wannan wurin karɓaɓɓa ce (a wajen Allâhu ta'âlâ). Idan aka karanta shi a gaban kabari, wannan kabarin zai cika da rahamt (tausayin Allâhu ta'âlâ) da albarkar sa. A Mazhabar Hanafiyya, idan mutum ya yi azumi ko sallah na nafila, ko ya yi sadaka ko karatun Kur'an al-karim ko ya yi addu'a ya bayar da ladar kyauta

ga wasu Musulmi, masu rai ko waɗanda suka mutu, ladar za ta je gare su. Wasu malaman Musulunci sun ce wannan hukuncin ya shafi har da ayyukan ibada na farilla. Ba ana raba ladar ba ne ga mamatan, ana bayar da cikakkar ladar ne ga kowane mammaci. A Mazhabobin Malikiyya da Shafi'iyya, sun ce, ayyukan ibada da ake yi a fili, da suka ƙunshi karatun Kur'an al-karim, ba a bayar da su kyauta ga wasu Musulmi. Za a sanya masu albarka ne a kan kowane aikin ibadar da aka yi.

An rubuta a cikin littafin **Kitab-ul-fiƙh 'ala-l-madhahib-il-arba'a** cewa: "Ziyarar maƙabarta sunnah ne ga maza domin mamatan su zame masu gargaɗi, su kuma riƙa tunawa da lahira. A Mazhabar Hanafiyya da ta Malikiyya, sunnah mu'akkada ce yin ziyarar a ranakun Alhamis da Juma'a ko Asabar. A Mazhabar Shafi'iyya sunnah Mu'akkada ce yin ziyarar a lokacin La'asar a ranar Alhamis, da lokacin fitar rana a ranar Asabar. Mai ziyarar zai karanta ayoyin Kur'an al-karim ga mamacin, ya kuma yi masa addu'a. waɗannan abubuwan suna da amfani ga mamacin. Idan ka shiga maƙabarta, sunnah ne yin wannan addu'ar: "**As-salamu 'alaikum ya ahla dar-il-ƙawm-il-mu'minin! Inna insha-Allahu 'an ƙaribin bikum lahiƙun**." Ana ziyartar kowace maƙabarta, ta kusa da ta nesa. Hasali ma sunnah ne yin tafiya mai nisa domin ziyartar salihin Musulmi da Waliyyai 'rahima-humullahu ta'ala. Yana ɗaya daga cikin muhimman ayyukan ibada a ziyarci kabarin Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam'. Ya halatta tsohuwa ta ziyarci maƙabarta, a cikin shiga ta kamala. Amma haramun ne ga tsohuwar ta je ziyarar idan hakan zai haifar da fitina da ɓarna. Bai halatta a yi ɗawafi ga kabari ko sumbatar ƙasar kabarin ko kuma roƙon wani abu daga mamaci a yayin ziyarar ba." Ana iya neman ceto daga wajen Waliyyai 'rahima-humullahu ta'ala, domin neman tsira da albarkar Allâhu ta'âlâ.

Akwai abubuwa biyu da aka rasa,
Za a ƙona su duka, ba tare da la'akari su waye ba.
Idaniya da ke zubar da jini ba za ta iya biya haƙƙinsu ba;
Daya shi ne matashi, ɗayan kuma ɗan uwa Musulmi!

MUJALLADI NA UKU, WASIKANA TARA

Mujalladi na tara babi na uku na littafin 'Maktubat' wanda Imam Rabbani Mujaddid-i-alf-i-thani Ahmad Faruƙi 'rahima-hullahu ta'ala' ya rubuta ga Mir Muhammad Nu'man. Ya yi bayanin ayar Kur'an al-karim da take cewa: "Ku karɓi abin da Rasulullah ya zo maku da shi!" Bayanin an yi shi ne cikin harshen Larabci, ga fassararsa cikin harshen Hausa:

Bism-illah-ir-Rahman-ir-Rahim! Aya ta bakwai a cikin suratul Hashr tana cewa: "**Ku karɓi abin da Rasulullah ya zo maku da shi. Ku guji ayyukan**

saɓo, ku ji tsoron Allah!" [Aikata umarni da guje wa hani baki ɗayan su, su ake kira biyayya ga Musulunci]. Allâhu ta'âlâ ya ƙara da cewa: "….Ku ji tsoron Allah" bayan faɗar "Ku guji aikata abin da aka hane ku…," ya nuna cewar ya fi muhimmanci a guji aikata saɓo (wato haram). Taƙwa ita ce ginshiƙin Musulunci. Barin abubuwan da suke da kokwanto shi ake kira **wara'**. Rasulullah 'sallallahu 'alaihi wa sallam' yana cewa: "**Wara' ita ce ƙashin bayan addinin mu.**" Ya faɗa a cikin wani Hadisin cewa "**Babu wani abu kamar wara'**." Wannan yana nuna yadda addinin mu ya tsananta a kan guje wa aikata haram, wanda yake da nasaba da yawan abubuwan da za a guji aikatawa, kuma ya fi dace wa a guji aikata haram. Domin aikata abin da aka hore ka, ya ƙunshi har da abubuwan da za a guji aikatawa. Domin aikata umarni, yana nufin a guji ƙin aikata shi. Haka nan yana da matuƙar amfani saboda yana saɓa wa son rai. Idan aka aikata umarni, rai ma zai samu wani kaso na jin daɗî a ciki. Karancin son rai wajen aikata wani abu shi yake ƙara nuna amfanin aikata shi. Wato ita ce hanya mafi sauri da za ka samu yardar Allâhu ta'âlâ. Su kuma Ahkam-i-islamiyya, wato horo da hani na Musulunci, suna musguna wa son rai. Shi son rai maƙiyin Allâhu ta'âlâ ne. an faɗa a cikin Hadith-i-ƙudsi cewa: "**Ku yaƙi son ranku, domin maƙiyina ne**." don haka, a cikin dukkan turuƙ-i-'aliyya (hanyoyi da tsarin Sufanci), wadda ta fi tsanantawa wajen ɗa'a ga Musulunci, ita ce ta fi kai wa kusa ga Allâhu ta'âlâ. Domin tana tsanantawa wajen adawa da son rai. Wannan shi ne ra'ayin masana, kuma ita hanyar da muke bi. Saboda wannan dalili ne babban malamin nan Behâaddîn Bukhârî, babban jagoran mu, ya ce: "Na samu hanya mafi sauri wajen samun yardar Allâhu ta'âlâ." Domin hanyar tana yaƙi da son rai. Haka nan hanyar ta shahara ga tsanantawa wajen ɗa'a ga Musulunci, yana da sauƙi matuƙa ga mutum mai hikima da basira wanda ya karanta litattafan jagororin mu, ya fahimci wannan batun. Mutumin zai ga gaskiya a bayyane. Na yi bayanin yadda take a bayyane a cikin babi-babi daban-daban. Allâhu ta'âlâ ya san gaskiyar komi. Taimkon Sa zai isar mana. Shi ne nagartacen wakil. Salati (tsira da aminci) da salam (gaisuwa da girmamawa) su tabbata ga shugaban mu Muhammad 'alaihis-salâm' da Alayensa da Sahabbansa 'radiyallâhu ta'âlâ 'anhum ajma'in', da sauran mutane da suke bin tafarki madaidaici!

MUJALLADI NA UKU, WASIKA TAMANIN DA HUƊU

Hamd (dukkan godiya) ta tabbata ga Allâhu ta'âlâ, aminci ya tabbata ga bayinsa da ya zaɓa yake kuma ƙauna! Mutumin da yake son cigaba da tafiya akan wannan hanyar [ya kuma samu yardar Allah], da farko dole ne ya gyara aƙidarsa bisa koyarwar malamai waɗanda suke shiryayyu, [wato malaman Ahl as-sunnat]. [Waɗannan manyan malaman sun samo iliminsu ne daga

Sahabbai. Kar a yi masu zargin sanya ra'ayin su ko tunani irin na falsafa]. Muna roƙon Allâhu ta'âlâ ya albarkaci waɗannan malaman da lada mai tarin yawa bisa ayyukan da suka yi! Bayan haka, wannan mutumin dole ne san ilimin Fiƙihu, wanda wajibi ne ga kowane mutum. Haka nan kuma dole ya yi aiki da abin da ya koya. Bayan haka, dole ne ya yi zikirin Allâhu ta'âlâ a kowane lokaci. [Wato, ya riƙa tuna Allâhu ta'âlâ a kowane lokaci da (martabobinsa) da ake kira Sifat-i-dhatiyya]. Sai dai yin zikiri yana da sharaɗin sai ka koyi yadda ake yi daga wani muhimmin mutum wanda yake kamil (wato wanda ya samu kamala ƙarƙashin jagorancin wani muhimmin mutum muƙaddami,) kuma mukammil, (wato wanda jagoransa kuma muƙaddamin sa ya bai wa iko, yake da ijazat (izini) ya jagoranci wasu Musulmi zuwa ga shiriya). Idan ya koya daga waɗanda ba su kamala, [musamman shehunnan da ba su da ilimi mayaudara] ba zai samu shiriya ba. Da farko dole ne ya yawaita zikiri; ta yadda bayan kowace sallar farilla da nafilolin su, babu wani abu da zai yi sai zikiri, har karatun Kur'an al-karim da sauran ayyukan ibada na nafilfili za a bar su har sai ya kammala. Ana iya yin zikiri ko da alwala ko babu. Za a cigaba da yin haka ba ƙaƙƙautawa, ko a tsaye ko a zaune ko ana tafiya ko ana kwance. Kar ka bar wani lokaci ya wuce ba tare da ka yi zikiri ba a lokacin da kake tafiya a kan hanya ko a lokacin da kake cin abinci da yayin da za ka kwanta bacci. Wasu baitukan waƙe na Farisa na cewa:

Ka yi zikiri, idan dai kana raye, a kowane lokaci, kuma kodayaushe!
Da zikiri mahalicci zuciya take tsarkaka, ba dawasu hanyoyi ba.

Ya yi ta zikiri mai tarin yawa, har ya zamana ba ya tunanin ko buƙatar komi baya ga zikirin, ya zamo Allâhu ta'âlâ ne kaɗai a zuciyarsa. Babu waɗansu sunan wani abu face na naShi, ko ɓurɓushinsu ba zai gitta a zuciyarsa ba. Ko da a ce ya tursasawa kansa ya yi tunanin wasu abubuwan da ba Allâhu ta'âlâ ba, zai gaza kawo su a zuciyarsa. Wannan yanayi na zuciya na kasa kawo komi a cikinta in ba Allâhu ta'âlâ ba, shi ne farkon (samun arziki) na kusanci da shi. Wannan yanayin shi ne albishir na samun Matlub na ɗaukaka da soyayya (ta Allâhu ta'âlâ). Wasu baitikan Larabci cikin fassarar Hausa:

Ta yaya ne za mu cim ma babban matsayin na Su'ad,
Tare da cewa akwai manyan tsaunuka da kwari masu zurfi a tsakani!

[Su'ad suna ne na ma'shuƙa (abin ƙauna).] Allâhu ta'âlâ shi kaɗai yake sa mutum ya samu komi. Aminci ya tabbata ga matafiya tafarki madaidaici! [An faɗa a cikin babi na goma sha bakwai na mujalladi na uku cewa: "Yin zikiri a cikin zuciya ya sa ƙaunar abubuwa ta fita ransa waɗanda ba Allâhu

ta'âlâ ba. Son waɗannan abubuwan yana cutar da zuciya. Idan har zuciya ba ta kore wannan cutar ba za ta iya samun imani na gaskiya da yin ɗa'a ga Ahkam-i-islamiyya ba, wato horo da hani na Allâhu ta'âlâ. niyya wajen yin ɗa'a ga waɗannan abubuwan shi ma zikiri ne, da rashin yin tunanin son rai yayin da yake aikata mubah (abin da aka halatta)." Cutar zuciya ita ce bin son rai. Son rai shi ne maƙiyin Allâhu ta'âlâ. Ba ya son a yi masa ɗa'a. kuma maƙiyin kansa ne da kansa. Yana shagaltar da zuciya ta sanya gaɓɓai su aikata haram da miyagun ayyuka. Yana son a yi sakaci da addini da zama babu imani domin ta samu zama cikin shagala. Yana cutar da zuciya da sanya wa a yi abota da kafirai da mutanen da ba su da Mazhaba, da karanta litattafai da jaridun su, da sauraren shirye-shiryen su na rediyo da kallon na talabijin. Abin da ke wanke cutar zuciya shi ne ɗa'a ga Musulunci, hakan kuma na sanya ƙunci ga rai (nafs). Yana rage shagala da raunana sha'awar sa da ƙarfin sa wanda ka iya juya zuciya].

Waye a duniyar nan da yake tursasa son ransa ya samu nasara?
Babu shakka duk wani abin da aka ƙaddara zai tabbata!

WASIKA ta ƊARI da GOMA SHA HUƊU

Akwai babi-babi ɗari da ishirin da biyar a littafin Makatib-i-sharifa wanda 'Abdullah Dahlawi 'rahima-hullahu ta'ala' ya rubuta, ɗaya daga cikin manyan malaman India. Wannan shi ne fassarar babi na ɗari da goma sha huɗu, wanda ya rubuta wa Hadji 'Abdullah Bukhari:

Babu naƙasu tare da Allâhu ta'âlâ. Yana faɗar gaskiya

A kowane lokaci, kuma ya nunawa bayinSa hanya madaidaiciya t. Salati da taslimi su tabbata ga jagoran mu Annabi Muhammad 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam' da Alayen sa da Sahabban sa 'radiyallâhu ta'âlâ 'anhum ajma'in'! Mabiya ɗariƙa da suke nan, [wato birnin Delhi], suna karanta Esma da rubuta musƙas (layu) bisa dalilin su na biyan buƙatun kansu. Suna jawo hankalin mutane zuwa gare su. Suka riƙi Amir-ul-mu'minin 'Ali 'karramallahu wajhah' wa 'radiyallahu 'anh' sama da sauran khalifofi uku 'radiyallahu 'anhum'. Waɗannan mutanen su ake kira **Shi'is** ('yan shi'a). Mutanen da suke nuna ƙiyayya ga waɗannan khalifofin uku da Sahabbai, su ake kira **Rafidis**.

[Malaman **Ahl as-sunnat wa-i-jamaa'at** 'rahima-humullahu ta'ala sun faɗa a litattafan su da dama cewa Hadrat Abu Bakr da Hadrat 'Umar da Hadrat 'Uthman suna gaba da Hadrat 'Ali 'radiyallâhu ta'âlâ 'anhum ajma'in', sun kafa hujja da ayar Kur'an al-karim da Hadissai da ijma'in malamai, wato haɗuwar Sahabbai da amincewar su 'radiyallahu 'anhuma

ajma'in'. biyu daga cikin litattafan su ne **Izalat-ul-khafa 'an khilafat-il-khulafa**, da **Kurrat-ul-'aynain** fi tafdhil-i-shaikhayn, dukkan su biyu Waliy-yullah Muhaddith Dahlawi 'rahima-hullahu ta'ala ya rubuta (1114 H. [1702 M.] – 1176 H. [1762 M.] a birnin Delhi). An rubuta littafin ne da harsunan Larabci da Farisa; an fassara na farko da harshen Urdu, kuma duka bugu biyun an yi su ne a Pakistan a shekarar 1382 H. [1962 M.] na biyun kuma an fassara shi zuwa Harshen Turkanci (Turkish) sannan aka fassara zuwa Ingilishi. Na Ingilishin ya fi mamaye mafi yawa na ƙarshen littafin, mai suna Sahaba 'The Blessed', ɗaya daga cikin wallafar Hakikat Kitabeɓi na garin Istanbul da ke ƙasarTurkiyya. Ya kuma taɓo wani sashe na littafin mai taken 'Documents of the Right Word'. Littafin Larabci mai suna **As-sawâiƙ-ul-muhriƙa** wanda shahararren malamin Musulunci Ibni Hajar-i-Makki 'rahimma-hullahu ta'ala' ya rubuta (899 H. [1494 M.] – 974 H. [1566 M.] Makka) Hakikat Kitabeɓi sun sake buga shi a Istanbul, ƙasar Turkiyya. Duk Musulmi mai tunani da ya karanta wannan littafin zai gane cewa mutanen da ba su da Mazhaba suna kan hanyar ɓata ne. Wasu daga cikin waɗannan mutanen suna kiran kansu Ja'fari a yau. Suna yaudarar matasa da ƙaryar cewa su ne mabiyan Imamai goma sha biyu. Gaskiyar magana ita ce, Musulman da suke bin Imamai goma sha biyu ana kiransu **Ahl as-sunnat**. Malaman da ke kan tafarkin gaskiya da ake kiransu Ahl as-sunnat 'rahima-humullahu ta'ala sun ce: "Kaunar Imamai goma sha biyu tana sa mutum ya mutu da imani."

Suna shirya jana'iza su yi walimar cin abinci da nufin yin 'dawr'. [Ba sa yin sallah a cikin jam'i, da kuma cikin masallaci] a yayin taron maulidi, suna yin ƙungiya ta waƙar ilahis (waƙoƙin bege) da mersiyas (waƙoƙin ta'aziyya). Suna sauraren kaɗe-kaɗe da bushe-bushe a wuraren ibada. Suna yin waɗannan ayyukan bidi'ar da makamantansu da dama da sunan Tariƙat (hanyar Sufanci). Suna ƙara shigar da wasu ayyuka da ba su da alaƙa da addini kamar su Jukisanci da Barhamaniyanci duk da sunan ɗariƙa. Suna abota da mutanen da suka shagalta da duniya da fasiƙai. Ba su bayar da muhimmanci ga tsayuwa da zama a cikin sallah, (wanda aka yi cikakken bayani a kai a cikin wannan littafin), da yin sallah cikin jam'i, da sallar Juma'a. babu wani aiki da suke yi da yake cikin Musulunci. Waɗannan ayyukan babu su a zamanin salaf-as-salihin. Malaman **Ahl as-sunnat wa-l-jama'at** rahama-humullahu ta'ala sun soki waɗannan ayyuka na bidi'a. muna miƙa godiya ga Allâhu ta'âlâ cewa babu ɗaya daga cikin waɗannan munanan ayyukan na bidi'a da ya wanzu tsakanin Sahabbai 'radiyAllâhu ta'âlâ 'anhum'. Mutumin da yake son zama Musulmi da bin tafarkin Salaf-as-salihin (malamai magabata) 'rahima-humullahu ta'ala, su nesanta kansu daga waɗannan 'yan ɗariƙar na ƙarya. Ɓarayi ne masu sace imani. Sun

ruguza addini da imanin bayin Allâhu ta'âlâ. Zikirin su da sauran ayyukan su suna motsa zuciya da rai. [Waɗannan abubuwan kamata ya yi su riƙa tsarkake zuciya daga ma-siwa (tunanin wasu abu wanda ba na Allâhu ta'âlâ ba) maimakon shauƙin wasu halaye da ayyuka]. Baya ga haka, abubuwa kamar kashf [karamomi, da bayar da labari a kan abubuwan dasuka ɓace da mu'amala da aljannu] ba shi da wani asali a Musulunci. Kafirai irin su Jukis su ma suna yin kashf da karamomi. Mutane masu zurfin tunani su kula, su riƙa bambance daidai da kuskure. Riƙo da Musulunci da son abin duniya wasu turaku ne da suke nesa da juna, waɗanda ba za su taɓa tarayya a wajen mutum ɗaya ba. Mutum mai tunani ba zai salwantar da addininsa ba domin samun wani abin duniya. Manyan malamai da shehunnai na birnin Bukhara mutane ne masu tawakkul (shine fawwala al'amurran su ga Allâhu ta'âlâ). Ba su damu da abin duniya ba. Waɗannan mutanen suna gudun dukkan irin waɗannan abubuwan. Sun yi tsayin daka wajen riƙo da koyarwar salaf-as-salihin 'rahima-humullahu ta'ala' da sunnar Rasulullah 'sallallâhu ta'âlâ 'alaihi wa sallam'. Duk abin da za su yi, suna zaɓar hanyar **Azimat**. Suna guje wa bidi'a. Suna guje wa abubuwan da suka zo ta hanyar haram ko makaruhi. Idan mubah (abin da aka haramta) yana kai wa ga haramun, to shi ma ya zama haramun. **Dhikr-i-khafi**, wato yin zikiri a asirce, ya fi yin **dhikr-i-jahri**, wato yin zikiri a bayyane. Waɗanda suke yin wancan zikirin (na farko), suna kai wa ga matsayin na 'ihsan' wanda aka bayyana a cikin Hadisi. Kowane lokaci zukatan su na karkata zuwa asalin fayz, [wato, Allâhu ta'âlâ]. Idan mutum mai imani ya samu tawajjuh da irin wannan muhimmin Sufin, sai zuciyar sa da latifa ɗinsa su fara zikiri nan take. Zai samu hudhur, wato, zuciyar da babu kowa a cikinta sai Allâhu ta'âlâ, wanda shi ne matsayin da ake kira **mushahada**, ana kiran jadhbas da fayz da suna **waridat**, waɗanda albarkoki ne da za su sa a wanke bawa na ƙwarai da haske a zahir (wajensa) da batin (cikinsa). Idan bawan ya fara karɓar fayz daga zuciyar murshid, babu wani tunani sai na Allâhu ta'âlâ da zai riƙa zuwa a zuciyarsa. Dukkan gaɓɓansa za su riƙa aiki bisa sunnah da 'azimat. Lallai wannan farin ciki ya isa ga samun babban raɓo. Ya Rabbi! Don girman Annabin ka da ka fi so Muhammad Mustafa 'sallallahu 'alaihi wa sallam' da kuma girman mashaikh-i-kiram 'rahmatullahi 'alaihim ajma'in', waɗanda su ne magadan wannan nagartaccen Annabin, ka sanya albarka mai yawa a abincin mu na yau da gobe. Fayz na Imam Rabbani mujaddid-i-alf-i-thani 'rahmatullahi 'alaih'sun sanya latifa ta mutane ta samu wannan albarkar. (A duba babi na talatin da tara na mujalladi na ɗaya, da babi na ishirin da uku da na ishirin da shida a mujalladi na shida na littafin **Endless Bliss** domin ƙarin bayani a kan 'latifa').

Na sadaukar da rayuwata a kan tafarkinka,

Mai kyaun suna da manufa, Muhammad!

Ina roƙon ka yi ceto ga wannan ƙaskantaccen bawa,
Mai kyaun suna da manufa, Muhammad!

Muminai sun sha wahalaƙwarai a wannan rayuwa,
Za a ba su lada mai yawa a gobe ƙiyama.

Zaɓin duniya dubu goma sha takwas a rayuwa,
Mai kyaun suna da manufa, Muhammad!

Wanda ya yi tafiya ya ratsa sammai bakwai,
Ya zarce kursi da sammai duka.

Wanda ya roƙi Haƙƙ akan al'ummarsa a Mi'raj,
Mai kyaun suna da manufa, Muhammad!

Me Yunus zai samu a duniya biyu in babu kai?
Babu ko shakka, kai Annabi ne na gaskiya!

Mutanen da suka yaƙe ka sun mutu babu imani;
Mai kyaun suna da manufa, Muhammad!

JAWABI NA KARSHE NA LITTAFIN MABUƊIN SHIGA ALJANNA

Mun lura cewa dukkan halittu, masu rai da marasa rai, suna bisa wani tsari ne na musamman. Mun gane cewa akwai tsari wanda baya sauyawa da alaƙa ta lissafi wajen yin kowace irin ƙwayar sinadari, a kowane hali, a kowane yanayi. Mun rarraba wannan tsarin da alaƙar zuwa ɓangarori irin su shari'a da kimiyya, ilimin sinadarai, ilimin sararin samaniya, da na halittar ɗan adam da makamantan su. Ta amfani da wannan tsarin da baya sauyawa (wato ilimin kimiyya da fasaha), mun kafa masana'antu da kamfanoni, da yin magani, tafiya zuwa duniyar wata, da ƙulla alaƙa da taurari da ƙwayar zarra. Muka ƙera radiyo da talabijin da kwamfuta, da hanyoyin sadarwa. Idan bacin tsarin halitta, kuma ya kasance komi ba a kan tsari yake ba, ba za mu iya amfana da waɗannan abubuwan ba. Kowane abu zai yamutse da wani abin, za su hargitse, bala'o'i za su afku. Dukkan abubuwan za su bace.

Tsarin na musamman, mai shiryayyun lambobi da ke saiti da alaƙa tsakanin halittu yana nuna cewa ba su suka samar da kansu ba ko dace da sa'a, dukkan wani abu halittar masani komai ne kuma mai iko akan dukkan komai, sannan mai ganin komai da jin komai, wanda yake yin dukkan abin da ya ga dama. Yana halitta da kawar da komi a lokacin da ya ga dama. Ya

sanya wasu abubuwan suka zamo silar halittar wasu abubuwan. Idan da ya yi halitta ba tare da sila ba, da ba za a samu tsari ba a cikin halittu. Abubuwa za su kasance a hargitse. Ba za a samu wasu alamu ba da suke nuna wanzuwarsa ba. Haka nan da ba za a samu kimiyya da wayewa ba.

Baya ga bayyana wanzuwar Sa ta wannan tsarin, ya kuma sanar da wanzuwar tasa ga bayin Sa, wanda hakan yake nuna irin kyautar da yake yi wa bayin nasa. A kowane ƙarni tun daga Annabi Adam ‘’alaihis-salâm’ Ya zaɓi mutum ɗaya daga kowace al’umma ta duniya, ya sanya shi ya zamo fiyayye kuma mafi muhimmanci a cikin mutanen, ya aiko masa da mala’ika, ya sanar da shi wanzuwar Sa da sunayen Sa, tare da umartarsa a kan abin da ya kamata mutane su yi, da wanda bai kamata su yi ba, domin su gudanar da rayuwa ta ƙwarai a duniya da lahira. Waɗannan zaɓaɓɓun muhimman mutanen su ake kira **Annabawa**. Umarni da hani da ake aiko wa mutane shi ake kira **Din** (addini) da **Ahkam-i-diniyya** (dokokin addini). Saboda ɗabi’ar mantuwa irin ta ‘yan adam, da yake yawan mance abubuwan da suka shuɗe, da kuma sheɗanun mutane, waɗanda ake samu a cikin mutane kodayaushe, da suke cusa abubuwa a cikin litattafan da aka saukar wa Annabawa ‘’alaihim-us-salawat-u-wa-t-taslimat, suna sauya Hadisan su, sai aka riƙa mantawa da addinan da suka gabata da kuma yadda aka gurɓata. Abin da ma ya fi muni shi ne, waɗannan sheɗanun mutanen sun ƙirƙiro wasu addinai na bogi.

Saboda tausayin Allâhu ta’âlâ ga mutane wanda shine mahaliccin komai, sai ya turo masu Annabin ƙarshe da sabon addini. Ya kuma ba su tabbacin cewa zai kare addinin har zuwa ƙarshen duniya, zai kuma yaɗa shi kusa da nesa duk da harin da ƙoƙarin gurɓata shi da sheɗanun mutanen suke yi.

Muna godiya mai tarin yawa ga Allâhu ta’âlâ, saboda mun yi imani da wanzuwa da ƙaɗaitar mahaliccin tun muna ƙananan yara, lokacin da muka samu damar sanin cewa sunan wannan mahaliccin Allah, kuma Muhammad ‘’alaihis-salâm’ shi ne Annabin ƙarshe, kuma **Islam** shi ne addinin da wannan Annabin ya zo da shi ga bayin sa, (mutane). Muna son koyon wannan addinin daidai. Baki ɗayan lokacin da muka shafe wajen neman ilimi a manyan makarantu da jami’o’i, mun binciki hanyoyin da za mu koya daga gare su. Amma matasan ƙasar mu sun shagaltu da bin masana kimiyya na bogi, waɗanda suka biye wa ‘yan firimason, da ‘yan gurguzu da ‘yan kwangila na wahabiyawa, suka ɗora su bisa aƙidar rashin Mazhaba. Kafirai da ‘yan bidi’a suna ƙulla maƙarƙashiya ta bayan fage, waɗanda suka sayar da imanin su saboda abin duniya, ta kai ga yana da wahalar gaske ka iya gane hanya ta gaskiya. Babu wata hanya da ta rage sai roƙon Allâhu ta’âlâ. Allah

mai girma ya albarkace mu da karanta litattafan malaman Ahl as-sunnat ‘rahima-humullahu ta’ala’. Sai dai hanyar da aka dora mu a kai da sunan ilimin kimiyya, wanda **masana kimiyya na bogi** suka yi, waɗanda suka gurɓata Musulunci saboda son zuciya, ta yi tasiri ƙwarai a zukatan mu. Muna godiya marar iyaka ga Allâhu ta’âlâ da ya azurta mu da farkar da mu da ya yi ta hanyar manyan malaman addini, har muka fahimci bambancin gaskiya da ƙarya. Mun iya gane cewa abin da aka cusa mana a zukata guba ce mai ƙyale-ƙyali, ba ilimi bane, muka gane cewa an jefa zukatan mu cikin duhun yaudarar su. Ba don mun yi cin karo da litattafan malaman Ahl as-sunnat ba, da ba mu iya bambance aboki da maƙiyi ba, da an yaudare mu da ƙarairayin maƙiyan addini. Da ba mu kuɓuce daga tarkon waɗannan maƙiyan ba waɗanda suka ɗauki suka da rashin ɗa’a a matsayin cigaba. Da mun riga sukar iyayen mu, da Musulmi na gaskiya da koyarwar musuluncin da muka samu daga gare su. Manzon Allah ‘sallallâhu ta’âlâ ‘alaihi wa sallam’ ya gargaɗe mu a kan faɗawa tarkon maƙiyan Musulunci: “**Ku koyi addininku da bakin rijal**!” Idan ba mu samu rijal ba, wato malamin Musulunci na gaskiya, sai mu koya daga litattafansu. Litattafan addini da ‘yan bidi’a suka rubuta, ko waɗanda ba su da ilimin addini waɗanda ba su da Mazhaba, suna cutarwa kamar litattafan kafirai.

Haramun ne ga mace ko budurwa ta fito da kanta ko gashinta ko cinyar hannunta da ƙafafunta waje, ga maza kuma su bayyana abin da ke tsakanin cibiya da guiwarsu a gaban jama’a. Ana nufin Allâhu ta’âlâ ya yi hani a kan haka. Mazhabobin nan huɗu na haƙiƙa da suke koyar da umarni da hani na Allâhu ta’âlâ sun bambanta da juna a kan tsiraicin namiji, wato gaɓoɓin jikinsu da aka haramta wani namiji ya gani a jikinsu. Wajibi ne ga kowane Musulmi ya rufe tsiraicinsa daidai da koyarwar Mazhabar sa. Haramun ne wasu su kalli wannan gaɓoɓin nasa idan suka bayyana. An faɗa a cikin littafin **Kimya-i-se’adet** cewa: “baya ga rufe kai da gashi da cinyar hannu da ƙafa, haramun ne ga mata da ‘yan mata su sanya tufafi mai shara-shara da mai ƙyale-ƙyali ko matsattse, ko su sanya turare a tufafin. Idan iyaye da mazan aure da ‘yan uwansu suka bari suka sanya, amincewarsu da barin nasu za ta sa su yi tarayya da su a cikin zunubi da kuma azabar da za a yi masu.” Ana nufin, za a yi masu azaba tare a cikin wuta. Idan suka tuba, za a yi masu gafara, ba za a ƙona su a wuta ba. Allâhu ta’âlâ yana son mutane masu tuba. A shekara ta uku bayan hijira ne aka hana ‘yan mata da suka kai shekarun balaga da manyan mata su bayyana kansu ga waɗanda ba muharramansu ba. Kar mu yarda da da’awar da ake yi cewa rufe jiki ga mata daga baya ne malaman Fiƙihu suka ƙirƙiro shi. Yaudara ce daga ‘yan leƙen asiri Ingila da wasu marasa ilimi da suka faɗa tarkon su, suna cewa mata ba sa rufe jikinsu

kafin a saukar da ayar da take bayar da umarni a kan hijab (mata da ‘yan mata su rufe jikinsu).

Za mu ƙara faɗa: idan yaro ya zama ‘aƙil (ya mallaki hankali) ya zama baligh (balaga), wato ya kai shekarun bambance abu mai kyau da marar kyau, ya kuma yi aure, ya zama farilla ga wannan yaron ya gaggauta koyon rukunnan imani guda shida, daga nan sai ya koyi **Ahkam-i-islamiyya**, wato farillai da halal da haram, ya kuma yi rayuwa bisa waɗannan dokoki da ƙa’idojin. Mace tana zama ‘aƙil da baligh ne yayin da ta shekara tara, shi kuma yaro sai ya kai shekaru goma sha biyu. Ya zama farilla su san waɗannan rukunnan da dokoki da ƙa’idojin ta hanyar tambayar iyayensu da ‘yan uwansu abokai. Haka nan kafirin da ya musulunta ya gaggauta zuwa wajen malaman addini, ya nemi ilimi daga gare su kai tsaye ko kuma su ba shi litattafai masu kyau. Farilla ne ga dukkansu biyun su yi abin da ya rataya a wuyan su, wato ga sabon musulunta ya nemi ilimi, shi kuma malamin ya taimake shi ya samu ilimin. Idan malamin ya ce “Ya yi kyau, ya yi kyau,” amma bai taimake shi ya koya ba, ko ya ba shi litattafan Musulunci, ya saɓa wa (umarnin) farilla. Mutumin da ya saɓa wa farilla, zai shiga wutar jahannama. Idan wanda ya musulunta ya fara neman malamin da zai koyar da shi ko litattafan Musulunci, ya isa ‘udhur a wurin su kar su fara koyo har sai sun samu inda za su koya. (Udhur yana nufin wani dalili na uzuri dazai ɗauke wa Musulmi ya aikata wata ibada ko ya hana shi guje wa aikata abin da aka hana. Kamar yadda Musulunci ya bayyana su, haka nan ya bayyana uzuri a kan umarni da hanin na Musulunci. Kamar yadda ake neman ilimi na umarni da hani na Musulunci daga litattafan malaman Ahl as-sunnat, haka nan kuma ake koyon abubuwan da suka shafi uzuri daga malaman Ahl as-sunnat ko daga litattafan su kaɗai. A yau Hakikat Kitabeɓi da ke garin Istanbul a ƙasar Turkiyya, ta zama wani rumbu ne na Musulunci, inda mutum zai iya samun dukkan litattafan da yake buƙata da aka rubuta da harsuna daban-daban).

Domin ilimantar da matasa su san koyarwar Musulunci ta haƙiƙa, mun karanta kuma muna taimakon mutane daga ko’ina a duniya, domin su samu nutsuwa da kwanciyar hankali a duniya da albarka marar iyaka a lahira, kuma insha-Allah za mu cigaba da wannan aikin na buga zaɓaɓɓun litattafan malaman Ahl as-sunnat masu muhimmanci.

Wannan addu’ar wadda ake kira **Salat-an-tunjina**, ana karanta ta domin neman biyan buƙata: “Allahumma salli ‘ala sayyidina Muhammadin wa ‘ala al-i-sayyidina Muhammadin salat-an-tunjina biha min jami’ul ahwal-i-wa-l-afat wa taƙdi lana biha jami’al hajat wa tutahhiruna wa tuballighuna biha

min jami' is-sayyi'at wa tarfa'una biha a'l-ad-darajat wa tuballighuna biha aƙsa-l-ghayat min jami'il khayrat-i-fi-l-hayat-i-wa ba'd-al-mamat."

An faɗa a cikin wani Hadisi cewa, yana da amfani matuƙa a riƙa karanta istighfari, domin neman kariya daga dukkan fitintinu da musifu, da tsira daga zalunci da hare-haren shedanu da maƙiya.

Rayuwata ta zo ta wuce kamar iska mai kaɗawa.
A gare ni ba komi ba ne face ƙyaftawar idanuwa.
Haƙƙi shaida ne: jiki shi mazaunine na rai.
Wata rana za ta fice daga wannan kejin, kamar tsuntsuwa.

WASIKA ta ƊARI da ISHIRIN DA UKU

Wannan wasiƙar ta Hadrat Imam Rabbani 'ƙuddisa sirruh' an rubuta ta ne ga Tahir-i-Bedahshi. An rubutacewa aikin ibada na nafila, ko da aikin hajji ne ba shi da amfani idan har ya sanya aikin farilla ya kuɓuce:

Ɗan uwana mai hankali. Wasiƙar da Molla Tahir, wanda yake da tsarki kamar sunansa, ta zo nan. Ɗan uwana! An faɗa a cikin wani Hadisi cewa: "**Allâhu ta'âlâ ba ya son a san bawansa da ɓata lokacinsa saboda kasala**." Yin aikin ibada na nafila maimakon yin aikin farilla kamar kana aikin banza ne. Don haka mu yi duba a kan abin da muke amfani da lokacin mu wajen yin sa. Mu san abin da yake ɗaukar mana hankali. Kana yin ibada ta nafila ne ko kuwa ta farilla? Ana aikata hani ko haramun a wajen aikin hajji na nafila. Ka yi tunani da kyau! Hannunka mai sanda ya ishi mai hankali. Ina miƙa gaisuwata a gare ka da abokan ka.

[Ana iya fahimta da wannan wasiƙar cewa nafilar da ake yi a lokuttan sallolin farilla biyar, ban da ta lokacin sallar Asuba, za a yi su ne da niyyar yin ƙada (ƙara'i)].

WASIKA ta ƊARI da ISHIRIN da HUƊU

Wannan wasiƙar, ita ma an rubuta ta ne ga Tahir-i-Bedahshi. Shi wujub (zamowa wajibi) ga aikin hajji suna da sharaɗi na sai mallakar kuɗaɗen da za a yi tafiyar da su. Zuwa aikin hajji ba tare da kuɗi da za ka yi amfani da su ba wajen tafiya, yananufin ɓata lokaci ne maimakon ka aikata wasu ayyukan na ibada. Wasiƙar ta yi bayani kamar haka:

Wasiƙa mai daraja daga ɗan uwana Khawja Muhammad Tahir-i-Bedahshi ta iso nan. Hamd (godiya da girmamawa) da ƙarin godiya sun tabbata ga Allâhu ta'âlâ (bisa ni'imarsa) wanda babu iyaka ga ƙaunar Sa ga faƙirai da kusanci gare su. Tsawon kwanakin rabuwa, ba su bayar da dama

ga hakan ba (sauyawa zuwa mafi muni). Wannan matsayin naka wani yanki ne na jin dadi marar iyaka. Ya kai ɗan uwana wanda yake ƙaunarmu! Ka yanke shawarar zuwa neman izini (a wajen mu). A lokacin da muke ban kwana, mun ce muna sa ran samun albarkar haɗa tafiya tare da kai. Sai dai istiharar[1] da muka yi ba ta nuna mana alamar amincewa ba. Abin bai kammala ba, don haka, za a amince da wannan tafiyar. Sai muka sauya ra'ayin mu. Kafin nan, tafiyar ka ba ta zamo abin amincewa ba ita ma. Duk da haka sai ka boye yanayin shiga damuwa. Fita (wannan tafiyar) tana da sharuɗɗa, na samun wadatattun kuɗi domin yin tafiyar. Idan mutum bai iya cika wannan sharaɗin ba, ɗauke masa wannan tafiyar zuwa aikin hajji. [Yana ɗaya daga cikin sharuɗɗan wajabcin aikin hajji a samun kuɗaɗen da za a yi tafiyar da su. (Wato ana nufin a cikin sharuɗɗan da ake son a cika, wajibi ne ga Musulmi ya mallaki kuɗi kafin aikin hajji ya zamo farilla a gare shi). Zuwa aikin hajji ba ya zama farilla ga mutum sai yana da kuɗin da ake buƙata domin yin tafiyar. Idan ya tafi aikin hajjin (ba tare da yana da kuɗi ba) to ya yi aikin hajji na nafila ne. shi aikin Umara ma, ba aikin farilla ko wajibi ba ne. wato aiki ne na nafila. Yin aikin nafila da zai sanya aikin ibada na farilla ya kuɓuce, yana sanyawa mutum ya aikata haram, wanda zai sa ya fita daga aikin ibada. Yana kai wa ga aikata zunubi. [A duba babi na ishirin da tara, (wanda babu fassararsa a yau!)] Ba daidai ba ne yin aiki wanda ba na farilla ba wanda zai sanya mutum ya rasa aikin farilla. Na faɗi wannan bayanin na gaskiya ne a wasu wasiƙu kaɗan nawa. Ban san ko sun isa hannunka ba. Wannan shi ne ƙarshen zancena. Ka san abin da ya kamata ka yi da saura. Wa-s-salam. [Akwai ƙarin bayani game da aikin hajji a cikin wasiƙa ta ɗari biyu da hamsin (250) wadda ba a kai ga fassara ta ba a halin yanzu)].

[1] Anyi bayanin 'Istihara' a sakin layi na ƙarshe a babi na Ishirin da biyar a mujalladi na shida na littafin **Endless Bliss.**